♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_"'It doesn't matter who we are, we all have our successes and failures, we all make mistakes, but what really matter is how we move forward and how much we learned from our mistakes"'_

*PAGE 1-2*

Mota ƙirar Elantra fara tas da baƙin tinted ce tayi parking a bakin gate ɗin wani tangamemen gida, fasalin gidan, da girmansa da kuma tsarinsa kaɗai ya isa ya tabbatar wa mutum cewa gida ne na masu arziki, komai na gidan ya haɗu

Horn aka danna kusan sau uku, kafin mai gadin da bai gaza shekaru 45 ba,  ya zo cikin sauri ya buɗe gate ɗin, duk da cewar ya ji ciwo a ƙafarsa, amma hakan bai hana shi yin sauri ba saboda gudun masifa

Motar na shiga cikin gidan ta tsaya, ganin hakan ne ya sa yana gama rufe gate ɗin ya zo da gudu ya tsaya yana jiran fitowarta

Buɗe ƙofar motar tayi, ta fara fito da kyakkyawar ƙarfarta da ta sha jan lalle, da takalminta flat shoes sky blue, kafin a hankali ta fito gaba ɗaya, tana sanye da doguwar rigar atampa dark blue mai manyan patterns sky blue, sai ɗan ƙaramin gyale sky blue tayi rolling kanta da shi

Kyakkyawar budurwa ce ajin farko, ta haɗu ta ko ina, tun daga fuskarta, tsarin jikinta da komai ma, ƙaton glass ɗin da ya mamaye kusan rabin fuskarta ta cire tana kallonshi
~~~~~~~~~~~~~~

Ya buɗe baki zai yi magana ta ɗauke shi da mari sau biyu, kaɗan ya rage ya faɗi, dafe kumatunshi yayi yana kallonta

Ta ce "Habu! Yaushe ka fara raina ni? Ko kuwa so kake mutane su fara raina ni? A gidanmu a ce sai nayi horn sau uku sannan zan samu damar shiga, bayan tun lokacin da aka ɗauke ka aiki sai da aka gaya maka horn ɗaya nake yi!"

Cikin girmamawa ya ce "dan girman Allah Hajiya kiyi haƙuri, wallahi ɗazu ne na ɗan fita mai mashin ya kaɗe ni, kin ga ma ƙafar ciwo take mun wallahi da ƙyar nake tafiya, ki yafe ni... "

A tsawace ta katse shi "kai dalla rufe mun baki, ina ruwa na da ciwon ƙafarka, Allah ya sa guntilewa ma tayi me ya shafe ni... To bari in gaya maka wallahi kwananka a gidan nan ya ƙare"

Bata jira jin me zai ce ba, ta shige motar ta bar shi nan yana rafka salati, a ƙaton wurin da aka ƙawata dan ajiye motoci tayi parking, kafin ta jawo handbag ɗinta sky blue ta fito

Kai tsaye babban parlourn su ta wuce, parlour ne da ya ji ababen more rayuwa masu masifar kyau da tsada, aljannar duniya kenan

Mutane biyu ne a parlourn suna fira, kallo ɗaya zaka musu ka gane iyayenta ne, kujerar da mahaifinta yake zaune ta nufa, ta zauna kusa da shi sai turo baki take kamar zata mishi kuka

Cikin kulawa da so ya kalle ta ya ce "Baby ya aka yi? Wa ya taɓa mun ke ne?"

A shagwaɓe ta ce "ba Habu ba ne... "

"Wane Habun? Ba dai mai gadi ba"

"Shi mana, wai har ni zanyi horn sau uku kafin ya iya buɗe mun gate, dan kawai yana so mutane su raina ni! " ta ƙarasa kamar zata yi kuka

Da sauri ya ce "a'a a'a Baby, don't cry(kar kiyi kuka), ai ba girmanki bane kiyi wa gateman kuka... Yanzu me kike so? "

"Daddy ai kai ma ka sani"

"A kore shi?"

"Umm"ta faɗa tana ɗaga kai

"An gama, tashi mu tafi" a tare suka miƙe tsaye

Mahaifiyarta dake zaune gefe tana kallonsu, ta ce "Alhaji, yanzu ma sake biye wa yarinyar nan

zaka yi, ka kori wannan bawan Allahn?! "

"Ƙwarai kuwa, ke ba kiji abunda ya mata bane?"

Miƙewa tayi cikin fushi ta ce "to me ya mata? Dan kawai be buɗe mata gate da wuri ba shi ne tashin hankalin? Kowa bai da uzuri ne sai naku? Watanmu huɗu da dawowa wannan sabon gidan, cikin watannin nan kuwa masu gadi ɗai-ɗai har goma sha uku ka kora saboda ita, in ka kori wannna sha huɗu fa kenan! "

"Eh na kore su, kuma zan kori fiye da haka ma in dai akan Baby ne, dan farin cikinta nake so "

Shiru kawai tayi tana kallon ikon Allah dan ta san duk surutun da zata yi ba zai hana ya kore shi ba dan ba yau aka fara ba, ita kuwa wacce ake yi sabida ita sai juye-juye take tana murmushi, ko a jikinta

Sama ya haura ya ƙirgo sauran kuɗin mai gadin, sannan suka fita harabar gidan shi da Babynshi, sun tarar da Habu kan benci ya zuba tagumi, yana ganinsu ya durƙusa ƙasa da sauri

"Malam Habu, ba na gaya maka sharaɗin Baby ba? Na gaya maka bata horn sau biyu, amma ba ka ji ba ko! "

"Dan Allah Alhaji kayi haƙuri, wallahi ƙafa ta ke da rauni, a yafe mun hakan ba zai sake faruwa ba nayi alƙawari"

"Dama kuwa ta ya hakan zai sake faruwa Malam Habu tun da yanzu zaka bar gidan nan"

"Alhaji ka tausaya mun, wallahi da aikin nan nake rufawa kai na da iyali na asiri, kar ka kore ni dan Allah " Habu ya faɗa cikin kuka

"Ai fa sai dai kayi haƙuri, tunda Baby ta furta kalmar kora a kanka, to ka zama korarre... Ga cikon kuɗinka, kar ka bari in fito in same ka a nan" ya ja hannu Babynshi suka koma ciki, Habu kuwa sai share hawaye yake ta yi

Suna shiga ɗakin, mahaifiyarta ta fito, kai tsaye wuein Habu ta nufa, ta kira sunanshi, "Malam Habu"

Da sauri ya ɗago ya ce "na'am Hajiya, dan Allah ki ba Alhaji haƙuri wallahi ba zan sake ba"

"Ka ga Malam Habu, na san ba kayi sati biyu a gidan nan ba, amma dai ka fahimci yanda Alhaji ya ba yarinyar nan muhimmanci, ba zai saurare ni ba tunda har tayi magana, amma kayi haƙuri ka je, in na samu labarin gidan da ke da buƙatar mai gadi, zan kira ka, kafin nan, ga wannan ka ja jari ka ji ko" ta miƙa mishi kuɗi, naira dubu hamsin

Har ƙasa yake yana mata godiya, kafin ta juya ta koma ciki, shi kuma ya shiga ɗaki dan ya tattaro kayanshi kamar yanda aka umarce shi

Bayan fitar Alhaji daga gidan, mahaifiyarta ta shiga ɗakinta, ta tarar da ita ta cire kayanta, daga ita sai towel, da alama dai wanka zata shiga, zama tayi a gefen gado, ta kira sunanta "SUNAIHA"

"Na'am Mummy"

"Zo nan"

Zuwa tayi kusa da ita ta zauna ta ce "gani"

"Yanzu Sunaiha abunda kike yi kina kyautawa kenan? "

"Me kuma nayi Mummy? "ta faɗa a shagwaɓe

"Da kike sa mahaifinki yana korar mutane ba gaira ba dalili, ba ki san hanyar samun kuɗinsu ba kenan har su samu abunda suka ci?"

"To Mummy raina ni fa suka yi"

"Hakan ba raini bane Sunaiha, kiyi wa mutane uzuri mana, ki daina biyewa Daddynki wata rana fa aure za kiyi, kuma ba ko wane namiji zai ɗauki wannan rashin kunyar ta ki ba"

Wani murmushi tayi da ya ƙara fito da kyaunta, ta ce "tab, ai Mummy duk wanda zai aure ni dole sai ya kasance mai haƙuri da ni ko yayi gaba... Kuma ma ai kin san irin mijin da nake so in aura"

Harara ta zabga mata, ta ce "ai shiyasa har yanzu kike gida a zaune muna auna tsayi ni da ke, kuma idan kika biyewa wannan shirmen na ki zaki tsufa a gidan nan ina gaya miki" ta miƙe kawai ta bar ɗakin a fusace

Ita kuwa dariya tayi ta kwanta kan makeken gadonta tana murmushi, ba komai ke sa ta murmushin ba illa tuna irin mijin da take mafarkin samu a rayuwarta, kusan minti biyar tayi a kwance kafin ta tashi ta faɗa toilet

*SUNAIHA ABUBAKAR NURADDEEN* , Cikakken sunanta kenan, ƴa ce ɗaya tilo a wurin iyayenta, mahaifinta Senator Abubakar Nuraddeen Mai Doki, babban Engineer ne kuma ɗan siyasa wanda ake damawa da shi har yanzu a jahar, mahaifiyarta kuwa Hajiya Binta Muhammad, Sunaiha ta kasance ƴar gata ce a wurin iyayenta, musamman mahaifinta da ya ɗauki son duniya ya ɗora mata tun lokacin da aka tabbatar musu da cewa Hajiya Binta ba zata

sake haihuwa ba sakamakon lalacewar da mahaifarta tayi, Alhaji Abubakar kuwa bai kasance mai son auren mata biyu ba, hakan ya sa bai ƙara aure, ya haƙura da Sunaiha da Allah ya ba shi
Tun tana ƴar ƙaramarta ya shagwaɓa ta, duk abunda take so shi yake mata ko da kuwa baya so ko mahaifiyarta ba ta so, in dai zata yi farinciki wannan ba damuwarsa ba ce, sanadiyar yanda mahaifinta ke mata ya sa take jin kamar ta fi kowa, hakan ya sa take da girman kai, ji da kai da kuma wulaƙanta mutane kuma ba ruwanta komai girmanka ko tsufanka ko namiji ko mace, ita kowa ta raina, ga shi kuma Allah yayi ta da farin jini da kuma kyau, kowa na sonta amma ita ba kowa take kulawa ba sai masu kyau da arziki kamarta, wannan halin na ta kuwa tun tana primary school, har ta kai secondary, sai a lokacin Hajiya Binta ta fara jin abun yana damunta sosai, tayi faɗa tayi nasiha amma a banza dan Sunaiha ta riga da ta hau layin da Daddynta ya ɗora ta, sai dai duk wannan ɗabi'un nata, tana ɗauke su ne akan waɗanda jininsu ya haɗu, duk da cewar idan halin ya motsa tana musu, amma bai kai wanda take yi wa sauran mutane ba.
Bayan ta gama secondary school ɗinta, Alhaji Abubakar ya tura ta london wurin wani yayanshi da ke can dan tayi karatu, ƴaƴanshi biyu, babbar mace ce sai namiji wanda tare da Sunaiha suka yi karatu, a can ɗin ma ba'a tsira ba dan ba abunda ya rage a ɗabi'unta. Wani lokacin iyayenta ke zuwa ganinta, wani lokacin kuma ita ce ke zuwa idan suka yi hutu, a haka har ta kammala karatunta ta dawo gida Nigeria
Daga nan Mummy (Hajiya Binta) ta fara takurawa Alhaji Abubakar da maganar aurar da Sunaiha, dan ta fi so ta ga tayi aure ko wannan halin na ta zai rage, amma da aka mata maganar miji sai cewa tayi ita har yanzu bata haɗu da irin mijin da take so ba, a cewarta akwai wanda take mafarkin samu, shi ne irin tsarin mijinta, dan haka idan ba irin wannan mijin ba, ba zata taɓa yin aure ba, wannan maganar ta matuƙar ɓata ran Hajiya Binta, amma sai ta ga shi Alhaji ko kaɗan abun ba damunshi yayi ba, sai cewa ma yayi zai taimaka mata wurin samun wannan mijin, ta kwantar da hankalinta, Hajiya Binta kuwa ta sa musu ido ta ga ikon Allah ta yanda za'a nemo wanda ake gani a mafarki, ta gaji da magana yanzu addu'a kawai take yi, Samari kuwa ƴaƴan manya, masu arziki sun fi a ƙirga waɗanda ke zuwa neman aurenta, amma ko wanensu da irin wulaƙancin da take korarsa da shi.

WANNAN SHI NE TAKAITACCEN BAYANI AKAN *ƳAR SENATOR*

_CI GABA_ ~~~~~~~~~~~

Senator Abubakar na office ɗin shi yana aiki, wani mutum ya shigo da sallama, sai da suka gaisa kafin ya nuna mishi kujera ya ce "zauna mana Alhaji"

Murmushi yayi sannan ya zauna, sake gaisawa suka yi, kafin mutumin ya ajiye file ɗin dake hannunshi ya ce "ranka ya daɗe ka manta da maganar fitarmu ne? "

"A'a Alhaji Sani ban manta ba, akwai wanda nake jira ne shiyasa"

"Akwai wanda kake jira kuma? "

"Eh, Alhaji Makama ne, although personal issue ne ba na aiki ba, amma yana da flight ne by 12 zai tafi China, shiyasa na ce ya zo nan kawai mu haɗu dan ka ga yanzu almost 11:20am"

Agogo ya duba, ya ce "to ba damuwa, Allah dai ya sa lafiya"

"Lafiya ƙalau, kawai magana ne akan Sunaiha"

Da mamaki ya ce "Ah! Ta dawo ne? Ko tana can? "

Murmushi yayi ya ce "ta dawo ai, ta kusan wata biyar ma da ta dawo, yanzu ma maganar aurenta ne ake yi"

"Allah sarki, ai wallahi ban sani ba, ashe har ta samu miji, ga yaron nan kusan kullum sai ya mun maganar ta"

"Wane yaro kenan? " Senator ya tambaye shi

"Yaron waje na, Usman, tun ranar da na aike shi gidanka, da ya dawo ya gaya mun ya ga hotonta a parlourn ku, kuma ta kwanta mishi, shi ne fa na ce bata ƙasar amma idan ta dawo sai ya zo su ga juna"

"Ai da tun lokacin ya kamata ka mun magana... Anyway, yanzu ma lokaci ba ƙure ba, dan bata tsayar da mijin ba, zai iya zuwa ya ganta, kasan dama ita mace allura ce cikin ruwa.... "

Alhaji Sani ya ƙarasa mishi "mai rabo kan ɗauka... Na ji daɗi sosai, in sha Allah zan gaya mishi sai ya shirya gobe ya je ganinta ɗin"

"Hakan ma yayi, zan sanar da ita"

"To na gode... Bari in je sai in jira ka a waje to"

"Ba damuwa"
Miƙewa Alhaji Sani yayi ya fita, a bakin ƙofa suka haɗu da Alhaji Makama, sai da suka gaisa kafin ya wuce shi kuma ya shigo ciki

Duk dai maganar ɗaya ce, shi ma ɗan wajensa ke son Sunaiha, shi ne ya zi nema mishi alfarma dan ya je ya ganta, Alhaji Makama shi ma babba ne a fagen siyasa, Senator Abubakar ya gaya mishi Sagir zai iya zuwa ganinta anjima da yamma, godiya Alhaji Makama yayi kafin ya bar office ɗin, sannan Senator Abubakar shi ma ya fito

Sunaiha na gidansu babbar ƙawarta, IKRAM, suna shirin zuwa wurin bikin wata ƙawarsu,

lokacin Daddynta ya kira ta, wayar na fara ƙara ta ɗauka da sauri dan ta san shi ne, ai kuwa da ta tabbatar shi ɗin ne, ba ɓata lokaci ta ɗaga

"Hello Daddy na" ta faɗa

"Baby na, kina ina? "

"Daddy ina gidansu Ikram, za mu je wurin bikin da na gaya maka ne"

"Mummynki ta san kin fito? Kin san wancan lokacin ma haka ta yi ta faɗa da kika fita tana bacci"

Dariya tayi ta ce "eh ta sani Daddy, tana parlour ma lokacin da na fito"

"To shikenan.... Dama zan gaya miki ne kina da baƙi dan ki koma gida da wuri, ɗayan zai zo yau da yamma, Sagir Abdullahi Makama, ɗayan kuma sai gobe"

Numfashi ta sauke tana girgiza kai, ta ce "shikenan Daddy, i'll be back on time"

"That's my girl, take care, ba zan dawo da wuri ba shiyasa na gaya miki yanzu"

"No p Dad, take care too" tana gama faɗr hqka suka kashe wayar

Wani numfashin ta sake saukewa ta ce "oh ni Sunaiha"

Ikram da ke faman shafa jambaki, ta ce "hey, what's wrong? "

"Hmm, i have a guest, da yamma"

Dariya Ikram tayi ta ce "to meye? Abunda ma na san za ki sa shi ne sahun waɗancan! "

"Ke ma kin sani ai, suna ɓata lokacinsu ne kawai, dan ina tunanin ma Prince ɗina ba'a garin nan yake ba, dan har yanzu ba mu haɗu ba"

"Prince dai, Prince dai, Prince dai... Wai a mafarkin naki gidan sarauta kike ganinshi? "
"Ko ɗaya, ba'a gidan sarauta nake ganinshi ba, but he's the Prince of my heart"

Dariya Ikram tayi sosai, ta ce "prince of ur heart, ban taɓa ji ba... To idan shi ne prince, who's the King of ur heart"

Murmushi tayi ta ce "My Dad, He's the KING, while My dream Boy is the Prince"

Dariya ta sake yi, ta miƙe tsaya ta ɗauki mayafinta da jakarta, ta ce "Allah ya ba ki lafiya Sunaiha ta, tashi mu tafi"

Sai da ta zabga mata harara kafin ta miƙe ta ce "Ameen.. Ki ci gaba da dariya, wata rana sai na gaya miki na haɗu da Prince ɗina"

"Hmm, all the best" daga haka suka fita

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~

_"'You should never be sorry for something you choose to do that is right and true, because right is right even if everyone else is wrong about it, and wrong is wrong even if everyone else is wrong"'_

*PAGE 3-4*
~~~~~~~~~~~~~~~

Kamar yanda Daddy ya gaya mata, tun ƙarfe huɗu ta dawo gida, ta gaya wa Mummy yanda suka yi da Daddynta

Mummy ta ce "ai ya kira ni, na sa a haɗa mishi abinci ma"

"Mummy  wa za'a haɗa wa abinci kuma? "

"Ji wani tambaya...  baƙonki mana, Sagir"

"But Mummy why? Ko so kike yayi tunanin na damu da shi ne? " ta faɗa rai a ɓace

Kallonta Mummy tayi da mamaki ta ce "Sunaiha abincin ne da za'a mishi kuma tashin hankalinki? "

"Yes Mom"

Numfashi Mummy ta sauke, kafin kuma maganar ta bata haushi, sai ta ce "to dan ubanki sai an girka mishi abincin sai dai ki mutu, wannan mugun halin na ki yayi yawa wallahi, me aka yi, aka yi abinci, abincin da kin san kin fi ƙarfinshi!!.. Dalla ni wuce ki bani wuri kafin in mangare ki Allah"

Bubbuga ƙafa ta fara yi ƙasa tana masifa kamar za tayi kuka, ta haura sama, Mummy ta bi ta da ido kawai har ta wuce sannan ta zauna ta ce "Allah ya shirya mun ke"

Komai ya kammala a ɗakin baƙi, zuwan Sagir kawai ake jira, bai zo ba kuwa sai ƙarfe biyar, har ɗakin baƙi ɗaya daga cikin ma'aikatan gidan ya kai shi kafin ya je main parlour ya gaya wa Mummy

Waya ta ɗauka ta kira numbern Sunaiha da ke ɗakinta, tana ɗagawa ta ce "ki sauƙo ga shi nan ya zo" ba ta jira jin amsarta ba ta kashe wayar

Sunaiha kuwa ji tayi ranta ya matuƙar ɓaci, ko motsawa daga wurin da take ba tayi ba kusan mintuna goma, kafin ta tashi ta je tayi wanka ta fito, bakin mirror ta zauna ta shafe jikinta da lotions ɗinta sannan ta saka turare ɗan kaɗan, ta jawo wayarta ta fara chatting, kiran Mummy ya sake shigowa, sai da ta ɓata rai kafin ta ɗauka

"Mummy gani nan fitowa" ta faɗa tana turo baki

"Kar ma ki fito, ki bari in zo in same ki, kuma saura ki fito kamar me takaba ki gani" ta kashe wayar

Kallon fuskarta take cikin madubi, kyakkyawar gaske ce, ita kanta tana yaba irin kyaun da Allah ya mata, wataƙila shiyasa sam kwalliya ba ya cikin tsarin rayuwarta, in dai za tayi wanka ta

shafa mai, to shikenan ta gama mai wuyar

Sai dai a cewarta dalili ɗaya ne ke hana ta yin kwalliya, wai tana taya Prince ɗinta kishin kanta ne, bata so tayi kwalliya wani ya gani wanda ba Prince ɗinta ba

Ta daɗe tana kallon kanta a madubi, kafin tayi tsaki ta ɗauko kwalli kawai ta sa ma idonta shi ma dan kar Mummy ta mata faɗa ne

Wardrobe ta nufa, doguwar rigar atampa kalar ja da baƙi ta ɗauka ta saka, kusan rabin kayanta dogayen riguna ne, ta ɗauko gyalen kayan, shi ma ja , ɗan ƙarami ne, sai kawai ta ɗora shi a kai ta zagaye wuyanta da shi, sai flat shoes ɗinta baƙi, sannan ta sauko parlour

Kallo ɗaya Mummy ta mata ta ɗauke kanta, ita ma bata tsaya wurinta ba kawai ta fita, sai a lokacin Mummy ta ce "Allah yayi mace har mace, kyakkyawa ga iya ɗaukar wanka, son kowa ƙin wanda ya rasa, amma ta ce ba ta da aiki sai na wulaƙanta masu sonta, wai ita matar Prince... Mtsww" tayi tsaki ta ci gaba da abunda take yi

Sunaiha kuwa tana zuwa ɗakin ta tura ƙofar ta shiga babu sallama, akwai wurin da aka tanada dan ajiye takalmi daga cikin ɗakin, amma ko kallon gefen bata yi ba ta wuce da takalminta ciki

Sagir na zaune kan kujera har ya fara gajiya, ba laifi yana da kyau dai-dai misali, tun shigowarta ta kafe shi da ido, wani kallo take mishi har ta kai kusa da kujera ta zauna, kafin ta ɗauke idonta daga kan shi tana kallon ƙaton tray ɗin da aka ciko mishi da kuloli, ruwa kawai ta ga ya buɗe ya sha

Ta sake ɗaga ido ta kalle shi, ta jingina bayanta jikin kujerar, ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya

"Sannunki da fitowa" Sagir ya faɗa yana kallonta

Kallo ta mishi mai kama da harara, sannan ta ce "ba ciwo nake yi ba bare ka ce mun sannu....(nuna tray ɗin tayi da hannu tana yamutsa fuska) ya dai sarkin yunwa! Naga kamar ba ka ci komai ba.. Ko dai a leda za'a juye maka ka kaiwa mutanen gida? "

Mamaki ne ya cika shi, buɗe ido yayi yana kallonta ,ya ce "ke!!! Me kika ce??! " ya faɗa yana miƙewa tsaye

"Ni kake tambaya abunda nace? Ai bana magana biyu"

"Ni kike kira da sarkin yunwa? Kin san ko ni waye kuwa? " ya faɗa rai a ɓace yana nuna kanshi da yatsa

Harara ta sake zabga mishi tayi tsaki ba tare da tace komai ba, Mamaki ne ya sake kama shi, ya ce

"Sagir Abdullahi Makama, ni kike ma wannan rashin kunyar? Kin san waye mahaifi na a garin nan kuwa? "

Miƙewa tayi ita ma, ta ce "Sagir Abdullahi Makama... Ina tunanin baka san wurin da ka zo ba ne shiyasa kake gaya mun sunanka da gadara.. In har ka manta ne, to kana gaban Sunaiha Abubakar Nuraddeen, ƳAR SENATOR, ka gane?"

"Ƴar senator?! Kina ƴar senator ɗin ne ake roƙon maza su zo su aure ki? "

A tsawace ta ce "kai Sagir!!! Dakata.. Ka koma gida ka tambayi Abdullahi Makama, wa ya miƙa ƙoƙon bararsa? Sunaiha ta fi ƙarfin haka wallahi, Shashasha kawai" ba ta jira jin me zai ce ba ta wuce bayan ta gama hararарshi

Shi kuwa tsayawa yayi kamar wani hoto, ya ma rasa yanda zai yi da ita, har ta wuce kallonta yake, haushin kanshi yake ji bai ma san dalilin da yasa mahaifinshi ya turo shi nan ba

Numfashi ya ja ya ce "zan yi maganinki tabbas... " a fusace ya bar gidan

Mutumiyar kuwa bayan ta koma parlour, ta cire mayafinta ta ajiye, ta zauna kan kujera ta ɗora ƙafarta kan center table ta rufe ido tana tunani, ɗaya daga cikin mai aikinsu ce ta zo da fruit salad cikin bowl, kasancewar wannan lokacin tana shan fruit salad

Ajiyewa tayi kan table ɗin ta ce "ranki ya daɗe ga fruit salad ɗin na haɗa miki"

Ko motsi ba tayi ba, hakan ya san tayi zaton ko bacci take yi, sai kawai ta ɗauka zata koma da shi gudun kar tayi laifi, sai bowl ɗin ya suɓuce mata a hannu sai kan ƙafar Sunaiha

Da sauri ta tashi sabida yanda ta ji sanyi a ƙafarta, tana ganin ko wacece bata twaya jin komai ba ta wanke ta da mari, ta ce "ke mahaukaciyar ina ce, wawiya kawai, duba ki ga abunda kika yi"

"Dan Allah ranki ya daɗe kiti haƙuri, wallahi tsautsayi ne"

"Tsautsayi ko! Za ki ga tsautsayi"

Wucewa tayi dinning area ta buɗe fridge ta ɗauko ruwa masu sanyi sosai ta tsiyaya a cup sannan ta dawo kusa da ita ta watsa mata su a fuska, sai da ta razana, har numfashinta ta ji ya tsaya kafin ta sauke ajiyar zuciya da ƙarfi tana shafa fuskar

Sunaiha ta ce "gobe idan kika sake ɗauko wani abu, ki bari tsautsayi ya sa ki zuba mun shi a jiki ki gani yanda zan yi dake"

Mummy dake fitowa daga kitchen wurin duba abincin da suke girkawa, ta tsaya tana kallonsu ta ce "lafiya? Me kuma ya faru? "

Kallonta kawai Sunaiha tayi, ta ɗauki wayarta ta haura sama, bin ta tayi da kallo kafin ta juya wurin mai aikin, ta ce "me ya faru? "

Tana kuka ta bata labarin yanda aka yi, tsaki Mummy tayi tana girgiza kai, ta ce "kiyi haƙuri kin ji ko... Je ki ƙarasa aikinki"

Ɗaga mata kai tayi, ta ɗauki bowl ɗin zuwa kitchen, sannan ta dawo ta gyara wurin tas

Tunda Sunaiha ta shiga ɗakinta bata sauko ba sai bayan sallar isha'i, shi ma lokacin ta ji dawowar Daddynta

Da gudu ta sauko ta rungume shi, ta ce "you're welcome Dad"

Cikin fara'a ya ce "thank you Baby na, ya gida"

"Ɗazu dai ba daɗi, amma yanzu komai normal tun da ka dawo"

Murmushi yayi ya ce "to zauna ki jira ni bari in fito"

Ta wuce kan kujera ta zauna, shi kuma ya wuce ɗakinshi dan yayi wanka, Mummy na zaune tana waya ko kallonsu ba tayi ba, har ta gama sannan ta bi bayanshi

Tsawon mintuna ashirin sannan suka fito, kai tsaye dinning area suka wuce dan a nan suka ga Sunaiha

Daddy ya ce "Baby yunwa ne? "

Murmushi tayi ta ɗaga mishi kai, bayan an gama zuba musu, suka fara ci

Gyaran murya Daddy yayi ya ce "Baby"

"Umm.. " ta amsa dai-dai lokacin da take kai cokali bakinta

"Ba ki gaya mun ya kuka yi da Sagir ba ɗazu"

Sai da tayi tsaki ta ce "manta da shi kawai Daddy, wannan ya ma fi kowa raina ni wallahi"

Ƴar dariya yayi ya ce "ya raina ki fa kika ce.... Ni kuma mahaifinshi ya kira ni wai bai ji dađin yanda aka yi wa yaronshi ba"

"To ni gaya mishi aka yi naji dađin abunda yaronshi ya mun ne? Wai har ni yake kallo ya tambaye ni wai na san ko shi waye? "

Dariyar ya sake yi ya ce "yanzu dai Baby shi ma bai miki ba? "

"Ko kusa ma"

"Alright, gobe ma đayan zai zo kinji"

"Daddy ni fa na gaji" ta fađa a shagwaɓe

"Yi haƙuri dai, kika sani ma ko shi ne Prince đin na ki? "

"Tab, God forbid, ba shi ba ne"

Mummy da ke ji kamar ta hađa kansu wuri đaya saboda haushi, ta ce "wai Alhaji sai yaushe kake so yarinyar nan tayi hankali ne? Yaushe kake so tayi aure? Kai shikenan duk yanda ta ce haka đin za kayi? Wannan wane irin rayuwa ne? Yanzu fa uban yaron nan ya gaya maka bai ji dađin abunda ya faru ba, maimakon ka tambayi me ta mishi dan kayi magana ta gyara, a'a kai wannan ba damuwarka ba ne... Alhaji ina tausaya ma rayuwar yarinyar nan ba ka ganewa wallahi, a ƙalla ta kori samari sun kai sha takwas, Sagir ne na sha tara.. "

Rai a ɓace ya ce "Haba Hajiya, wai me yasa ke bakinki baya furta kalma mai dađi akan Baby ne? Idan ban faranta ranta ba wa kike so in farantawa? "

"Ni ba wai na hana ka farantawa ƴarka ba, amma dai a riƙa sara ana duba bakin gatari, kar garin ruwan idon neman Prince ta je ta sa kanta a matsala, wulaƙancin yayi yawa"

"Ba wata matsala da za ta shiga in sha Allah, kuma sai wanda Baby ta ji tana so sannan zan bada ita"

"To ai shikenan, sai kuyi tayi.... Ke kuma ki ci gaba da biye mishi" ta ƙarasa tana nuna Sunaiha, sannan ta tashi rai a ɓace ta bar wurin zuwa đaki

Sunaiha ta ce "Daddy wai meyasa Mummy kullum sai ta mun fađa ne, komai nayi ba dai-dai ba ne a wurinta"

"ƙyale ta kin ji Baby, ai ni komai kika yi dai-dai ne a wurina, your Dad is always by your side"

Dađi ta ji sosai, sai kawai suka ci gaba da cin abincinsu, har suka gama sannan kowa ya wuce

ɗaki

Washe gari da safe kamar yanda Mummy ta sa aka haɗawa Sagir abinci, haka ma ta sake sa aka haɗa ma ɗan gidan Alhaji Sani, ƙarfe sha ɗaya da ƴan mintuna ya iso, sai da yayi zaman minti talatin kafin ta je ta same shi

Ya ganinta ya miƙe tsaye yana bin ta da ido har ta tsaya kusa da shi, sannan ya ce "lallai tsarki ya tabbata ga ubangijin halittu.... Ashe haka kike da kyau? Ba ke camera ke haskawa ba, ke ce kike haska camera, dan kin ma fi kyau a zahiri Sunaiha ta... "

Da sauri ta katse shi ta hanyar ɗaga mishi hannu "kai Malam hold on, me naji ka ce? Sunaiharka?"

"Eh mana, idan ban kira ki tawa ba, wa zan kira? "

"Hmm to bari ka ji, ya ma sunanka.... Umm.. I don't even know, abunda dai zan gaya maka shi ne, tun wuri ka je ka nemi dai-dai da kai, saboda Sunaiha ba sa'arka ba ce, ko da wasa kar in sake jin wannan ƙazamin bakin naka ya kira sunana ma, kai ko kunya baka ji ba? Dube ka dan Allah ka zo da wani ƙaton kanka wai 'Sunaiha ta' wallahi ka kiyaye ni"

Duba jikinshi yake yi yana so ya ga me ta gani da har take mishi wannan wulaƙancin, amma ba abunda ya gani wanda bai yi ba, ya ce "Sunaiha me.... "

Sake katse shi tayi "wai ba na ce kar in sake jin sunana a bakinka ba! Sunaiha ta fi ƙarfinka, ko maza sun ƙare a duniyan nan wallahi ba zan taɓa aurenka ba, ka hutar da kanka kawai" tayi tsaki ta fita daga ɗakin

Ya daɗe a zaune zuciyar na mishi zafi, sam bai ji haushin kalamanta ba saboda yana sonta sosai, abu ɗaya ne ke damunshi da ta ce wai ba zata aure shi ba, hakan na nufin ba ta sonshi kenan! Ya gaji da zaman ya tashi ya wuce

Lokacin da ta shigo parlourn, Mummy na ɗakinta, ita ma ba ta zauna a parlourn ba ta wuce ɗaki, sake shiryawa tayi sannan ta fito ta wuce ɗakin Mummy

Tura ƙofar tayi ta shiga, Mummy na duba kaya a wardrobe ko juyowa ba tayi ba

"Mummy" ta kira sunanta amma ba ta kalle ta ba, ta ci gaba da abunda take yi

"Mummy kin kyale ni"

"Ki koma kiyi sallama" abunda ta ce mata kenan

Sai da ta turo baki kafin ta koma waje ta sake shigowa da sallama, Mummy ta amsa, sannan ta

ce "ina gaya miki ki daina shigo mun ɗaki ba sallama, duk in da zaki shiga kar kiyi sallamar, amma dai ɗaki na dole sai kinyi, wannan ya zama na farko kuma na ƙarshe da zan sake yi miki magana"

"Ai mantawa nake yi"

"Dole za ki manta tunda ba ki ɗauke shi da muhimmanci ba ai... Kin kori na ashirin ɗin? "

"Ni ban kore shi ba"

"Kenan yayi miki? "

"Allah ya kiyaye, da wani ƙaton kan shi ɗin zai mun? "

"Hmm, Allah ya kyauta"

"Mummy ina so zan fita ne dan Allah"

"Zuwa ina? Ke ba kya da aiki sai yawo wai? "

"Mummy i'm sorry, ba yawo zan je ba, Ikram ce za ta je shopping shi ne ta kira ni ko zan je sai mu tafi tare"

"Ai saboda ta san ba kya da aiki sai na yawo shiyasa ta ce ki raka ta, to ba za ki je ba"

"Mummy dan Allah.... "

A tsawace ta ce "na ce ba za ki je ba ko!! Ki fita ki bani wuri"

Fashewa tayi da kuka, ta fita da gudu, Mummy ko kallonta ba tayi ba ta ci gaba da aikinta

Kusan minti goma sai ta fito, ta na kai wa wurin ɗakin Sunaiha ta ji tana waya

"Iky ki je kawai ba zan tafi ba"

"Amma shi ne kika ɓata mun lokaci kin san ba za ki tafi ba?"

"Mummy ce ta hana ni shiyasa, kin ga kuwa dole zan zauna"

"Shikenan"

Ta kashe wayar tana share hawaye, duk yanda Mummy ke mata ba wai dan bata jin haushi ba ne idan ta ga ran Sunaiha ya ɓaci, tana mata wasu abubuwa ne saboda ta gyara rayuwarta

Shiga ɗakin tayi ta ce "me kike yi? kuka? "

Shiru tayi ba ta ce komai ba, Mummy ta sake cewa "saboda na hanaki zuwa shopping ɗin ne? "

Ta ɗaga mata kai tayi tana goge hawayen da ya gangaro mata, Mummy ta ƙarasa kusa da ita ta ce "yi shiru to ya isa, ba na so yawonki yayi yawa ne Sunaiha, zaman ki a gida ya fiye miki, amma tashi ki tafi kar ki daɗe kinji ko"

Daɗi ta ji, ta ce "to Mummy na, na gode, yanzu zan dawo"

"To Allah ya kiyaye"

Toilet ta shiga ta wanke fuskarta, sannan ta fito ta ɗauki mayafinta ta fita bayan ta kira Ikram ta ce ta jira ta

A wannan ɓangaren kuwa, wani katafaren parlour ne mai girman gaske wanda aƙalla za'a iya cire bedroom biyu manya a cikinshi, set ɗin kujeru biyu ne a ciki, ko wane da na shi ɓangaren, da carpet ɗin shi, ɗaya royal ne ɗayan kuma normal cushions ne, parlourn ya haɗu ƙarshen haɗuwa, abun sai wanda ya gani

Manyan mata ne su uku a zaune kan cushions ɗin, kana ganinsu za ka fahimci iyaye ne, sai dai ko wacensu fuska sumul, alamun hutu,  sai list ɗin kayayyaki suke ta faman yi, daga ɗayan ɓangaren kuma ƴan mata ne su biyar kan royal cushions, gaba ɗayan su ba za su wuce shekaru sha takwas zuwa ashirin ba, kaya ne a gabansu kan center table, atampopi, laces da materials, suna ta dubawa, a taƙaice dai kallo ɗaya zaka yi musu ka fahimci shirye-shiryen biki suke yi

Ɗaya daga cikin matan, ta kalli ɓangaren yaran ta ce "wai ku har yanzu ba ku gama zaɓen kayan ba ne? "

Wacce ta fi su girma, ta ce "Hajiya wallahi mun rasa wanda ma za mu ɗauka ne"

"Me kuke nufi? Su ma ba su muku ba kenan"

"A'a Hajiya, sun yi, ai shiyasa muke ta ruwan ido wallahi"

Wata budurwa da ke sauko daga kan stairs riƙe da robar ice-cream a hannu, ta ce "ai sai kuyi tayi, ba na gaya muku ga wanda zamu ɗauka ba kun ce ba haka ba, ni yanzu ƴar kallo ce ai" ta ƙarasa maganar dai-dai lokacin da ta zauna kusa da Hajiya tana shan ice-cream ɗinta

Hajiya ta ce "ke wane colour kika ɗauka? "

"Material na ce muyi baby pink ɗin can sun ce su ba yara ba ne"

Wata budurwar ta ce "Hajiya kin gan shi nan fa, sai ka ce wasu yara! Wallahi ba ma sanshi"

Wata mata ta ce "kin ga SULTANA, yi shiru kyale su kawai"

"To Mami" ta amsa mata, sannan ta ɗauki remote tana canza channel

Suna haka ne wasu maza biyu suka shigo parlourn, kai tsaye wurin iyayensu suka wuce, Mami ta ce "yawwa kun ƙaraso?"

Ɗayan ya ce "eh Mami, ina list ɗin? "

Miƙa mishi tayi, ya kalla sannan ya ce "shi kenan? "

"Eh"

Hajiya ta ce "SAMEER, ina ango?"

"Sun fita, wai za su je su duba ɗinkin da suka kai"

Matar da ba tayi magana ba tun ɗazu ta ce "ni suka shanya kenan? Zaman jiransu fa nake yi nan"

Dariya suka yi, Sameer ya ce "ba laifin Ya SAFWAN bane fa"

Ta ce "ai na sani, wancan ɗan rainin hankalin ne, kuma fa shi na gaya wa su zo ina nemansu"

Sameer ya ce "me za suyi miki, sai in yi"

"A'a aikan zai muku yawa, ku je kawai"

"To shikenan" ya faɗa, har zai wuce, ya lura da ice-cream ɗin dake hannun Sultana, hankalinta na kan TV, ɗauke robar yayi bata ma sani ba sai ganin wucewarsa kawai tayi, ai kuwa tashi tayi da gudu ta bi shi tana faɗin "bana son haka, ka dawo mun da kaya na"

Dariya yake yi ya fita ɗakin da gudu yana ce ma ɗayan da suka shigo tare "kai na mata idan ka gama ka same ni a mota" sannan ya fita

Sultana na ganin ya fita, ta tsaya tana huci, ta ce "ai zaka dawo ne"

Shi kuwa ɗayan yana can cikin matan yana taya su zaɓen kayan, ɗaya daga cikinsu ta ce

"SAUBAN je ka dawo, may be ma sai ka raka ni na sake duba wasu"

"Ke yanzu waɗannan ba su miki ba?" cewar Sauban

"Eh wallahi"

"To bari in dawo" sai ya tashi ya fita

Hajiya ta ce "SALMA me naji kina cewa? Wasu kayan za ku nemo kuma, waɗannan ba suyi ba?
"

"Eh mana Hajiya, idan muka duba wasu sai muyi comparing mu ga wanda ya fi kyau"

Hajiya ta ce "Allah ya shirye ku wallahi, duk lokacin da za'a yi biki a gidan nan kun dinga ruwan ido kenan"

Ɗayar me suna SAJIDA, ta ce "of course Hajiya dole za muyi ruwan ido ai, muna so ne duk wanda ya kalle mu ya san mu ne ƙirjin bikin ai"

Mami ta ce "umm, shirme dai ba zai taɓa ƙare muku ba"

"Sun ji za su iya ne ai... Da ma zuwa muka yi muka duba waɗancan kayan ai zai fi" cewar Umma

Gaba ɗaya suka tashi, Hajiya, Umma da Mami, suka haura sama, suka bar ƴan matan suna ta surutunsu

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*YAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_"'Immature people want to win an argument even at the cost of relationship, but mature people opt to loose an argument in order to maintain a relation....'"_

*PAGE 5-6*

Dai-dai lokacin da su Sameer suka fito daga gidansu suka hau titi, wasu samari biyu na wucewa ta gefen titin, ɗayan ne ya bi motar da kallo har sai da suka ɓace mishi, sai ɗayan ya taɓa shi ya ce "wai Ado me kake kallo ne haka?"

Numfashi Ado ya sauke ya ce "halittar Ubangiji nake kallo... Aminu ka ga wasu kyawawan samari wai da suka wuce yanzu?! Allah ban taɓa tsammanin akwai masu kyau irin haka a Nigeria ba"

Murmushi Aminu yayi ya ce "wai su Sameer kake nufi?"

"Au, ka san su kenan, amma wannan unguwar ai ta manyan mutane ce, ya aka yi ka san su kuma? "

"Lallai na yarda kai baƙo ne, tabbas nan layin masu kuɗi ne, amma ai ko mu da muke layin bayin Allah ai mun san waɗannan"

"Ban gane ba Aminu, ka fito mun a mutum mana"
~~~~~~~~~~~~~~

"Hmm.. Dama cewa kayi in zagaya da kai ka ga gari, to tunda har zagayen na mu ya biyo ta nan, zan baka labarin mutanen gidan nan... Zo ka gani"

Jan shi yayi zuwa kusa da gidansu Sameer ɗin, sai dai ɗayan tsallaken suke, ya ce "duba da kyau, tun da muka shigo layin nan, ka ga gidan da ya kai wannan girma?"

Baki a buɗe Ado ke kallon gidan ya ce "ai tun da na shigo garin nan ma ban ci karo da babban gida kamar wannan ba"

"To wannan gidan shi ne ake yi wa laƙabi da ' _Gidan Kyawawa_ ', tun daga kan manya har zuwa ƙanana, maza da mata, in dai ahalin gidan nan ne, to kyawawan gaske ne, kamar yanda ka ga waɗancan masu kyau, to haka sauran suke... Sai dai akwai wasu guda biyu waɗanda su kuma ba wanda ya kai su kyau a gidan... "

Katse shi Ado yayi ya ce "yanzu Aminu kana nufin duk kyaun waɗancan akwai waɗanda suka fi su anan?! "

"Ƙwarai kuwa, ɗayan sunanta Sultana, ɗayan kuma *SADEEQ* amma an fi kiranshi da _TIGER_ "

"Tab, amma kam zan so ganin waɗannan wallahi"

"Shawara ɗaya zan baka, in ma har ka samu ganinsu, to kar ma ka ɓata bakinka wurin yi mishi magana, dan ka ga sauran nan za ka iya musu magana su amsa ka, amma wannan Tiger ɗin ko kallonka ma ba zai yi ba, miskili ne wallahi... Kuma ba ma lallai ka iya ganinshi ɗin ba"

"Meyasa? Ba garin nan yake ba ne?" Ado ya tambaye shi

"A garin nan yake, amma yana da wuya ka ga fuskarshi, wani lokacin ba ya ɓoye fuska, amma ya fi yawan ɓoye fuska, face-mask yake sa wa da madubi, idan ba wanda ya san shi ba yana da wuya yayi saurin gane  shi, amma fa duk da haka idan ka kalle shi zaka iya gane yana da kyau... Sannan kuma duk motocin da ke cikin gidan nan gilashinsu tas suke, amma na shi ya rufe shi da baƙin tinted.... "

"Meye hakan kuma?"

"Baƙauye kawai... Wannan abun da ake sa wa mota baka gane wanda yake ciki"

"Au, na fahimta... To ci gaba"

"In ci gaba da me? Dalla wuce mu tafi, ba aiki na kenan ba, na gaji"

Ado ba dan ya so ba ya bi Aminu suka wuce, amma a ranshi ya ji yana so ya ga wannan Sadeeq ɗin saboda ya ga wane irin kyau ne Allah ya ba shi

Matasa ne su biyu cikin wata mota baƙa da baƙin tinted, ɗayan ya sa baƙin glass da face-mask, ɓakin giransa da gashin kansa baƙi mai kyau da ya sha haɗaɗɗen aski sai rabin sajensa, su ne kaɗai abunda ake gani a fuskarsa, ɗayan kuwa glass kawai ya saka, shi ke driving, ko wanensu ya sha jeans da t-shirt, ba za su gaza shekaru talatin ba

Wanda ke driving ɗin ya kalli ɗayan ya ce "Tiger, anya kuwa Ayman ya aikawa su Saif da IV?"

Ƙyale shi yayi kamar bai ji abunda ya ce ba, ya sake cewa "da kai nake yi fa Tiger, ni fa iskancin nan na ka ne bana so"

Kamar ba zai yi magana ba, sai kuma ya ce "sau nawa kake so in gaya maka na aika musu? "

"Sau goma, kayi biyu saura takwas"

Murmushi Tiger yayi wanda bai shirya mishi ba, ya ce "to Safwan ko na uku ba zan yi ba"

Shi ma Safwan ɗin ƴar dariya yayi ya ce "ba dai ka ce kai ɗan rainin hankali ba ne ko! Ina gaya maka wannan miskilancin na ka ba zamu shirya da shi ba, is better ma idan muna tare ka ajiye shi"

Yana danna wayarshi ba tare da ya kalle shi ba, ya ce "amma dai ka san yanda nake fira da kai bana yi wa kowa ko? Amma tsabar rashin godiyar Allah sai kayi mita"

"Mita ko?  Yayi kyau" Safwan ya faɗa lokacin da ya shiga wani layi, hakan yayi dai-dai da isowar su Sunaiha

Ba wanda ya san da wani, kaɗan ya rage su bugi juna, da sauri ko wanensu ya taka burki

Da sauri Sunaiha ta fito daga motar, ta zo gaban motarsu ta tsaya, ta daki gaban motar ta ce "fito nan"

Safwan ya saki baki yana kallonta, ta sake dukan motar, "na ce ka fito, so nake in ga kai ɗin waye?"

Safwan ya kalli Tiger ya ga ko a jikinshi, dan wayarshi ma yake kallo, sai kawai ya buɗe motar ya fito ya zo jikin motar ya jingina, ya naɗe hannu yana kallonta

"Kai mahaukacin ina ne? A wace makaranta ka koyi driving, kai baka san ana yin horn ba ne

idan zaka shiga kwana? Wallahi da ace ka bugi motar nan da ka gane baka da wayau"

Ikram da ke gefenta, ta ce "Sunaiha kiyi haƙuri mana, ai dai ba abunda ya faru"

"Shiyasa nake ja mishi kunne saboda kar nan gaba wani abun ya faru in nuna mishi shi ba kowa bane"

Ikram ta sake cewa "wai kin san da wa kike magana kuwa? Dan Allah ki zo mu wuce.. "

A tsawace ta ce "ke dalla can ki rufe mun baki, ni ina ruwana da ko shi waye? Wannan matsalarsa ce" kallon cikin motar tayi ta glass ɗin gaba, ta hango alamar mutum a ciki, sai dai bata gane yanayin fuskarshi ba kasancewar shi ma glass ɗin yana da ɗan duhu, sai ta ce "shi wancan wane shafaffe da man ne da ba zai iya fitowa ba?"

Juyawa Safwan yayi dan ya ga ko yana kallonsu, amma har ynx wayarshi ce ta dame shi

Tsawa ta sake daka mishi, ta ce "ba da kai nake magana ba?"

Jin yanda ta mishi magana ne ya sa shi ma ya mata tsawan da sai da ta razana "stop it!!! Kar ki sake ɗaga mun murya, dan nayi shiru ina sauraren ki ba shi zai sa ki ɗaga mun murya ba, na ƙyale ki ne saboda ke mace ce, ban da time ɗin da zan tsaya sa'insa da mace shiyasa na tsaya ki gama surutunki in wuce, amma kina neman ki wuce gona da iri, kina jin ke wata ce? "

"Ƙwarai kuwa, ni wata ce shiyasa har nake gaya maka magana kuma dole ka saurare ni"

Kafin yayi magana, Ikram ta ce "dan Allah Safwan kayi haƙuri, kar ka ce komai, ka wuce kawai"

Bai yi mamakin jin ta kira sunanshi ba, kallonta kawai yayi, sannan ya sake yi ma Sunaiha wani kallo kafin ya juya ya shiga mota, yayi reverse sannan ya wuce

Kasancewar layin na manyan mutane ne, ba hayaniyar jama'a, shiyasa har suka gama ba wanda ma ya san su na yi

Sunaiha ta bi motar da harara, sannan ta ce ma Ikram "Kar ki sake mun irin wannan abun, kina wani lallaɓa shi, shi ɗin ɗan gidan uban waye? So kike ya raina ni ko me?"

"Hmm, zo ki shiga mota mu tafi"

"Ba magana nake miki ba! Waye shi? "

Numfashi Ikram ta sauke, ta ce "sunanshi Safwan Muhammad Saraki"

Tsaki Sunaiha tayi ta ce "Muhammad Saraki? Ni ban taɓa jin wannan sunan a ƴan siyasar garin

nan ba, na ɗauka ɗan wani babba ne, ashe ma ba kowan kowa ba ne....hmm zai gane yayi da ƳAR SENATOR"

Ita ma Ikram ɗin tsakin tayi, ta ce "lallai na yarda ba ki zauna a garin nan ba sosai shiyasa har kike ganinshi ba kowa ba, to dukiyar gidansu ya fi na mahaifinki da yake Senator" ba ta jira jin me zata ce ba ta juya ta shige motar

Sunaiha da mamaki ta ce "ya fi mahaifina?! Senator ɗin? Tab, dole kuwa zan nemo information akansu" ita ma ta shiga motar suka wuce ba tare da ta ce ma Ikram komai ba

Ta ɓangaren su Safwan kuwa bayan ya shiga motar ya wuce, sai ya kalli Tiger ya ce "wai kai wace irin rayuwa ce kake fama da ita? Atleast ma ka nuna ka ga me ya faru amma ko a jikinka"

Ba abunda ya iya ce mishi, Safwan ya ci gaba "wallahi in banda ɗayan yarinyar nan, Allah da sai na tsinke ta da mari, yarinya sa'ar Salma ta tsaya tana ɗaga mun murya!"

Sai a lokacin Tiger ya kalle shi, ya ce "Hmm" sai kawai ya ɗan kwantar da seat ɗin ya kwanta

Ba wanda ya sake magana har suka isa wurin da za su je, Safwan ne kawai ya fita ya je dawo, sannan suka wuce gida

Su na shiga parlour, duk da su Hajiya na zaune amma Tiger yayi kamar bai gansu ba, ya sa kai zai wuce, Hajiya ta kira shi,  "Sadeeq"

Ba tare da ya amsa ba, ya cire glass ɗin idonshi, dama ya cire face-mask tun lokacin da suka shigo gidan, zuwa yayi kusa da ita ya zauna

Hajiya ta ce "lafiya? Me aka yi maka kuma?"

Umma ta ce "amma Hajiya kina son wahalar da kanki, yanzu wannan ɗin ne kike tambayar me aka mishi? Shi har sai anyi mishi wani abu ne? Idan ba wani babban abu ba ko ya ta mugunta kin taɓa ganin fara'ar Sadeeq ne? Sai kuma in yana tare da Safwan"

Safwan ya ce "ai Umma nima ba kullum ba"

Hajiya ta ce "na sani halinshi ne haka, amma yanda na san Sadeeq ɗi na, na san wannan ba hali ba ne kawai, akwai wani abu, Safwan me ka mishi? "

Safwan yayi dariya ya ce "yau na shiga uku da Hajiya, me zan mishi kuwa? Ai ni ya kamata ma in ɓata rai ba shi ba"

Umma ta ce "ƙyale shi Safwan, na san ba abunda ka mishi, ta fi abunka, ya zauna nan kullum yana ɓata rai yana fama da mugun hali, kar Allah ya sa yayi aure, ka zauna ga ka nan ka Hajiya

ai" ta ƙarasa maganar tana kallon Sadeeq da ke ta wani cin magani

Safwan yayi dariya, a ranshi ya ce 'dama ai na san sai ba Umma ba, dole sai tayi wannan maganar ta aure'

Hajiya ta ce "wai meyasa kika cika takurawa yaron nan ne, ke kullum sai kin mishi maganar aure? Tun ranar da aka sa bikin Safwan kullum sai kin goranta wa yaron nan, kuma ya gaya miki akwai wacce yake jira"

"Aikin banza kenan, wacce yake jira ɗin ya taɓa gaya miki ko wace ce? Ko ya gaya miki ko a ina take? Hakan ya nuna miki ba wata wacce yake jira, dan kawai ya rufe bakinmu ne kuma ba zai rufu ba, kar Allah yasa kayi auren, ka zauna mu zauna" ta tashi ta wuce rai a ɓace

Hajiya tayi murmushi, ta ce "Sadeeq ba ka gaya mun ba, menene"

Kamar me ciwon baki ya ce "ba komai Hajiya, na gaji ne, zan je in watsa ruwa" bai jira amsawarta ba ya miƙa ya wuce, Safwan ya bi bayanshi yana ƴar dariya

Daga gefen stairs ɗin dake parlourn ya tura wata ƙofa, za kayi zaton ko ɗaki ne, amma wata ƴar corridor ce da ta ji flowers, ɗan tafiya kaɗan suka yi, sannan suka hau matattakala zuwa sama, sannan suka tura ƙofa, wani babban parlour ne sai dai bai kai girman wancan da ke gefen su Hajiya ba

Safwan ya zauna kan cushion yana miƙe ƙafa, Sadeeq kuwa ya sake tura wata ƙofa, wata ƴar hanya ce da ƙofofi guda huɗu, sai ya buɗe ɗaya daga cikinsu

Ɗaki ne mai ɗan girma, ba wani tarkace a ciki, komai tsaf tsaf duk da cewar komai na ciki baƙi ne da fari, kan makeken gadonshi ya jefar da wayarshi, sannan ya ajiye glass ɗinshi ya faɗa toilet, bai fi minti goma ba ya fito cikin shirin wasu ƙananan kaya, sun yi matuƙar karɓar jikinshi

Lokacin da ya fito parlourn, Safwan ba ya nan, hakan ya sa ya fahimci ya wuce na shi ɗakin, sai kawai ya buɗe fridge ya ɗauki ruwa ya sha sannan ya fita

Kai tsaye ya koma wancan parlourn, stairs ya hau, daga gefe ya sake buɗe wata ƙofa, haka yake shi ma kamar dai wancan, corridor ne sai dai wannan babu stairs, ƙofa kawai ya tura sai ga shi a parlourn Umma, tana zaune tana waya

Zuwa yayi kusa da ita ya zauna a ƙasa, ya ɗora kanshi kan ƙafarta, ƙyale shi tayi sai da ta gam wayan ta ajiye, sannan ta ce "menene?"

"Maa, i'm really sorry"

"Sorry for what?"

"Ɗazu kin wuce cikin fushi kuma saboda ni, dan Allah kiyi haƙuri, kin san duniyan nan ba wanda na tsani ganin fushinsa kamar ke, you're my world, you're my happiness and everything (ke ce duniya ta, ke ce farinciki na da komai na wa), kiyi haƙuri, dan Allah" ya faɗa cikin murya mai sanyi

Ajiyar zuciya tayi, ta ce "kana so in haƙura?"

Ya ce "eh" ba tare da ya ɗaga daga kan ƙafarta ba

"Ka gaya mun wace ce wannan yarinyar da kake jira, a ina take? Meyasa kake jiranta da ba zaka gabatar mana da ita ba har yanzu, kullum magana ɗaya kawai kake maimaita mana, shiyasa ni na ma kasa yarda akwai wacce kake so ɗin"

Tashi yayi ya zauna kan kujerar, ya riƙe hannunta yana fuskantarta, ya ce "Maa, ki yarda dani, wallahi akwai wacce nake so, amma ba zan iya gaya miki ko wace ce ba bare kuma in gabatar miki da ita yanzu, amma nayi miki alƙawari za ki santa idan lokaci yayi"

A sanyaye ta ce "Sadeeq har yanzu ban ji gamsashshiyar amsa ba, abunda na saba ji ne kullum ka sake maimaitawa.... Sadeeq ina son ganin aurenka, ka duba ka ga Safwan, tare ku ka taso, komai tare kuke yi, sai yanzu da aka zo kan aure shi ne za ku yi shi daban-daban? Abbanku da ya ce a ƙyale ka ayi auren Safwan da kar a tauye shi, ba wai fa dan yana so ba ne ya ce haka, shi kanshi yana so ya ga aurenka Sadeeq, ba zaka iya faranta ran iyayenka ba?"

"Ki daina wannan maganar dan Allah, na fi kowa son ganin farincikinku... "

"To meyasa ba zaka yi mana abunda muke so ba? " ta katse shi

"Maa... Zan yi in sha Allah"

Shiru tayi tana kallonshi kamar mai son gano wani abu, ya sake cewa "kiyi haƙuri"

"Hmm... Shikenan ta shi ka tafi"

Murmushi ya mata, sannan yamiƙe ya bar ɗakin, ita kuwa ta bi shi da ido har ya fita, girgiza kai tayi, ta tashi ta shige bedroom

Sunaiha kuwa lokacin da ta dawo gida, ɗakinta ta wuce kai tsaye saboda ranta a ɓace ya ke

Mummy na saukowa, ta ga ɗaya daga cikin mai aikinsu tana aiki a dinning area, ta ce "Hindatu yarinyar nan ba ta dawo ba ko? "

Cikin girmamawa ta ce "a'a ta dawo, yanzun nan ta wuce"

"Hmm, yanzu ta dawo shi ne ko nema na ba zata iya yi ba?!... Shikenan je kiyi aikinki" ta juya ta koma sama

Tana shiga ɗakin Sunaiha ta ganta tana shirin shiga wanka, ta ce "yanzu ke kinfi ƙarfin zuwa ki ce mun kin dawo! "

Fuska ba annuri take kallonta, ta ce "Mummy raina ne a ɓace shiyasa"

"Ranki ne a ɓace? Shi ya hana ki zo ki ganni! Eh lallai ba laifinki ba ne.... Kin ga missed calls ɗina da na mahaifinki? Shi ma ɓacin ran ya hana ki ɗauki wayar ko?"

"Mummy dan Allah ki bari in huta, na gaya miki raina a ɓace yake amma kina ta mun wasu tambayoyi, haba!" ta faɗa rai a ɓace

Mamaki ne ya cika Mummy, ta ce "ni Sunaiha? Rashin kunyar ta ki ta fara kawowa kaina? To wallahi kar ki yarda in fara kai miki hannu, ni na haife ki ba ke kika haife ni ba... Kuma minti goma na baki ki gama shirinki ki fito ɗan kina da baƙo tun ɗazu yake jiranki a ɗakin baƙi"

Tana wani cin magani ta ce "baƙo kuma? Waye? "

"Ki kira ubanki ki ji... Minti goma dai na baki" Mummy ta faɗa sannan ta bar mata ɗakin

Zaunawa Sunaiha tayi kan gado kamar za tayi kuka, ta ce "kai dan Allah, wannan wane irin masifa ne wai? Ko wane kare da doki sai ya zo ma mutum da zancen soyayya bayan na gaya musu ina da prince ɗina!! Mtsww.. Shi kuma wannan ko daga gidan uban wa ma yake oho"

Tana cikin maganar, wayarta tayi ƙara, jin ringtone ɗin da ta sa wa mahaifinta ne ya sa ba ta ɓata lokacin wajen ɗauka ba

"Hello Daddy"

"Na'am ƴar Daddy.... Kin dawo? "

"Eh, kuma wai Mummy ta ce ina da baƙo, i'm not in the mood wallahi"

"Ayya, menene? "

"Wani ɗan rainin hankali ne ya ɓata mun rai wallahi"

"To ke me ya haɗa ki da irin wannan mutum haka?... Amma dai ki manta da shi kawai, baƙon ba irin wanda zan kora ba ne da sai in sallame shi, kiyi haƙuri ki tafi kinji"

A shagwaɓe ta ce "waye?"

"Al'ameen, ɗan governor"

Tsaki kawai tayi, ya ce "sorry Baby na, ki tafi saboda ni"

Shirun minti ɗaya tayi kafin ta ce "shikenan" ba ta jira shi ba ta kashe wayar......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~
~~~~~~~~~~~~~~

_No one will manufacture a lock without a key.Similarly, God wont give problems without solutions.So defeat your problems with great confidence. Just Do It...._

*PAGE 7-8*

Shiryawa tayi tsaf ta je ta samu ɗan governor a ɗakin baƙi, lokacin da ta isa ma yana kokarin fitowa

Tsayawa yayi yana kallonta, ya ce "ashe kin dawo"

"To da na dawo sai aka yi me? " ta faɗa tana mishi wani kallo

"Kin san minti nawa nayi a nan? "

"To ni ina ruwa, kai ka ji za ka iya fa.... Kai bari in gaya maka, soyayya ce ko! To ba zaka samu ba a wurin Sunaiha, so don't waste ur time(kar ka ɓata lokacin ka) "

"Hmm, Sunaiha ni kike gaya wa haka? To bari ki ji ke ma, ban zo nan saboda ina sanki ba, dama zuwa nayi in jaddada miki bani da lokacin soyayya yanzu, karatu na ne a gaban, ina si inyi achieving goal ɗina, so i'm sorry, ki riƙe soyayyarki ƴan mata" da tattausar murya yayi maganar

"Wow... Ashe ka fi sauran hankali, ka yi kyaun kai, nima ina da prince ɗina, i have nothing to do with you (ba abunda zanyi da kai)... A sauka lafiya" ta faɗa kafin ta ruga shi fitowa daga ɗakin

Yana da sanyin zuciya, shiyasa ko ta kan kalamanta bai bi ba, ya girgiza kai ya fice

Tana shiga parlour tayi arba da Daddynta, ya ce "ya dai Baby?"

Cikin ɓacin rai ta ce "Daddy na sha gaya maka na gaji da waɗannan mutanen da kake turo mun, i told you i have my own prince and i'm waiting for him (na gaya maka ina da prince ɗina, kuma shi nake jira), dan haka ka daina wahalar da kanka" tana gama faɗar haka ta wuce

Ƙarasawa yayi kusa da Mummy dake zaune kan kujera tana kallonsu, ya zauna

"Wato Hajiya sam ban gane inda yarinyar nan ta dosa ba sai yanzu, tana ta cewa prince amma na kasa fahimtar ɗan gidan sarauta ne... Oh God, yi haƙuri Baby na, wallahi Hajiya yanzu na gane, in Allah ya yarda kuwa zanyi wa mai martaba magana, dama muna da kyakkyawar alaƙa da shi, kuma akwai wani yaronshi, Yarima Muhseen, yana yawan ƙorafi akan ya ƙi ya fitar da mata, shikenan sai ya zo ganin Baby, May be ma shi ne prince ɗin na ta.. Ko Hajiya? " ya ƙarasa zancen yana kallon Mummy

Ita kuwa tun da ya fara maganar bata ma ɗaga ido ta kalle shi ba, TV kawai take kalli duk da ba abunda ake yi take saurare ba, maganar Daddy take saurare, yana kai wa ƙarshen maganar shi da tambayar da ya mata, ba tare da ta kalle shi ba ta ce "umm haka ne" sai kawai ta miƙe ta bar mishi parlourn

Shi kuwa bai gano yanayin maganar Mummy ba, hakan ya sa ya zauna yana shawarar yanda zai je fada gobe

Washe gari kamar yanda ya shirya ma zuwa fada, ya tafi suka tattauna da mai martaba, ya ji daɗin yanda ya kawo mishi wannan zancen dan ya daɗe yana so ya ga auren Muhseen, amma kullum cewa yake bai tashi yin aure ba... Ba wani ɓata lokaci mai martaba ya gaya mishi a yau ɗin nan zai turo da Muhseen ya zo su sasanta kansu da Sunaiha, haka Senator ya baro gidan cike da murna dan shi gani yake yayi ma Babynshi abun arziki yau, zai haɗa ta da prince ɗinta

Da yamma Sunaiha na kwance a ɗakinta, mai aikinsu ta shigo da sallama duk da cewar ta san ba amsa mata za tayi ba, amma hakan bai hana ta yi sallamar ba

"Kinyi baƙo, Yarima ne, wai ki zo inji Hajiya"

"Na ji" abunda ta amsa mata da shi kenan, kafin ta fita

Ba ta fi mintuna goma ba ta shirya ta fiti, kai tsaye ɗakin baƙin ta nufa

Yana zaune kan kujera, kai daga ganinshi ka ga jinin sarauta saboda yanda ya wani ɗaure fuska, sai wani bafade ɗaya dake gefenshi a ƙasa

Kallonsu take har ta saku kujera ta zauna, amma Yarima ko ɗaga ido bai yi ya kalle ta ba, ita ma ganin haka ya sa ta kunna wayarta tana chatting, aƙalla sun ɗauki minti goma sha biyar zuwa ashirin a haka, kafin bafaden ya ce "Hajiya, Yarima fa ke yake jira, amma kin zo ko sallama babu bare kuma ya sa ran gaisuwa"

Wani kallonm tayi ma bafaden, ta ce "ni yake jira? To uban me zan mishi? Ko ni na gayyato shi?
"

Da sauri ya ce "hattara dai, ki gyara kalamanki Hajiya, a gaban Yarima kike... "

"To Yariman ubana ne?.... Kai wai ma in tambaye ka, kai ne ka zo gani na ko kuma shi? Ko kuwa shi ɗin kurma ne kai ne bakin shi?"

A fusace ya ce "ke Hajiya, ki san me yake fitowa daga bakinki ko jikinki ya gaya miki, Yarima ba kamar sauran mutanen da kika sani ba ne, dole ki girmama shi, ki gode Allah ma da ya zo ganinki amma..... " ɗaga mishi hannun da Yarima yayi ne ya sa shi yin shiru yana huci

Kallon Yariman tayi kafin ta mayar da kallonta kan bafaden, ta ce "Allah sarki, ashe Yariman na ka yana sonka shiyasa ya dakatar da kai, amma ai da bari zai yi ka kai ƙarshe ni kuma in ɗauke ka da mari wallahi, Sunaiha kake tunanin zaka iya duka? To ba uban da ya isa dan ka ji in gaya maka, Yariman naku ma yayi kaɗan bare kuma kai banza a banza, kai ruwan sama na idan ka ga ya dake ni, to ni na tsaya, sakarai kawai" ta ƙarasa maganar tana jan tsaki

Shi kuwa ganin irin kallon fmda Yarima ke mishi ya sa bai ce komai ba

Cikin isa da izza, Yarima ya ce "Audi je waje ka jira ni" ba musu ya ja ƙafa ya fita

Sai da ya ƙare mata kallo tsaf, sannan ya ce "mace har mace, mace kyakkyawa, ga kyaun sifa, kyaun fata, ga iya ado, ta haɗu dai ta ko wane fanni, duk namijin da ya kalle ta zai ji wani iri a ranshi, amma sai kyaun ya tashi a banza saboda ba kyaun hali, anya kuwa Sunaiha ba kiyi asara ba?! " Numfashi ya ja kafin ya ci gaba
"Kin san a rayuwa mutum yana cin darajar wasu, to ke ma kin ci darajar masu daraja shiyasa har kika ganni a gidanku... Tun kafin zuwa na na san wacece Sunaiha, na kuma san halinki, ba yanda za'a yi in iya son mace kamarki, tabbas nafurta kina da kyau, amma a wurin mutum mai hankali, kyaun fuska ba shi bane kyau sabida ko wane lokaci zai iya ɓacewa, amma kyaun hali shi ne asalin kyau, ina so ki sani, duk waɗanda suke cewa su na sanki, wallahi ba ke suke so ba, kyaunki suke so, idan sukasamu abunda suke nema a wurinki za ki neme su ne ki rasa, wanda duk yake son Sunaiha ba kyaun Sunaiha ba, ƙoƙari yake yi ya ga ya fara gyara halin Sunaiha kafin komai... A shawarce, ki bi duniya a hankali, anyu dubunki waɗanda suka fi ki isa, izza, girman kai, dukiya da matsayi, amma yanzu babu su sai tarihinsu, to ke ma haka ne wata rana sai dai labarin *Ƴar Senator* , ba alfahari ba, amma ko ni da nake jinin sarauta ba na abunda kike yi, ni kaɗai nake yawo na, duk wani abu da zai nuna matsayi na nisantarshi nake yi, i need freedom, ban son takurar sarautar nan, wannan bafaden ma, mai martaba ya ce lallai sai ya biyo ni, amma ni kaɗai ke yawo na, ni da nake na miji ma kenan, sai ke mace?! You better change your life and character(ki canza rayuwarki da ɗabi'unki), na bar ki lafiya"

Yana ƙoƙarin wucewa ta ce "Allahu akbar, sannu sheikh, ashe a ɗiyan mai martaba akwai Malam mai wa'azi..... Ayya, to ka gaida mai martaba ka ji, mtsww" ta ja wani tsakin sannan ta zauna ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya

"Hmm, i pity you (na tausaya miki)" abunda kawai ya faɗa kenan ya fice

Sai da ta gama zamanta kafin ta koma parlour, yau Daddynta yana gida, su na fira da Mummy ta shigo

Farincik fal a fuskarshi, ya ce "irin wannan daɗewa haka Baby, da alama dai yau anyi nasarar samun prince ɗin nan, ai da tun farko kika mun bayani gidan sarauta yake da tuni an wuce wurin... "

Katse shi tayi da "wane wuri za'a wuce kuma Daddy? Ni sam wannan ba prince ɗina bane, ya

wani cika mun kunne wai shi nasiha yake mun, mtwss... Daddy prince ɗina ba jinin sarauta ba ne, kar ma ka sake komawa masarautar kowa"

Shiru yayi kafin ya sauke ajiyar zuciya ya ce "shikenan, je ki huta"

Baki a buɗe Mummy ke kallonshi tana kallon Sunaiha har ta wuce, ta ce "Alhaji!!! Ta je ta huta fa ka ce"

"Eh mana, to me zata miki? Kina ji fa ta fe ya cika mata kunne"

"Ya cika mata kunne da nasihar da ya mata ba, ai ya kyauta mata dan shi ya mata abunda mahaifinta ya kasa yi mata"

"Kamar ya? Me kike nufi? Duniyan nan akwai wanda ya isa yayi wa Baby abunda ni na kasa yi mata ne? Ko akwai wanda ya fi ni sonta ne?"

"So? So fa ka ce, haka ake so? To wallahi wannan ba soyayya ba ce, wannan lalata mata rayuwa ne kake yi"

"Gatan da nake nuna mata shi ne lalata rayuwa? Wai meyasa ba kya ƙaunar yarinyar nan ne? Wallahi da ba dan ke kika haife ta ba da sai in ce kin tsane ta"

"Yanzu ma ai ka faɗa, kana tunanin duniyan nan akwai wanda ya kai ni sonta ne? Ni na haife ta, ni ce mahaifiyarta, ba ka yi mata rabin son da nake mata, wannan sagarta ta ɗin da kake yi ba shi ba ne so, ka ɗora ta ne a kan tafarkin da zata lalata future life ɗinta, mace ce, dole gidan wani za ta je, ba ko wane namiji ba ne zai ɗauki wannan halin na ta ba, ina tausaya mata amma baka ganewa sai ranar da ta zo tana kuka da kai sannan zaka fahimci me nake nufi... In Allah ya yarda, ba zan sake magana akan waɗannan mazajen da kaje kawo mata ba, ka ci gaba da kawo su ita kuma ta ci gaba da wulaƙanta su..." ta tashi a fusace ta bar mishi parlourn zuciyarta har zafi take yi dan abun na su ya fara kai ta ƙarshe dan dai ba yanda za tayi ne

"Lallai ma matar nan.... Shikenan" ya faɗa shi ma rai a ɓace

Yana nan zaune, wayarshi tayi ƙara, kamar kar ya ɗaga, sai kuma dai ya ɗauka dan ba zai iya ƙyale mai kiran ba

"Da girman kujerarka mai girma Senator" aka faɗa daga ɗayan ɓaangaren cike da fara'a

Yana ƙoƙarin kawar da ɓacin ran na shi ya ce "Alhaji Usman, ba ka rabo da nishaɗi ko! "

Murmushi yayi irin na manyan mutane, ya ce "rayuwa sai da nishaɗi ai, idan ba haka ba kuwa damuwar mutum ma sai ya sa mishi wani ciwon"

"Haba dai, Alhaji Usman ai kai kam ba wani abu da yake damunka da har zai sa maka ciwo, damuwa sai mu"

"A'a.. Ina so ma in tambaye ka ai ko lafiya, dan muryarka da alamun damuwa"

"Hmm bari kawai Alhaji Usman, al'amarin Baby ne, kaan ina so in ga tayi aure amma har yanzu ta kasa tsayar da mijin da take so, wai akwai prince ɗinta da take jira"

"Zancen banza kenan, wai ko ina akwai irin waɗannan yaran?"

"Wallahi kuwa, akwai wata da ka sani irin ta ne? "

"Wata ko dai wani? Hmm, Alhaji Abubakar, yanzu ka ga ana dab da kuran sallar magrib, idan ba damuwa idan aka yi isha'i ko za ku iya haɗuwa?"

"To shikenan ba komai, sai mu haɗu wurin da muka saba haɗuwa kawai"

"Yawwa to nagode" daga haka suka ajiye wayar

Alhaji Usman ya ce "wai akwai prince ɗin da take jira.... Lallai ma"

Umma da isowarta kenan ta ce "lafiya dai? Kai da wa kuma?"

Kallonta yayi cikin kulawa ya ce "Senator Abubakar ne muka gama waya da shi, ina tunanin lokaci yayi da zan ɗauki matakin da na gaya miki"

"Wane irin mataki kuma?"

"Zan fita bayan isha'i, idan na dawo za ki ji"

"To Allah ya sa in ji alkhairi.... Ka tashi ka je kayi alwala to kafin a kira sallah"

"To Hajiya ta" ya faɗa dai-dai lokacin da ya miƙe yana mata murmushi, ita ma murmushin ta mayar mishi kafin ta raka shi ɗakin

Kamar yanda suka yi magana da Senator cewar su haɗu bayan isha'i, hakan kuwa ya faru, su na zaune da drinks a gabansu duk da cewar ba wanda ya buɗe

Senator ya ce "muna magana ɗazu, na ji kamar akwai magan a bakinka"

"Haka ne, amma ya maganar Sunaiha da na ji kana yi? Gaya mun menene matsalar"

"Hmm... Akwai yaron da Baby take yawan mafarkinshi wanda har ta kamu da tsananin ƙaunarsa kuma tayi alwashin in har ba shi ba to ba za tayi aure ba, sai dai matsalar ba ta ma san a garin da yake ba bare kuma gidansu, haan ya sa nayi ta kawo mata samari kala-kala amma duk ta kore su, ta kori samari kusan ashirin da biyu zuwa da uku... "

Da mamaki Alhaji Usman ya katse "ashirin? Kana me? Kuma ka biye mata?"

"Eh mana, farincikin ta nake so"

"Lallai, ashe wannan ma nashi mai sauƙi ne"

"Wa kenan?" Senator ya tambaya

"Sadeeq mana, ya ƙi ya fitar da mata ga shi har an saka ranar auren Safwan nan da sati ɗaya ya rage, kullum sai ce mun yake zai fitar da mata amma har yanzu, to dama na gayawa mahaifiyarshi duk ranar da na gaji da halinshi ni da kai na zan nemo mishi mata kuma dolenshi ya aure ta"

"Yanzu dai idan na fahimce ka, abunda ke raina ne kai ma ka zo da shi"

"Haka ne, ina so ya zo ya ganta, in har ta amince da shi ai shikenan"

Senator ya ce "ina fatan za ta amince, ko dan mu ƙarfafa zumuncin nan na mu da yake neman rugujewa, tunda sai mu fi wata ma bamu gaisa ba ko a waya, amma ka ga idan muka zama surukai ai shikenan"

Dariya Alhaji Usman yayi ya ce "to ai kai ne da matsalar, kullum ba ka da lokaci, amma muna fatan amincewarta"

"Amincewarsu dai"

"Kai dai ka bar shi kawai a yanda na ce ɗin..... Bari in tafi, ka ga ƙarfe tara saura ƴan mintuna, na bar Hajiya ta ita kaɗai"

"Wai kai har yanzu wannan soyayyar ta ku tana nan, kun girma fa" Senator ya faɗa yana dariya

"Haba ai soyayyar gaskiya ba ta tsufa, kai dai sai munyi waya goben, sai inji yaushe zai zo"

"To shikenan, Allah ya tabbatar mana da alkhairi, mu kwana lafiya"

Daga haka ko wanensu ya wuce gida.......

Masu magana har yanzu ba su san waye SADEEQ ba, da masu cewa sun ƙagu su san labarinshi, to duk kuyi hkr, in sha Allah a next page da labarin *GIDAN KYAWAWA* za ku fara, anan za ku ji ko waye *ABUBAKAR SADEEQ USMAN SARAKI*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_Never walk away from sincere friends...When u see some faults, be patient and realize that nobody is perfect..It’s affection that matters, not perfection…_

*PAGE 9-10*
~~~~~~~~~~~~~~

*ALHAJI AL-AMEEN SARAKI*, tsohon custom ne, wanda ya tara arziki ba laifi, yana da mata ɗaya da yara uku maza, shi ɗin cikakken bahaushe ne kuma kyakkyawan gaske, matarsa kuma bafulatanar ruga ce, asalin fulani kenan son kowa ƙin wanda ya rasa

Alhaji Al-ameen Saraki, yayi iya bakin ƙoƙarinshi wurin tarbiyar yaranshi, aikinshi bai taɓa ɗauke mishi hankali ba daga iyalinshi, ya tabbatar da yaranshi sun samu ilimi na addini da na boko dai-dai gwargwado

Bayan yayi ritaya, ya ɗan taɓa harkar siyasa kafin daga baya kuma ya ajiye ta, sai dai har yanzu wasu manyan ƴan siyasa suna zuwa wurinshi domin neman shawara

Bayan kammala karatun yaranshi, yayi ƙoƙari wurin ganin ko wanensu ya samu irin aikin da yake so, tun suna yi a ƙarƙashin wasu, yanzu har ta kai ko wanensu yana da waɗanda suke aiki a ƙarƙashinsa, ganin arziki ya zauna musu yasa suka fara batun aure, babban ɗanshi shi ya fara aure, kafin sauran biyun suka yi a rana ɗaya

Arziki na ƙara yawaita ma ko wanensu, hakan ya sa suka yanke shawarar haɗa kuɗi, suka gina wani katafaren gida mai parts daban-daban wanda duk wanda yake cikin garin Gombe, ya yarda cewar in dai za'a ƙirga manyan gida a garin, to dole wannan gidan zai zo a na biyu ko na uku, sun yi haka ne saboda su rayu ciki su da iyalansu, saboda su ƙara danƙon zumunci tsakaninsu, da tsakanin matansu da kuma yaransu, sun so Alhaji Al-ameen da mahaifiyarsu Hajiya Amina zu zauna tare da su, amma ba su yarda da hakan ba, hakan yasa suka yi musu na su gidan daban a nan layinsu, sai dai a ɗan kwai tazara a tsakani

Babban ɗanshi, sunanshi Alhaji Muhammad Al-ameen Saraki(Alhaji), sunan matarshi Hajiya Hajara(Hajiya), Alhaji aikinshi sayar da motoci, yana ɗauko motoci daga ƙasashen waje yana shigowa da su Nigeria, yana da kyakkyawar alaƙa tsakaninshi da manyan kampanonin da ke ƙera motoci a ƙasar waje. Sai na biyu, Alhaji Usman Al-ameen Saraki(Abba), matarshi Hajiya Aziza(Umma) wacce ta kasance ƙanwar Hajiya Hajara, uwa ɗaya uba ɗaya, Abba hamshaƙin ɗan kasuwa ne, yana da kampanoni guda huɗu manya a jahar Gombe, kuma yana branches a wasu jahohin. Sai na ukun Alhaji Aliyu Al-ameen Saraki(kawu ƙarami) matarshi Hajiya Basira(Momi), babban likita ne shi kuma, yana da na shi asibitin har guda biyu, haka ma yana da manyan Chemist za su kai guda biyar.... Dukiya kam Alhamdilillah

Gaba ɗaya yaran gidan su goma sha biyu ne, Sadiya ita ce babba, sai Sameera, Saudat, Safwan, Sadeeq, Sameer, Sauban, Salma, Sultana, Sajida, Safna sai auta Sajeed

Alhaji da Hajiya yaransu biyar, Sadiya, Sameera, Safwan, Sauban da Sajida. Abba da Umma yaransu uku, Saudat, Sadeeq da Sultana. Kawu ƙarami da Momi kuma yaransu huɗu, Sameer, Salma, Safna da Sajeed

Yaran sun tashi tare, ba tare da nuna banbanci tsakaninsu ba, sun shaƙu da junansu sosai kamar yanda iyayensu ke so, sannan su na yawan kai ma Grandpa da Grandma ziyara, yaran

sun gado kyau ta ko ina, ko wanensu na ji da kyau kamar yayi magana, hakan ya sa ake musu laƙabi da _Gidan Kyawawa_ , ba sa da girman kai ko wulaƙanta mutum

Mutum ɗaya ne ya fita daban a gidan, shi ne *Sadeeq Tiger* , miskilallen mutum ne, ba wai girman kai ba ne ke damunshi, shi dai kawai ba ya son hayaniya ko kuma shiga sabgar mutane, ga saurin fushi da shegen zuciya, hakan ya sa ƙannenshi suke shakkarsa, in dai bai shi ya so yin abu ba to ba zai yi ba. Kamar yanda bai da abokin fira a gidan sama da Safwan da suke komai tare kasancewar sati biyu Safwan ya ba shi, to sai kuma Anty Sadiya da jininsu ya haɗu sosai, ita kuma duk wani sirrinshi ko damuwarshi ta sani, ita da Umma(wacce shi kaɗai yake kiranta da Maa), su kaɗai ke iya sa shi yayi abunda bai yi niya ba saboda bai son ɓata musu rai ko kaɗan

Sadeeq ƙwararren likita ne shi ma, a asibitin Kawu ƙarami yake aiki, wanda kusan ragamar asibitocin a hannunshi su ke, Dr.Abubakar Sadeeq Usman Saraki. Safwan kuma babban lawyer ne mai zaman kansa, ba ya karɓar case ɗin manyan mutane sai dai talakawa da kuma waɗanda aka zalunta, shiyasa mutane da dama sun san shi, Barr. Safwan Muhammad Saraki. Sameer da Sauban su na final year a university, Salma da Sultana yanzu suka shiga university, Sajida tana SS3, Safna kuma SS1, sai auta Sajeed pry.5

Anty Sadiya da Anty Sameera da Anty Saudat duk sunyi aure, Anty Sadiya yaranta biyu duka maza, Armaan da Aryaan, Anty Sameera kuma ƴarta ɗaya da ta ci sunan Hajiya, wato Hajara, suna kiranta da Ihsan, sai Aunty Saudat da ba ta daɗe da aure ba, har yanzu ba ta haihu ba

Yanzu kuma suna shirin auren Safwan, saura sati ɗaya a fara biki, shirye-shirye suke ta yi kamar ba gobe, kowa ya so a haɗa auren Safwan ɗin da Sadeeq amma oga Tiger ya ce akwai wacce yake jira, hatta Grandpa ya kira shi amma ya shaida mishi shi fa aure ba yanzu ba yana da wacce yake so amma ba yanzu zai aure ta ba, Grandpa bai son takurawa Sadeeq hakan ya sa bai tsawaita bincike ba, Abba kuwa ranshi ɓaci yake yi idan yana cewa yana jiran wata, hakan ya sa ya ce kar wanda ya sake mishi maganar auren, ayi na Safwan ɗin kawai

Shi kuwa Sadeeq da gaske yake yi yana da wacce ya riga ya mutu a kan sonta, jinta yake har cikin ranshi, kullum zuciyarshi bugawa take yi akan ta, ya tsani ya ji wani ya furta wata kalma mara daɗi akan ta, ba zai iya jurewa ba, son ta har cikin jininshi yake ji yana mishi yawo, ba ranar da baya tunaninta haka ma ba daren da ba ya mafarkinta... Amma har yanzu ya ƙi gaya wa kowa wacece kuma ya ƙi gaya wa kowa dalilinshi na ƙin bayyana ta, Anty Sadiya kawai ta san ta, amma kuma ba wanda ya san da hakan

*TAKAITACCEN BAYANI KENAN A KAN GIDAN KYAWAWA*

_CI GABA_

Kamar yanda Abba ya gaya wa Umma cewar idan ya dawo zai gaya mata, hakan ya hana ta bacci dan tana so ta ji hukuncin me zai yanke? Wane laifi tayi? Dan ita sam bata ma kawo

zancen Sadeeq ba

Tana zaune tana nazari kuwa, sai ga shi ya shigo ɗakin da sallama sai murmushi yake mata, ita ma cike da fara'a ta miƙe tana mishi sannu da zuwa, ta karɓi hularsa da yake miƙa mata, ta kai cikin jerin hulunoninsa dake cikin wardrobe

Sai da ya shiga toilet ya watsa ruwa, ya fito sanye da jallabiya, dai-dai lokacin da ta ajiye mishi coffee, ɗauka yayi yana mata murmushi ya ce "na gode Hajiya ta, Allah yayi albarka"

"Ameen mijina na kai na" ta faɗa lokacin da take zama kusa da shi

Sannan ta ce "ɗazu ka ce idan ka dawo za ka gaya mun wani abu"

Sai da ya gama shan coffee ɗin kafin ya ce "magana ce akan Sadeeq, na samo mishi matar da zai aura in Allah ya yarda"

Buɗe ido tayi ta ce "ka nemo mishi mata kuma? "

"Eh, ai na gaya miki duk ranar dana gaji da al'amarin Sadeeq zan ɗauki mataki, to yau an kai ƙarshe"

"Amma Alhaji bai kamata kayi hakan ba, ya ce fa yana da wacce yake so"

"Kin taɓa ganinta? Ko ya gaya miki wace ce? Wataƙila ma aljana ce ta aure shi shiyasa yake ta wani cewa yana jiran wata"

"Ba wata aljana, da gaske yana da wata, dan ya rantse mun akan hakan kuma na yarda dan Sadeeq bai taɓa rantsuwa akan ƙarya ba, kai maka sani"

Murmushi yayi ya ce "uwa dai uwa ce, to na ji, kin yarda, amma kin san tunda har na yanke wannan hukunci ba zan canza ba ko, zai auri wannan ɗin da na zaɓa mishi matuƙar ta amince da shi, in ya so daga baya idan ya gama jiran waccen ɗin sai ya aure ta ita ma"

"Amma Alhaji.... "

Katse ta yayi ta hanyar ɗaga mata hannu ya ce "ya isa Hajiya ta, kin san ba na son yawan jayayya da ke dan ba zan so in ɓata miki rai ba, na gama wannan maganar, sai da safe" daga haka ya kwanta ya kyale ta

Ita kuwa ta daɗe zaune tana tunanin yanda Sadeeq zai ɗauki wannan maganar ta Abbansa, dan ta san sai anyi da gaske, kafin daga bisani ita ma ta shiga ta watsa ruwa ta zo ta kwanta

Daga ɓangaren Senator kuwa bayan ya koma gida, ganin har yanzu Mummy a sama take, ba ta

gama fushin ba, shiyasa bai ce mata komai ba yayi shirin kwanciya

Washe gari da safe kuwa ya gama shirin fita, ya shiga ɗakin Sunaiha amma ba ta ciki, haka ya sa ya wuce garden, zaune ya same ta tana shan tea da snacks, zama yayi kan ɗayan kujeran

Ya ce "Baby na"

"Umm, Good Morning Daddy"

"Morning Baby, how was your night? "

"Good and fine"

"Haka nake so.... Yawwa Baby, anjima za kiyi wani baƙon"

Wani kallo ta mishi ta ce "baƙo kuma?? Wai Daddy meyasa ba za ka gane ba ne, duk fa waɗannan da kake kawo wa ba prince ɗina a cikinsu, kuma wallahi ba zan taɓa sauya matsayin prince a rai na ba, ka ƙyale ni haka nan in huta mana, wata rana prince ɗina da kanshi zai zo nema na"

"Ayya Baby na, kiyi haƙuri kin ji, wannan yaron wani tsohon abokina ne, ba zan iya ce mishi a'a ba, ni kai na zan so haɗa zuri'a da shi, dan Allah kiyi haƙuri"

"No Daddy, ba zan ma zauna gidan nan ba yau, kar ma ya zo, na gaji da ganinsu haka nan, i'm tired"

"Hmm, Baby.. Kin ga na riga da na amsa mishi akan yaron ya zo yau, idan har kuma na ce kar ya zo kin kunyata ni fa kenan, ko kina so in kunyata a idon duniya? "

Kamar za ta mishi kuka ta girgiza kai, ya ce "to dan Allah ki bari ya zo, idan ma bai miki ba, nayi miki alƙawarin ba zan sake kawo miki kowa ba sai ranar da prince ɗinki ya zo"

Kallonshi tayi ta ce "you promise?"

"Yeah, i promise"

Numfashi ta sauke ta ce "ya zo ɗin, shi ma sai ya shiga layin sauran, dan ba zai mun ba"

Murmushi yayi ya ce "to shikenan Baby na, ƙarfe nawa?"

Sai da ta ɗan yi nazari sannan ta ce "12-1pm"

"Yawwa Baby na, thank you... Sai na dawo" ya miƙe ya barta sai wani turo baki take tayi

Shi kuma bai bar gidan ba sai da ya tabbatar da ya kira Abba ya gaya mishi ko ƙarfe nawa Sadeeq ɗin zai zo

Cike da murna Abba ya kashe wayar, sannan ya kira layin Sadeeq

Da sallama Sadeeq ya fara, Abba ya amsa kafin ya ce "ka zo bedroom ka same ni, kayi sauri kuma dan zan fita ne"

"Ok" abunda kawai ya amsa da shi kenan ya kashe wayar, shiru yayi yana tunani dan muryar Abba ta tabbatar mishi da dalilin kiran nan da ya mishi serious issue ne, shafa fuskarshi yayi sannan ya tashi ya bar ɗakin zuwa part ɗin su Abba.........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

_Today’s new paper is tomorrow’s waste paper. Life is a test paper friendship is the best paper. Don’t waste it like a tissue paper...._

*PAGE 11-12*

Da sallama Tiger ya shiga parlourn su Abba, yana zaune yana jiranshi, a hankali ya taka zuwa cikin parlourn, ya zauna ƙasa kafin ya ce "Abba ina kwana"

"Ka tashi lafiya? "

"Lafiya ƙalau"

Abba ya kira sunanshi "Abbakar"

"Na'am Abba"

"Menene matsayi na a wurinka?"

Sai da ya ɗan yi shiru yana mamakin tambayar kafin ya amsa da "Abba kai mahaifina ne mana"

"Ina da iko a kan ka?"

"Abba kai mahaifina ne fa, ka fi kowa iko da ni,  zan iya yi maka komai da kake so matuƙar bai saɓawa Allah ba, za ka iya yin komai a kaina... Wannan wace tambaya ce haka kake yi kuma?"

"To Alhamdulillahi tun da ka faɗi hakan da bakinka.... Sadeeq" ya kira shi a karo na biyu

"Na'am"

"A matsayi na na mahaifinka, na yanke wani hukunci a kanka, na fitar maka da matar da za ka aura"

Nan take Tiger ya ji gabanshi yayi wani mummunan faɗuwa, ya ce "Mata fa Abba"

"Eh mata fa Sadeeq, na gaji da ganinka a haka.. Sadeeq duk girman mutum ko arzikinsa, kimarsa da darajarsa ba za su taɓa cika ba sai yana da aure, na jira in ga iyakacin hankalinka, amma kullum zance ɗaya kake nanatawa, to na gaji, dan haka ni na fitar maka da mata.... "

Ɗaga kai Tiger yayi zai yi magana amma Abba ya ɗaga mishi hannu, "bari in gama magana, za ka je ka ga yarinyar, in har ta amince da kai, dole za ka aure ta ko kana so ko baka so"

"Abba dan Allah kayi haƙuri amma ina da wacce nake so fa"

"Eh ba damuwa ai, ka auri wannan ɗin, duk lokacin da ka gama jiran waccen ɗin sai ka aure ta ita ma"

"Abba amma.... "

Katse shi Abba yayi, ya ce "no more excuses Sadeeq, this is my final say... In har ka ga ba ka aure ta ba, to ita ta ce ba ta sonka, zan turo maka da address ɗin gidan, daga 12 zuwa 1pm za ka tafi.... Sai na dawo" yana gama faɗar haka ya miƙe ya wuce

Gaba ɗaya Sadeeq ya kasa gane me yake ji a jikinshi, duk da ACn da ke kunne a ɗakin amma zufa yake yi, idanunshi a rufe yana sauraren bugun zuciyarshi, ya ji an taɓa shi

Buɗe jajayen idanunshi yayi ya sauke akan Umma, sannan ya gyara zama, ita ma ta zauna tana shafa kan shi

Ta ce "Sadeeq kayi haƙuri da hukuncin Abbanka.... "

Bai jira ta kai ƙarshen maganarta ba, ya katse ta "haƙuri? Maa haƙuri fa kika ce, Maa kin san me Abba yake shirin yi kuwa? Aure fa ya ce zanyi, zan auri wata daban ba.... " sai ya kasa ƙarasa maganar

Ta ce "na sani Sadeeq, amma tun farko laifinka ne, da ace ka gaya mishi ko wace ce da hakan bai faru ba, amma ka ƙi ka gaya mana wace ce kake so ko kuma meyasa ka ƙi gabatar mana da ita, shi kuma har ya gaji ya fitar maka da mata, sai dai ban ga abun tashin hankalin ba, kai fa namiji ne Sadeeq, kana da damar da zaka auri mata huɗu, kuma kana da arzikin riƙe su, kayi yanda ya ce kawai, ka auri wannan daga baya kuma sai ka auri wannan ɗin da kake jira"

"Maa ba za ki gane ba wallahi, ba fa arziki bane kawai ke ba mutum ikon yin aure ba, adalci shi ne babban abunda ake dubawa, kuma Maa wallahi ba zan iya yin adalci ba, ita kaɗai nake so, babu wata mace da nake jin zan iya so kwatankwacin yanda nake sonta, wallahi ita kaɗai nake so, ita kaɗai nake ji a raina, infact Maa, bani da ra'ayin mata biyu ko kaɗan, gaba ɗaya tsarin rayuwa ta na mace ɗaya ne kuma ita kaɗai... Maa dan Allah kiyi mishi bayani, i so much love her, she's part of me Maa, dan Allah" ya ƙarasa maganar kamar zai yi kuka, idanunshi sun yi ja

Sosai Umma ta tausaya mishi, ba ta taɓa tsammanin Sadeeq yana da lokacin kallon wata mace ba ma, amma yau shi ne ya cire duk wani miskilancinsa ya gaya mata irin son da yake yi ma wata, lallai ko wace ce wannan yarinyar ta ciri tuta a zuciyar Sadeeq, yau ta ƙara yarda da cewa yana matuƙar sonta fiye da tunaninta

Shiru tayi kawai tana kallonshi, kafin ta ce "Kayi haƙuri Sadeeq.... Ina zuwa"

Tashi tayi ta shige bedroom, tana wucewa shi ma ya miƙe ya bar parlourn yana jin kanshi na sara mishi

Dai-dai lokacin da Umma ta fito daga ɗaki, shi kuma Safwan ya shigo

"A'a ango manya, har ka tashi?"

Murmushi yayi ya ce "eh wallahi Umma, Sadeeq ne ya tashe ni tunda safe, wai zamu fita"

Kallon ɗakin Umma tayi ta ce "to ina yake ma? "

"Ina parlourn mu fa ya fito daga ɗakinshi ya ce in jira shi Abba na nemanshi, to na ga Abba ya fita shi ne na zo inji me ya tsaya yi"

"To ai ni yanzu na bar shi na shiga ɗaki, fitowa na kenan ka ga har ya fita"

"Kuma ba mu haɗu a hanya ba....." sai kuma yayi shiru kafin ya ce "bari in sake duba shi"

Ya juya zai fita Umma ta kira shi, "Safwan zo ka ji" dawowa yayi ya zauna ganin ita ma ta zauna

Ta ce "Safwan ka san kiran me Abbanku ya mishi?"

"A'a"

"Mata ya zaɓa mishi wacce sai aura"

Da mamaki Safwan ya ce "mata kuma Umma?"

"Eh" bayani ta mishi yanda Abba ya yanke wannan hukuncin, da kuma halin da ta bar Sadeeq kafin ta shiga ɗaki

Safwan ya ce "dole ma zai yi haka Umma, yana fa da wacce yake so"

"Na sani Safwan, kuma wallahi na yarda yana sonta"

"Umma gaskiya wannan karon Abba bai so a zauna lafiya ba, Sadeeq ɗin ne zai zaɓarwa mata! Ai ko ba wacce yake so bai kamata a ce an yi mishi zaɓen mata ba... Tiger fa!"

"Safwan, Sadeeq ɗin ma fa yana da laifi, idan na ga Abbanku bai kyauta ba, sai kuma in ga ai Sadeeq ya fi shi laifi"

"Hmm Umma kenan, yanzu dai bari in je in ganshi"

"To shikenan" cewar Umma

Safwan ya tashi ya fita babban parlourn gidan, Sadeeq ba ya nan, sai ya wuce part ɗin su, Sauban ya gani parlourn su a zaune, ya tambaye shi ko Tiger ya shigo nan

Sauban ya ce "a'a, ban gan shi ba tun da na fito, ko motsin shi ma ban ji ba"

Safwan ya sake fita, sai da ya zagaye gidan nan tsab, amma ba alamar Tiger, sai ya dawo part ɗin ƴan matan, duk da ya san Sadeeq ba zuwa yake yi ba, amma sai da ya tafi

Salma da Sajida ne a parlourn suna kallo

"Salma kin ga Tiger? "

"Ya Safwan ai tun da na tashi ban fita ba"

"Nemanshi nake yi tun ɗazu wallahi"

Ta ce "amma kai ma Ya Safwan ka so ka wahalar da kanka, me ya kai ka zagayen gidan nan nemanshi? Ba gq waya a hannunka ba, ka kira shi kawai"

"To ai ina ta kiranshi amma switch off"

Kafin Salma tayi magana, sai ga Sultana ta shigo, gaida Safwan tayi sannan ta zauna

Safwan ya ce "Sultana ke da kika fito daga waje, kin ga Tiger?"

"Ba ya gidan nan ai, tun ɗazu na ga ya ɗauki motanshi ya fita"

Safwan ya dafa kai, ya ce "oh Allah, Allah ya sassauta mishi wannan zuciyar"

Sajida ta ce "Ya safwan menene?"

Sultana ta ce "ke kam kin shiga uku da gulma"

Sajida ta ce "na gaya muku ƴar jarida nake so in zama, to shiyasa nake ɗaukar rahoto tun daga gida... Kuma ai idan kuma son jin labari ni kuke fara nema, kenan gulmar tana muku amfani" ta ƙarasa maganar tana murguɗa mata baki, kafin ta kalli Safwan ta ce "Ya Safwan gaya mun mana, me aka mishi?"

"A'a, ki bari idan ya dawo sai ki je ki same shi, ki tambaye shi me aka yi mishi har ya fita, sannan ina ya je bayan ya fita, sannan kuma me yayi da ya fita, kin ga za ki fi ɗaukan rahoton yanda ya kamata"

Zaro ido tayi ta ce "wa!!? Ni? Rufa mun asiri, ai yi wa Oga Tiger waɗannan tambayoyin sai kai"

Dariya maganar ta ba su gaba ɗayansu, Salma ta ce "da kin kai ƙarshen ɗaukar rahoto yarinya"

Safwan dai fita yayi yana ƙara kiran layin Sadeeq, ya bar su suna dariya

Sadeeq kuwa tun fitarshi daga gidanvyake kiran wayan Anty Sadiya amma a kashe, hakan ya sa ya kashe na shi wayan, ya wuce gidanta

Horn yayi a bakin gate ɗin gidanta, mai gadi ya buɗe ya wuce yayi parking, ƙofar parlourn ya nufa ya danna bell

Wani yaro ne ɗan kimanin shekara biyar ya buɗe ƙofar, da murna yana tsalle ya ce "yeeee!!! Uncle Tiger oyoyo"

Murmushi kawai yayi ya ɗaga shi suka ƙarasa cikivyqna tambayanshi ina Amminsu

Ya ce "tana kitchen"

"Aryaan fa?"

"Yana bacci... Bari in je in kira Ammi"

Sauke shi yayi da gudu ya wuce kitchen ya gaya mata Uncle Tiger ya zo

Fitowa tayi tana murmushi ta ce "Oga Tiger"

Murmushi yayi ya ce "ina kwana Antyna"

"Lafiya ƙalau" ta amsa dai-dai lokacin da take zama, sannan ta ce "Oga Tiger ya aka yi?"

"Antyna akwai matsala, na kira wayanki a kashe"

"Subhanallahi, wayan ɗazu Armaan ya zuba mun tea a kanta...  wace irin matsala kuma Sadeeq?"

"Anty Sadiya Abba ne ke shirin aura mun wata daban"

Zaro ido tayi ta ce "auren wata kamar ya?"

"Wai ya zaɓa mun wata ƴar abokinshi, yau ɗin nan yake so in je in ganta... Anty Sadiya ke kin san wurin da zuciya ta take, ban san ya za'a yi in auri wata ba, Anty Sadiya ba ƙaramin cutuwa

zan yi ba idan aka yi auren nan, dan Allah ki san abun yi"

Shiru tayi tana kallonshi cike da tausayi, dan ta san irin son da yake wa budurwarshi

Ta ce "Sadeeq tun da har an kai haka, kawai ka gaya mishi ko wacece"

"Anty Sadiya kin san dalilin da yasa ba zan iya gaya ma kowa ba yanzu, just find a way out"

"Hmm.. To wace yarinya ce? "

"Wai ƴar abokinshi ce, zai turo mun da address ɗin ya ce"

"Bai turo bane har yanzu? "

"Waya na a kashe yake ai, ban sani ba"

"To yanzu ka kunna wayan sai ka gani, ka je gidan, sai ka gaya ma yarinyar kana da wacce kake so, ba ka sonta kuma ba zaka aure ta ba, duk macen da ta san kanta ba za ra yarda ta auri mutumin da ya ce baya sonta ba, ka ga shikenan kun rabu lafiya, ka je kawai"

Shiru yayi dan bai ji wannan shawarar ta ratsa shi ba, sai kuma ya ce "to shikenan, na gode... Bye" bai jira komai ba ya miƙe ya bar gidan ha tare ma da ya san wurin da za shi ba, dan bai da niyan komawa gida bare har ya je wurin waccan yarinyar, haka ma bai kunna wayarshi ba

Daga ɓangaren Sunaiha kuwa, ƙarfe 12:30pm, tayi wanka ta saka riga da wandon jeans, sannan ta ɗauko after-dress ta saka, tayi rolling kanta da gyalenshi

Zama tayi kan kujerar mirror tana kallon fuskarta, haka kawai ta tsinci kanta da shafa hoda, da kwalli har da su pink lipstick, ba ƙaramin kyau tayi ba, ko dan bata saba da yin kwalliyar ba ne shiyasa!?

Chatting ta hau yi, har ƙarfe ɗaya ta wuce, sai a lokacin ta ankara, haƙura tayi zuwa ƙarfe biyu amma ba ta ji labarin zuwan kowa ba, hakan ya sa ta tashi ta ɗauki mukullin motarta kasancewar tana fashin sallah sai bata tsaya yin sallar ba

Mummy na harabar gidan tana magana da wani ma'aikacin gida, ta ga zata wuce, ta ce "Sunaiha ina za ki je? Ba baƙo za kiyi ba? "

"Mummy ƙarfe biyu fa yanzu, ba zuwa zai yi ba kuma ni ina da wurin zuwa, in ma har ya zo a gaya mishi ya jira ni ko ya dawo gobe" ba ta jira jin me Mummy za ta ce ta sa kai ta wuce, t j motarta ta bar gidan

Wani wurin shan iska ta tafi, ta ja ɗaya daga cikin kujerun da aka zagaye da table ta zauna,

ƙaton madubinta na 'no respect' ta cire ta ajiye kan table, kafin tayi ordering ɗin cold drink, wayarta take dannawa tana sipping ɗin juice ɗin a hankali

Wani kyakkyawan saurayi ne ya zo da ja wata kujerar dake kusa da ita ya zauna, yqna kallonta kafin ya ce "Assalamu alaikum"

Ko ɗagakai bata yi ta kalle shi ba, bare ya san ta ganshi, ya sake cewa "ƴan mata excuse me"

Nan ma bata kalle shi ba, numfashi ya ja ya ce "ki ja ajinki yanda kike so, you deserve it ai.. Amma dan Allah ki tausaya mun ki saurare ni, tun shigowarki nan nake kallonki, kin masifar burge ni wallahi, shiyasa har na zo gare ki, kin ji Cutie pie"

Sai a lokacin ta ɗaga ido ta zahga mishi wani harara, murmushi yayi ya ce "alhamdulillahi, na samu daibkin kalle ni ai, saura ki mun magana, ki gaya mun sunanki.... Oh sorry, ban gaya miki suna na ba ko, i'm Najeeb Hameed Namadina"

Ganin surutun na shi gaba yake yi ya sa ta ce "malam ka tashi ba ni wuri, ban so nan dan in saurare ka ba" sai kawai ta ci gaba da danna wayarta

Fizge wayar yayi ya ce "i need ur time dan Allah, na san ba saboda ni kika zo ba, amma atleast ki ji me na zo da shi"

Mudubinta ta ɗauka ta mayar kan fuskarta, ta naɗe hannu kawai tana kallon wani gefe, murmushi ya sake yi ya ce "komai kika yi burge ni yake yi wallahi... Yanzu dai tunda kina ji na, ki gaya mun sunanki dan Allah"

"Suna na ba zai maka amfani ba, saboda ba wani abu da zanyi da kai, ina da wanda nake so, kuma ya fi ka komai, dan haka ka tashi ka wuce"

"Hmm.. Ai oo waye wannan ɗin bai dame ni ba, kawai ki ba ni dama, ina mai tabbatar miki da cewa sai na sa kin manta da shafin soyayyar sa kin kama nawa, ko wane ne shi, sai na wanke shi daga cikin zuciyarki tas.. Ja da Najeeb a fagen soyayya is not easy dear"

Kallonshi take yi sosai jin yanda yake maganar with full confidence, Prince ɗin nata za'a wanke daga cikin zuciyarta???...

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

_When you keep saying you are busy, then you will never be free. When you keep saying you have no time, then you will never have time. When you keep saying that you will do it tomorrow, then your tomorrow will never come...Just do it at the exact time_

*PAGE 13-14*

Ganin irin kallon da take mishi ya sa ya ce "kina tantama ne?...Ki jaraba ba ni lokacinki ki gani yanda zan mayar da ke cikin ƴan kwanaki ƙalilan, zan nuna miki soyayyar da ba ki taɓa tsammaninta ba, zan kula dake tamkar yanda uwa take kulawa da jaririnta, zan mayar dake ƴar gata a cikin mata, in mayar da ke tamkar sarauniya.. Just give me a chance"

Yanzu kam kalamanshi sun ɓata mata rai, a fusace ta ce "kai dalla surutunka ya fara mun yawa... Wai zaka kula da ni, zaka mayar da ni ƴar gata, za kayi wannan za kayi wancan... To yanzu cikin wahala ka ganni ko iuma cikin ƙuncin rayuwa?"

"Calm down Baby, ai duk wanda ya kale ki ya san ke ƴar hutu ce kuma ƴar gata, zan ninka miki ne akan wanda kike da shi, ina sonki Cutie, ina ƙaunarki"

Dukan table ɗin tayi, ta ce "enough! Kar in sake jin kalmar kana so na ya fito daga bakinka, zuciya ta tana da wanda take so, shi ɗin ne shi kaɗai, ba wani kuma ba za'a samu wani ba har

abada.. Dan haka kar in sake ganin wannan fuskar ta ka, ka bani waya na kuma"

Murmushi kawai yake yi yana kallonta, kafin ya miƙa mata wayar, ya ce "ga shi, kiyi haƙuri na ɓata miki rai da nayi, anjima zan sake kiranki dan in ƙara bada haƙuri"

Harararshi tayi ta ce "wa za ka kira? Da number dai ake kiran mutum ko, to kuma ba za ka samu ba"

Ƙara faɗaɗa murmushinshi yayi da ya ƙara bayyana kyaunshi, ya ce "Cutie, Najeeb ba ya wasa da any single opportunity da ya samu, musamman akan abunda yake so... Tun da na karɓa wayan na ki, na kira layi na da wayar, sai na samu numbernki, dan haka ni tun ɗazu na wuce wannan, sai na kira ki dai"

Ba ta iya ce mishi komai ba, ta fizge wayarta, ta wuce ta bar shi a wurin, murmushi ya bi ta da shi kafin shi ma ya wuce

Sadeeq bai fi minti biyar da barin gidan Anty Sadiya ba, sai ga Safwan, gaisawa suka yi kafin ya ce "ina su Armaan?"

"Aryaan yana bacci, Armaan kuma yanzu ya bar ɗakin nan, may be ya shiga play-room, ban sani ba dai"

"Ok.. Anty Sadiya, Tiger bai zo gidan nan ba?"

"Ya zo, bai ma daɗe da fita ba, ina tunanin ba hanya ɗaya ku ka biyo ba, da kun haɗu"

"Eh, ni ta baya na biyo, amma gida zai koma?"

"Ina tunanin haka, amma bai gaya mun ba"

"Bari in koma gida to"

"Safwan dan Allah ka dinga tausasa mishi zuciyar nan"

"Anty Sadiya ta ya zanyi haka? Ke fa kin san waye Sadeeq.. Yanzu dai bari in je, idan ki ka shigo sai muyi magana"

"Ni fa sai nan da kwana uku zan zo"

"Haba dai, amma kin san saura kwana biyar a fara biki ko! Ya kamata ke ma ki zo gobe, Anty Sameera gobe za ta zo, Anty Saudi kuma ta ce sai jibi"

Dariya tayi ta ce "Saudi ko!, bari ta ji ka ba ruwa na ka santa... Ni dai ko yaushe za su zo matsalar ku ce, nikam sai nan da kwana uku, idan kuma ba ku so sai in zauna abu na"

"A'a ba sai kin zauna ba, ki zo kawai, ai dama na san matsayi na, yanzu da ace bikin Tiger ne, kina kan gaba"

"Ai bikin Tiger tun ana saura sati biyu ayi biki zan zo gida"

"A'a ki bari dai daga an ce an saka ranar bikin, ko wata nawa ne, kawai ki dawo gida"

Dariya tayi ta ce "kuma fa haka ne, good idea"

"Umm, ni dai sai anjima, ki gaida Yaya babba da su Aryaan"

"To za su ji, ka gaishe mun da su Hajiya"

"Aha"
Daga haka ya fita ya koma gida, ya sake dubawa amma aka tabbatar mishi da Sadeeq bai dawo gida ba, haka yayi ta kiran layinshi amma har yanzu a kashe, dole ya haƙura ba wai dan ya so ba

Sunaiha kuwa bayan ta bar wurin, sai da ta biya gidan su Ikram, sai kusan ƙarfe shida sannan ta koma gida, ta tarar da Daddynta ya dawo amma yana shirin sake fita

Ya ce "Baby kin dawo? "

Cikin shagwaɓa ta ce "umm"

Ya ce "menene?"

"Daddy kawai gajiya ne"

Murmushi yayi ya ce "ayya, to sannu, sai ki je ki watsa ruwa, ki huta.... Yawwa, Baby baƙonki aka ce bai zo ba ko?"

"Eh" ta amsa a gajarce

"Ban san me yasa bai zo ba, amma idan na dawo zan kira Abbanshi in ji ko lafiya"

"To Daddy, bari in shiga, na gaji... Mummy fa?"

"Tana ɗakinta"

"Ok, take care" ta haura sama, ɗakin Mummy ta fara tsayawa ta gaishe ta, sannan ta wuce ɗakinta

Ƙarfe 9:24pm, Abba da Kawu ƙarami suna parlourn Alhaji, kasancewar ɗazu ya dawo daga ƙasar Japan, fira suke yi sosai dan ya kusan sati biyu a can, su na gaya mishi abubuwan da aka tsara na auren Safwan

Sosai Alhaji ya ji daɗi, dan ya ƙara yarda ko da bayan ranshi ne, ƙannenshi za su iya kulawa da iyalanshi tamkar yana raye, dama abunda suke so kenan gaba ɗayansu

Alhaji ya ce "ya maganar Sadeeq wai, har yanzu bai gaya maka wacce yake so ɗin ba?"

"Hmm, Alhaji kawai ka ƙyale wannan yaron, ni na gama da wannan matsalar"

Kawu ƙarami ya ce "kamar ya?"

"Na zaɓa mishi wacce zai aura mana, duk lokacin da ya gaji da jiran waccan ɗin sai ya aure ta idan yana da ra'ayi"

Kawu ƙarami ya ce "to amma yana sonta?"

"Yau na tura shi, ban sani ba.. Amma ko ba ya sonta sai ya aure ta, dan ba zan bari a dinga zaginmu a gari ba"

"Amma hakan kamar bai dace ba, kamata yayi a takura mishi har sai ya gaya mana ko wacece, sai ya aure ta hakan zai fi"

Alhaji ya ce "a'a Aliyu, hakan da yayi shi je dai-dai, tun yaushe ake magana ɗaya amma abu ya ƙi ƙarewa, idan aka bar shi haka wata rana zai iya jawo mana abun kunya"

Kawu ƙarami ya ce "amma ai ka san halin Sadeeq, ba wani abun kunya"

"Na sani, amma kar ka manta akwai sheɗan"

"Haka ne kuma, to Allah ya mana zaɓi mafi alkhairi... Amma wace yarinya ce wannan?"

Abba ya ce "ƴar gidan Senator Abubakar Mai doki ce"

Alhaji ya ce "wai har yanzu abotanku na nan?"

"Eh, shiyasa ma muke so mu ƙara ƙarfin abotan ai"

"To Allah ya sa hakan shi ne alkhairi"

Gaba ɗaya suka amsa da ameen, kafin suka watse kiwa ya wuce part ɗinshi, ganin ƙarfe goma saura ƴan mintuna

Abba na kai wa cikin parlourn su, kiran Daddy ya shigo wayarsa, sai da suka gaisa kafin Daddy ya ce

"Baby ta ce mun yaron nan bai samu zuwa ba, Alkah dai ya sa lafiya?"

Da mamaki ya ce "bai zo ba?"

"Eh"

"Oh sorry, na manta ya kira ni ɗazu ya gaya mun yana da emergency amma idan ya kammala da wuri zai tafi, ina tunanin aiki ya mishi yawa ne" abun da Abba ya faɗa kenan dan bai so Senator ya fahimci wani abu

"Allah sarki, ba komai ai, gobe sai ya zo kawai"

"To Allah ya kaimu lafiya, ina gaida iyali"

"To za su ji, na gode.. Sai da safe" sai ya kashe wayar

Abba kuwa cike da ɓacin rai ya nemi nunbern Sadeeq ya kira shi, ya kuwa yi sa'a ta shiga

Sallama Sadeeq yayi amma bai tsaya amsa mishi ba, ya ce "kana ina?"

"Ina parking space, yanzu na shigo gida"

"Ka zo part ɗin mu ina nemanka" yana gama faɗar haka ya kashe wayar

Bai fi minti biyar ba, sai ga shi ya shigo , a tsaye ya tarar da Abba, risinawa yayi zai gaida shi, Abba yayi saurin dakatar da shi

"Miƙe tsaye kawai, ban ga amfanin wannan ladabin ba tun da har zan iya sa ka kayi abu amma ka nuna mun ban isa ba, ba ni da iko da kai"

Cikin muryarshi mai sanyi ya ce "kayi haƙuri Abba, ba na ƙi zuwa bane dan in ɓata maka rai ko kuma in nuna maka ba ka isa da ni ba kamar yanda ka ce, uzuri ne ya riƙe ni a asibiti"

"Wane irin uzuri ne?"

Rasa abun da zai gaya mishi yayi saboda ƙarya yake yi ba wani asibutun da ya tafi ma, daga gidan Anty Sadiya wurin aikin wani abokinshi ya tafi, sai ya ce "Abba ka san aikin mu fa, kayi haƙuri, nayi maka alƙawari gobe zan tafi"

Shiru Abba yayi kafin ya sauke numfashi ya ce "shikenan, Allah ya kaimu lafiya"

"Ameen Abba, na gode... Sai da safe"
Sai ya juya kawai ya fita

Part ɗinsu ya wuce, ya ga su Safwan, Sauban da Sameer a parlour, ko kallonsu bai tsaya yi ba, ya buɗe ƙofa ya wuce ɗakinshi

Yana shiga Safwan ya turo ƙofar, ya ce "wai kai meye matsalarka ne? Ina ka tafi tun safe nake nemanka, ba inda ban je ba da na san kana zuwa amma ba ka nan, na kira wayanka kuwa ya fi a ƙirga, ina ka tafi k... "

Katse shi Sadeeq yayi da "dan Allah ya isa, ba gani na dawo ba! Ko ɓacewa zanyi ne?"

"Oh haka ma za ka ce? Yayi kyau"

Juyawa Safwan yayi zai fita, Sadeeq ya riƙe mishi hannu, ya ce "i'm sorry... Gobe za ka raka ni"

Safwan ya ce "ba inda zan tafi"

Kallonshi kawai Sadeeq yake yi bai ce mishi komai, sai kuma Safwan ya ce "shikenan.. Amma ina?"

Sakin shi Sadeeq yayi ya nufi wurin mirror yana faɗin "wurin da Abba ya ce"

Ƙarasawa Safwan yayi kusa da shi ya ce "me za kayi idan ka tafi? Ka yarda za ka aure ta ne? Waccan ɗin kuma fa da kake so?" haka Safwan ya jero mishi tambayoyi

"Ban ce maka na yarda ba, haka kuma ba zan taɓa daina son wacce nake so ba, ba kuma zan ita haɗa ta da wata ba"

"To me zaka yi?"

"Ba wani abunda zanyi" sai kawai ya wuce toilet dan ya watsa ruwa

Safwan na wurin a zaune har ya fito yayi shirin kwanciya, Safwan ya ce "Tiger ka san dai abokin Abba ne, kar mu je kayi abunda bai kamata ba, za'a ji kunya"

"Tare za mu tafi, idan ka ga zanyi abunda bai kamata ba sai ka gaya mun" daga haka ya juya ya kwanta, Safwan ya kai minti uku yana kallonshi kafin shi ma ya fita ya wuce ɗakinshi

Sunaiha na kwance kan gadonta, wayar ta ta fara ƙara, kallon wayar tayi ta ga number ce, hakan ya sa ba ta ɗaga ba, an kira ya kai sau huɗu tana kallo, ta wuce tayi wanka ta shirya ta kwanta

Jawo wayar tayi, ta ga saƙo kamar haka: 'Cutie meyasa kike so sai kin azabtar da ni ne? Ina ƙaunarki fa, kuma rashi ɗaga waya ta ba zai hana ni kiranki ba, doke sai na samu gurbi a zuciyarki, ba san iya haƙurin rashinki ba Cutie'

Tsaki kawai tayi, ta kunna data ta fara chatting, sallama ta ga anyi mata da numbern Najeeb ɗin dan har ta hardace ƙarshen numbern, sai da saƙon ya kai fiye da minti ashirin kafin ta shiga,amma ba ta amsa ba

Haka ya jero mata sallama sau bakwai, kafin ta iya tura mishi '

'Wai ba za ka ƙyale ni ba? Ina da prince ɗina na gaya maka'

Ya turo mata da amsa 'Prince dai prince dai, kina ta maganar prince bayan ba ki ko gama yarda da irin son da kike mishi ba'

'Haka kake tunani?'

'Eh mana, idan kin yarda da irin son da kike mishi ai ba za ki ji tsoron ba ni lokacinki ba, saboda kin san duk abunda zan yi ba zan iya cire shi a ranki ba, amma tun da kin san soyayyar ba ta ƙarfi shiyasa kike tsoro kar in ruguza ta kamar yanda na gaya miki'

'Wannan ba hujja ba ce'

'To idan kin yarda da soyayyarki, ki bani dama ki ga na wa salon, ni kuma sai na ba ki mamaki'

'Shikenan... Ni kuma zan tabbatar maka da ba za ka iya cire prince a raina ba, dan ya fi ƙarfinka'

Emoji ɗin dariya ya tura mata sannan ya ce 'za ki gani kuwa, thank u dear'

Ba abunda ta ce mishi, sai kawai ta kashe datar, ta kwanta.

Washe gari kamar yanda Sadeeq ya tsara ƙarfe biyu za su tafi, haka suka shirya bayan sun

dawo daga wurin da suka tafi dan shirye-shiryen bikin Safwan

Safwan ya shirya yana jiran Sadeeq, ganin har yanzu bai fito ba, sai ya bi shi ɗakin, lokacin da ya shiga Sadeeq ya gama shirinshi tsab, cikin jerin set ɗin glasses ɗinshi ya ɗauko ɗaya baƙi ƙirar Versace, ya saka, ya buɗe drawern da ke jikin mirror, ya ɗauko wani ƙaramin kit da ke cike da face-masks ɗin shi, ya buɗe ya ɗauko wani navy blue kalan jeans ɗinshi

Riƙe mishi hannu Safwan yayi, ya ce "dan girman Allah yanzu dai ka ajiye wannan abun, yanzu fa ba wani wuri za mu tafi ba, daga gida direct gidansu za mu tsaya fa"

Sadeeq bai ce mishi komai ba, ya saki face-mask ɗin kawai miƙe ya bar Safwan da kit ɗin, shi ya rufe shi ya mayar da shi cikin drawer sannan ta fita

Parking space ya nufa, ya tarar da Tiger cikin motarshi yana jiranshi, dai-dai lokacin da Momi tayi parking mota ta fito

"Angwaye ba zama ko"

Murmushi Safwan yayi ya ce "Sannu da dawowa... Yanzu ai na tambayi Umma ta ce kin fita"

"Wallahi kuwa, to sai kun dawo"

"Yawwa" ya amsa mata sannan ya shiga motar su ka wuce

Kallon Sadeeq yayi ya ce "amma kana ganin Momi ba za ka iya fitowa ku gaisa ba?"

"Umm" abunda kawai ya amsa da shi kenan ya mayar da hankalinshi kan tuƙin da yake yi, Shi ma Safwan bai ƙara ce mishi komai ba, dan daga jin wannan amsar ya san maganar ce ba ya so

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*

♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

_Good thoughts kills the stress before it kill you, help every one before some one help you, you live the life before it leave you, reach the GOAL before some one kick you..._

*PAGE 15-16*

Dai-dai gate ɗin gidansu Sunaiha, Sadeeq yayi parking motarshi, kallonshi Safwan yayi ya ce "ba za ka shigar da motar ba ne?"

"Umm" ya amsa mishi, kafin ma Safwan ɗin ya samu abun faɗa har ya fice daga motar, girgiza kai Safwan yayi shi ma ya fito daga motar

Safwan ya tsaya suka gaisa da mai gadin, yayi mishi bayanin kansu

Mai gadin ya ce "yallaɓai ai Alhaji ya sanar da ni za ku zo, Hajiyar ma tana ciki"

Shi yayi musu jagora zuwa cikin gidan ya haɗa su da wani mai aiki dan ya kai su ɗakin baƙi, dab da za su shiga ɗakin, Sadeeq yayi ɗan ƙaramin tsaki, ya ce "excuse me, ina zuwa"

"Menene?"

"Ka shiga, ina zuwa" sai ya juya ya koma, Safwan kuma ya kutsa kai cikin ɗakin bayan ma'aikacin shi ma ya wuce

"Assalamu alaik... " fuskar da ya gani ne ya hana shi ƙarasa sallamar da ya fara

Zaune take kan kujera tana kallon wayarta, lokaci ɗaya kuma tana shan ruwan da ta zuba a cup, ta sa atampa purple da ratsin fari

Miƙewa tayi tsaye ita ma lokacin da ta ganshi, kallon juna suke yi kafin ya ce "ba dai ke ce Sunaihar da... "

Saurin katse shi tayi da "dama kai ne na ɓata tsawon lokaci na ina jiranka a nan? Lallai ban taɓa dana sanin jiran wani ba irin yau, to bari ka ji, tun wuri ma ka fita ka bar gidan nan, dan kai kam wallahi ba za ka taɓa samun soyayya ta ba, ko da kuwa kai ne autan maza... Ashe duk isar ka sai ka zo barar soyayya, ni yanda na ga Ikram ta baka girma, na ɗauka kai wani ne, ashe ba ka ma isa ba, to wallahi Ƴar Senator ta fi ƙarfin mutum irinka kuma.... "

Wani mahaukacin tsawa ya daka mata, ta tsorata sosai, dan kam Safwan ya iya tsawa har ya gaji, "keep quiet!! Enough, ya ishe ki haka... Ki san irin kalaman da za ki gaya wa Safwan kin gane ko, ni ba irin mutanen da kika sani ba ne da za ki gaya musu magana son ranki, ina ɗaga miki ƙafa ne kasancewarki mace dan wallahi na san idan na dalla miki mari sai kin kwanta a asibiti... Ke a tunaninki na zo nan ne saboda in nemi soyayyarki ko me?  Ba na mu'amala da mutanen da ba su san darajar ɗan adam ba, ɗan uwa na na rako nan kuma shi ma ba dan yana sonki ba, ki ma gode ma Allah ba shi kika gani ba dan da sai ya kumburar miki da fuska, wawuya kawai.... Kuma wannan gidan ke kika ɗauke shi gida, ko ba ki ce in tafi ba zan wuce dan ba ma zan so in ƙara ko da second ɗaya a tare da ke ba saboda hakan illata mun rayuwa yake.. Ba ni ba, ba ɗan uwa na ba, kap danginmu ba wanda kika cancanci ya zauna dake, shashasha da ba ta san kimar mutane ba" yana gama faɗin haka ya juya ya bar ɗakin

Tunda Sunaiha take ba wanda ya taɓa mata irin abunda Safwan ya mata, kuka ta fashe da shi, da gudu ta isa parlour, Munmy na saukowa daga stairs ta ganta, da sauri ta ƙarasa wurinta, Sunaiha ta rungume ta tana kuka

Mummy ta ce "lafiya? Menene?" amma shiru Sunaiha ba ta amsa ta ba, sai kuka take ta yi

"Sunaiha kiyi shiru ki ga mun menene? Me ya faru? Me ya miki?" ta jera mata tambayoyi, amma ganin ba ta da niyan ba ta amsa ya sa ta fara rarrashinta a hankali har ta daina kukan, sannan suka zauna ta gaya mata irin cin mutuncin da Safwan ya mata

Mummy ta ce "kin gaya mun abubda ya ce miki, amma ban ji abunda ke kika yi mishi ba"

Cikin muryar kuka ta ce "Mummy ba fa abunda nayi mishi, haka kawai ya dinga zagi na" ta sake fashewa da wani kukan kafin ta ci gaba "wallahi Mummy bai da mutunci, na tsane shi kuma sai ya gane ya kuskurensa"

Tsaki Mummy tayi ta ce "to me za ki iya mishi? Duk namijin da ya iya zuwa har cikin gidanku ya gaya miki magana haka bai duba matsayinki ko na mahaifinki ba, kin san kuwa ya fi ƙarfinki ko! Ke ni bari ma ki ji, ban fa yarda haka kawai ya gaya miki wannan maganar ba, dole akwai abubda kika mishi, ke ɗin! Na san halinki fa sarai"

Kallon Mummy tayi ta sake sakin wani kukan ta ce "dama ai na san ba yarda za kiyi ba, bari Daddy na ya dawo shi da yake so na" ta tashi ta haura sama tana kuka

Mummy ta ce "eh ki jira shi, shi da yake biye ma haukanki, nikam ba da ni ba"

Daga ɓangaren Safwan kuwa, bayan fitarshi daga ɗakin, ta wurin gate suka haɗu da Sadeeq yana shigowa, Safwan ya ja mishi hannu suka fita, dai-dai mota Sadeeq ya tsaya yana kallon fuskar Safwan

Safwan ya ce "ka zo mu wuce gida"

Sadeeq ya ce "menene?"

"Na ce maka mu tafi gida, wannan yarinyar ba za ka aure ta ba"

Kallonshi kawai Sadeeq ya ke yi, Safwan ya ce "ka daina mamakin abunda na faɗa, tunani kake yi ya aka yi ni nayi abunda nake ƙoƙarin hana ka ko? To na san da kai ne sai kayi abunda bai dace ba dan ni ban yu komai ba.... Tiger wannan yarinyar ba kalan Saraki's family ba ce, ka zo mu wuce" ya faɗa yana ƙoƙarin tafiya

Sadeeq ya ce "me za ka gaya ma Abba?" cak Safwan ya tsaya, sannan ya juyo ya kalli Sadeeq ya ce "gaskiya zan gaya mishi, kawai ka zo mu tafi"

Sadeeq bai sake cewa komai ba, ya kiƙa ma Safwan mukullin motar dan yayi driving, suka shige motar suka koma gida

Sunaiha na kwance tana tuna maganganun Safwan, kiran Najeeb ya shigo wayarta, sai da ya kira sau biyu, a na ukun sannan ta ɗauka

"Hi Cutie, i missed u alot"

"Really" ta amsa mishi dan so take ta samu relief daga abunda Safwan ya mata

"Of course dear, kusan awanni huɗu fa ban ji ki ba, sai na ji duniyar ta daina mun daɗi"

Murmushi tayi ta ce "to ai yanzu ka ji ni"

"Sosai kuwa, sai na ji zuciya ta tayi fari tas, ban san ya aka yi ba lokaci ɗaya kika tafi da ni haka, ke ce kaɗai tauraruwar da ke haska rayuwa ta, idan ina tare da ke sai inji tamkar na fi kowa farinciki a duniyan nan, idan kuma ba na tare da ke, komai ba na iyawa sai aikin tunaninki ko zan samu in ga haske... Gaskiya Cutie ke ta daban ce, i love u, duk wanda ya same ki ya

more"

Murmushi ta sake yi ta ce "ai kai ma ka san ko wanene wannan da zai more ma samu na, My Prince, ko ka manta?"

Ɓata rai yayi ya ce "sau nawa nake gaya miki idan ina magana dake ki daina sa mun zancen wani?"

"Sau nawa nake gaya maka Prince bugun zuciyata ne, ka taɓa ganin wurin da mutum yake ba tare da zuciyarshi ta buga ba? Infact ma ai har yanzu ba ka kai matsayin da za ka gindaya wa Ƴar Senator sharaɗin da za ta bi ba"

"Hmm, shikenan, yanzu ina aiki, we'll talk later"

Ba abubda ta ce mishi sai ta kashe wayar, a hankali ta rufe ido ta ce "where are u My prince? Yaushe zan ganka? Yaushe za ka fito mun a zahiri ba a mafarki ba? Ina sanka sosai, zan iya yin komai saboda kai, atleast ka gaya mun garin da kake, i promise to come and meet u, ko ba'a ƙasar nan kake ba, zan zo"

Cikin kunnenta ta ji zazzaƙar muyarsa yana mata magana "Sorry Sunie, i'm always with u, kuma very soon za ki ga prince ɗinki... I so much love u Sweetie"

A firgice ta tashi zaune tana ta waige-waige, ta miƙe tan zagaya ɗakin, duk wani lungu da kusurwar da ke ɗakin sai da ta leƙa, har ƙarƙashin gado ba ta bari ba, sai da ta gaji sannan ta zauna tana tuna abunda ya gaya mata, murmushi tayi wanda ya fito tun daga cikin zuciyarta, ta ce "i hope so My prince, i will wait for u, na san za ka zo tunda har ka gaya mun haka" nan take ta ji wani irin farinciki ya lulluɓe ta, gaba ɗaya ta manta da maganganun Safwan

Kusan ƙarfe takwas na dare, Abba ya dawo daga wurinsu Grandpa, yana fitowa daga mota ya haɗu da su Safwan, gaida shi suka yi, kafin ya ce

"Ban ji feedback ba fa, kuma kun ce yau za ku tafi gidan, ko dai ba ku je ba?"

Safwan ya ce "Abba mun tafi, amma wallahi wannan yarinyar sam ba ta dace da Sadeeq, ba ta da tarbiya..."

"Yi mun shiru Safwan" Abba ya katse shi, "wannan shi ne shirin da kuka shirya? Ka ce mun ba ta dace da shi ba, ba ta da tarbiya, ko? Ai na sani dama, tunda na ji ya wani dage akan zai tafi na san akwai wani abun da yake shiryawa, wato abun da kuka shiryan kenan"

Safwan ya ce "Abba wannan ba zancen shiri ba ne wallahi, da gaske nake gaya maka, ba ta da.... "

"Safwan ka mun shiru kafin in ɓata maka rai, waye ban sani ba a cikinku, kai ko Sadeeq? Bakinku ɗaya, na san tsab za ka ga kayi abunda zai faranta mishi rai, shiyasa kai ne mai bakin magana ko! Kun san tun yaushe na san Senator? Ko kun san shekara nawa muka yi tare? Ba wani halinshi da ban sani ba, ta ya za ka ce ƴarshi ba ta da tarbiya kuma kuyi tsammanin zan yarda?... Amma shikenan, yanzu ba dai kunyi yanda kuke so ba, ku tafi kawai, nima zanyi yanda ya kamata"

Sadeeq ya ce "Abba... "

"Ban son jin komai" Ya katse shi, sannan ya wuce ciki, kallon juna suka yi, ba wanda ya ce komai, suka shiga mota suka bar gidan, dama wurin Grandma za su tafi

"Angwaye, ai ni har nayi fushi" cewar Grandma

Safwan ya ce "fushi kuma Granny? Meyasa to? "

"Haba Safwan, tun ranar da ku ka kawo kayan nan ku ka ajiye ba ku sake dawowa ba sai yanzu"

"To Granny kin san abubuwa sunyi yawa ne wallahi shiyasa"

"Haka je, Allah ya nuna mana an gama lafiya.... Wannan kuma fa, lafiya?"

Kallon Sadeeq yayi, sannan ya ce "Abba ne, Granny wallahi wata yarinya ce Abba ke son haɗa Sadeeq da ita, kuma sam yarinyar ba ta da kamun kai"

"Tooo! Garin ya kuma Usman zai yi haka? Ina so Sadeeq yayi aure shi ma amma na fi so ya samu yarinya natsatsiya"

"To wallahi wannan yarinyar kam sam ba abun so a cikinta" inji Safwan

"Ban yarda da wannan zancen ba Safwan" a tare suka juya dan ganin ko waye, Grandpa ne, a hankali yake tafiya yana ƴar sandarshi a hannu

Sadeeq ne ya tashi ya taimaka mishi har ya zo ya zauna, Sadeeq ya ce "Grandpa har yanzu ƙafar na nan dai?"

Ya ce "bari kawai Abbakar, ni kullum ma abun gaba yake yi"

Safwan ya ce "sannu Grandpa.. Tun tuni na gaya maka ka bari a fitar da kai waje amma ka ce a'a"

"Safwan ni fa ba son zuwa wata ƙasa nake yi ba... Yanzu dai ba wannan ba, na ji kana wata magana, Safwan na san waye Usman, ba yanda za'a yi ya nemi wa Abbakar mace mara tarbiya, sai dai idan kun yi mata kuskuren fahimta ne"

"Grandpa wallahi ba kuskuren fahimta ba ne, haka yarinyar take"

"Safwan, Sadeeq, ina so ku tattara wannan zancen ku ajiye, idan ma kun san ran Usman ya ɓaci akan wannan abun, to ku gaggauta ba shi haƙuri, saboda mahaifinku ne, ba ku fi shi sanin dai-dai ba, ba kuma zai yi wa ɗan da ya haifa mugun zaɓi ba, kar in sake jin wannan maganar"

Granny ta ce "amma Alhaji ba za'a duba maganar yaran nan ba?"

"Ba abunda zan duba, kuma shi ya haifi ɗanshi, ba zan hana shi iko da shi ba tunda ba saɓon Allah ba ne"

Ganin Grandpa bai ba zancen muhimmanci ba ya sa ba su sake yin magana ba, Sadeeq dama ba iya jayayya yake yi da Grandpa ba sabida yanda yake nuna mishi kulawa, sun daɗe a gidan, sai kusan ƙarfe goma sannan suka koma gida

Mummy da Daddy su na zaune a parlour yana ba ta labarin wuraren da suka ziyarta yau, sai ga Sunaiha ta sauko, kan wata kujera ta je ta zauna kafin ta gaishe su

"Baby ya baƙon na ki, ya zo?"

Ɓata rai tayi kafin ta ce "sun zo Daddy, amma tun da nake ba'a taɓa ci mun mutunci irin yau ba, har zagi na yayi, wai kap danginsu ba wanda na cancanci ya zauna da ni, Daddy ya gama da ni yau, na tsane su kap ɗin dangin na su" taƙarasa maganar hawaye na zubuwa daga idonta

"Subhanallahi, kin ga Baby ya isa, bari in fara kiran Mahaifinshi inji"

Mumny ta ce "Allah ya waddaran naka ya lalace wallahi, mtwss"

Daddy dai bai ce mata komai ba ya shiga kiran layin Abba, amma not reachable, sai ya ce "ba network, bari anjima ko zuwa safe zan kira shi, ko kuma bari in ajiye mishi saƙo ta whatsapp tunda yana yawan zuwa online irin lokacin nan"

Nan ya shiga whatsapp ɗinshi, kai tsaye ya nemo numbern Abba, ganin ya canza profile picture ɗinshi ya sa ya tsaya buɗewa, da tambarin kampaninshi ne, amma yanzu kuma hoton Sadeeq ne wanda yayi a New Zealand, kan gada yayi hoton kusa da ruwa, yana da jeans baƙi da riga blue, ya sa madubi baƙi, agogon hannunshi blue, yanayin hoton unexpected pic ne, amma yayi masifar kyau

Daddy na miƙa wa Mummy wayan ya ce "kin ga fa yaron nan"

Kamar ba za ta ansa ba sai kuma ta miƙa hannu ta karɓa, kallon hoton tayi sosai, ta ce "Masha Allahu laa ƙuwata illa billah... Yanzu Alhaji yaron nan iyayenshi hausawa ne? A ƙasar nan suke"

"Eh mana, ba shi ne Sadeeq ɗin ba to"

"Lallai... Allah yayi wa kowa zaɓi mafi alkhairi, ai ya kyauta mun wallahi"

Sunaiha ta ce "a'a Daddy, Safwan dai ba Sadeeq ba"

"Baby Safwan ka ai saura kwana huɗu nake tunani ya rage a fara bikinshi, Sadeeq dai, shi Safwan rakiya yayi"

Shiru tayi tana tuna Safwan ya gaya mata ɗan uwanshi ya rako, sai ta ce "eh haka ne.. Wato shi Sadeeq ɗin shi ne shafaffe da mai, ko zuwa bai yi ba sai ya aiko Safwan"

Daddy ta ce "ba Sadeeq ya zo ba?"

"A'a, Safwan ne... Mummy dan Allah in ga fuskar ɗan rainin hankalin nan, sai nayi maganinsu wallahi" ta faɗa lokacin da ta miƙe ta ƙarasa kusa da Mummy ta karɓi wayar

"Prince!!!" ta faɗa a razane tana sakin wayar, kan jikin Mummy wayar ta faɗi

Sunaiha ta sake cewa "Prince ne, wallahi Daddy prince ɗina ne wannan" maganar take yi sai ka ce wacce ta zauce

Mummy ta ce "ke ki natsu dan Allah, wane Prince ɗin?"

"Mummy Prince ɗina da nake ta jira, dama na sani kana so na prince kuma ba za ka mun ƙarya ba, ɗazu ya gaya mun very soon zan ganshi kuma ya cika alƙawari" farinciki ya lulluɓe ta har ji take kamar tayi kuka saboda daɗi

Daddy ya ce "Baby kin tabbata wannan shi ne prince ɗin da kike gani a mafarki?"

"Wallahi Daddy shi ne, dan Allah ka gaya mishi ina sonshi dan Allah, i can't do without him"

"Ki kwantar da hankalinki Baby, ai wannan mai sauƙi ne, ki sa ma ranki shi ne mijinki... Alhamdulillahi " ya ƙarsa magabar shi ma cikin murna

Sake ɗaukan wayan tayi, tayi saving ɗin hoton sannan ta tura ma kanta ta miƙa mishi wayar, ta ɗauki wayarta ta wuce ɗaki tana ta jin daɗi ta ce "yau zan yi kwanan farinciki, i love u Daddy"

tafiya take tana tsalle tana juyi, duk wanda ya kalle ta a wanna lokacin ya san tana cikin tsananin farinciki......

♦💫♦💫♦
*YAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*YAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

_Speak less to people whom u love most, because if they can't understand ur silence, then, they can never understand your words....keep quiet for the sake of ur relation_

*PAGE 17-18*

Sunaiha na wucewa ɗakinta, Daddy ya kira layin Abba, sai da ta kusa tsinkewa sannan ya ɗaga saboda yana tunanin abunda zai ji daga bakin Senator

Sallama yayi kafin Daddy ya ce "Alhaji ya gajiya"

Abba ya ce "Alhamdulillahi, ya fama da jama'a.. Kaga ban kira ka ba in...."

Daddy ya katse shi da "a'a ai ni ya kamata in kira ka ba kai ba, saboda in yi maka godiya, yau ina cikin farin ciki sosai saboda burin Baby ya kusa cika"

Da mamaki Abba ya ce "wane buri kuma?"

"Ina prince ɗin da na gaya maka Baby ta ce shi kaɗai za ta aura... Ashe wai Sadeeq ne wannan prince ɗin na ta"

Murmushi Abba yayi ya ce "ikon Allah, kenan shi ne wanda take so?"

"Sosai ma kuwa, saboda shi ne fa take gida har yanzu, ba irin neman da ba muyi mishi ba, ashe muna tare da shi ma... Gaskiya ne da hausawa suka ce rashin sani yafi dare duhu" ya ƙarasa maganar yana dariya

Cike da farinciki Abba ya ce "masha Allah, amma na ji daɗin wannan maganar sosai wallahi, nima buri na zai cika kenan na ƙara ƙarfin zumuncin mu"

"Tabbas, yanzu saura ka tambayi Sadeeq din mu ji, Allah ya sa shi ma yana sonta kamar yanda take son shi, saboda ta ce ɗazu ba su samu haɗuwa ba, da Safwan suka haɗu, yanzu ma a dp ɗinka ta ga hotonshi"

Abba bai yi mamakin jin Sadeeq bai tafi ba, ya tura Safwan dan ya san zai iya fiye da haka ma, sai kawai ya ce "dole ma zai so ta, idan ma ba ya sonta zai koya ne, bare kuma Sunaiha wa zai kalle ta ya ce ba ya so?"

Murmushin jin daɗi Daddy yayi ya ce "godiya nake, to sai da safe dai idan ku ka yi maganar da shi sai inji yaushe ya kamata in zo mu tattauna akan auren na su, dan ban so ya ɗauki lokaci"

"Kar ka damu, in sha Allah da safe za ka ji ni"

"To nagode, Allah ya tashe mu lafiya"

"Ameen" daga haka suka kashe wayar

Mummy na zaune gefe tana kallon Daddy yana waya, wani irin baƙin ciki, ne ya tokare mata wuya, ji take kamar ta dalla mishi mari, kallonta yayi yana fara'a ya ce "Hajiya kin ji abun arziki ko, wallahi.... "

"Arziki?!" ta katse shi, "arziki a ina? Wannan ne abun arzikin? Anya kuwa Alhaji kana son yarinyar nan kamar yanda kake ikirari? Kana so ka siya mata mutunci kuwa? A ina ka taɓa jin

iyayen mace sun je neman auren namiji da har kake wani cewa a gaya maka yaushe za ka zo kuyi magana, kar ka manta ƴarka mace ce ba namiji ba, dan haka su za su zo ayi magana ba wai kai za ka je ka same su ba.. A ma ture maganar zuwa neman auren da za ka je yi mata, ka tsaya kayi binciken wane yaro ne ƴarka za ta aura? Ko kuwa kai dai burinka kawai Sunaiha ta auri prince ɗinta! Kar ka ga ka san halin mahaifinshi kayi tunanin haka yake shi ma sabida yanzu ka haifi ɗa ne ba ka haifi halinshi ba dan ni ga zahiri nan na gani a Sunaiha, haihuwarta kawai nayi amma ba hali na ko ɗaya da ta ɗauka, sannan bayan ba ka san halinshi ba, ba ka da tabbacin yana sonta ko kuwa a'a, yanzu fa abunda na ji mahaifin yaron yana cewa wai ko ba ya sonta dole zai so ta, wa ya gaya muku namiji mai hankali yana son mace saboda kyaun fuskarta ko kyaun sifarta? Wallahi duk namijin da ya san kanshi kuma yake da hankali yana son mace ne saboda tarbiyarta, ɗabi'unta da addininta, idan ba ta da waɗannan wallahi da ita da bola duk ɗaya ne ko da kuwa tafi matan duniyan nan kyau, sakaran namiji shi ke fara duba kyaun fuskar mace ko kyaun jikinta ya ce yana sonta, shi ma ba son gaskiya ba, yana gama cin moriyarta zai jefar da ita a lokacin da ta fi buƙatarsa, dan haka nake ba ka shawara ka daina wannan rawar jikin ka tsaya ka gyara future life ɗin ƴarka kar ku zo kuna dana sani"

Daddy da tun da ta fara maganar ya saki baki yana kallonta, ya ce "Ah, ikon Allah, wai mutum ya haifi yaro ya dawo yana faɗar munanan maganganu akanshi, shiyasa nake gaya miki wallahi ba kya son Baby... "

A fusace ta ce "eh ba na sonta, ba kai kayi mun naƙudarta ba! Ai ka fi ni sonta... Kar ka manta wata tara tayi a ciki na kuma ka fi kowa sanin wahalar da nayi cikin waɗannan watannin, sannan kwana biyu nayi a asibiti ina wahalar naƙudarta kai sheda ne, sannan na haife ta da ƙyar kamar zan mutu, sannan kake tunanin wai kai ka fi ni sonta, to ko da normal haihuwa nayi kaman sauran mata kai ka san ba za ka fi ni sonta ba dan ni uwa ce, soyayyar uwa kuwa daban ce, kuma daga ita ban sake samun wata ba, kai kuwa yanzu idan kayi ra'ayi tsab za ka sake auro wata ta haifa maka wasu yaran, amma ni ita kaɗai ce, amma still a haka ba na sonta kai ne mai sonta, to shikenan kayi yanda kake ganin shi ne dai-dai" ta ɗauki wayarta da ke kan table ta haura sama, ba abunda Daddy ya ce mata sai ƙara miƙe ƙafa da yayi kan table ɗin ya ci gaba da abunda yake yi

Tana kai wa dai-dai ɗakin Sunaiha ta ji tana waya, ko ba'a gaya mata ba ta san da Ikram ne take wayar jin yanda take ta murna tana bata labarin ta ga prince kuma Daddynta ya ce shi ne mijinta

Sosai Ikram ta tay ta murna, sannan tayi musu fatan alkhairi kafin suka kashe wayar, juyowar da za tayi ne ta ga Mummy tsaye a bakin ƙofa tana kallonta, "Mummy lafiya?" ta tambaye ta da mamaki

Numfashi Mummy ta sauke kafin ta ƙarasa ciki ta zauna, ta ce "Sunaiha, ni mahaifiyarki ce, da nafe ba zan sake sa baki na akan wannan abun na ku ba, amma ba zan iya barin ƴata tayi abunda za ta zo tana kuka ba"

"Mummy me ya faru?"

"Sunaiha, na yarda da soyayyar da kike yi wa yaron nan, amma ina so ki kama kanki, ki sani ke mace ce, duk wannan rawar jikin da kike yi wa ɗa namiji ba girmanki ba ne, namiji ko da ace yana sonki wallahi udan kina wannan abun a gabanshi sai ya sa ki kuka, bare kuma ba ki da tabbacin yana sonki ɗin... Sunaiha ina so kiyi rayuwar farinciki, ina so ki zauna a gidan mijin da zai so ki fiye da yanda za ki so shi, ina so ki auri mijin da zai dinga girmama ki da mutunta ki a matsayinki na matarsa. Sunaiha, mace ta auri mijin da ba ya sonta wallahi babban masifa ne, ba ƙaramin wulaƙanta ki zai yi ba, dama kin iya cewa ba kya son raini, to wallahi idan kika sake kika auri wandaba ya sonki to za ki ga ainihin abunda ake kira da raini... Dan haka nake so ki daina wannan kaɗaɗin, ki fahimci wane irin miji za ki aura, yana sonki ko ke kaɗai ke sonshi?"

"Umm, kai Mummy, ni to yanzu da kika zauna kika sa ni gaba kina mun waɗannan maganganun, na ma rasa gane wai wa'azi kike mun, ko umarni kike ba ni ko kuwa shawara ce? Kina ta cewa kar in auri wanda ba ya so na, zai wulaƙanta ni, zai raina ni, zai yi me zai yi me, to gaya miki aka yi prince ba ya so na ne? Mummy prince yana so na sosai saboda ya tabbatar mun da haka a mafarki na ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba, ɗazu ma sai da ya sake gaya mun he so much love me, prince ba zai taɓa wulaƙanta ni ko ya raina ni ba dan yana so na nima ina son shi, so pls Mummy don't spoil my mood, kawai ki je ki kwanta sai da safe" ta ƙarasa maganar tana turo baki

Tagumi Mummy tayi tana ta kallonta, kafin ta sauke ajiyar zuciya ta ce "Sunaiha Allah ya miki zaɓi mafi alkhairi kuma Ya shirya ki" ta miƙe ta fita ranta na ƙuna

Tashi Sunaiha tayi ta yi shirin kwanciya, ta sa ma ƙofar mukulli sannan ta dawo ta kwanta

~WASHE GARI DA SAFE~

Ƙarfe goma saura, Safwan na bacci, ya dinga jin hayaniya sama-sama, a hankali ya buɗe ido ya sauke kan agogon ɗakinshi, ya ce "ikon Allah, to wannan surutun fa? Kuma kamar daga main parlour amma har nan ina ji!"

Saukowa yayi daga kan gadon, sai da ya shiga toilet sannan ya fito, yana sanye da three quater da singlet, ƙofar ɗakin Sadeeq ya tura ba ya ciki, ya duba ɗakin Sauban ba ya nan, ɗakin Sameer shi ma ba ya nan, ya ce "ah'ah!"

Sai ya fito parlourn su, abunda ya ba shi mamaki ganin Sadeeq zaune yana rungume da wayarshi, ko me yake kallo? Shi ma dai three quater ɗin ne a jikinshi da singlet, Safwan ya ce "Tiger ashe ka nan, wai hayaniyan menene haka?"

"Idan ka fita za ka gani ai"

Tsaki Safwan yayi ya ce "Allah ya shirye ka... Mutum ma yana zaune yana jin hayaniya, ba zai iya zuwa ya ga ko lafiya ba"

"Kai da ka damu sai ka dawo" ya faɗa ba tare da ya kalle shi ba

Ba abunda Safwan ya ce mishi, ya fita. Kai tsaye main parlourn ya nufa, yana shiga ya ga gida masha Allahu, wannan hayaniyar ashe duk na jikokin Saraki ne, kap ƴan gidan nan a parlourn suna fira banda iyayensu maza sai Sadeeq, su Anty Sadiya ne yaranta, da Anty Sameera da ƴarta da Anty Saudat, da sauran ƴan matan gidan gaba ɗaya da ƴan samari, da su Hajiya da Umma da Momi, abun gwanin sha'awa sai fira suke su na ta dariya sai kace waɗanda suka daɗe ba su haɗu ba

Sultana ce ta lura da shi ta ce "Anty Sameera ga angon nan, dama ai na gaya miki in dai ya ji surutun mu da kanshi zai fito"

Dariya suka yi, Anty Sameera ta ce "ai kuwa ba kiyi ƙarya ba"

Ya ji daɗin ganin su sosai dan ko ba'a gaya mishi ba, akwatunansu da ya gani sun tabbatar mishi da sun zo bikin ne, sai da ya sake gaida su Hajiya kafin ya zauna ya ce "na ji ana cewa ga ango, dama gulma ta ake yi kenan"

Anty Saudat ta ce "ai dama dole za muyi gulmar ango, sai yanzu ka ga daman tashi ko"

Safwan ya ce "yanzu ma ai laifinku ne da ban tashi ba"

Momi ta ce "to ai sai ka tashi ka koma"

Dariya suka yi, Anty Sadiya ta ce "tun safe muna gidan nan kusan awa ɗaya, kana jin mu amma ka kyale mu, yanzu da ka ga daman fitowa ma ba za ka iya gaida mutane ba"

"Oh ni, Anty Sadiya ba ki jira kika gani ba ko zan gaida ke ko kuma ba zan yi ba... Ni ib gaya miki ban ma ganki ba dan ai sai gobe kika ce za ki zo, me ya kawo ki yanzu to"

Anty Sadiya ta ce "jar uba! Safna tashi ki kai mun akwati na mota in koma gida"

Sajida ta ce "haba Anty Sadiya yi haƙuri"

Sai da ta harari Safwan kafin ta ce "shikenan na haƙura"

Armaan ne ke gudu da waya a hannunshi, Sajeed na bin shi, da ƙyar ya kama shi ya karɓa ya ce "wallahi yaron nan ya raina ni sai na fara zane ka, wai ba ka san ni babanka ba ne ko! Dan kawai ka ganni ɗan ƙarami? Ji kanshi, sai na cire ka daga cikin ƴaƴana, in ɗauki Aryaan kawai da Ihsan"

Kallonshi suke suna dariya dan Sajeed kam akwai son girma, Anty Saudat ta ce "gaskiya Kawu Sajeed sai ka fara zane yaron nan naka"

"Wallahi kuwa Anty Saudat, bar ni da shi... Amma fa ba Kawu Sajeed ba, Uncle Sajeed, Kawu sunan tsofaffi ne" ya ƙarasa yana ɓata rai, dama da gangan tayi dan ta san ba ya son sunan, wai Kawu

Umma ta ce "to kai da kake da yara har uku ai ka tsufa"

"Nikam Umma ki daina ce mun tsoho, dan ban kai Grandpa ba"

"To Uncle Sadeeq, amma dai yanzu ayi ma yaran haƙuri kar ka zane su"

"Shikenan, ka gode ma Allah Kakarka ta sa baki" ya faɗa yana wani ɗaga kafaɗa yana kallon Armaan irin shi babban nan, Armaan kam dariya ma yake yi dan bai ko gane me yake cewa ba

Hajiya ta ce "ni dai ku tashi haka nan kusan abun yi, ku je ku duba shirye-shiryen da yaran nan suka yi idan akwai abunda za ku gyara, sannan na ji kuma zance karɓo ɗinki, kuma za ku je ina ne ma? ku dai yi abunda ya kamata, kwana biyu ya rage dai, amfanin zuwan ku tun yau ɗin kenan"

Anty Sadiya ta ce "to Hajjaju za muyi abunda ya kamata, amma dai kun san ba zan iya komai ba yanzu ba tare da na ga Oga Tiger ba, ku bari in je in ganshi"

Safwan ya ce "Allah mun gode maka, mu da ba'a so dai muke zuwa mu gaida mutum, wanda kuma ake ji da shi sai dai a isko shi, amma ba za'a iya mana godiya ba"

Umma ta ce "kana ma da bakin magana kai"

"Kuma fa Umma yana parlour na bar shi"

"Na sani ai"

Anty Sadiya ta ce "ni dai ba ruwanku, tsakaninmu ne"

Tana ƙoƙarin tashi sai ga shi ya turo ƙofa ya shigo, su Hajiya ya sake gaidawa shi ma, dan tun asuba suke zuwa gaida su, ya ƙarasa kusa da Anty Sadiya ya zauna, ya ce "Morning" a hankali yayi maganar kamar mai tsoron kar a ji

"How you dey (ya kake?) " ta amsa mishi

"Da sauƙi"

Anty Sameera ta ce "wai mukan gaisuwar nan ko sai mun biya ne?"

Anty Saudat ta ce "mutum nawa suka gaida ke tun shigowarki, amma kika da mu da wannan gaisuwar"

"Abun yana mun hot ne shiyasa"

Ɗan murmushi yayi ya ce "ina kwana"

"Ba na so tunda sai na roƙa" murmushin ya sake yi wanda bai ko kai ko ina ba, ya gaida Anty Saudat ita ma, sai da ta ja aji sannan ta amsa, ba abunda ya ce mata dai

Ya kalli Anty Sadiya ya ce "ina son magana da ke fa"

"Tashi mu tafi ɗakinka, nima ina buƙatar ƙarin bayani dan na ga message ɗinka ta whatsapp" a tare suka miƙe su ka bar parlourn

Hajiya ta ce "umm.. Dan Allah mu je mu kam muyi abunda za muyi"

Dariya suka yi saboda yanayin yanda Hajiya tayi maganar, ita su Umma da Momi suka nufi hanyar store room, matan kuwa suka wuce part ɗinsu, Sajida da Safna suka ɗauki akwatunan, Safwan kuwa da su Sameer sai suka wuce dinning dan yin breakfast, aka bar Uncle Sajeed da yaranshi a parlour

Safwan na gama breakfast ɗin ya wuce part ɗinsu, yana shiga ya tarar da su Tiger a parlour, ya ce "au wai har yanzu ba'a gama maganar ba?"

Anty Sadiya ta ce "mun gama... Sadeeq ka dai ji me na gaya maka, dole sai kayi haƙuri"

"Amma wallahi kin san dai zan cutu da yawa, har yanzu ina sonta kuma ba zan iya daina sonta ba har abada"

"Na sani Sadeeq, amma wannan shi ne kawai mafita"

Zama Safwan yayi ya ce "idan dai na fahimci zancen nan, kamar ki na so ki ce ne ya auri waccan yarinyar?"

"Eh haka nake nufi, ba yanda zai yi"

"Anty Sadiya wallahi ba ki san yarinyar ba ne shiyasa, sam ba ta da tarbiya, ni dai ban bada goyon baya ba, after all ma yana da wacce yake so fa, idan har muka takurawa Abba zai haƙura ne"

"Safwan ba yanda za'a yi muyi jayayya da iyayen mu, ba zan baku goyon baya ba nima, haƙuri ya zama dole, kuma ya aure ta, ban son wani dogon zancen, in dai na isa in bada shawara a ɗauka, to i'm done" ta tashi kawai ta bar musu parlourn

Safwan ya ce "wai yanzu kai ka anince za ka aure ta?"

Shiru yayi kafin ya ce "ba yanda zan yi Safwan, zan aure ta"

Da mamaki Safwan ya ce "are you in your senses(kana cikin hankalinka kuwa?) za ka aure ta fa? To idan ka aure ta ita kuma waccan da kake so fa, ka haƙura da ita kenan?"

"Haƙuri fa ka ce, ba zai taɓa yiwuwa ba har abada, zan auri wannan saboda ba zan iya ce ma Anty Sadiya a'a ba, ka sani.. Waccan ɗin kuma idan lokacin da nake jira yayi sai in ƙara da ita"

"Two wives? (Mata biyu?)"

"Yeah"

"Hmm, Allah ya bada sa'a"
Sadeeq dai bai amsa shi ba haka suka yi ta zaman kurame

Da yamma Abba ya sami Alhaji kampaninshi, sun daɗe su na fira kafin Kawu ƙarami ya zo ya same su

Ya ce "ashe kai ma kana nan"

Abba ya ce "eh, ai na ma ji daɗin zuwanka, dama zanyi magana da ku idan muka koma gida, to sai muyi yanzu"

Alhaji ya ce "lafiya?"

"Lafiya ƙalau, akan maganar Sadeeq ne da muka yi, yarinyar ta amince da shi, to shi ne Senator yake so ayi magana dan a cewarsa ba ya so a ja abun"

Alhaji ya ce "eh haka ne, nina ba zan so a ja shi ba, dan ma lokaci ya ƙure ne ai da sai a haɗa da na Safwan, amma yanzu ma ba matsala bari a kammala na Safwan ɗin sai mu sa rana"

"To shikenan, amma yana so dai kuyi magana tun da kai ne waliyinshi"

Kawu ƙarami ya ce "ni fa zan so ku fara tuntuɓar Sadeeq ku ji ta bakinshi, kar ayi mishi dole"

Abba ya ce "ko fa ba ya so sai yayi haƙuri, dan ba zan yi magana biyu ba"

Alhaji ya ce "a'a Usman, gaskiya Aliyu ya faɗa, dan haka anjima idan na koma gida, zan kira Sadeeq ɗin muyi magana"

Abba ba dan ya so ba ya ce "shikenan Allah ya kaimu lafiya... Bari in tafi, akwai wanda zan je wurinshi"

"Allah ya kiyaye" Alhaji da Kawu ƙarami suka ci gaba da fira

Kamar yanda Alhaji ya ce zai yi magana da Sadeeq idan ya dawo, hakan aka yi, ɗakinshi ya kira shi

"Sadeeq, Abbanka ya gaya mun zaɓin da ya maka, kuma yana so in je in samu Senator muyi magana.. Amma kafin nan, ina so in san ra'ayinka akan yarinyar, kana sonta ka amince za ka aure ta? "

Kasa amsa mishi yayi sai da ya sake cewa "Sadeeq kai nake saurare fa"

"Alhaji na amince zan aure ta"

Alhaji yayi mamakin jin ya amsa mishi kai tsaye, ya ce "kana sonta?"

"Alhaji musulmi ba zai ƙi ɗan uwanshi musulmi ba ai, na dai amince zan aure ta"

"To wacce kake so ɗin kuma fa?"

"Zan aure ta daga baya"

"Sadeeq ka tabbata har ranka kake bani wannan amsar?"

"Umm" ya amsa a gajarce

"To shikenan, Allah yayi maka albarka, ya sa alkhairi a tsakaninku"

Ce mishi kawai yayi "nagode" sai ya tashi ya wuce, Alhaji ya san waɗannan amsoshin ba su kai zuciyarshi ba, amma ya ƙyale shi kawai

Hajiya ta ce "yanzu auren nan ai sai anyi shi kenan, yaron nan fa bai so"

"Na sani amma ba abunda zan yi tunda kina jin me ya ce, na mu kawai addu'a ne"

"To Allah ya mishi zaɓi mafi alkhairi... Shi ma Abbansu ya nace ne wallahi, sai ɗazu Ummanshi ta mun bayani"

"Allah dai ya kyauta... Tashi ki haɗo mun tea"

"To, ameen"

Sunaiha na waya da Najeeb dan yanzu tana ɗan sake mishi, ta ce "yawwa Najeeb na manta ban gaya maka wani abu ba, ka taya ni murna"

"To Cutie gaya mun, menene? "

"Na ga prince ɗina"

Ya ji zafin maganar, amma ya daure ya ce "da gaske?"

"Wallahi kuwa, jiya na ganshi, yanzu ma Daddy ya gaya mun gobe Abbanshi zai zo suyi magana, shikenan buri na ya kusa cika, san zama matar prince" maganar take cike da murna

"Hmm, congrats"

"Thank u dear"

"Sai da safe zan kwanta"

"Ok, bye" ta faɗa ba tare da ta fahimci ranshi ne ya ɓaci ba, ta kashe wayar

"Oh Allah My Prince, Mummy ta hana ni zuwa ganinka yau, amma don't worry very soon zan dinga ganinki ko da yaushe,  Allah ya nuna mun auren mu, za ka sha love, nayi maka tanadi sosai, za ka ga salon soyayyar Ƴar Senator.... Tab, Sunaiha matar Sadeeq... I love you Prince" ta faɗa tana lumshe cike da farinciki

Daga ɓangaren Najeeb kuwa, yana kashe wayar ya ce "tabɗi, ta ga prince fa, ai wallahi ba zai yiwu ba, ba zan iya haƙura da ke ba Sunaiha, dole zan san waye wannan prince ɗin dan in raba ku....to idan kuma Allah ya rubuta cewa matarshi ce fa?... Impossible, ai wallahi ko aure kika yi Sunaiha ba zan ƙyale ki ba, ke ta wa ce ni kaɗai, ke ta Najeeb ce ba Prince ba".......

♦💫♦💫♦

*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

_Always ask God to give u what u deserve, not what you desire.It's bcoz your desires may be few, but you deserves a lot!_

*PAGE 19-20*

Kamar yanda suka tsara haɗuwa Alhaji da Daddy, hakan aka yi, har gida Alhaji ya zo ya same shi, Shi da wasu abokanan shi guda biyu, shi kuma Senator tare yake da abokinshi, cikin kamala da dattijantaka suka tattauna akan yaran na su, Alhaji ya tabbatar mishi da bayan bikin Safwan da kwana uku in sha Allah za su kawo kayan lefe da sadaki sai a sa rana, dan gaba ɗayansu ba so suke yi a ja bikin zuwa wani lokaci ba musamman ma Senator, cikin farinciki suka yi sallama suka wuce

Baƙi sun fara cika gida kasancewar gobe za'a fara shagalin biki, Umma ta fito harabar gidan suka haɗu da Anty Saudat tana ƙoƙarin shiga ciki, ta ce "yawwa Umma tun safe nake nemanki, ganinki yayi wuya a gidan nan yau"

Dariya Umma tayi ta ce "to gani, lafiya? Ba kun gama duk wani shirinku ba?"

"Umma mun gama, duk ba wannan ba, ɗan matso ta nan dan Allah"

Komawa suka yi gefe wurin flowers suka tsaya, Umma ta ce "menene wai?"

"Umma jiya da daddare da za mu kwanta Anty Sadiya ta ke gaya mana wani zance, abun ya tsaya mun a rai wallahi.. Wai Abba yayi wa Sadeeq zaɓen mata"

Lokaci ɗaya fuskar Umma ta sauya, ta ce "haka ne Sauda, ni kai na abun nan ba da son raina zai faru ba, yanzu ma maganar nan da muke dake, su Alhaji sun tafi gidan su yarinyar"

"Tabɗi, amma meyasa Abba zai yi haka?"

"Sauda ko da ace Abbanku yana da laifi kin san Sadeeq ya fi laifi ko! Sau nawa ake tambayarshi zancen yarinyar da ya ce yana so amma yana ƙyale mutane"

"Whatever dai Umma, ke kin san hakan bai dace ba, sai kace dai wata mace?! Auren dole fa!"

"Umm, Sauda ki aje wannn maganar ma, ki je kiyi aikin gabanki" ba ta jira cewarta ba ta wuce abunta

Ita dai sam abun nan bai mata daɗi ba, ji take yi kamar ita za'a yi ma wannan auren, duk da ta san namiji ne zai iya auren wasu, amma ba ta ji daɗi ba, juya wa tayi ta nufi part ɗinsu Sadeeq ɗin, ta ƙofar baya ta bi

Tana shiga kuwa ta tarar da zai fita kallonta yayi ya ce "Sister lafiya?"

"Sadeeq zaɓin auren da Abba ya maka ne bai mun daɗi ba wallahi ko kaɗan, Sadeeq kan sonta kuwa?"

Numfashi ya sauke kamr ba zai yi magana ba, sai kuma ya ce "Sister ba zan ce miki ba na sonta ba, amma ina da wacce nake so"

"To meyasa ba ka gaya mun ba tun farko, da ni zan samu Abba da kai na in mishi bayani, zai haƙura, amma ka ƙyale ni ba ka gaya mun ba, ga shi ance har Alhaji ya je gidansu"

"Kaddara ta ce a haka Sister, don't worry"

"Wane irin don't worry Abbakar!? Ka san yanda auren wanda ba ka so yake da zafi kuwa a rayuwa? Ko wuri ɗaya aka haɗa ka zama da wanda ba ka so an cutar da kai bare kuma zaman aure, Sadeeq ni ka ɗai na damu da damuwarka kai sam ba ka damu da ni ba, ina jiye maka

yanda za ka rayu da wacce ba ka so a matsayin mata... "

Katse ta yayi ta hanyar rufe mata baki da yatsarshi, Saudat tana matuƙar son Sadeeq a rayuwarta, ba ta son ta ga abunda zai sa shi cikin damuwa da shi da Sultana,  saboda su kaɗai ne ƙannenta da suke uwa ɗaya uba ɗaya, amma ganin yanda Anty Sadiya ke nuna kulawarta akan Sadeeq ɗin tun tashin su, hakan ya sa ita take ɓoye na ta, shi kanshi Sadeeq ɗin ya san da haka, shi ma ba son damuwarta yake yi ba sai dai ba ya nuna mata kamar yanda ita ma take yi

A hankali ya yanje hannunshi, ya ce "meye haka Sister?"

"Sadeeq meyasa ni kaɗai na damu da kai, kai ba ka damu da ni ba? Yanzu irin wannan ba za ka gaya mun ba sai dai inji a wani wuri bayan lokaci ya ƙure? "

"Stop saying that Sister, na damu da ke fiye da yanda kika damu da kanki, abunda ya sa ban gaya miki ba, na san za ki je ki samu Abba ki mishi magana kuma gidan nan zai iya ƙin jin maganar kowa amma banda ke, to kuma Anty Sadiya ta mun bayani idan har banyi wannan auren ba, Abba ba zai ji daɗi ba, he did alot to me, wannan ne ba zan iya haƙura ba?"

"Wannan fa abu ne daya shafi rayuwarka gaba ɗaya, aure ne fa!"

Rufe ido yayi a hankali ya buɗe, dan har ya gaji da maganar, ya ce "Sister na san meyasa kika damu har haka, saboda kin ɗanɗana irin haka ne kema a rayuwarki, amma there's difference between me and you (akwai banbanci tsakanin ni da ke), ke mace ce, ni kuma namiji ne, so kawai ki taya ni addu'a"

Shiru tayi tana nazarin maganarsa, ta ce "shikenan, Allah yasa hakan shi ne alkhairi"

"Ameen... Bari in wuce"

"Ina za ka tafi? Safwan fa?"

"A'a fa kin sani surutu da yawa, i'm tired(na gaji), ki neme shi, ni asibiti zan tafi" daga haka ya mayar da glass ɗinshi ya wuce yana ƙoƙarin sa face mask

Ƙarasawa tayi ciki sai ta haɗu da Sameer, ta ce "Sameer, Safwan fa?"

"Ina tunanin ya fita, akwai wurin da za su tafi sai kuma aka kira Oga Tiger asibiti wai ana nemanshi, shi ne ya wuce shi kaɗai"

"Ok, kai me za kayi?"

"Gidansu aboki na zan tafi"

"Dan Allah to zo in aike ka, idan kana dawowa sai ka biya ta gidana ka ɗauko mun abu"

"Ba matsala, mu je"
Tare suka fita daga part ɗin

Ƴan uwa da abokan arziki waɗanda ke wasu garuruwa duk sun zo, an gama duk wani tsare-tsare yanda komai zai tafi lafiya kamar ko yaushe

Hajiya ce ta kira Umma zuwa ɗakinta, suka zauna, ta ce "Aziza ɗazu Alhaji ya kira ni yake gaya mun wai sun tsayar da magana bayan bikin Safwan da kwana uku za'a fara na zancen na Sadeeq"

"To, Allah ya sa alkhairi ne, ni dai wallahi Yaya har yanzu ban san meyasa na kasa haƙura da wannan abun ba, yana damu na"

"Ki cire damuwa kuwa Aziza, tun da har kika ga muna ta rokon Allah ya tabbatar mana da alkhairin wannan lamarin, amma har yanzu maganar ƙara ƙarfi take yi, to in sha Allah akwai alkhairin"

"Allah ya sa, amma kin san halin Sadeeq, ni ba shi na fi ji ba, yarinyar da Allah ya haɗa shi"

"Ba abunda zai faru, ai tunda ita tana son shi, za ta san yanda za ta jawo hankalinshi kanta, mace ce fa"

"Hmm, to ban ce komai ba dai, amma da Safwan ne zan iya cewa za ta iya jawo hankalinshi cikin sauƙi, amma wannan me taurin zuciyar?!"

Dariya Hajiya tayi, ta ce "ke kika haifi Sadeeq, amm kin fi kowa shakkar halinsa"

"Ai dole ne Yaya, kar ya cutar da yarinyar mutane nake ji, da ace ma ba wacce yaje so ɗin ne, amma yanda yake son yarinyar nan ba kaɗan ba ne"

Dariya ta kuma yi, ta ce "ni dai ba ma wannan ya sa na kira ki ba, kin ga yanzu dai ita wannan yarinyar ya kamata ta halarci bikin nan, kin ga ko ba komai za ta san ƴan gida su ma za su santa, to nayi magana da Alhaji shi ne ya ce to a gayyato ta"

"Eh haka ne, shawara ce mai kyau, kin ga dama ba wanda ya santa a gidan nan.. To ya za'a yi kenan?"

"Ina Salma da Sultana? Su zo su tafi gidan"

"To ai ba su san gidan ba"

"Gidan Senator Mai doki ne fa, ai idan suka je unguwar gidan ba zai musu wahala ba"

"To shikenan bari in musu magana"

"Yawwa, nima gani nan fitowa yanzu"

"To"
Umma ta tashi ta fita, kai tsaye bayan gidan ta tafi dan ta san suna can, kiransu tayi, ta musu bayanin aiken, Sultana ta ce ai ta ma san gidan Senator ɗin saboda sun taɓa bi ta unguwar da Sameer ya ke gaya mata gidajen waɗanda je wurin

Umma ta ce "yawwa to abun ma ya zo da sauƙi, ku tashi ku tafi dan ku dawo da wuri"

Tashi suka yi suka shiga ciki, suka shirya sannan suka fito suka wuce

Salma ke driving, har suka kai unguwar, Sultana ta nuna mata gidan, horn suka yi, mai gadi ya buɗe musu gidan ya ɗan risina yana gaishe su, saboda ƙirar motar ta su ya tabbatar mishi da ƴan babban gida ne

Wucewa suka yi ciki, tayi parking motar suka fito, wata mai aiki suka gani ta nufi baya, sai suka tsayar da ita dan su ji ko masu gidan na ciki, ta gaya musu su na nan, godiya suka yi kafin suka wuce, ita kuwa sai da suka shige sannan ta iya wucewa saboda kallonsu kawai take yi

Mummy na ƙoƙarin haww stairs, ta ji sallamarsu, duk da cewar ba ta san su ba, amma da fara'arta take amsa musu, ta dawo

"Ku zauna mana" ta faɗa tana nuna musu wuri

Sai da suka zauna sannan suka gaishe ta, ta ce "amma ban gane ku ba, kuyi haƙuri fa"

Murmushi Salma tayi ta ce "ƙannen Sadeeq ne"

"Sadeeq?.... Oh sorry, ƴan gidan Saraki?"

"Eh"

"Allah sarki, ya gida, ya mamanku?"

"Lafiya ƙalau, ta ce a gaishe ki ma"

"Ina ansawa"

Sultana ta tashi ta miƙa mata basket ɗin da aka yi decorating da flowers sannan aka yi rapping ɗinshi da wani net mai shining, pink colour, ta ce "ga shi ta ce a kawo wa Antynmu"

Karɓa Mummy tayi tana bin shi da kallo, ta ce "na menene?"

"Na bikin Yayanmu ne, Ya Safwan"

"Ayya, ai kuwa ta gode, bari in kira muku ita.... Au, ban ma san sunan yaran ba" ta faɗa tana murmushi

Sultana ta ce "Sunana Sultana, wannan kuma Salamatu"

Duka Salma ta kai mata, ta ce "wallahi ba haka suna na ba, Sunana Salma"

Dariya Sultana ke yi, dan haka take mata duk lokacin da aka tambaye ta sunan Salma, ita ma Mummy dariyar take, ya ce "ƙyale ta kinji Salma, ai ta ma fi kama da Salamatu"

Dariya Sultana ke yi, ta ce "ba wani, ke take nufi, dan ke ce Salamatu ai"

Girgiza kai Mummy tayi, ta ce "Allah ya shirye ki, na fahimci ke kam ba kya jin magana"

Salma ta ce "wallahi kuwa"

Mumny dai na dariya ta haura sama, ɗakin Sunaiha ta shiga, kwance take tana kallo cikin laptop, Mummy ta ajiye mata basket ɗin akan gado

Kallonshi tayi, ta ce "Wannan fa?"

"Ƙannenki suka kawo miki, ki tashi suna parlour sai ki ji ko na meye"

"Ƙanne na kuma? Ni ɗin?"

"Ƙannen prince ɗin na ki nake nufi"

Tsaki tayi ta ce "ni fa ba na son iyayi wallahi, dama ana cewa dangin miji shegen iyayi ne da su ga takura, tun ba'a yi auren ba har sun fara biyo ni gida! Ni fa ba su nace ina so ba"

Mummy ta ce "iko sai Allah, lallai kuwa ba ki so zaman lafiya ba in dai haka za kiyi, su na parlour su na jiranki, idan kin ga dama ki je ki same su" daga haka ta fita, sai da ta koma parlour ta tarar har an kawo musu drinks da snacks sai dai ba su ko taɓa b, ta gaya musu su jira ta kaɗan tana zuwa, sai ta wuce

Kusan mintuna sha biyar suka yi a zaune ba ta fito ba, Sultana haushi ne ya cika ta, ta ce

"Salma wai matar nan na da niyan fitowa kuwa? Ni fa kin san wulaƙanci da rainin hankali ne ba na so"

Salma ta ce "kin riga ni magana ne kawai, dalla tashi mu tafi"

Miƙewa suka yi za su wuce, sai ga ta ta sauko, tafiya take ɗaya bayan ɗaya tana musu wani kallo har ta ƙarsao cikin parlourn, ta ce "sannunku"

Wani wawan kallo Sultana ke mata, ta ma kasa cewa komai, Salma ce ta ce "sannu"

Daga hak ba ta ce musu komai ba ta ci gaba da danna wayarta, ga su a tsaye su na kallonta, tsaki Sultana tayi ta juya ta fita, Salma ce mai ɗan sauƙi, ita ta iya ce mata "sai anjima"

Ko ɗaga kai ba tayi ta kalle ta ba, ta ce "uhm" ita ma Salma ta fita ta samu Sultana tana juya motar, sannan ta tsaya ta buɗe motar ta shiga suka bar gidan, ba wanda ya ce komai har suka isa gida, kuma ba su nemi Umma ba bare ma su ba ta labarin yanda aka yi, kawai suka shiga sha'anin su

Mummy kuwa tana ganin Salma ta fita, ta sauko da duk abunda Sunaiha ta yi musu a kan idonta ne

"Sunaiha wace irin rayuwa ce dake fisabilillahi? Yaran nan saboda ke suka zo, amma ji wani wulaƙanci da kika musu! Kannen wanda za ki aura ne fa, kina da labarin har da su idan kika bi su za ki ji daɗin zaman gidan aure?! Kuma Sunaiha waɗannan sun fi ƙarfin wulaƙanci ko a wurin ubanki ma da yake Senator bare kuma ke ƴarshi, idan ba ki san labarin ƴan gidan Saraki ba, ki tambayi uban naki zai miki bayani"

"Mummy dan Allah ya isa, ba so nake ina gaya miki magana mara daɗi ba, amma ke kullum burinki ki ɓata mun rai.. Yanzu dan Allah idan va so kike su raina ni ba, ta ya kike tsammanin zan sake musu fuska? Su ƴan uwan miji da kike gani, idan suka ga mutum ya sake musu fuska sai ki ga duk sharar da suka ɗauko a kanka za su sauke shi, amma irin haka da na musu shi zai sa ki ga sun kama kansu"

"Wai ke kullum al'amarin ki gaba yake yi? Magana nake amma shiga yake ta kunnen dama yana fita na hagu, ni kike gaya ma halin ƴan uwan miji?.... Shikenan dai, na fahimci duk yanda zan miki bayani ba za ki iya gane me zan gaya miki ba, Sunaiha ba zan miki baki ba, amma idan ba ki gyara halinki ba, namiji shi zai gyara ki... Allah ya bani ikon daina miki magan akan wannan halin na ki, kiyi yanda kike so"

Rai a ɓace ta bar parlourn, ita kuwa Sunaiha ko a jikinta, ta ci gaba da danna wayarta

Da daddare kowa na part ɗinshi, baƙi ma suna na su ɓangaren, ƴan matan ne zaune a parlournsu, sun kasa yin bacci sai fira suke ta faman yi banda Safna da tayi bacci, kowa na faɗin irin kwalliyar da zai yi gobe dan gobe za'a fara da Fulani's day

Sultana dai tana gefe komai ba ta ce musu ba, Anty Sameera ta ce "Sultana wai ke ba ki gaya mana kalan haukan da za kiyi ba"

Sajeeda ta ce "ni kam tun ɗazu na ga sai wani ɓata rai take tayi"

Salma ta ce "kun san fa halin mutumiyar, wani zubin haka take kaman Tiger"

Anty Sadiya ta ce "wa ya ɓata mata rai?" ta tambaye ta, dan sun san shi ne kawai abunda zai sa tayi haka, in dai abu ya ɓata mata rai, ta kan daɗe tana tuna wannan abun, sai tayi ta baƙin rai

Salma ta ce "ba ɗazu kin ji Umma ta aike mu ba?"

"Eh"

"To, ita wannan matar da Tiger zai aura ta mana wani ɗan iskan wulaƙanci, na rantse ji nayi kaman in kafta mata mari"

Sultana cikin ɓacin rai ta ce "shiyasa na fita, dan wallahi da na ƙara minti ɗaya a wurin wallahi da sai anyi mara daɗi ni da ita... Anty Sameera kin ga wani rainin hankali kuwa! Mun daɗe fa muna jiranta sai da ta ga dama sannan ta wani zo tana rangwaɗa tana mana kallon uku saura kwata, ta zauna, wai sannunku.. To gaya mata aka yi ciwo muke yi da za ta wani ce mana sannu?!"

Anty Sameera ta ce "ita kuwa wannan haka take? Ko dai ba ta gane ku ba?"

Sultana ta ce "ba ta gabe mu ba?"

Salma ta ce "wallahi ta gane mu duk salon iskanci ne"

"Eh lallai akwai magana" cewar Anty Sameera

Anty Saudat ta ce "wane magana! Ai wallahu ubanta za ta ci, ba dai Sadeeq ba ne, in dai ta ce da wannan halin za ta shigo to zai gyara mata zama"

Sajeeda tayi dariya ta ce "episode by episode kenan"

Anty Sadiya ta ce "hmm, Allah ya shirye ta to, amma sai nake ganin da ƙyar Sadeeq ya mata wani abu, wannan miskilancinshi ma zai iya bari ya tsaya har ya fahimci halinta? Muyi mata

magana dai"

Anty Saudat ta ce "wa zai mata magana? Ni kin ga ban ma santa ba ko, amma wallahi har ta bani haushi"

Anty Sameera ta ce "umm, Allah ya musu magani, ni dai bari in je in kwanta, kun san dai gobe idan aka tashi da asuba ba zancen sake kwantawa" ta miƙe ta shige tsohon ɗakinta
Haka su ma su Salma, Sultana da Sajeeda suka wuce kowa ya shiga ɗakinshi, Anty Sadiya da Anty Saudat kuwa sun daɗe suna fira kafin suka je suka kwanta

Su ma iyayensu gaba ɗayansu su na ɗakin Alhaji saboda ya kira su

Alhaji ya ce "abunda ya sa na kira ku, da zan dawo na biya wurinsu Baba(grandpa), nayi mishi bayanin komai da ya shafi Sadeeq da Sunaiha ɗin, shi ne ya bada wata shawara kuma na ga hakan zai fi"

Hajiya ta ce "wace shawara?"

"Ya ce a maimakon a ce anyi auren Safwan, sannan cikin kwanaki kaɗan a sake cewa za'ayi na Sadeeq, duk mutanen da suka zo daga nesa kuma su sake dawowa, why not a ɗaura auren lokaci ɗaya, in ya so daga baya ku mata sai kuyi bikinku, amma mazan nan da yawa aikin su suka baro suka zo, kawai gwara a haɗa"

Kawu ƙarami ya ce "wannan shawara ce mai kyau kuwa, hakan ya kamata a yi, ko ya ka ce?" ya ƙarasa yana tambayar Abba

Ya ce "a'a ai hakan yayi, ba wata damuwa, su ma dai dan sun mayar da bikin kamar dole ai da ban ga amfanin yin bikin ba kuma"

Umma ta ce "a'a kamar ya ba sai anyi ba"

Hajiya ta ce "ai shi ne, biki kam wajibi ne ma sai anyi, idan ba haka ba ita kanta yarinyar za ta ji ba daɗi ne"

Momi ta ce "ai auren ma dan Baba ne yayi magana, da sai in ce shi ma da bari aka yi a yi na su daban, a tsanake kamar yanda aka yi na kowa"

Kawu ƙarami ya ce "ai kinji dalilin da ya sa za'a haɗa, kuma ma ɗaurin aure har wani shiri ake masa? Dama mutane ne kawai ake buƙata, ku. A duk waɗanda aka gayyata a na Safwan su ɗin ne dai kowa zai sake gayyatowa a na Sadeeq ɗin, da mu da su yaran su kansu"

Alhaji ya ce "haka ne... Yanzu dai gobe idan ɗaya daga cikinmu ya samu ganin Sadeeq ɗin ko Safwan sai ya gaya musu, ko ni ko kai Usman ko kai Aliyu, dan nasan gobe iyayen nan na su

mata ba su da lokacin mu ma bare na yaran" ya ƙarasa da sigar zolaya

Dariya su kayi, Umma ta ce "ai ku ma kun sani kam"

Sun ɗan taɓa hira, kafin suka tashi kowa ya wuce part ɗinshi su ka kwanta........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_Do not count what u have lost, Just see what u have now, because past never comes back, but sometimes future can give u back ur lost things…🤗_

*PAGE 21-22*
~~~~~~~~~~~~~~

Kamar yanda aka shirya events din da za'a yi, yau ake fulani's day, kap ƴan matan sun yi shigar fulani tun daga sama har ƙasa, har yanayin kitson kansu na fulanin ruga ne, suka yi kwalliyar su so simple ta ƴan ƙauye, ba ƙaramin kyau suka yi ba masha Allah, sai kyaun na su ya sake fitowa kamar ka sace su

Haka suka fito suka haɗu da sauran ƴan biki suka nufi harabar gidan suka shige motoci, su Sameer da Sauban, Aymaan da Saif (abokan nan su Safwan da Sadeeq), su ne suka ja motocin har wurin bikin, su ma kayan fulanin ne a jikinsu, sai dai wando jeans suka sa, baƙi

Gaba ɗaya waɗanda suka halarci bikin duk irin shigar su suka yi, amarya na kayan fulanin ne sai dai na ta blue ne ba fari ba, ta sha ado masha Allah, tayi kyau sosai, dama ita ma ba baya ba in dai kyau ne

An daɗe ana ta hidimar biki abun gwanin burgewa, kafin Safwan da Sadeeq suka ƙaraso, amma Sadeea bai fi minti goma ba ya bar wurin, su kuma sai kusan magrib sannan suka kammala bikin

Sannan kowa ya wuce gida.  Salma, Sultana, Sajeeda da Safna ne kawai suka bi tawagar amarya saboda yanda ta dage sai sun biyo ta, a can suka yi sallar magrib da isha'i, sai kusan ƙarfe goma sannan aka maido su gida

Ɓangaren Sunaiha kuwa, tun bayan la'asar suka fita da Najeeb suka zaga gari sai dab da sallar magrib sannan ya dawo da ita

"Cutie i'm so happy, ban taɓa tsammanin za ki yarda muje outing ba"

Murmushi tayi ta ce "ba abun mamaki ba ne ai, ka san meyasa na yarda?"

"A'a sai kin faɗa"

"Saboda satin nan gaba ɗaya ina cikin farin ciki fiye da tunanin ka, shiyasa nake kokarin kyautatawa wasu"

"Ke kuwa me ya faranta miki rai har haka?"

"Prince mana. Ka san kuwa nan da kwana uku za'a yi aure na da Prince!"

Drink ɗin da ya kurɓa ne ya sarƙe shi saboda yanda maganar ta razana shi, ya ce "aure?? Aure fa kika ce Cutie! Within three days za kiyi aure?!"

"Eh mana, meye abun tsorata kuma bayan ka san da zancen, ai na gaya maka na samu Prince ɗina, daga haka kuwa ai kasan sai zancen aure kuma"

Shiru yayi naɗan lokaci, ya ce "amma Cutie kin mu adalci kenan?"

Wani irin kallo ta mishi ta ce "adalci kuma? Dama na taɓa gaya maka ina sonka ne? Ai tun farkon haɗuwarmu na gaya maka ina da masoyi, to meye abun ɓacin ran kuma?"

Maganar ma ƙin fita tayi saboda tsananin mamakin da yake ciki, kusan mintuna biyar bai ce mata komai ba, ta ce "Meye kuma Najeeb!"

Da ƙyar ya ita faɗin "ba komai, i'm going home"

Ɗaga kafaɗa tayi ta ce "ok bye" ta buɗe motar ta fita, shi kuma ya daɗe cikin motar kafin ya iya wucewa

Tana shiga gida kai tsaye ɗakinta ta wuce, sai da ta watsa ruwa tayi sallah sannan ta fito ta nufi ɗakin Mummy, tana zaune kan sallaya tana karatun Qur'ani, sai ea ta kammala kafin tayi addu'a ta miƙe tsaye ta ninke sallayar da hijab ɗinta ta ajiye a ma'adanarsu, ta nufi hanyar toilet

Sunaiha ta ce "Mummy ba ki ganni ba ne?"

Kamar ba za ta mata magana ba, sai dai ta juyo ta ce "na ganki mana, ya aka yi?"

"Hmm.. Mummy kin sauya, menene?"

"Babu" ta amsa mata a gajarce, ta shiga toilet

Lokacin da ta fito Sunaiha na nan a zaune tana chatting, kujerar mirror ta ja ta zauna tana goge jikinta, Sunaiha ta ce "Mummy gobe zan tafi event ɗin su Prince, Arabian Night"

"Allah ya kaimu lafiya"

"Ameen Mummy" haka suka ci gaba da zaman kurame har Sunaiha ta gaji ta wuce ɗakinta kafin Daddynta ya dawo, Mummy kuwa tana sane take ta ƙyale ta yau

Tiger kuwa da daddare yana ɗakinshi kasancewar abokanansu, Aymaan da Saif suna nan parlour su na ta fira da su Sameer, sai ga Safwan ya shigo, lokacin ya tarar da yana waya, yana shigowa, Sadeeq yayi sallama ya kashe wayar

Tiger ya ce "ango, ka kuɓuto?"

"Bari kawai, na gaji wallahi yinin yau kawai, to bare kuma jibi da za'a ɗaura auren.... Wai ma ka

ce ango, angwaye dai"

"Hmm"

"Sadeeq wallahi bari in gaya maka gaskiya, na rantse da ina da iko ba za ka auri yarinyar nan ba, ni sam ba ta burge ni, amm na rasa meyasa Abba ya nace akan sai ka aure ta, ita ma Anty Sadiya ta haka wannan shawarar.. Da yake ma dai her wish is your command, yanda take so haka kake yi, amma wannan yarinyar ba matar aurenka ba ce, ba ku dace ba"

Kallonshi kawai Sadeeq yake yi, ba abunda ya ce mishi, sai ga su Aymaan sun shigi, Saif ya ce "wai Tiger ba zaka taɓa sauyawa ba ko, ɗazu sai nemanka nayi na rasa, aka ce ai ka daɗe da barin wurin, wai tsoron mutane kake yi ne? Kai kullum ka fi so ka zauna kai kaɗai"

Aymeen ya ce "dalla ƙyale ɗan rainin sense, ai yanzu dai aure zai yi, sai in gani idan kullum yana ɗakinshi tana nata ne, mu yake ma wannan rashin mutuncin, matarshi kuwa gyara mishi zama za tayi"

Dariya Safwan yayi ya ce "tirƙashi, wa ya ga mace ta gyarawa Tiger zama" ya sake sakin dariya

Saif ya ce "ni faɗan ma da nake so zanyi da shi kenan, yanzu Tiger ashe har da kai aure za kayi shi ne ba sanarwa! Ka daina wannan rayuwar ba me kyau ba ce wallahi"

Safwan ya ce "ya ce zai yi Suprising ɗin mutane ne that's why" Safwan ya faɗi hakan ne dan ba so suke a san auren dole Tiger zai yi ba

"Whatever dai Safwan, yanda muke da ku bai kamata a ce har mu muna cikin waɗanda za'ayi suprising ba"

Safwan ya ce "to kuyi haƙuri "

Aymaan ya ce "shikenan.. To amma ban ga ta shi amaryar ba ɗazu"

"Za ku ganta in sha Allah"

Haka dai suka ci gaba da firar ba abunda Tiger ya ce musu sai kace wani kurma, har su ka gaji suka wuce domin su kwanta

Washe gari ma haka aka tashi da hidimar bikin, tun safe suke ta hidima suna fama da mutane, Sadeeq na so yayi magana da Anty Sadiya amma ya kasa shiga cikin gidan saboda yawan mutane, ga wayarta a kashe

Sai kusan la'asar kafin ya samu wayarta ta shiga, ya gaya mata yana son ganinta, part ɗin su Alhaji suka haɗu kasancewar ƙofar bayan gidan ta gefen su yake

"Oga Tiger ya aka yi?"

"Anty Sadiya kin ga auren nan an haɗa shi da na Safwan nan d three days, sannan kuma wai sai a dawo a sake yin wasu events daban, wahalar za tayi yawa, kiyi ma Umma magana dan Allah ba sai anyi wani event ba"

"Meyasa kuma? Ka taɓa ganin auren da ba event ko ɗaya? Sai ka ce wata bazawara!"

"Anty ba haka bane, ni wannan taron ne ba zan iya ba.. Please help me"

"Shikenan na ji, amma to tunda ka ga gobe za'ayi dinner sai a haɗa kawai, jibi kuma idan aka ɗaura aure da safe da yamma za'ayi walima shi ma sai a haɗa"

"Walimar dai, amma ba zancen yin dinner"

"A'a Sadeeq... "

"Dan Allah Anty Sadiya, just say yes"

"Hmm, to zan mata magana"

"Yawwa, nagode" sannan ya miƙe ya fita ita kuma kai tsaye wurin su Hajiya ta wuce

Ta kira Umma gefe ta mata bayani, ta kuwa amince da hakan, dama tayi wannan tunanin ita ma, ta gaya mata za ta yi ma Hajiya magana

Bayan sallar magrib aka fara shirin wucewa wurin arabian night ɗin, mata sukayi shirin jallabiya baƙi maza kuma fari da makawiya, amarya kuma jallabiya kalar ja ta saka ango kuma baƙi, arabian dishes aka yi da haɗin lipton ɗinsu, waƙoƙin larabawa ke tashi, daga bisani kuwa suka fara gabatar da programs ɗin da suka shirya yi na larabawa

Sai ƙarfe takwas sannan Tiger ya zo, ya sa baƙin jeans da farar jallabiyarshi mai kyau, sai dai bai saka makawiya ba, gashin kanshi kawai ya gyara, yayi kyau sosai kamar balaraben gaske, yana nan jikin motarshi ya ga shigowar wata mota

Hajiya Sunaiha ce, ta sha jallabiyarta baƙa ita ma, da ɗan simple makeup ɗinta, kallo ɗaya ya mata ya ci gaba da wayar da yake yi, sam ba ta ma lura da shi ba, tana tsaye a wurin sai ga Salma da Sajeeda sun fito daga cikin hall ɗin, a hankali Salma ta gaya wa Sajeeda ga Sunaihar Tiger

"Wow!! Masha Allah, Salma she's so cute"

"Yeah, she's cute amma ba hali... Wallahi ba dan da mutane ba Allah bazan gaishe ta ba"

Sajeeda ta ce "nikam gaida ita zanyi"

Wurinta suka nufa, suka gaishe ta, ba ta so amsawa ba, amma ganin Salma ya sa ta amsa ba yabo ba fallasa, Sajeeda ta ce "zo muje ciki in gabatar da ke"

Cikin salon tafiyarta ta izza, ta bi bayansu suka koma cikin hall ɗin tana bin wurin da ido, ya sha decoration sosai fari da baƙi, ballons kuma fari da ja, sai glubs multi colours da ke ƙara ƙayata wurin, kallonsu kawai Tiger ke yi har suka shige, ya ce "Hmm" Allah kaɗai ya san abunda ke ranshi, ya daɗe wurin kafin ya shiga ciki, daga farkon hall ɗin ya samu kujera ya zauna

Har aka kusa gama event ɗin sannan ya bar wurin, ƙarfe 9:21pm, Sunaiha ta fito ba tare da tayi sallama da kowa ba, ta wuce gida, ƙarfe goma aka gama komai, suna shirin wucewa, Nasreen(amaryar Safwan) ta tambayi Sultana ina Sunaiha, Safna ta gaya musu ai ta daɗe da wucewa, murmushi tayi ta ce "an dace kenan, wannan kam da alama yanda mijinta yake haka take"

Sultana tace "ke ma dai kya faɗa Anty Nasreen"

"To Allah ya kyauta" suka wuce wurin mota, yau Safwan yaraka amaryar shi har gida, Saif yayi driving ɗinsu, su kuma su Salma yau ba su bi ta ba, gida suka wuce kai tsaye

Kafin dawowar ƴan bikin ne, Umma tayi Hajiya bayani a kan maganar su ta ɗazu da Sadiya, da farko ta nuna rashin amincewarta, amma daga baya kuma ta yarda da hakan, ta ce za tayi ma Alhaji magana zuwa dare idan ya shigo dan su samu su gaya wa Senator, su ma idan akwai shirin da za suyi sai su sani

Umma ta ce "amma Hajiya kuma nake ganin ya kamata a ce by now mun san mahaifiyar yarinyar nan, itama ta san mu"

"Ni kaina nayi wannan tunanin, ina ganin gobe sai ki tafi gidan na su sai ku tattauna da ita ma"

Murmushi tayi ta ce "to meye amfanin ki in har ni zan tafi? Sadeeq ɗinki ne fa"

Dariya tayi tace "haka ne, to Maman Salma(Momi) za ki raka ni sai mu tafi"

Momi dake jin su tun ɗazu tace "a'a Hajiya, idan ja bi ki wa zai taya ta kula da baƙin? Ki je kawai mu muna nan"

"To ya muku kyau, zan tafi ɗin" dariya suka yi suka ci gaba da maganar, Momi ta musu sallama

ta wuce ɗakinta saboda ta gaya musu kanta na ciwo

Tana shiga part ɗinta ta ɗauki wayarta tayi kira, "Hello"

"Anty Basira, ya gajiya" aka amsa daga ɗayan ɓangaren

"Alhamdulillahi"

"Kiyi haƙuri ban shigo event ko ɗaya ba, wallahi uzuri ne, amma dai gobe zan zo"

"Ki ɗin kam, dan ina nemanki"

"Lafiya kuwa Anty Basira?"

"Da sauƙi dai"

"Subhanallahi, to Allah ya ƙara sauwaƙe mana... Sai gobe ɗin to"

"Yawwa, ki gaida mun Yaya"

"Za taji" suka kashe wayar

Ɓangaren Najeeb kuwa, tun jiya yake cikin damuwa, tabbas ya san da labarin prince kuma ta gaya mishi ta ganshi, amma abunda ya ba shi mamaki wai har an sa ranar aurensu

"Yanzu yarinyar nan rasa ta zanyi kenan?... Impossible!!" ya faɗa da ƙarfi yana dukan kujerar da yake zaune a kai

Yayanshi da ke zaune ya ce "Najeeb kana da lafiya kuwa?"

"Wane irin lafiya kuwa Bross, wacce nake so ce ke shirin yin aure"

"Aure fa? To kai ba ka sani bane? Dama ba ta sonka?"

"Wannan kuma it's secret, amma wannan abun ne ba zai yiwu ba"

"Me kenan? Auren ko me?"

"Cire ta a raina dai, wallahi Bross i'm in love with her"

"Daga baya kenan ai, dole ka cire ta a ranka yanzu tunda matar wani za ta zama"

"Wa?! Ai wallahi idan ka ga na cire ta raina to mutuwa nayi, amma wallagi ko aure tayi ina tare da ita sai wurin da ƙarfi na ya ƙare"

"Ka na tare da wahala kuwa Najeeb, na ka wasa ne... Nikam sai da safe" ya miƙe ya wuce ɗaki

Najeeb ya ce "hmm Bross kenan, it seems like ya manta waye Najeeb, duk abunda na sa ma raina to sai na same shi ko ta wane irin hali ne, idan kuwa aka ce ba zan samu ba sai dai ayi two zero.... Cutie you choose prince over me ko! Za ki gane, i know what to do"......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_A relationship should have determination & purification like a MIRROR... Which never loses its ability to REFLECT even if BROKEN into thousand pieces..._
~~~~~~~~~~~~~~~~

*PAGE 23-24*

Hajiya ce da Mummy zaune a parlour, sai Salma da tayo rakiya, Hajiya ta ce "to kin ji abunda muka tattauna jiya, amma fa idan ba takura"

Murmushi Mummy tayi ta ce "a'a ba wata takura, jiya da daddare munyi maganar da Alhaji ai kasancewar Alhaji Muhammad ya kira shi"

"Eh jiya ne da na gaya mishi, sai ya ce to zai kira Senator suyi magana"

"Ba damuwa Hajiya, ai nan da kwana biyu ne ɗaurin auren da walimar ko, ya isa ai mu gayyaci mutane tunda dama ba wasu mutane da yawa zan gayyata ba ni, ita ma Sunaihar ba ƙawaye ta ke da su ba, shi ɗin ne dai kuma kin ga maza ai wurin auren kawai za su tafi"

Hajiya ta ce "nayi tsammanin ko ƴan uwanta za su haɗa wani event ne ai"

"Ƴan uwanta ɗin da nake tsammanin za su iya haɗa wani event ɗin in ma za suyi ɗin kenan, ba ƙasar nan suke ba, kuma da muka yi magana da su cewar an sa ranar auren Sunaiha, sun gaya mun ba za su samu shigowa ba dan lokaci ya ƙure musu sai dai bayan biki za su zo"

"Allah sarki, to shikenan tun da ba matsala... Gobe in Allah ya yarda zan aiko mata da kayan da za ta saka ranar walimar"

"A'a Hajiya kar ki damu, za mu shirya komai... "

Katse ta Hajiya tayi da "kar muyi haka da ke, ai na san tsab za ku iya haɗa komai ko da a kwana ɗaya ne, amma ordering kayan za mu yi, the same design da na Nasreen, haka muke so su fito"

Mummy tayi dariya ta ce "to Hajiya, mun gode"

"Na shiga uku, godiya kuma na me? Ai an zama ɗaya, Sunaiha ai ta zama ƴar mu kuma, duk abunda aka yi mata ta cancanta ne"

"Haka ne, Allah ya ba mu haƙurin zama da juna, ya kaimu ranar"

"Ameen" sun ɗan fara taɓa fira, Salma na ɓara fuska ta ce "Hajiya mu tafi"

Mummy ta ce "Salma gidan namu har ya ishe ki?"

Murmushi kawai tayi, Hajiya ta ce "kin san yau za a yi dinner, suna can su na shirye-shirye, duk ji take na takura mata"

Mummy ta ce "ai kam ba dađi"

"To tashi mu tafi, tunda ta biye miki"

Mummy dai dariya tayi, Salma kan har ta kai ƙofar parlour tana ƙoƙarin fita, Hajiya ta ce "wai nikam ban ga ƴar ta wa ba"

"Ta đan fita ne shiyasa"

"Ayya, to ki gaishe ta, sai anjima" suka yi sallama suka wuce

Mutane na cikin gida suna ta hidimar bikinsu, Momi kuwa tana đaki tare da Sarah, ƴar Yayarta ce

"Anty Basira jiya muna magana, kin ce akwai matsala, lafiya dai?"

Wani kallo ta mata, ta ce "wane irin lafiya kuma? Kina da labarin jibi auren Safwan da Sadeeq za a yi!"

"Sadeeq kuma?"

"Kwarai kuwa"

"Shi ne ba sanarwa?"

"Oh, ke abunda ya dame ki ma kenan? Sadeeq fa na gaya miki zai yi aure"

"To Anty Basira me zan ce? Allah ya sa alkhairi Ya ba su zaman lafiya"

"Tooo!!! Sarah kan ki đaya kuwa? Ina soyayyar da kike yi wa Sadeeq đin? Ina son yake da har nake gaya miki zai yi aure amma kike wannan addu'ar"

"Kina bani mamaki Anty, na sani na yarda na so Sadeeq, kuma har yanzu ina son shi a raina, amma tun ranar da ya gaya mun inyi haƙuri yana da wacce yake so kuma Anty Sadiya ta gaya mun, sai na haƙura saboda mutunci na ya fiye mun komai, dan haka tunda har ya samu zai auri wacce yake so đin ni ban ga abun tashin hankali ba, nima Allah ya ba ni wanda ya fi mun shi alkhairi"

"Tabđi! Sarah?!... To ai wacce zai aura đin ba ita ce yake so ba"

"Anty Basira, dan Allah ki ajiye wannan maganar, ko ma wacece ni ba abunda ya shafe ni ba

ne.... Ni kin ma ga tafiya ta, ina can cikin mutane ina aiki na kika kira ni" tashi tayi ta bar ɗakin

Momi kuwa ta bi ta da kallo dan tayi mamakin yanda Sarah ta nuna rashin damuwarta akan auren Sadeeq ɗin, saboda ita shaida ce akan irin son da Sarah ke wa Sadeeq

"Sunaiha yanzu wai ke shikenan kin yarda da wannan auren sai ka ce wata bazawara?" cewar Ikram da ke waya da Sunaiha, misalin ƙarfe takwas na dare

"To meye a ciki Ikram?!  Ai ba kamar bazawara ba, wallahi ko kamar menene rai na ba zai taɓa ɓaci ba, Prince ne fa ko kin manta?"

"Amma ni dai ba'a kyauta mun ba saboda na so in raƙashe a bikin ƴar senator"

Dariya tayi ta ce "to a haka tsarin Prince ɗina yake, kuma dole kowa ya bi"

"Hmm, wannan Prince ɗin dai... Allah ya ba da zaman lafiya to"

"Ameen dearie... Ina zuwa kamar na ji muryar Daddy"

"Ok" ta katse wayar sannan ta miƙe

Tana sauka parlour kuwa ta tarar da Daddynta a dinning area yana waya, Mummy ta gama serving ɗinshi, mai aikinsu ta ɗauki wata kular da Mummy ta miƙa mata ta kai kitchen, tana juyowa ta buge Sunaiha dan bata san da ita ba

Ba ta tsaya ɓata lokaci ba ta ɗauke ta mari, a gigice ta ce "dan Allah kiyi haƙuri, wallahi ban gan ki ba ne"

"Za ki ganni ne ai, wawuya kawai, kina abu sai kace mahaukaciya, wallahi ki..... "

Riƙe mata hannu da Daddy yayi ne ya sa tayi shiru, Mummy tayi wa mai aikin alama da hannu tayi haƙuri ta tafi, Sunaiha kuwa ta ja kujera ta zauna tana raka ta da harara, bai fi mintuna uku ba ya katse wayar, sannan ya ce

"Baby kiyi haƙuri ki sassauta zuciyarki mana, ba na so kina yawan ɓata ranki akan waɗannan mutanen"

"Daddy ba ka ga abunda ta mun ba?"

"Ko ma me ta miki, kwantar da hankalinki, ke da very soon ma za ki bar musu gidan... Kin san ma da surukinki ne nake waya yanzu!"

Farin ciki ne ya ziyarce ta lokaci ɗaya, ta ce "menene Daddy?"

"Gaya mun yake gobe za'a kawo lefenki"

Murmushi take sosai da ya fito da dimples ɗinta, ta ce "oh God, Daddy sai nake jin komai tamkar a mafarki, nan da two days fa zan zama matar Prince ɗina da nake gani kamar wasa"

"Baby ni kai na daɗi nake ji  za ki auri Prince ɗinki"

"Mummy ke ba ki ce komai ba"

Tsaki tayi, ta ce "to me zance miki? Ni taimako ɗaya zan miki a bikin nan ai, na kira waɗanda za su miki gyaran jiki, in and out, sun ƙware sosai, gobe za su sauka a gidan nan, ba ke ba yawo kuma, ƴan garin nan tun safe za su zo su fara na su kafin ƴan Maiduguri da ƴan Sokoto su iso su ɗora da na su"

"A hakan ma kin taimaka Mummcy na" ta faɗa tana dariya

Mummy ta ce "Allah ya shirye ki.."

Ƴan dinner kuwa duk sun gama shirinsu, sai yau suka yi make up, sai dai light makeup ne, Sun sa ankon su na doguwar riga light blue sai style ɗin da aka musu da royal blue, kalan kayan Amarya kenan, royal blue, sai head ɗin ta light blue, veil royal blue, maza ma ɗinkin shadda suka yi light blue, aikin gaban rigarsu iri ɗaya, royal blue, Ango kuma shaddarshi royal blue, tun daga kan mutanen wurin har decorations ɗin, sun yi kyau sosai sun bada kala, gwanin burgewa, kowa ya hallara banda oga Tiger, dama zuwa dinner ba ya cikin tsarin shi, ko lokacin bikinsu Anty Sadiya, Anty Sameera da Anty Saudat, duk bai tafi wurin dinner ba

Sun gwangwaje sosai a wurin dinner, yau kam sai kusan 12 sannan suka watse, banda su Anty Sadiya da suka dawo tun goma da rabi, a gajiye suka dawo gaba ɗayan su hakan ya sa ba su tsaya dogon fira ba, suka yi wanka suka kwanta

Washe gari har ƙarfe goma ƴan matan ba su tashi ba saboda gajiya. Sultana ce ta fara farkawa, agogon ɗakinta ta duba, ta ce "kaii!! Yaran nan ma sun raina ni, shi ne aka rasa wanda zai tashe ni?"

Ta miƙe ta faɗa toilet, ba ta fi mintuna sha biyar ba ta fito sanye da doguwar riga ƴar kanti, kai tsaye parlourn su ta fito, amma ganin TV a kashe hakan ya sa ta fahimci ba wanda ya tashi, dan ko ba zaman kallo za suyi ba to sai an samu wanda ya kunna TV, ta bi ɗakunan ɗaya bayan ɗaya tana buɗewa duk suna ta bacci, sai dai Anty Sadiya ba ta nan da Anty Sameera

Tana buɗe ɗakin Anti Saudat, ta ga tana ƙoƙarin fitowa, ta ce "Sultana... Yau na makara ban san ya aka yi ba"

Sultana ta ce "ai ba ke kaɗai ba, yau kaman an mana magani wallahi, su Salma ma ba su tashi ba"

"To zo mu sauka ƙasa, yunwa ma nake ji ni"

Dariya tayi ta ce "su Anty Saudat sarakan ci"

"Zan mazge ki fa, kin raina ni da yawa"

Dariya ta kuma yi, kafin suka bi hanyar waje, daga bakin ƙofa suka tsaya baki a buɗe su na kallon ikon Allah, sai kallon juna suke yi kowa a tambaya a bakinshi

Sultana ta ce "Anty Saudat na waye wannan?"

"Ta ya zan sani kuwa Sultana!? Zo mu ƙarasa dai"

Akwatuna ne set huɗu masu kyaun gaske, ko wane set ɗaya yana da akwatuna shidda da kit, akwai Navy blue, dark purple, ash sai golden colour, ko iya akwatunan aka bar mutum da su ya ishe shi kallo, bare kuma abubuwan da ke ciki, abun ba'a cewa komai, naira ce ke magana

Zama suka yi, Sultana ta ce "Hajiya waɗannan kuma fa?"

"Hmm, wai na ki ne"

Da mamaki Sultana ke kallonta, ta ce "ni kuma Hajiya?"

"Eh, mu ma haka muka tashi da shi, Alhaji muke jira ya dawo ya mana cikakken bayani"

Kamar za tayi kuka ta ce "wallahi ba zan yarda ba ba rantse, shikenan kuma yanzu mu auren dole za'a koma yi a gidan nan! Wallahi a mayar da kayan mutane ma kafin ayi abunda ran kowa zai ɓaci.... " buɗe ƙofar da aka yi ne ya sa tayi shiru tana kallo ta ga ko waye, ganin Tiger ya sa ta miƙe ta ƙarasa wurinshi ta ce "Ya tiger wallahi ka gaya wa Alhaji ni ban tashi yin aure ba, ga Salma nan ai ta girme ni, ita a mata auren mana, wallahi ba na so... "

Katse ta yayi "shhh..! Waye ya ce zai miki aure yanzu to, ke wani lokacin ba ki da kai, kin san wannan shirmen na ku ba ya tsari na"

"Ya Sadeeq ba shirme ba ne fa, kalli ka ga wai waɗannan na wa ne, ban shirya ba wallahi... Kuma Hajiya ta gaya mun"

Kallon akwatunan yayi, yayi ɗan gajeren tsaki ya ce "to meye a ciki? Allah ya baku zaman lafiya" bai tsaya saurarenta ba, ya bi ta gefenta ya wuce

Ai kuwa ta hau kuka tana buga ƙafa, ƴan ɗakin sai dariya suke ta mata, Anty Sameera ta tashi tana rarrashinta, ta ce "ke Sultana ƙyale su, ba na ki ba ne, na Oga Tiger ne fa, wanda za'a kai gidan su Matar da zai aura"

A hankali ta ce "da gaske?"

"Eh, haba Sultana, wa a isa ya miki auren dole a gidan nan yanzu Safwan ya sa rigar lawyer mu shiga kotu, sai inda ƙarfinmu ya ƙare"

Murmushi tayi ta na ɓoye fuska alamun ta ji kunya sannan suka zauna, Hajiya ta ce "wai... Haloƙo, irin wannan masifa haka?" ta ƙarasa tana dariya

Sultana ta ce "to Hajiya ana zaman lafiya kawai ki ce ga lefe na, ta ina zan fara to, ai tunda aka yi wa Oga Tiger auren dole to kowa ma ba zai tsallake ba"

Dariya kawai suka yi, Anty Sadiya ta ce "ku muke jira dama ku zo ku ga kayan sai a tafi kai wa, motocin na hanya, je ki tayar da sauran"

Hajiya ta ce "ƙyale su dan Allah su gani a videon da kika yi, idan aka buɗe wani aikin za su kuma jawowa"

"To shikenan" an yi rapping ɗin akwatunan, an musu decorations sosai, shiyasa Hajiya ta hana a buɗe su

Ba'a fi mintuna goma ba sai ga mutanen sun ƙaraso, aka kwashi kayan, sai da aka fara kai ma su Grandma suka gani duk da su ma ba buɗewa suka yi ba, suka sa albarka sannan aka wuce da su gidan Senator

Tarba ta musamman aka musu a gidan Senator, an haɗa musu liyafa sosai. Duk wanda ya kalli zubin akwatunan da yanayin yanda aka ƙawata su sai ya ce Masha Allah, kowa ya matsu su wuce dan a buɗe akwatin a ga kayan da aka zuba, lokacin da za su wuce aka haɗo musu liyafar suka wuce da ita

Da gudu Ikram ta shiga ɗakin da ake gyaran amarya, Sunaiha ta ce "menene?"

"Sunaiha guest what!"

Ɗan girgiza kai ta yi tana jiran abunda zai fito daga bakinta, ta ce "yanzu ƴan kawo lefe suka wuce, kin ga kayan kuwa?"

Murmushi tayi ta ce "kaɗan daga aikin Prince ɗina kenan Ikram, na san zai iya mun fiye  da haka ma"

Matan da ke mata gyara suka ɗaga kai suka kalle ta kawai, wata ƙawarta ce ta sake shigowa

"Ƴar Senator... Congrats" ta faɗa cike da murna, "lallai yau na sake tabbatar da Prince ɗin nan da gaske yake yi, ashe ba ke kaɗai kika haukace akan shi ba... Wai kin ga kaya!? Ko set ɗaya ba'a gama buɗewa ba amma har na kusan suma saboda burge ni da suka yi, gaskiya kin dace Sunaiha, congrats once again"

Sunaiha tana wani hura hanci tana jin kanta, ta ce "ai ba ma za ki gane na dace ba sai kin ga Prince ɗin"

"Ai zan ganshi bayan auren in Allah ya yarda, although dai ya hana mu sha shagali"

Ikram ta ce "bari kawai Leemerh(Halima), nima idan na tuna a bikin Sunaiha ba wani casu haushi nake ji"

Sunaiha ta ce "na gaya miki umarnin Prince ne, kuma ba yanda za kuyi"

Ɗayavdaga cikin masu gyaran ta kalli ɗayar ta ce "wannan kam akwai zakwaɗi, Allah ya raba ta da sharrin namiji"

Ɗayar ta ce "matsalar ta ce, in ma ta haɗu da sharrin shi in ma kar ta haɗu, bai dame ni ba, Allah dai ya haɗa ta da dai-dai ita, addu'ar kawai a zan mata kenan"

"Ke kuwa wannan wace irin addu'a ce? "

"Hmm, yi aikin gabanki kawai, ba ki san wacece ƴar Senator ba shiyasa"

"To Allah ya kyauta" suka ci gaba da aikinsu, su kuma su Sunaiha su na ta firarsu

Da yamma masu zuwa wurin Bridal Shower duk sun tafi, gidan ba wasu mutane da yawa kuma mafi yawansu dattijai ne, su na main parlour su na fira

Kawu ƙarami ya dawo ɗaukar abu, sai ya kira Momi a waya ta zo ta same shi

"Wai wannan shan ƙamshin na meye ne? Ina tambayarki abu kina wani ɗaure fuska"

Ba tare da ta ce komai ba, ta buɗe drawer ta ɗauko ta miƙa mishi, sai da ya karɓa ya ce "Basira menene matsalar wai? Dama mata kuna fushi a lokacin biki ne?"

"Dan Allah Malam kar ka dame ni, duk wa ya ja mun ɓacin ran idan ba kai? Tun yaushe nake nuna maka yarinyar nan tana son Sadeeq, amma ka ce wai yana da wacce yake so, to yau ina take wacce yake so ɗin? Karshenta dai auren dole zai yi yanzu, da ace kayi magana da yanzu ita ce zai aura, amma tsabar baƙin ciki, saboda ba ka so wata daga cikin danginmu ta sake shigowa gidan nan, sai ka ƙyale ko a jikinka... To shikenan, ba dai aure ba ne! Ya je yayi, zan ga....."

A tsawace ya dakatar da ita "ke Basira ya ishe ki haka, kin wani tsare ni kina mun maganar banza wadda ga ta da amfani a wuri na.. Magana dai kike yi akan Sarah ko! To ba n bada goyon bayan ya aure ta ba, kuma ba zan bayar ba, da ma kin daina tayar da jijiyar wuya, dan gobe za'a ɗaura... Kuma ma ai na ga ita yarinyar da kike wannan masifar saboda ita, kaman hadda ita ake hidimar bikin, amma ke kin wani zauna abu yana damunki, tun ranar da aka fara zancen auren nan ai nake lura da yanayin ki, to wannan ke ta shafa, ni kin ga tafiya ta" ya gyara zaman babbar rigarshi, ya fita ya bar ta wurin a tsaye

Tana huci, ta ce "to shikenan, ba dai haka ka ce ba? Ayi auren, za ka sha mamaki".......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

🌙 *MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION*🌙
_We shine all over the world_

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

If you succeed in cheating someone, don't think that the person is a fool...realize that the person trusted you
much more than you deserved ...!!

*PAGE 25-26*

Kamar yanda hausawa suke cewa, rana ba ta ƙarya, haka ne kuwa domin yau ne ranar da mutane da yawa suke jiran zuwanta, masu farinciki da wannan ranar da masu baƙin ciki, tun safe ake ta shirye-shirye, manya da ƙanana, kowa sai ƙoƙarin shirin zuwa wurin auren suke yi, daga ɓangaren ƴan gidan amare da na angwaye dan ƙarfe goma aka tsara za'a ɗaura auren kuma yanzu ƙarfe tara da rabi

Daga ɓangaren amarya Nasreen, mahaifinta da ƴan uwanshi da abokansa duk sun yi shigarsu ta kamala, ta manyan mutane, motoci ne jere a ƙofar gidan aƙalla za su kai goma, ciki suka shiga suka wuce bayan waɗanda suka riga su isa

Haka ma ɓangaren amarya Sunaiha, mai girma Senator da muƙarrabansa, abokanan aikinsa na ɓangaren siyasa na wurin aikinsa da sauran abokan arziki, suka cika motoci suka nufi wurin ɗaurin auren. Ɓangaren angwaye ma ba'a bar su a baya ba, dan abokanan Alhaji, Abba, Kawu ƙarami da Grandpa, su kaɗai ma yawan su ya isa su iya taron auren, bare kuma an haɗa da abokanan angwayen da na ƙannensu da mazajen yayunsu, abun dai sai wanda ya gani, haka suka sa angwayen a mota ɗaya, sun sha fararen shadda masu tsada, anyi aikin babban rigar da brown colour, hularsu ma brown da ratsin fari, takalmi brown, sun yi kyau gwanin sha'awa kamar wasu twins

Kai tsaye babban masallacin dake jahar Gombe suka nufa, a nan za'a ɗaura, dandazon mutane ne masha Allah, manyan mutane, ciki har da ƴan jaridan da Senator ya gayyato dan a yaɗa a gidajen radio da TV, ƙarfe goma dai-dai aka fara addu'o'i,  Alhaji Muhammad shi ne waliyin Sadeeq, Kawu ƙarami kuma shi ne waliyin Safwan, a nan take suka biya sadakin ko wace naira dubu ɗari-ɗari, aka ɗaura aure tsakanin BARR.SAFWAN MUHAMMAD SARKI DA NASREEN AL-MUSTAPHA, sai kuma DR.SADEEQ USMAN SARAKI DA SUNAIHA ABUBAKAR NURUDDEEN, duk wanda ka kalli fuskarsa za ka tabbatar yana cikin farin ciki sosai banda Oga Tiger, da fuska a ɗaure yake gaisawa da mutane

Ba dan ran shi ya so ba yake ta hoto da abokanan iyayensa da na surukinsa, sai dan Abba ya
~~~~~~~~~~~~~~

sa shi dole, ai kuwa su na gama wa ya ɓace, Safwan ya neme shi ya rasa, Aymaan ne ya shiga duba shi, Safwan kuma ya ji da mutane

Kira ne ya shigo wayar Aymaan ɗin, ɗagawa yayi ya ce "Tiger ina ka shiga ne?"

"Me zan maka?"

"Haba Tiger, kana angon? Sauran abokanan ku ne fa ke so kuyi hoto tun da dai yau Allah ya sa fuskarka ta zama free, no glass no facemask" ya ƙarasa da sigar zolaya

"Aymaan ban gayyato kowa ba saboda ban son takura, dan haka ku ji da su....ni gida ma nake so ka zo ka mayar da ni"

Shiru Aymaan yayi yana mamakin Sadeeq kafin ya ce "kana ina?"

"Ina mota na mana, ba da ita muka zo ba"

Kashe wayar Aymaan yayi, bai fi minti goma ba ya zo ya same shi, mukullin motar kawai ya miƙa mishi

Kallon shi Tiger yayi ya ce "meye haka, mu je mana"

"Nikam ban gama shagali ba, kai ka tafi"

"To idan na tafi da motar da wane Safwan zai koma? Ka san cika motocin nan za'a yi"

"Kai!! innalillahi, gaskiya ka takura mun dai....mu tafi" ya faɗa rai a ɓace yana ƙoƙarin buɗe motar, Tiger kuwa yi yayi kamar bai gan shi ba, ya buɗe motar ya shiga

Sai da suka fara tafiya kafin ya gaya mishi wurin da zai kai shi, ba su kai minti talatin ba suka iso gaban wani gida, ba babban gida ba ne amma ba za'a kira shi ƙarami ba, madaidaici ne dai-dai misali, amma yana da kyau sosai, horn yayi mai gadi ya zo ya buɗe musu suka shiga ciki

Tiger ya ga Aymaan bai da niyan kashe motar, ya ce "ba za ka shiga ba ne?"

"In shiga inyi me a gidan da ba kowa? Kai dai da ka ji zaka iya zaman kaɗaici ka shiga kayi ta fama da aljanunka"

Murmushi kawai Tiger yayi ya fito daga motar dan ba ya jin zai iya tsayawa dogon surutu, yana fita Aymaan ya juya motar ya fita ya koma wurin su Safwan

Tiger kuwa sai da ya ɗan zagaya gidan kafin ya buɗe ƙofar palourn ya shiga, madaidaicin

parlour ne komai na ciki brown da milk colour ne, yayi kyau sosai ba laifi dan kayan ba wasu masu tsada bane

Hular kanshi ya cire ya ajiye kan center table, ya cire babbar rigar ya ajiye kan kujera sannan ya zauna ya ɗora ƙafa ɗaya akan ɗaya ya shiga danna wayarshi yana neman number

Bai fi mintuna biyu ba ya kai wayar kunnenshi yayi sallama

Daga ɗayan ɓangaren ya amsa kafin ya ce "Kana gidan?"

"Eh, amma ba wancan ɗin ba fa, ƙaramin"

"Ok to, ga ni nan zuwa"

Suka kashe wayar, ba'a yi minti goma ba, sai aka danna door bell ɗin parlourn, ya miƙe ya je ya buɗe

Cike da murna ya ce "ango ka sha ƙamshi"

Ɗan murmushi yayi ya ce "Yarima ba ka son zaman lafiya"

Hararashi yayi, ya ce "a'a malam, Muhsin suna na ba Yarima ba"

"Oh! Nima Sadeeq suna na ba Ango ba"

"Ramawa kayi kenan...to bani hanya in wuce"

Ya bi ta gefenshi ya ƙarasa cikin parlourn ya zauna, Tiger kuwa bai zauna ba sai da ya ɗauko musu ruwa da drinks cikin fridge sannan ya zauna

Yarima Muhsin ya ce "i'm sorry Tiger, ban samu zuwa auren ba, jiya nayi missing flight sai yau da sassafe na samu, mai martaba bai ko san na dawo ba, Audu driver kawai na kira na ce ya same ni airport, kar ya gaya wa kowa"

"Don't mind (kar ka damu), an gama ai, yanzu ma na ji dadi da ka zo"

"Ai shiyasa na ce wurinka zan fara zuwa kafin in isa gida....amma dai da wa aka yi auren? Ƴar Senator ɗin?"

A hankali Tiger ya ɗaga kai kafin ya ce "ita ce"

"Hmm, ashe da kai Allah zai haɗa ta, za'a yi maganin iskancinta kenan"

"Hmm, Muhsin kenan, ni ba sai na samu lokacin ta ba ma?"

"Me kake nufi?"

"Ka gane ai"

"Allah ya shirye ka to...yanzu dai ina so in je gida amma kafin nan mu tafi in ga gidan amarya dan ba lallai in zo anjima ba"

"Wane gidan amarya kuma bayan wannan da kake ciki?"

Kallon parlourn Muhsin ya sake yi, da mamaki ya ce "ban gane ba! Wannan gidan za ka ajiye ta? Ƴar Senator ɗin?"

"To meye matsalar wannan gidan?"

"Haba Sadeeq, ƴar babban gida ce fa, wannan gidan ma ba matsala yana da kyau, amma a irin matsayin ta, wallahi ta fi ƙarfin wannan gidan...ina ɗayan gidanka, nayi tsammanin can za'a kai ta dan ya ninka wannan girma kusan sau uku, ya fi wannan tsaruwa, ya fi shi kyau, ya fi kayan alfarma masu tsada da komai ma"

Numfashi Tiger ya ja, ya ce "na fi ka sanin hakan Muhsin, saboda tsarin gidan, fasalinsa, kayan da ke ciki and everything, ni nayi shi, amma kamar ka manta ko saboda wa nayi wannan gidan...My Princess Jewel, saboda ita nayi, kuma ba wacce za ta shiga gidan idan ba ita ba"

"Wai kana nufin har yanzu kana sonta? Bayan kuma kayi aure?"

"Muhsin, idan har bugun zuciya ta zai iya tsayawa kuma in rayu, to tabbas zan iya daina son Jewel"

"Babbar magana, to amma a iya sani na ba ka da ra'ayin mata biyu...."

"Kuma ba zan haɗa mata biyu ba Muhsin" Tiger ya katse shi

Kallonshi Yarima ke yi sosai, ya ce "this is serious!.....hmm, Sadeeq, i'm going (zan tafi), sai gobe idan mun haɗu"

Murmushi Tiger ya yi kafin ya ce "na gode da zuwanka" ya miƙe ya raka shi har wurin mota, suka yi sallama sannan ya dawo cikin gidan ya ci gaba da zama shi kaɗai

Ɓangaren su Safwan kuwa, tunda Aymaan ya gaya mishi wurin da Sadeeq yake, bai sake komawa ta kanshi ba, suka ci gaba da shagalinsu, kuma cikin ikon Allah ba wanda ya sake

tambayar wurin da Sadeeq yake sai wasu abokansa, kasancewar sun san halinshi sai ba su damu ba tunda ga Safwan

A parlourn Hajiya kuwa, Umma ce da Anty Sadiya, sai Hajiya, Anty Sadiya ce ta kira su zuwa nan saboda tana so suyi magana, ga gidan ko ina a cike

Hajiya ta ce "kiyi magana mana kin kira mu kin yi shiru bayan kin san mun bar mutane"

"Hajiya, so nake ku sa baki, kuyi wa Sadeeq magana, ni dai kayi iya yi na amma ya ƙi ji"

Umma ta ce "yau ke kin mishi magana bai ji ba, kike tunanin zai ji na mu?"

Hajiya ta ce "magana ma akan me?"

"Hajiya kina ganin yaron nan, yanzu ya kira ni, wai ƙaramin gidanshi za'a kai amarya, na gaya mishi hakan bai dace ba, a babban dai za'a kai ta, amma ya ce sam bai yarda ba"

Hajiya ta ce "to meye laifin ƙaramin gidan? Duk ba gida bane?"

"Gida ne Hajiya, amma ya mata ƙarami"

Umma ta ce "gaskiya kam, ai hakan ba zai yiwu ba, ya zai ce a matsayin ta na ƴar gidan Senator a kai ta wannan ƙaramin gidan?"

Hajiya ta ce "amma kuna ba ni mamaki,  kuna ta zancen matsayi, ina ruwanmu da matsayinta!? Ba ƴar Senator ba, ko ƴar sarki ce tunda ya ce ga gidan da yake so a kai ta dole nan za'a kai ta, saboda gidanshi ne kuma matarshi ce, ba wanda ya kai shi iko da ita yanzu, ko ina ne dole a bi umarnin shi...kuma ma ban ga laifinshi ba, saboda yaron nan yana da wacce yake so amma aka tilasta masa auren wata, so yanzu ku za ku bari yayi yanda yake so da matarshi matuƙar bai saɓawa Allah da addini ba"

Anty Sadiya ta ce "Hajiya kin san ina goyon bayan Sadeeq a komai, amma gaskiya wannan ni dai ban ga ya kyauta ba, saboda mu kan mu sai ya jawo mana abun faɗa a wurin danginta, a irin matsayi da arziki na Saraki's Family, a ce wai a wannan ɗan ƙaramin gidan za mu ajiye ƴar Senator....."

A tsawace Hajiya ta kira ta "Sadiya!!! Kar in sake jin ƙorafinki a wannan maganar, yanda Sadeeq ke so haka za'a yi, period"

Ganin yanda Hajiya ta fara ɗaukar abun da zafi, ya sa Umma ta ce "Hajiya, kwantar da hankalinki, yanda kika ce a yi hakan za'a yi, a ƙaramin gidan za a sa ta, ba matsala.....Sadiya zo ki wuce ku fara shirin walima, lokaci ya kusa"

Ɗaga kai kawai Sadiya tayi ta fita, Hajiya ma ta bi bayanta ba tare da ta ce komai ba, Umma ta ce "hmm, Sadeeq, Sadeeq! Allah ya kyauta, Ya shirya mun shi, wato tun da ba da sunan Sunaiha ya gina wancan gidan ba, ba za ta shiga ba" tayi shiru tana nazari kafin ita ma ta fita

Sunaiha kuwa yau bakinta har kunne saboda tsabar farinciki musamman idan ta tuna an ɗaura aurenta da Prince ɗinta yau za ta kwana a gidanshi, ta san har yau ba su taɓa haɗu wa ba, amma hakan bai dame ta ba sam

Tana zaune a ɗakinta gaban madubi, da ƙawayenta su uku har da Ikram, sai saƙawa take tana kwancewa

A hankali Ikram ta taɓa ta, ta ce "Amarya tunanin ya isa haka, tun ɗazu nake kallonki sai wani murmushi kike ta yi"

Murmushi tayi wanda ya ƙara fito da kyauta, ta ce "bari kawai Iky, yau ina cikin farin cikin da ba zan iya misaltawa ba, yau ɗin nan, wata rana ce da ba zan taɓa mantawa da ita ba a kap tarihin rayuwa ta....sai dai Ikram ina tsoron abu ɗaya"

"Me kenan?"

"Ikram ina tsoron kar ya kasance mafarki ne nake yi kamar yanda na saba yi, ina yawan mafarkin aure na da Prince, Allah ya sa wannan zahiri ne ba mafarkin ba" ta ƙarasa maganar da alamar tausayi

Dariya Ikram tayi ta ce "kin ji ki, wane irin mafarki kuma, wannan zahiri ne, ke matar Prince ɗin ki ce yanzu, ko sai na wanka miki mari sannan za ki gane ba mafarki ba ne" ta yi maganar tana dariya

Dariya ita ma Sunaiha tayi, ta ce "a'a na yarda, dan ban saba ganinki a mafarkin ba, daga ni sai Prince ɗina kawai"

"Oho to, yanzu dai ki tashi ga kayan da surukarki ta aiko da shi nan na walima, nan da mintuna talatin za su aiko da motoci domin tafiya walimar, dan haka ki tashi ki shirya"

Kafin tayi magana, sai ga wata ƙanwar Mummy ta shigo, ta ce "Sunaiha dama ba ki sa kayan ba har yanzu? Dan Allah ki tashi, ga masu Make up nan tun ɗazu suka zo, wacce za ta miki ke kaɗai take jira, har an gama yi ma wasu ƴan matan"

Ikram ta ce "maganar da nake gaya mata kenan Anty"

Sunaiha ta ce "yanzu zan shirya"

"Kuyi sauri dai" daga haka ta fita

Tashi Sunaiha tayi ta ɗauki kayan zuwa ɗakin da closet ɗinta yake, a nan ta shirya ta fito, Ikram da ke ɗakin kasancewar sauran sun fita a musu make up su ma, ta ce "wow!!! Masha Allah... Sunaiha kin gan ki kuwa?! Kayan nan kamar an auna ki, sun masifar karɓar jikinki, kin yi kyau sosai wallahi"

Ɗinkin fitted gown ne na material light brown, da wasu stones golden colour, a ɗan kwai ratsin milk a cikin style ɗin rigar, sun yi kyau ba kaɗan ba

Murmushi Sunaiha ke tayi, ta ce "thank u Iky"

Mai make-up ɗin ce ta shigo, ba ɓata lokaci ta zauna kan kujera aka fara kwalliyar, ba wani heavy make-up aka yi ba, ɗan simple ne, amma sai kwalliyar tayi masifar kyau, ko dan ba ta saba yin kwalliyar ba ne? Head ɗin ta golden colour ne da ratsin milk shi ma, nan ta shiga rangaɗa mata ɗauri mai kyau gaske, mai steps kusan goma sha biyar, sannan aka ɗauko mata wani dogon veil mai kamar alkyabba sai dai bai da hula, ta saka, golden colour ya fi yawa a ciki, sannan light brown

Allahu Akbar, Allah gwanin iya halitta, ba Ikram ba kam, har mai make-up ɗin sai da tayi ta yaba irin kyaun da Sunaiha tayi, a nan take Ikram tayi ta mata hotuna sun fi kala goma saboda ba za ta iya haƙurin sai sun fita ba, sai da ta gama kafin ta ce "riƙe wayar nan, bari in je in gani idan an ce ki fito" ta ja mai make-up ɗin suka fita

Tana nan zaune tana ta kallon kanta a madubi, saƙo ya shigo wayarta, dubawa tayi ta ga sunan Najeeb, ta shiga karanta saƙon kamar haka:

'Cutie pie, na sani yau ɗin nan ita ce ranar da ta fi miki ko wace rana a duniya, ita ce ranar farincikin ki, amma a wurin Najeeb, wannan ranar ita ce rana mafi muni da baƙin ciki, ɓacin ran da nake ciki ba zai hana in taya ki murna ba saboda na san kina cikin farinciki, Congratulations....Amma ina so ki sani, Najeeb yana sonki, kuma aurenki ba zai taɓa sa in daina sonki ba ko kuma in rabu dake, ina tare da ke ko da yaushe, dan Najeeb ba ya saurin karaya, kuma ba ya saurin barin abunda yake so...kar ki manta alƙawarin da na miki a haɗuwa ta da ke na farko, na gaya miki sai na shafe son Prince ɗinki a zuciyarki, na dasa miki son Najeeb, to ki kasance cikin shiri, dan ko wane lokaci son Najeeb zai iya yi wa zuciyarki dirar mikiya, The Game Starts Now (yanzu aka fara wasan)....I Love You My Cutie Pie'

Tana kai wa ƙarshen saƙon, ta ji gabanta ya faɗi, ta dinga jin tsoro, sai dai ta rasa tsoron menene, a hankali ta rufe ido tana fitar da numfashi kaɗan-kaɗan......

KUYI HAƘURI NA RASHIN JIN YAR SENATOR TSAWON LOKACI, HAKAN YA FARU NE SABODA EXAMS ƊIN DA NA TSAYA RUBUTAWA, AMMA YANZU ALHMDLH, BA ƘARAMIN ABU ZAI SA IN SAKE MAIMAITA IRIN HAKAN BA, I'M SORRY😔 NA GODE DA KULAWARKU KUMA😍🫶♥

♦💫♦💫♦
*YAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*YAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~
~~~~~~~~~~~~~~~

_There is no market for your emotions, so never advertise your feelings, just display your attitude....._

*PAGE 27-28*

Sunaiha ta kusan mintuna goma sha biyar a zauna, kafin Ikram ta shigo ta ja ta suka fita dan motocin sun iso, gaba ɗaya suka shiga suka ɗauki hanyar hall ɗin da za'a yi walimar

Babban hall ne mai girma gaske, anyi decorating ɗin shi sosai da milk and golden colour, duk wanda ya shiga wurin sai ya yaba irin kyau da ƙayatuwar wurin

Ko wane table da ke wurin a zagaye yake da kujeru biyar-biyar, su ma an musu decorations, sai daga ƙarshen hall ɗin, aka jera wasu kujeru guda biyu na zaman mutum ɗaya-ɗaya, kujerun royal ne golden colour, sun yi kyau sosai musamman da aka ƙara ƙayata su da balloons da wani abu mai sheƙi

Su Anty Sadiya, Anty Samira da Anty Saudat ne ke kai wa suna kawo wa cikin hall ɗin, kafin suka ji ƙarar motocin amare sun iso, kusan lokaci ɗaya suka shigo wurin, hakan ya sa tare suka shigo hall ɗin

Amarya Nasreen da Amarya Sunaiha, duk wanda ya kalle su ba ya son ya ɗauke ido, sai dai a ce masha Allah dan angwaye kam sun yi dacen kyawawan mata, kayansu, jakarsu, har takalmin su duka iri ɗaya. A hankali suke takawa tare da ƙawayensu dake bayansu har suka ƙarasa wurin da aka tanadar musu, suka zauna, sannan aka fara gabatar da abunda ya tara su, tsit kake jin hall ɗin har tsawon awa ɗaya kafin malamar ta rufe da addu'a tare da musu fatan zaman lafiya a gidajensu

Nan aka fara hotuna da Amare, sai dai Nasreen ce kawai ke sakewa da mutane tana musu dariya, Sunaiha kam wani kallon rainin hankali ma take musu, Ikram na jin haushin abun sai dai ta rasa ta yanda za ta mata magana ta daina abunda take yi. Su Sultana kam ko ta gefenta ba su koma ba, Anty Sadiya da Safna kawai suka tsaya yin hoto da ita

Ba su ɓata lokaci a wurin ba, suka watse saboda yamma nayi, dan su je suyi shirin anjima, motocin da suka kawo su, su suka sake mayar da su gidajensu

Sai da suka koma gida, Sunaiha ta shiga ta cire kayan jikinta, Ikram ta biyo ta

"Bakinki da magana" cewar Sunaiha ba tare da ta kalli Ikram ba

"Ai dole za ki fahimci hakan...Sunaiha wai sai yaushe kike so ki daina ja wa kanki zagi a wurin mutane ne? Yanzu dan Allah meye fa'idar wannan wulaƙancin da kika yi ta wa mutane? Kina...."

Katse ta Sunaiha tayi da "dan Allah ya isa Ikram, i heard enough!...ke kin san ni, kin san wacece Sunaiha, akan me zan tsaya in saki fuska su raina ni, ni fa na gaya miki tsakani na da dangin miji sai dai kallo amma banda lokacin ba su fuska su raina ni, dan haka ki ƙyale ni, kar in sake jin kin mun irin wannan magana"

"Sunaiha, ina so ki tsaya ki fahimce ni, wallahi...."

"Ba abunda za ta fahimta" muryar Mummy suka ji ta katse Ikram, tare suka juyo suna kallonta, sai da ta ƙaraso cikin ɗakin sannan ta ce "Ikram, Sunaiha ba za ta taɓa fahimtar duk wani abunda za ki gaya mata ba, ki ƙyale ta da halinta kawai, ta ce ba ruwanta da dangin miji sai dai mijinta kawai ko?! To ki ƙyale ta, ina tabbatar miki da sai ta neme su da kanta....zo mu ke in sa ki wani aiki" daga haka ba ta sake cewa komai ba ta fice daga ɗakin

Ikram ma kallonta kawai tayi ta fita, Sunaiha kuwa tsaki tayi ta zauna ta ce "wai zan neme su, to uban me za su mun? Uhm, daga ni sai Prince ɗina ba wani wanda zan nema ni" sai ta miƙe ta shiga cire kaya

Tiger kuwa tun da safe da ya bar wurin ɗaurin auren ba su sake haɗuwa da Safwan ba sai dab da sallar magrib, yayi alwala ya fito parlourn part ɗinsu ya zauna, lokaci kawai yake jira ya wuce masallaci, a lokacin Safwan suka shigo da su Sameer, Sauban, Saif da Aymaan

Sauban ya ce "Oga Tiger wai dama kan gida? Mun kira layinka ya fi sau talatin baya zuwa"

"Yanzu na kunna wayar" abunda kawai ya faɗa kenan ba tare da ya kalle su ba

Saif ya ce "wallahi Tiger wannan ba abu ne mai kyau kake yi ba, taya za'a ce ana wurin ɗaura auren ka, ka wuce ka bar mutane ba sallama ba komai, haba dan Allah, wannan abun naka ya fara wuce hankali"

Aymaan ya ce "ni ba na ɗauka idan ya gama zama da aljanunshi zai neme mu bane? Amma shiru kake ji, har abokansa da suka zo suka gaji suka wuce"

Kaman suna magana da kurma haka ya mayar da su, ko kallonsu ba ya yi, sai faɗa suke ta yi, idan wannan ya sauke wannan ya ɗauka, har Safwan ya fito ya same su, dan su na shigowa ko kallon Sadeeq bai yi ba ya shiga ciki, duk da ya damu tun ɗazu dan bai san wurin da ya ke ba, amma da ya ganshi a gida ya ji daɗi sai dai ya ji haushin abun da yayi

"Kun ji za ku iya ɓata bakinku ne, me na gaya muku, in har za ku kwana a nan ba amsa muku zai yi ba, shiyasa ko lokacin shi ma banda shi ni"

Aymaan ya ce "yanzu dai ba kyale mu kayi ba! To anjima zan ga wanda zai raka ka wurin Amarya"

Miƙewa Sadeeq yayi, ya tsaya kusa da Safwan ya riƙe mishi hannu tare da mishi murmushi, ya ce "i'm sorry dude! Na san ba ka ji daɗi ba, amma ni kuma yanda nayi shi ya mun daɗi....kai kuma ba zan neme ka ka raka ni ba, dan na san hanyar gida na, so calm yourself down" ya ƙarasa maganar yana kallon Aymaan kafin ya fita

Dariya Safwan yayi, ya ce "wai kai dama kana tunanin raka shi wurin Amarya? Tabɗi"

Aymaan ya ce "A'a ai wallahi na fasa"

Dariya suka sake yi kafin suka fita zuwa Masallaci su ma

Ƙarfe bakwai da rabi na dare, kowa ya sake wanka an canza kaya, sai dai ba wanda yayi kwalliya, su Anty Sadiya na parlourn gefensu gaba ɗayansu

Anty Samira ta ce "ni dai dan Allah ku tsayar da magana haka nan, kun san ƙarfe takwas za'a kawo amaren nan, kuma muna so mu riga shi isa"

Anty Sadiya ta ce "wace magana za'a tsayar? Ni ai kin san gidan wa zan tafi, ina gidan Tiger, Amaryarshi zan tarba"

Anty Samira ta ce "ai dama ba da ke nake yi ba, dan kowa ya san wurin da kike"

Sultana ta ce "ni dai Anty Nasreen zan tarba"

Salma ta ce "nima dai haka"

Safna ta ce "Anty Sadiya ni kam ina tare da ke, Anty Sunaiha zan tarba"

Salma ta ce "hmm, wato Safna ina ganin sai ranar da matar nan ta miki wulaƙancin da ba za ki iya shanye ba sannan za ki daina sonta"

Anty Sadiya ta ce "dan kawai ke ba ta miki ba shikenan sai ki ce wata za ta daina sonta!? Ba na son haka fa, ki kiyaye ni, kowa ra'ayin shi yake faɗa ai"

"Allah ya ba ki haƙuri, amma idan kika ganni lahira, to kai ni aka yi, ko ba haka ba Sultana?" Ta ƙarasa da tambayar Sultana

"Ai Salma kina ma da lokacin magana akan wannan matar, ke ni fa na tsane ta wallahi"

Anty Saudat da ke ta kallonsu, sai yanzu ta ce "to me za'a yi da mutum irin Sunaiha, kun ga Sisters, ina bayanku ni"

Anty Samira ta saki baki ta ce "ikon Allah, wai ku biyu kawai ke tare a Sunaiha? To ina tare da ku ni kam" ta faɗa tana kallon Anty Sadiya

Sajida kuwa dariya tayi ta ce "yanzu dai ni ce a tsakiya, ga uku a ɓangaren Barrister, uku a ɓangaren Doctor, to ina zan shiga?"

Safna ta ce "Anty Sajida ki shigo ɓangaren Tiger"

"A'a, ina tsakiya dai, duk waɗanda suka fara shirin wucewa su zan bi"

Anty Sadiya ta ce "ai ke dama kullum ba ki da alƙibla....ku tashi mu fita, Hajiya ta ga mun shirya kafin ta sake dawowa ta ci gaba da faɗan mu kaɗai ake jira"

Haka suka bar ɗakin, ƴan  ɓangaren Sunaiha suka nufi gidan Tiger, ƴan ɓangaren Nasreen suka nufi gidan Safwan dan tarbar amaren da ƴan uwansu

Amare kuwa ko wacensu ta sha atamfa, banda kwalli da lip-gloss ba abunda suka shafa ma fuskarsu, manyan motoci na alfarma aka aika domin ɗauko su

Sosai Mummy tayi wa Sunaiha nasiha ta kuma ja mata kunne akan ta kama kanta, sai dai zuciyarta na gaya mata ba lallai ma idan Sunaiha na ɗaukar maganarta ba, ai kuwa haka ɗin ne dan a wurin da Mummy ta gama nasihar, a nan ta bar mata shi, ba abunda ta ɗauka, burinta kawai ta ganta a gidan Prince. Ɗakin Daddynta ta shiga, ba wata nasiha da ya mata sai gaya mata da yayi zai yi kewarta kuma idan tana buƙatar wani abu ta kira shi ta sanar da shi, a nan sai da tayi ƙwalla kafin ta fito suka wuce

Sunaiha da Nasreen ba wacce aka kai gidanta sai da aka far kai su wurinsu Grandpa, sun musu nasiha su ma ba laifi, sannan aka kai su wurinsu Hajiya, Umma da Momi, su ma sun musu nasiha suka musu addu'a sannan aka wuce da kowa gidan mijinta

Momi kuwa ana wuce wa da amaren ta tashi ta koma ɓangarenta dan yau kusan fiye da rabin wuni tana ɗakinta, tana shiga Umma ita ma ta shiga, ta same ta a zaune

"Hajiya Basira, yau na ce lafiya kike kuwa? Tun jiya nake ganinki sai a hankali, yau ma ga shi ana ta hidimar bikin nan amma ba da ke ba, sai can ba'a rasa ba ki fito kiyi minti biyar zuwa goma ki dawo ɗaki...abun ya dame ni nayi wa Hajiya magana ta ce mu bari a gama da ƴan bikin nan ko zuwa gobe mu ji ko lafiya? Amma na ji ba zan iya bari sai gobe ba shi ne na biyo ki"

Murmushin ƙarfin hali tayi, ta ce "Umman Sadeeq kenan, kawai bana jin daɗin jiki na ne shiyasa"

"Allah sarki, amma shi ne ba za ki gaya wa kowa ba"

"Kin ga hankalin kowa na kan bikin nan, ba so nake ku damu ba har hankalinku ya kasu kashi biyu, shiyasa na ƙyale ku"

"Duk da haka dai baki kyauta ba...to kin sha magani?"

"Eh na sha"

"Ki samu ki ɗan kwanta to, Allah ya baki lafiya, zan gaya wa Hajiya"

"To na gode"

"Ba komai" daga haka ta fita

Tsaki Momi tayi ta ce "wai kun damu, ba dai anyi auren ba, mu zuba ni da ku, shege ka fasa...ku kun zo ke da yayarki kuna aure a gida ɗaya, sannan ku biyu kawai kuna da ƴaƴa takwas a gidan nan, za ku kwashi banza da yawa, ni ake wa baƙin ciki kar wata dangi na ta sake shigowa mu ci arzikin tare, to wallahi za ku sani, duk wanda ya ci tuwo da Basira miya ya sha" ta sake jan wani tsaki ta miƙe ta shiga bedroom ɗinta

An kai Nasreen gidan mijinta Safwan, gidan babba ne ya yi kyau sosai dan ya zuba naira a ciki, Anty Saudat da sauran iyayenta da suka kawo ta, suka sake mata nasiha sosai, sannan suka baro gidan, suka bar ta da ƙawayenta da su Sultana da Salma har sai da ango ya zo da abokansa, suka yi siyan baki, sannan kowa ya wuce ya bar amarya da ango tare da musu fatan alkhairi da fatan zaman lafiya da zuri'a ɗayyaba.

Sunaiha ma an kai ta gidan mijinta Sadeeq, Anty Sadiya da Anty Samira da sauran ƴan uwan Mummy suka mata nasiha, sannan ƙanwar Mummy wacce take kira da Anty, ta ja Anty Sadiya wani ɗakin

Ta ce "Sadiya, tun da muka shigo gidan nan magana ɗaya muke yi ni da sauran jama'a, a matsayinku da matsayinmu bai kamata a ce an kawo Sunaiha a ƙaramin gida irin wannan ba, ya haka?"

Dama Anty Sadiya ta san za'a yi haka, ta ce "Ayya mu ma ba haka muka so ba, akwai gidan da za'a ajiye ta, wannan na ɗan lokaci ne, an kawo ta ne kafin a kammala wasu ƴan gyare-gyare a wancan gidan"

"Au, ba a nan za ta zauna ba dai kenan?"

"A'a ba'a nan bane"

"Oho to, yanzu na ji magana, to shikenan ni bari in wuce kin ga duk sun fita ni kawai ake jira"

"To, Allah ya huta gajiya, sannu mun gode" sai da ta raka ta har mota, sannan ta dawo ta sa su Safna da Sajida gaba da ƙawayen Sunaiha, Ikram, Leemerh da Rufaida, suka wuce gida saboda Sadeeq ya gaya mata kar wanda ya tsaya jiranshi, su wuce kawai idan ba so suke su kwana a gidan ba, zai mata transfer ɗin kuɗin da za ta ba wa ƙawayen Sunaiha

Lokacin da Anty Sadiya ta ba Sunaiha haƙuri akan za su wuce, mijinta na hanya ita kaɗai yake so ya gani, ba ƙaramin daɗi ta ji ba, ai kuwa su na fita, ta ce "haba, ai ni na san Prince ɗina ya san abunda nake so ko ban faɗa ba, dama uwar me za ku zauna kuyi mishi idan kun jira shi idan ba sa ido ba?!...mtwss" ta shiga danna wayarta tana jiran isowar Prince ɗinta.......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*"'We are the moonlight writers we shine all over the world.'"*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_Sometimes we maintain silence to protect a beautiful relation, but don't forget, too much of silence creates a distance in every beautiful relation...Think....!_

*PAGE 29-30*

Har kusan ƙarfe tara da rabi Sunaiha na zaman jiran Sadeeq amma ko motsin shi ba ta ji ba, hakan ya sa ta gaji da zaman ta miƙe ta buɗe toilet ta shiga, ba ta fi mintuna goma ba ta fito daga ita dai towel, ta buɗe wardrobe ta ɗauko wasu kayan baccinta, riga da wando (pyjamas) pink color ta saka, sannan ta fito daga ɗakin

Kallon parlourn tayi da kyau, ba wani babba bane dan kujeru huɗu ne a ciki, three seater ɗaya, two seater ɗaya, dai one seater guda biyu, amma kujerun masu kyau ne. Ba wani kayan birgewa da yawa a parlourn amma tsarinshi yayi

"Ikon Allah, wai dama haka girman parlourn nan yake? To ni taya zan zauna a gidan nan?!" Ta faɗa tana wani ɓata fuska, sai kuma ta ce "whatever dai, in dai da Prince zan zauna ba komai, i'll manage"

Sai ta duba ta ga ƙofa uku a parlourn bayan wanda ta fito na ɗakinta, buɗe ƙofan farko tayi ta ga hanya ce da zai sada ta da bayan gidan, sai ta rufe ta buɗe na kusa da shi, kitchen ne, ta ƙarasa ciki kayan kitchen ɗin ba laifi sai dai ba su yi mata yawa yanda take so ba, ta ce "wannan kayan fa? To wai meyasa suka ce ba da buƙatar komai daga wurinmu, ai da Daddy ordering ɗin su zai mun...oh! Na manta sun ce wai haka ƙa'idar gidansu yake, to na ɗauka kayan arziki za su saka mun! Mtsww" tayi tsaƙi tare da buɗe ƙofar da ke cikin kitchen ɗin, store ne, akwai kayan abinci sosai a ciki, ba tayi magana ba dan su sun yi

Fitowa tayi ta tura ƙofar ƙarshen amma ta ji shi a rufe, sai tayi mamakin jin ƙofar a rufe, sake turawa tayi dan ta tabbatar. Duba agogon parlourn tayi, ƙarfe 9:58pm, sai a lokacin ta tuna cewa ba ta da numbern Prince ɗin nata

"Damn it" abunda ta faɗa kenan rai a ɓace, "to ina Prince ya shiga haka? Ƙarfe goma fa ko ya manta da ni ne?... Kai ba zai yiwu ba, may be wani abu ya tsayar da shi, bari in kira Daddy ya turo mun numbern shi"

Tana shirin wucewa aka buɗe ƙofar, juyawan da za tayi, tayi ido biyu da Tiger, sakin baki tayi tana kallonshi, wani irin farinciki ne ya ziyarce ta wanda ba za ta iya misaltawa ba, zuciyarta har bugawa take yi da sauri, ji take kamar tayi tsalle ta rungume shi amma kamar an ɗaure ta a wurin, kallonshi kawai take tana ƙara faɗaɗa murmushinta
~~~~~~~~~~~~~~

Ganin kallon da take mishi ba mai ƙarewa bane, kuma ta tare mishi hanya, ya sa a tsawace ya ce "ke dalla mayya meye kike wani kallo na? Ki matsa ki bani wuri ko in bi ta kanki"

Farincikin da take ciki ne ya sauya zuwa mamaki, a hankali ta ce "Prince!?"

"Malama na ce ki matsa!"

Yanda ya maimata maganar ya tsorata ta, hakan ya sa ta matsa mishi a hankali ya wuce, kitchen ya shiga bai fi mintuna biyar ba ya fito da bottle water a hannunshi, ko kallon gefenta bai yi ba ya shiga ɗakin ya mayar da ƙofa ya rufe

Sai a lokacin ta iya rufe baki, a hankali take tafiya har ta kai wurin cushion ta zauna, ta ce "Prince! Ni yayi wa haka? Anya kuwa ya gane ni? Dole ma zai gane ni, amma meyasa ya mun haka? Dama yana gidan nan nake ta jiranshi? Kuma yanzu ya fito amma ya mun wannan wulaƙancin?" Tambayoyin da tayi wa kanta kenan tana ji kamar tayi kuka dan ba tayi tsammanin haka wurin Prince ɗin ta ba

Kusan mintuna uku, sai kuma ta ɗan yi murmushi ta ce "Inaaa! A yanda nake gani a mafarki, Prince yana matuƙar so na, dole akwai dalilin da ya sa ya mun haka, may be gajiya ne, Allah sarki....Na san da safe zai neme ni kuma ya ba ni haƙuri, ni kuma zan ja class kafin in haƙura.....Amma gaskiya Prince a zahiri ka fi kyau, ga kwarjini, you're the best Prince, nayi sa'ar samunka" ta sake wani ƙayataccen murmushi sannan ta kwanta a kan cushion ɗin tana ta murmushi har bacci ya ɗauke ta ba ta sani ba

Da asuba Tiger ya fito zai wuce masallaci ya ganta parlour a kwance tana ta bacci, yi yayi kamar ya wuce, amma tuna muhimmancin sallah ya sa shi tashinta, sai da ta buɗe ido kafin ya wuce, haka ya dawo ya same ta a kwance, ba ta tashi ba, haka ya sake tashinta, sai da ta zauna kafin ya shiga ɗaki, ita ma ta miƙe ta shiga ɗakinta tana murza ido

Da misalin ƙarfe takwas na safe Kawu Karami na ɗaki da Momi, ya gama shiri zai fita

Ya ce "wai Basira me ke damunki ne yanzu? Kwana biyu kenan ina lura da ke sai wasu abubuwa kike yi da ban gane kanki ba...."

Katse shi tayi da "dama ta ya za ka gane kai na Aliyu?"

"Aliyu?" Ya maimaita da mamaki, "yau ni kike kira ea suna na?"

"Eh, ba sunanka bane? Ai Aliyu tun da na fahimci ba ka so na, to ba za ka sake gane kai na ba, ba dai aure ba ne, kuma an yi ko, to ku jira ku gani"

"Au, yanzu na fahimta ai, dama auren nan ne ya sa kike haka? To ba abunda za mu gani a

auren nan sai alkhairi in sha Allah, ki sa zuciyarki a ruwan sanyi ma zai fi...ki tashi ga shi can su na haɗawa ma'auratan breakfast, ki je ayi da ke, ni zan fita" yana kai wa ƙarshen zancensa ya fita

"Hmm, lallai ma Aliyu har yanzu ba ka gama sanin wacece ni ba, amma za ka fahimta"

Wayarta ta ɗauka ta kira Yayarta, mahaifiyar Sarah, bugu biyu ta ɗauka

"Hello Yaya"

"Na'am Basira, kun tashi lafiya?" Aka amsa daga ɗayan ɓangaren

"Lafiya amma ba lau ba"

"Subhanallahi, lafiya? Ko dai gajiyar bikin ne?"

"Wane gajiyar biki kuma Yaya? Ai ba wannan maganar kuma, ni yanzu abunda yake damu na bai fi rashin aurawa Sarah, Sadeeq ɗin da aka yi ba"

"Hmm, bari kawai Basira, ai ni na bar wa Allah, tun da dama can yaron ba sonta yake yi ba, kuma ga shi mijinki bai ba da goyon baya ba"

"Kin haƙura fa kika ce Yaya! Ai ba za ta saɓu ba bindiga a ruwa, in ke kin yafe wallahi ni sai in da ƙarfi na ya ƙare"

"Ban gane ba, Sarah ma fa ta manta da shi yanzu"

"Wa ya gaya miki? Wallahi har yanzu Sarah tana son Sadeeq, kawai ba yanda ta iya ne shiyasa ta ce ta haƙura, amma ke za ki so Sarah ta rasa abunda take so ne?"

"A'a ba zan so haka ba, amma ya zan yi?"

"Ni zan gaya miki yanda zan yi, amma ba yanzu"

"To shikenan Basira, sai na ji ki"

"Yawwa, sai anjima"

Kashe wayar tayi ta ce "ni na san abun yi ai, amma a hankali zan bi komai, dole sai Sarah ta auri Sadeeq, sai mun ci arzikin gidan sosai kamar yanda waɗancan munafukan za su ci"

Miƙewa tayi ta bar ɗakin, kai tsaye general parlour ta nufa, ta samu Hajiya da Umma a zaune, gaishe su tayi kafin ta zauna

Hajiya ta ce "Basira ya jikin? Jiya take gaya mun ba kya jin dadi ban samu zuwa duba ki saboa gajiya wallahi, yau kuma mun tashi da haɗawa yaran nan breakfast"

"Jiki alhamdulillahi ai, na ji sauki, dama stress ne kawai...haɗa breakfast ɗin yayi ai dan bai kamata amare su fara shiga kitchen ba kwana ɗaya kawai"

Dariya Hajiya tayi ta ce "haka ne kam"

Anty Saudat ce ta shigo da wasu baskets, babba ɗaya da ƙarami ɗaya da kuloli a ciki ta ajiye a gaban su Hajiya, Salma ma ta biyo bayanta da wasu irin waɗancan ta ajiye

Anty Saudat ta ce "Hajiya an gama haɗa komai, ga shi nan ku duba"

Hajiya ta ce "Basira ki duba ki gani ko yayi?"

Murmushi ta yi ta ce "haba Hajiya, yaran nan fa ƴan zamani ne, na tabbata komai yayi"

Umma tayi dariya ta ce "to ina sauran? Ku zo ku kai musu kun ga ƙarfe takwas ya wuce"

Anty Saudat ta ce "sun shiga su shirya ne, ni ba zan tafi ba dan jiki na sai a hankali, Anty Sadiya da Sultana za su kai na su Tiger, Anty Samira da Salma za su kai na Safwan"

Umma ta ce "to shikenan"

Ba su fi minti goma ba, suka fito suka wuce

Mummy na dinning area da Daddy su na breakfast, Daddy ya ce "wato Hajiya tun jiya da aka ɗaura auren nan nake cikin farinciki har zuwa yanzu, saboda burin Baby ya cika, na tabbata za tayi farinciki har ƙarshen rayuwarta"

"Wane irin farinciki? A irin tarbiyyar da ka ɗora Sunaiha ba za ta taɓa jin daɗin rayuwar aurenta ba"

A fusace ya ce "wannan wace irin magana ce? Hajiya wai meyasa bakinki ba ya furta alkhairi akan yarinyar nan ne? Ke kullum cikin yi mata munanan kalamai kike?... To bakinki ya sari ɗanyen kashi, ni na san yaron nan yana sonta"

"Yana sonta a mafarki ko? Ni na san yaron nan tilasta masa auren ta ku ka yi"

"Me ya baki tabbacin ba ya son ta?"

"Kar ka manta jiya ya zo gidan nan gaishe ni, a yanayin shi kawai na gane ba ya son auren, dan

ba sabon angon da za ka gani a irin yanayin da yake jiya"

"Zancen banza kenan, to ba gajiya ba ne! Kin ga Hajiya, idan kina so mu zauna lafiya da ke a gidan nan kar in sake jin kin yi mummunan furuci akan Baby" bai jira jin ta bakinta ba ya tashi ya fita

Kallonshi take yi har ya fita sannan ta sauke numfashi ta ce "hmm, ba baki nayi wa ƴa ta ba, amma na san sai tayi da na sanin auren Sadeeq, saboda zama da wanda ba ya sonka, musamman zaman aure akwai babbar matsala"

Tana ci gaba da breakfast ɗinta, wayarta tayi ƙara, ta duba ta ga Hajiyar London, matar Yayan Senator kenan

Da fara'a ta ɗaga wayar "Hajiyar London"

Ita ma dariya tayi ta ce "na'am Hajiyar Nigeria, tun da ba za ki daina kira na da wannan sunan ba"

"To ai ku ne kun mayar da ƙasar wasu na ku"

"Wallahi bari kawai Hajiya, har yau ina jin haushin rashin zuwa bikin Sunaiha, exam ɗin Shareef ya tsayar da mu da aikin Alhaji"

"Ba komai ai Hajiya, kin san na gaya miki ma ba wani bikin da aka yi"

"Haka dai kika ce, to ya take? Ko ba kuyi waya ba?

"Kin san halin Sunaiha ai, may be ma ba ta tashi ba"

"Kaii! Amarya ba ta tashi ba yanzu?"

"Sunaiha ce fa, Allah dai ya shirye ta kawai"

Dariya tayi ta ce "ameen to, ki gaishe ta dan Allah, sai na kira ta dai"

"To zan gaya mata, ki gaida su Shareef" daga haka suka kashe wayar, ta ci gaba da breakfast ɗinta

Sadeeq na zaune a parlour da laptop a gabanshi kan center table ya ji anyi knocking ƙofar palourn, kai tsaye ya je ya buɗe kasancewar Anty Sadiya ta kira shi

Sai da suka zauna sannan suka gaisa, Anty Sadiya ta ce "ina Amaryarmu?"

Tiger ya ce "ta ya zan sani"

"Haba Tiger, ku kwana gida ɗaya kuma ka ce ba ka san wurin da take ba?"

Sultana ta ce "to Anty Sadiya ta ya zai sani mana, ɗakinsu ɗaya ne?"

Anty Sadiya ta ce "ki rufe mun bakin ki! Dake nayi magana?"

Turo baki Sultana tayi, Sadeeq ya ce "Anty Sadiya ba ta tashi ba, shikenan!?"

"Ban sani ba...ke tashi mu wuce" ta ƙarasa tana taɓa Sultana

"Bye Ya Tiger" cewar Sultana

"Ki gaida su Hajiya" Anty Sadiya ba ta ce komai ba, suka fita

Dawowa yayi ya zauna, bai fi mintuna goma ba sai ga Sunaiha ta fito, tana murza ido ta ƙarasa cikin parlourn, idonta ya sauka kan basket ɗin da su Sultana suka kawo

Cikin murna ta ce "yawwa, Mummy kamar ta san yunwa nake ji, bari in je inyi brush in yi sallah in zo in ci"

Yana zaune amma ko kallonta bai yi ba har ta gama surutunta ta koma cikin ɗaki, ba ta wani jima ba ta sake dawowa, kusa da Sadeeq ya zauna ba ta ce mishi komai ba, wai ita fushi take yi da shi tana jira ya mata magana

Haka ta gama fitar da kulolin, ta je kitchen ta ɗauko plate da cup, ta haɗa tea, sai da ta gama ci tsaf ba wanda ya ce ma wani komai, ta miƙe ta je tayi wanka, ta dawo sanye da riga t-shirt da jeans a jikinta

Wannan lokacin ya rufe laptop ɗin yana danna wayarshi, ta kalle shi ta ce "Prince, wai meke damunka ne? Ni sai nake ganin kamar ba ka ji daɗin gani na ba, kuma na ga a mafarki kamar ma ka fi ni so mu haɗu... jiya na maka uzuri saboda gajiya, yanzu kuma na kyale ka shi ne ko magana ma ba za ka mun ba ko!" Ta ƙarasa zancen da sigar shagwaɓa

Wani wawan kallo ya mata, ya ci gaba da danna wayarshi, ta ce "Prince magana nake yi fa"

A tsawace ya ce "ke dalla kiyi mun shiru!!! Wai waye Prince? Kin san a gaban wa kike ma kuwa?"

Tsawar da ya mata ya sa ta razana sosai sai da ta rufe idonta, ajiye wayarshi yayi gefe ya fuskance ta da kyau

Ya ce "ke, sauka ƙasa ki zauna"

Baki a buɗe take kallonshi, ya sake daka mata tsawa "nace ki sauka ko!!"

Da sauri ta zauna ƙasa, saboda yanda ta ga fuskarshi da yanayin yanda yake magana ya sa lokaci ɗaya tsoronshi ya kamata

"Ina so ki buɗe kunnenki da kyau ki saurari abubuwan da zan gaya miki...kin ga na farko, kar ki kuskura in sake jin wannan ƙazamin bakin na ki ya kira ni da Prince dan ba a gidan sarauta kika ganni ba, ki kira ni da Abbakar, Sadeeq ko kuma Tiger. Secondly, na ji an ce wai a mafarki kuka sanni har kike so na ko? To ki sa wa ranki Sadeeq ɗin da kike gani a mafarki ya banbanta da wannan Sadeeq ɗin da kika aura, idan wancan yana sonki, yo ni tsanarki nayi saboda kin hana ni kasancewa da Princess Jewel ɗina, wacce nake so, kuma ita kaɗai nake so sannan ita kaɗai zan so har ƙarshen rayuwa ta. Dan haka ki sani, ba wai gidan Prince kika shigo ba, nan gidan Tiger ne, sannan nan ba gidan da za ki ji daɗi ba ne ko kiyi irin rashin kunya da wulaƙancin da kika saba, nan gidan da za ki sha wahala ne, gidan da za kiyi hankali.... Wai ke Ƴar Senator ko? To nan ba gidan Senator ba ne, ki sa a ranki daga yau tashin asuba za ki fara, wannan sallar da kike yi na safe zai koma na asuba, sannan ba za ki sake kwanta wa ba idan kika yi sallah, gyaran gidan nan za kiyi in and out kafin gari ya waye, sai kuma ki haɗa mun breakfast, da rana ki dafa abinci, da daddare ma haka, sannan gyaran gidan nan sau biyu kullum...."

Tun da ya fara magana hawaye ke bin fuskarta, a hankali ta buɗe baki za tayi magana, ya sake katse ta a tsawace

"Keep your mouth shut, ki saurare ni ban kammala ba.... ba zancen ƴan aiki a gidan nan, mai gadi kawai na ajiye. Sannan maganar ki fita yawo ma babu, ni zan ware miki rana da kuma lokutan da za ki fita, sai abu na gaba, daga yau kar in sake ganinki cikin waɗannan ƙananan kayan, kayan arziki su za ki saka. Na ƙarshe kuma, duk ranar da ƴan gidanmu suka shigo gidan nan kika musu wannan wulaƙancin na ki, za ki ga true colors ɗin Tiger. Ba na da kirki, ba na da kyau, idan kika tsallake ɗaya daga cikin abunda na gaya miki...! Hmm...but you can try me... Tashi ki je ki cire kayan nan ki saka wasu, sannan ki zo ki kwashe kayan nan da kika yi amfani da su kuma ki haɗa mun breakfast, now!"

Gaba ɗaya ko motsi ta kasa yi, "ba za ki tashi ba!" Ya faɗa da ƙarfi

Da gudu ta kai ɗaki, tana shiga ta zube kan gado, kukan da take ta danne wa ta saki, kuka take sosai tana jin kalamanshi na dake dawowa kunnenta, rufe kunnenta tayi da hannu biyu tana girgiza tana ta kuka......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_It's not hard to sacrifice something for someone, but it's hard to find someone who deserves ur sacrifice...._

*PAGE 31-32*

"Najeeb wai meye haka, tun da uwar safen nan ka sa hoton yarinya kana ta kallo, bayan kai da bakinka ka gaya mun jiya aka yi aurenta" cewar Yayan Najeeb

"Hmm, Yaya na gaya maka ina sonta, zuciya ta ba za ta iya haƙura ba har sai na same ta..."
~~~~~~~~~~~~~~

"Amma ai ita ba ta sonka, ka gane mana" ya katse shi cikin jin haushi, "Najeeb yarinyar nan da tana sonka ba yanda za'a yi ta yaudare ka, ta je ta auri wani ta bar ka anan"

"Ni fa Yaya ba yaudara ta tayi ba, saboda tun haɗuwar mu ta gaya mun tana da wanda take so"

"Ok! Kenan kai ka yaudari kanka ko,...Najeeb akwai maganar da ake cewa, son maso wani ƙoshin wahala, lallai kana cikin wahala"

"Ba wani wahala Yaya, ko ka manta Najeeb ne? Ba na kyale abunda nake so cikin sauƙi"

"Na sani, amma kai ma kar ka manta duniyar nan ba ka a kowa sai Allah sai kuma ni, na gaji da fitinarka"

"Kar ka damu, wannan karon ba wata fitina da zan jawo maka, amma tabbas sai na mallake ta ko da kuwa na kwana ɗaya"

Kallonshi Yayan na shi yayi sosai, kafin ya sauke ajiyar zuciya ya ce "lallai Najeeb ka wuce sani na yanzu, Allah ya shirye ka" daga haka bai ƙara cewa komai ba

Ɓangaren Sunaiha kuwa, ta ɗauki lokaci tana kuka, kafin ta tuna da yace ta haɗa breakfast, da sauri ta miƙe dan yanzu tsoron shi ya cika zuciyarta, gani take yi kamar maganarshi gaskiya ce da ya ce Prince ɗinta na mafarki daban yake da na zahiri, tabbas yanda take tsammanin zamanta da Prince zai kasance, kwata-kwata ba zai yiwu ba in dai wannan shi ne halinshi ba wai jaraba ta take son yi ba

Tana wannan tunanin har ta sauya kayan jikinta zuwa atamfa ɗinkin riga da skirt, ta share hawayenta sannan ta fito, yana nan wurin da ta bar shi, kallonshi take tayi tana so ta gamsar da zuciyarta wannan ba Prince ɗinta ba ne, amma ta kasa yarda saboda ita ta san wannan shi ne Prince ɗin da ta ɗauki tsawon shekaru tana mafarkinshi kuma tana burin mallakarshi

Numfashi ta ja kafin ta wuce kitchen, a nan ma ta daɗe tana ta kallon kitchen ɗin, ta rasa ma me za ta fara yi, dan a iya rayuwarta ba ta taɓa shiga kitchen sunan dafa abinci ba, in dai ta shiga kitchen to ɗayan biyu ne, ko dai ta shiga ba da umarnin abunda za'a dafa mata, ko kuma ta shiga ta ci wa masu aikin mutunci, sai yau ga ta a kitchen wai za ta dafa abinci

"Tab, to ni ta ina ma zan fara? Komai ban iya ba" ta faɗa tana ta kalle-kalle. Can ta shiga store ta ɗauko indomie uku da kwai biyar ta fito, ta ajiye, sannan ta sake komawa ta ɗauko tukunya ta ɗora kan electric cooker, ta ce "na gode Allah ma akwai wuta, dan ni tsoron kunna gas nake ji"

Ruwa ta ɗibo ta zuba, ta tsaya har ya tafasa sannan ta zuba indomie ɗin gaba ɗaya tare da magginshi, yana fara tafasa, ta fasa kwai ta zuba tayi ta juyawa. Abunda ya ba ta mamaki shi ne, indomie yayi amma ruwan bai shanye ba, kuma kwaɓe

"Ah ah, a iya sani na ana dafa mun indomie da kwai a ciki, amma ya wannan ya banbanta kuma? Mtsww" tsaki kawai tayi ta ɗauko plate ta juye, ta kai mishi

Mamaki ne ya cika shi ganin abunda ta kawo mishi, ya ce "meye wannan?"

"Ba indomie ka ce in dafa maka ba?"

"Yanzu wannan indomie ne? Haka ake dafa indomie a garinku? Lallai ban taɓa ganin wawuyar mace irinki ba, komai lalacewar mace za ta iya dafa indomie, amma ke ki ce ko indomie ba ki iya dafa wa ba?"

Cike da tsoro ta ce "abunda nake so zan gaya maka kenan ɗazu ka dakatar da ni, ban iya dafa komai ba wall...."

Katse ta yayi da "za ki iya ne, ko wallahi in karya ki a gidan nan, har kin isa ki ce ba ki iya dafa abinci ba a matsayinki na ƴa mace!? Ke wannan gata aka nuna miki ko kuma cutar da ke aka yi?....Yanzu gaya mun, indomie nawa kika ɓannatar a nan?"

Kamar me tsoron magana ta ce "indomie uku da kwai biyar"

"Jar uba!! Gaya miki aka yi ni shanu ne da zan ci indomie uku? Ga ɓannar abinci ga rashin biyan buƙata...dalla malama ki tashi ki ɗauke mun wannan ƙazantar, ni indomie ɗaya za ki dafa mun ba a kwai ba, kuma wallahi kika sake mun ɓanna irin wannan sai ba kusan zubar miki da haƙori"

Da sauri ta miƙe ta ɗauki plate ɗin ta sake koma wa kitchen, kuka ta sake fsshewa da shi, ta ce "wai nika wace irin amarya ce? Haka auren yake dama? Aka ce idan ka auri wanda kake so za ka ji daɗi, to haka daɗin yake?" Ta ci gaba da kuka

Da sauri ta share hawayenta gudun kar ya shigo ya same ta a tsaye, sai ta fara tunanin wa za ta kira? Tayi tunanin kiran Mummy, dai kuma ta ce "ba zan iya kiran Mummy ba, saboda yau na fara gane dalilin da yasa take so in koyi girki amma na biye wa Daddy da ya ce ko aure nayi da ƴan aiki za'a kai ni, to yanzu idan na kira ta faɗa kawai za ta mun"

Tana cikin tunani kawai ta tuna da Ikram, ba ɓata lokaci ta shiga kiranta

"Amarya a gidan Prince, irin wannan kiran sassafe haka? Ashe za ki iya tuna wa da ni yanzu" cewar Ikram cikin sigar zolaya

"Kin ga Ikram ki riƙe wannan maganar tukuna, yanzu taimakonki nake buƙata"

"Wane irin taimako kuma Amaryar Prince?"

"Umm, kin san me, Prince ne wai indomie yake so in dafa mishi, kuma kin san ban iya ba, to shi ne nake so ki gaya mun yanda zan yi"

"Amma abun nan da mamaki, amarya da shiga kitchen, kuma amaryar ma Ƴar Senator? Haba mana dan Allah, ki mun maganar da zan ɗauka. Ko dai gwada ki yake yi?"

"A'a, abincin da aka kawo mana ne, ba ya so, kin ga kuma ba zan bar Prince da yunwa ba"

"Amma ai a sani na daga gidansu za a aiko muku da abinci, su ba su san abunda yake ci ba?"

Ran Sunaiha ya ɓaci ganin Ikram na neman ƙure ta, ta ce "Ikram idan za ki gaya mun, ki gaya mun, idan ba za kiyi ba kuma sai in kira wata"

"A'a zan gaya miki, dan gwara mu bar shi a tsakanin mu ko a ji kunya...dama yanzu na tashi nima ina so zan dafa indomie, Umma ta wuce wurin aiki, zan kira ki video call, sai ki ga yana zan yi ke ma kiyi"

Sunaiha ba ta ma tsaya cewa komai ba, ta kashe wayar, ta kira ta video call, dariya Ikram tayi kafin ta ɗauka. Ba ɓata lokaci suka ajiye wayar yanda suna iya ganin juna suna aiki, duk abunda Ikram tayi shi Sunaiha ke ƙoƙarin yi, Ikram ma tana lura da yanda take yi, har suka kammala sai dai Sunaiha ta yanke hannu wurin yanka albasa, ta ji jiki kam, da ƙyar ta ga an gama

Ikram na dariya ta ce "gaskiya Sunaiha kin ba da mata, common dafa indomie"

"Malama kar ki dame ni"

"Ba laifinki ba ne, nuna miki nayi...sai na zo anjima dai, may be around 1pm zan shigo"

"Sai kin zo" ta amsa ta sannan ta kashe wayar

Kallon indomin tayi da kyau, ita kanta ya burge ta, dan idan aka ce za ta iya dafa indomie haka, za ta ƙarya ta. Cike da murna ta ɗauko shi ta fito parlour, sai dai ba ta ganshi ba, tana tunanin ko yana ɗaki, sai ga shi ya fito, ya yayi wanka ya shirya cikin jeans da t-shirt, ya sa madubin shi baƙi as usual, yana riƙe da facemask da wayarshi a hannu

Ba ƙaramin kyau ya mata ba, a hankali ta ce "ga shi na gama"

Bai ko damu ya buɗe plate ɗin ya gani ba, sai ce mata yayi "ki gyara gidan nan, ɗakinki, palour, kitchen, da harabar gidan nan, sannan da back-door ɗin nan, shi ma ki share wurin, idan kin gama, akwai turare a bedside drawer na ɗakinki ki sa a ko ina, idan kika gama kuma sai ki dafa abinci dan ba wani abincin da za'a sake kawo miki... Saura kuma in dawo ba ki gama ko ɗaya

ba, ba jimawa zan yi ba" bai jira jin me za ta ce ba kawai ya ɗauki makullin motarshi kan center table ya fita yana sa facemask

Baki a buɗe take kallonshi har ya fita, ta ce "ikon Allah, wai wannan wane irin mutum ne?"

Ji tayi kamar ta yi ihu ko za ta ji sauƙi a ranta. Ba ta tsaya ɓata lokaci ba, ta fita harabar gidan, ba wani datti yayi ba, tayi tsaye tana kallon girman gidan, bai da wani girma dan ba zai wuce ɗaukar mota biyu da ɗan space kaɗan ba

Mai gadi na ganinta ya zo da gudu ya durƙusa, ya ce "Hajiya barka da safiya"

Ko kallonshi ba tayi ba, ya sake maimaita wa "Hajiya barka da safiya"

A tsawace ta ce "kai dan Allah ka kyale ni, dole ne amsa gaisuwar? Come on tashi ka bani wuri"

"Allah ya huci zuciyarki" ya miƙe ya koma kan kujera ya zauna, ganin ta ƙi wuce wa ya sa ya buɗe ƙofa, ya ja kujerarsa ya fita

Numfashi ta sauke ta ce "yawwa, na gode Allah ya fita, dama ina tunanin yanda zan share wurin nan a gabanshi"

Nan ta fara duba wurin da za ta ga tsintsiya, bayan gidan ta zagaya a nan ta ganshi, ta zo ta share sama-sama, ita kanta ta san wannan ba shara tayi ba, kawai dai ta kakkaɓe wurin ne, ta sake komawa cikin parlourn, shi ma sama-sama ta gyara shi sannan ta shiga ɗakinta ta gyara, ta duba wurin da ya gaya mata akwai turare, ta ɗauko ta kunna.

Guda kan ya sha ƙamshi dan kusan turare goma sha uku ta kunna ma gidan bayan wanda ta fesa, sai dai ba abunda yayi kyau a gyaran na ta, musamman idan mutum ya shiga ɗakinta zai sha dariya, saboda yanda ta hargitsa gadonta, wai ita tayi gyara

Ji tayi gaba ɗaya jikinta na mata ciwo, ta gaji sosai har da kuka tayi, ba shiri ta faɗa toilet tayi wanka, ta sake saka atamfa sai dai wannan ɗinkin doguwar riga ce, ta dawo parlour ta zauna, sai a lokacin wani yunwa ya taso mata, yanda ta gaji ba ta jin za ta iya haɗa ko da tea ne bare kuma ta ce za ta dafa indomie tun da yanzu dai ta iya

Indomie ɗazu ta tuna da shi, ta miƙe ta ɗauko, yayi sanyi kuma ta san ba za ta ji daɗin cin shi ba, ama yunwa take ji sosai, haka ta dawo parlourn ɗauke da shi da gorar ruwa, ta cinye shi tsab ta sha ruwa, sai kawai ta kwanta a wurin dan ta ma manta da labarin abincin rana, tana kan tana tunanin wannan rayuwar da Allah ya kawo ta, wani wahalallen bacci yayi awon gaba da ita

Tiger kuwa yana fita gidansu ya wuce, yana shiga parlour ya tarar da Sameer da Sauban suna buga game, suna ganinshi suka gaishe shi cike da fara'a

Sameer ya ce "Ya Sadeeq koro ka amarya tayi ne?"

Sauban ya ce "ai sai da na gaya maka kar ka yarda muyi wannan bet ɗin dan zan yi winning, ni na san Oga Tiger sai ya riga Ya Safwan shigowa gidan nan, dan haka sai ka ba ni kuɗi na"

Sameer ya ce "gaskiya Oga Tiger ba ka kyauta mun ba"

Murmushi kawai yayi yawuce ya bar su nan Sauban sai dariya yake yi. Kai tsaye part ɗin Hajiya ya fara wucewa, sai da suka gaisa, ta ce

"Ya Sunaiha?"

"Tana gida"

"Yanzu nake so in je in samu Mominku dan a haɗa muku abincin rana"

"Hmm....bari in ƙarasa wurin Maa"

"Ba ta jin daɗi ma, ka san halinta dama, in dai aka yi taro a gidan nan sai tayi ciwo ko na kwana ɗaya"

"Subhanallah, bari in je"

Ya miƙe ya fita, part ɗin iyayenshi ya nufa, yana shiga parlourn, Umma na fitowa daga bedroom ɗinta

"Ah ah, Saddikul Akbar" ta faɗa tana ƙoƙarin zama kan Cushion

Kusa da ita ya zauna yana kallonta, ya ce "Maa, ya jikinki?"

Murmushi tayi ta ce "wa ya gaya maka?"

"Hajiya, amma ai ko ba'a gaya mun ba, alamunki sun nuna"

Murmushin ta sake yi, ta ce "ai na ɗauka Amarya za ta sa ka manta da mu, sai na ga ka shigo da wuri"

"Maa, kina tunanin akwai wacce za ta iya shiga rayuwa ta har ta sa in manta da ku? Ai ko da zan manta da kowa, banda ke Ammi na, you mean the world to me, ko Abba ba zai iya maye gurbin ki a wuri na ba, bare kuma wata..dan Allah kar ki sake faɗar wannan maganar"

Shafa fuskarshi tayi ta ce "come on dear, I'm just joking, na san yanda kake ji da Ummanka

Balarabe na"

Daɗi ya ji har cikin ranshi, yayi murmushi, sai ta ce "ina amarya?"

"Tana gida...yawwa Maa, dan Allah ki gayawa Hajiya kar a dafa abinci da mu"

"Meyasa kuma"

"Na yi ordering ɗin abinci, kuma na one week nayi, abincin ɗazu ma sai da ya mana yawa, yanzu take gaya mun za su haɗa abincin ita da Momi"

"To shikenan"

"Yawwa, bari in tafi, Allah ya ƙara miki lafiya Maa" ya miƙe ya mata peck a goshi kafin ya fita

Garden ya nufa, a nan ya tarar da su Anty Sadiya, sai da ya gaishe su, kafin ya ce "ina su Sultana?"

Anty Sameera ta ce "suna kitchen"

"Anty Saudat fa?"

"Sun tafi asibiti, ita ma jikin sai a hankali" cewar Anty Sadiya

"Allah ya sauwake, zan kira ta"

Yana ƙoƙarin wucewa, Anty Sadiya ta ce "zo muyi magana kafin ka wuce"

Gefe suka koma, ya ce "ba dai zancen Sunaiha za ki mun ba?"

"A'a wannan ba yanzu ba...akan Momi ne, me ke tsakaninka da ita?"

"Me ta gaya miki?"

"Ni ba ta gaya mun komai ba, amma nayi observing ba ka gaida ita, ba ka mata magana, duk abunda zai sa ku haɗa hanya ma ba ka so"

"Kinyi kuskuren fahimta" ya faɗa yana mayar da glass ɗinshi

"Hmm, Sadeeq kalle ni da kyau, ka san na sanka, me Momi ta maka? Na tabbata ma yanzu ba ka shiga wurin ta ba"

"Anty Sadiya, dan Allah ina da abun yi, kin san ba na abu sai da hujja, to ki bari idan na gama

tattara hujjoji na, zan gaya miki komai, ina sauri yanzu, bye" bai ƙara ko da minti ɗaya ba, ya juya ya wuce ya bar ta tsaye tana mamaki......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~

_You're a part of a puzzle in someone else's life. You may never know where u fit, but remember that someone else's life may never be complete without u in it... So enjoy being special!_

*PAGE 33-34*

Anty Sameera ta ƙaraso kusa da Anty Sadiya ta ce "Ya dai Maman Aryaan, har kun gama da
~~~~~~~~~~~~~~~

mutumin na ki?"

Numfashi ta sauke, ta ce "hmm, bari kawai Sameera, ni wallahi wani lokacin Sadeeq yana ɗaure mun kai"

"Ke kenan, to mu kuma me za mu ce? Allah dai ya shirye shi kawai....ynx Momi ta kira ni a waya, tana nemanmu ciki"

"Hmm, mu je to" daga haka suka shiga ciki

Ɓangaren Tiger kuwa, yana barin gidan kai tsaye kampanin Alhaji ya wuce, suka gaisa kafin ya wuce kampanin Abba

"Malam Sadeeq ka tashi lafiya?" Abba ya tambaye shi bayan sun gaisa

"Lafiya ƙalau Abba, na shiga gida ba kwa nan shi ne na fara biyowa ta wurin ku kafin in ƙarasa asibiti tun da za mu haɗu da Kawu Ƙarami a can"

"Ai ka kyauta, ka je wurin Alhaji kenan?"

"Eh"

"Su Baba fa (Grandpa)?"

"A'a ban tafi ba, sai na dawo dai"

"To shikenan, ya matar ta ka? Ba wata matsala?"

A hankali ya ce "babu"

"To Allah yayi albarka... Sadeeq" ya sake kiran sunanshi

"Na'am"

"Sadeeq na san halinka, duk cikinku ba wanda ya kai ka zafin zuciya, sai kuma ga shi Allah ya haɗa ka da wacce ba ka so, jiya na so mu zauna da kai amma ban samu ganinka ba, Sadeeq dan Allah kar hakan ya sa ka cutar da ƴar mutane, ka sani duk abunda ka mata sai kun tsaya a gaban Ubangiji tare, kar ka yarda ka ɗauki alhakinta dan Allah, ka bi ta a hankali na tabbata wata rana za ka ji daɗin aurenta"

Shiru Sadeeq yayi na ɗan lokaci, kafin ya ce "shikenan Abba, Nagode"

"Allah ya maka albarka"

"Ameen , zan wuce"

"To Allah ya kiyaye"

Miƙewa yayi ya bar office ɗin, ya kama hanyar zuwa asibitin su

Sunaiha kuwa tana ta baccin gajiya har kusan ƙarfe ɗaya, Ikram ta shigo tana ta sallama amma ba ta farka ba har sai da ta taɓa ta

Da sauri ta miƙe, tana ganin Ikram sai ta sauke ajiyar zuciya tana rufe ido, kafin ta zauna, Ikram ma zama tayi tana kallonta da mamaki

Ta ce "Ya dai? Me ya tsorata ki kuma?"

"Hmm ba komai" ta faɗa a gajarce tana dafa kai

Cikin rashin gamsuwa Ikram ke kallonta, ta ce "Sunaiha, let's be serious, ni sam ban yarda da wannan natsuwar ta ki ba"

Ɗaga ido tayi ta kalle ta, ta ce "kamar ya ba ki yarda dani ba kuma?"

Ajiye jakarta tayi gefe, ta ce "Sunaiha kin san na sanki ki!? There's no way da za ki ɓoye mun abu kuma ki ce ba zan gane ba...Sunaiha, what's wrong with you (meke damunki?), Dan wannan firgita da kika yi ba na natsuwa ba ne"

Rufe ido ta sake yi, kafin a hankali ta buɗe su, suka sauka kan agogon dake ɗaki, sakin baki yi tayi, sannan ta ce "Iky ƙarfe nawa nake gani?"

Duba wa Ikram tayi, ta ce "1:21pm, ko kin daina gani ne?"

"Innalillahi" ta faɗa kafin ta miƙe tsaye, ta ce "Ikram dan Allah zo ki taya ni dafa abinci, na tabbata Prince ya kusa dawowa"

"Abinci?"

"Eh, ki tashi mana"

"Tab, Sunaiha!?" Ta kira ta tana kallonta sosai, dan so take ta tabbatar wa zuciyarta wai da Sunaiha take magana

"Ki tashi mana dan Allah"

Yanda take janta ya sa Ikram ba ta iya cewa komai ba, ta miƙe suka wuce kitchen ɗin. Shinkafa da miya suka dafa, sai coslow da suka yi, sai dai fiye da rabin aikin Ikram ce tayi, ita Hajiya Sunaiha ido kawai ta zuba mata, sai kuma miƙe mata wasu abubuwa ko kuma ta ɗauko, har suka kammala kusan 2:48pm suka fito kitchen ɗin ɗauke da abincin da za su ci a plate bayan sun sa ma Sadeeq na shi a kula

"Sunaiha, kafin mu fara cin abincin nan, ki gaya mun what's going on? Meyasa ke kika yi mishi breakfast ɗazu? Yanzu kuma kin yi na rana? Kin manta ke amarya ce? Bai kamata ki fara shiga kitchen yanzu ba, after all ma, kin manta matsayin ki da na mahaifinki ne a garin nan? Ƴar Senator!? Ko da ba za'a kawo muku abinci daga gidansu ba, to at least ya kamata akwai ƴan aiki a gidan nan, kuma......"

"Enough Ikram! (Ya isa Ikram!)" Ta katse ta tana kallonta, kafin ta ci gaba "kin cika ni da tambayoyi kala-kala, wane kike so in fara amsa miki? Ki bari mu ci abinci first, yunwa nake ji kuma na gaji, ban saba kai wannan lokacin ba tare da na ci abinci ba"

"Na sani ai... Sunaiha gidan nan akwai matsala ni nayi observing, daga kawo ki jiya-jiya!?"

Rufe ido tayi tana girgiza kai da alamar ta dame ta, "dan Allah Ikram ki bari mu gama cin abinci, i will answer your questions (zan amsa tambayoyin ki)"

Ikram ba ta sake cewa komai ba suka fara cin abincin, ko rabi ba su ci ba sai ga Tiger ya turo ƙofar parlourn, a tare suka ɗaga ido suka kalle shi, Ikram ce ta ce "na gaida Ango a kyauta, me korar mutane dan kar ya ba mu kuɗin siyan baki"

Murmushi yayi, ya ce "ya gajiya"

"Alhamdulillah, ai kai ke da gajiya... sannu da dawowa"

"Thank you" ya amsa mata, kafin ya buɗe ɗakinshi ya shiga

Sunaiha na ganin ya shiga ta miƙe, ta ce "ina zuwa"

Dariya Ikram tayi ta ce "su Sunaiha an dan daɗin miji, to a dawo lafiya, amma ba jiranki zan yi ba, cin abinci na zan yi"

Murmushi Sunaiha tayi, a ranta ta ce 'in da ma na fara sanin daɗin mijin da ake cewa, daga jiya zuwa yau Allah kawai ya san irin kukan da wannan auren ya saka ni, amma har yanzu ina masifar son Prince'

Kitchen ta shiga ta ɗauko abincinshi cikin tray, sannan ta dawo ta shiga ɗakin, kan table ɗin dake cikin ɗakin ta ɗora, ta ce "ga abincin nan"

A hankali ya kalle ta bayan ya gama cire agogon hannunshi, "ke a gidanku ba'a koya miki sallama ba ne?"

"Yi haƙuri" ta faɗa sannan ta koma daga bakin ƙofa tayi sallama

"Sai kin koma daga waje, idan za ki shigo sai kiyi sallamar tun da ba ɗakin babanki bane"

Ba ta ce komai ba tayi yanda ya ce, ya amsa sallamar sai dai ita kanta ba ta ji shi ba, ƙasa ya nuna mata, ya ce "zauna"

Ba musu ta zauna, ya ce "wa ya dafa abincin nan?" Ya tambaye ta fuska a ɗaure

Cikin tsoro take ba shi amsa, "ni da Ikram"

"Ke da Ikram na ce ki dafa abinci ko ke kaɗai?"

"Ni...ni kaɗai, kawai ta...ta taya ni ne"

"Ƙarya kike yi, ita tayi ke kuma kika taya ta ko?"

Girgiza kai take yi, ta ce "a'a"

A tsawace ya ce "zan karya ki a ɗakin nan"

Cikin firgici ta ce "eh..eh, ita tayi"

Kallonta yake kafin a hankali ya ɗauke idonshi daga kanta, ya ce "me kika gaya mata? Kuma wallahi kika mun ƙarya za ki ga yanda zan yi dake, is better ki gaya mun gaskiya ko me zan miki kuwa, idan kika mun ƙarya na gane, ba ƙaramin illata ki zan yi ba"

Hawaye na shirin sauka fuskarta, ta ce "Wallahi wallahi Prin.... Umm...ba...ba abunda na gaya mata, na rantse maka da Allah"

A hankali ya ce "na sa ki rantsuwa ne? Simple question kawai na tambaye ki, kuma ki mayar da hawayen nan, dan idan kika yarda suka zuba sai kin cika kofi da su"

Da sauri ta rufe ido tana ƙoƙarin mayar da hawayen, sannan ya ce "to ba wannan ba, ko gidanmu, ko gidanku, ko wasu daga cikin ƙawayenki kika gaya wa wani abu da ya shafi ni dake, Allah kawai ya san irin hukuncin da zan miki"

Ɗaga kai tayi, dan ta ma kasa yin magana, ya ci gaba "ki je idan ta wuce, ki dawo ki kwashe wannan abincin, dan ke nace ki dafa mun ba wata ba, sannan idan ma kin san ba ki kai wa mai

gadi abinci ba, ki zuba ki kai mishi"

Da sauri ta ce "mai gadin!??"

"Ba mutum bane? Ko ba ya cin abinci?"

A hankali ta ce "yana ci" sannan ta fita daga ɗakin

Lokacin da ta koma parlourn Ikram kam ta gama cin abinci sai dai ba ta tashi daga wurin ba

Tana ƙoƙarin ɓoye damuwarta ta ce "kin ƙoshi ne"

"Full tank, alhamdulillah, ba kin shiga wurin Prince kin manta da ni ba? Har fitowa fa kika yi na ga kin sake komawa"

Murmushin yaƙe tayi, ta wuce kitchen ta zuba abinci a kula ta dawo parlour, ta zauna tana miƙewa Ikram kular, "dan Allah ki kai wa mai gadi to tunda kin gama"

"Mai gadi? Sunaiha na ga a gida ma lokacin da Mummy tayi zancen kai wa mi gadi abinci kika ce sai dai ya siyo da kuɗinshi kar daɗin ya mishi yawa, har daɗi ya goyi bayanki aka fasa...shi ne yau ke da kanki kika zuba wa mai gadi abinci?"

"Um...kin san aka ce wai idan mutum yayi aure hankali yake ƙarawa"

"Ai kam na yarda, tunda har kika fara hankali to tabbas dole kowa sai yayi hankali idan yayi aure, nima bari in zo inyi auren ko zan ƙara wani hankalin akan nawa" ta faɗa kafin ta miƙe ta fita

Girgiza kai Sunaiha tayi, ta ce "i hope i can stop you from getting married, saboda ba komai a auren nan face wahala da tashin hankali, na so ace ban yi auren nan ba kawai muyi ta haɗuwa da Prince ta mafarki yanda muka saba muna soyayyarmu har sai ranar da dan kanshi ya zo nema na, kwana ɗaya kawai amma na koma kamar ba ki ba?" Ta faɗa hawaye ba gangarowa kan kyakkyawar fuskarta, da sauri ta goge dan kar Ikram ta dawo ta same ta a haka

Su Hajiya na parlour da Umma da su Salma da Sajeeda suna ƴar hirarsu, Sultana da Safna kuwa sun tsare TV suna kallon wani indian series, hankalinsu ya koma can musamman Sultana da ba ta rabo da kallon indian series

Sameer na shigowa ya lura da yanda Sultana take kallon TV, yayi murmushi ya ɗauki remote ya canza tashar zuwa na kwallo, da sauri ta juya dan ta ga ko waye, suka yi ido biyu a Sameer, ɓata rai tayi ta ce "Ya Sameer wai meye haka? Ka mayar mana da kayanmu"

"An ƙi, ki koma parlourn ku ki kalla"

"Ai na ga kai ma nan ba parlourn ku ba ne, ka koma naku tunda kuna da shi"

"To ba zan yi ba a nan nake son kallon"

Kamar za tayi kuka ta kira Hajiya kasancewar ba su lura da abunda ma suke yi ba

"Hajiya kin ga Ya Sameer ko!? Ki gaya mishi ya mayar mana da channel ɗinmu"

Hajiya ta ce "Sameer ka fita ido na in rufe, meyasa kake son takura wa yarinyar nan ne kullum? In dai za ta kai ƙara to Sameer dai Sameer dai?"

Umma ta ce "ni fa Hajiya ban son kina wa Sameer haka, ta je parlourn su ta ƙarasa mana, awa nawa tayi ma tana wannan kallon? Nan fa har cewa nayi ta shirya za su tafi gidan su Safwan da Sadeeq amma ta ce kanta ke ciwo, suka fasa"

"Ai ciwon kai ba zai hana kallo ba, Sameer dai ba ya son zaman lafiya da ita na lura"

Ganin Hajiya ta koma yi wa Umma bayani a maimakon ta yi wa Sameer faɗa shi da mata dariya, sai kawai ta miƙe za ta je wurin shi karɓar remote ɗin, yana ganinta ya miƙe ya fara zagaya ɗakin tana bin shi, ganin ba ta da niyyar haƙura sai ya jefa mata remote ɗin kan cushion ya nufi ƙofar fita amma tsabar haushin da ya bata, ji take idan ba dukanshi tayi ba, ba za ta ji sanyi ba duk da kuwa ta san ya fi ƙarfinta

Tana kai wa ƙofa suka yi karo da Safwan, ya ce "ah ah, wai Sultana ke kullum cikin gudu kike ne? Lafiya?"

Salma na gefe tana dariya dan ita hakan daɗi yake mata, ta ce "Ya Safwan ita da mutuminta ne"

"Sameer ko? Shiyasa na ganshi da gudu shi ma....kin ga Sultana ƙyale shi, zan miki maganinshi"

Tana turo baki ta juya ta wuce parlourn su ba tare da ta ce komai ba, shi kuma ya ƙarasa ciki yana faɗin "Sultana manya"

Sai da suka gaisa da su Hajiya da Umma, da sauran ƙannenshi, sannan Umma ta ce "Safwan ai na ɗauka Amarya ba za ta bari ka fito ba yau"

Murmushi yayi ya ce "Umma kenan, har ta isa?"

Hajiya ta ce "isa na nawa kuma? Shi Sadeeq da yake ba mijinta ce ba, ai tun safe ya fito, kuma da ranan nan ma ya sake shigowa"

Safwan ya ce "wannan miskilancinshi ma zai iya sa ta koro shi"

Dariya suka yi gaba ɗaya, ya ce "ina su Anty Sameera?"

"Suna nan ciki, Saudat ce ma muke jiran dawowarta, dan ba ta jin daɗi, shi ne suka je asibiti da mijinta ɗazu"

Tana gama faɗar haka kuwa, sai ga ta ta shigo, gaisawa suka yi, Safwan yake tambayar ta ya jiki

"Alhamdulillah" ta amsa kafin ta miƙa wa Hajiya takardar da likita ya ba su, ta wuce wurinsu Anty Sadiya

Kallonta Hajiya ke yi har ta wuce, kafin ta ce "to ni idon nan ba madubi me zan karanta? Ungo Safwan ka duba mun"

Karɓa yayi ya duba, cike da murna ya ce "ƙaruwa za'a samu a Saraki's Family"

Cikin farinciki Hajiya ta ce "haba dan Allah?"

"Wallahi kuwa, abunda na gani kenan, ai kin san ina da alaƙa da likita"

Hajiya ta ce "kai Masha Allahu La Ƙuwwata Illa Billah, Alhamdulillah, Allah ya raba lafiya"

"Ameen Ya Allah " Safwan da Umma suka amsa

Su Salma kuwa ihu suka sa, suna murna za su ƙara samun wasu ƴaƴa

Momi da ke ƙoƙarin saukowa daga kan stairs, ta ji suna wannan murnar, ta ce "duk ku gama wannan murnar, wallahi in dai Sadeeq ba zai auri Sarah ta daɗi ba, to sai anyi yanda ba kwa so, da ni kuke zance, ba boka ba Malam, amma zan ba ku mamaki"

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*

*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
https://m.facebook.com/Moonlight-writers-association-109698351308376/

*""We are the moonlight writers we shine all over the world.""*

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~

_Always be the reason of someone's happiness never just a part of it. Be a part of someone's sadness never the reason for it._

*PAGE 35-36*

Tunda Sunaiha ta baro ɗakin Sadeeq, ya shiga yayi wanka ya fita ya bar su tare da Ikram, ba yanda Ikram ba tayi ba dan Sunaiha ta gaya mata abunda ke faruwa dan ita jikinta ya bata akwai matsala, amma Sunaiha ta dage akan ba komai, haka Ikram ta haƙura, sai da suka yi sallar la'asar, kafin ta bar gidan

Kasancewar dama Sadeeq ɗin yana waje, haka ya sa ba ta fi minti biyar da fita ba ya shiga gida. A kwance ya same ta, tana jin shigowarshi ta miƙe da sauri, ba ta yarda suka haɗa ido ba ta wuce ɗakinta, shi kuma ya zauna a parlourn

Ba ta fi mintuna goma ba, ya ga ta fito da alama shara tayi, ta wuce kitchen ta share dan Ikram tayi mata wanke-wanke, sannan ta fito ta share ƙofar baya, ta dawo parlour shi ma ta kakkaɓe shi, yana kallon yanda take yi, dan kallo ɗaya za kayi mata ka gane wannan aikin ba abunda ta saba da shi bane, kuma ta gaji, har ta gama bai ce mata komai ba, ta fita harabar gidan

Yanzu ma mai gadin sai da ya zo ya gaishe ta sai dai bai damu ya tsaya har sai ta amsa ba, ya ɗauki kujerarshi ya fita, ta samu ta share wurin sannan ta koma ciki. So take ta ɗan zauna ta
~~~~~~~~~~~~~~

huta amma tsoron Tiger ya sa ta wuce kitchen

Kiranta yayi, da sauri ta fito ta tsaya mishi a kai, wani wawan kallo ya mata, ya ce "ba za ki iya zama bane?"

Kan cushion ta zauna, ya sake cewa "ƙasa za ki zauna...idan kika ƙara gani na parlourn nan a zaune ke ma kika zauna kan cushion ba ƙasa ba, sai na mare ki" ba ta ce mishi komai ba ta koma ƙasa ta zauna, ya ci gaba "me za kiyi yanzu?"

"Abinci zan dafa"

"Ki bar shi ba zan ci ba, ke ki ci wancan ɗin da kika kawo mun ɗazu, abu ɗaya za ki mun, ƙarfe goma ki haɗa mun tea"

Wani irin daɗi ta ji, har da sa mishi albarka tayi a ranta, a zahiri kuma ta ce "to"

Za ta bar parlourn ya ce ta dawo ta zauna, ba musu ta zauna. Wayarshi tayi ƙara, Anty Sadiya ce, ɗauka yayi tare da yin sallama

"Tiger ka koma gida ne? Dan za mu zo yanzu" cewar Anty Sadiya

"A'a kar ku zo yau, ku bari sai gobe"

"Meyasa kuma?"

"Ku bari sai gobe dai na ce"

"Hmm, to Allah ya kaimu, ka gaishe ta"

A tare suka kashe wayar, Sunaiha na jin shi ko ɗaga kai ba tayi ta kalle shi ba, kallon TV kawai take yi, ji tayi yana wata wayar

"I'm so sorry My Jewel, wannan ƙaddararren auren ne ya hana ki gani na, amma gobe zan zo kin ji"

Shiru ya ɗan yi yana sauraren ɗayan ɓangaren kafin ya sake cewa "meyasa za kiyi tunanin haka? You i love only you dear, kuma ke kaɗai ɗin ce har abada, ba wata macen da zan so bayan ke, i love you...amma gobe zan zo sai in wanke laifi na, Happy?" Murmushi yayi kafin ya ce "to bye, take care" sannan ya kashe wayar

Tun da ya fara wayar nan, Sunaiha ke jin zuciyarta na mata zafi kamar ana hura mata wuta a ciki, wasu zafafan hawaye ke sauka kan fuskarta, ba tare da tunanin me zai ce mata ba, ta miƙe ta bar parlourn da gudu, kan gado ta kwanta tana wani irin kuka mai cin rai sosai

"Me nayi da nayi deserving irin wannan wulaƙancin? A gaba na mijina ke magana da wata har yana mata kalaman soyayya, ni da ko murmushi bai taɓa yi mun ba? Kenan da gaske ne ba ya so na? Ashe haka mutane ke ji idan suka ce suna so na ni kuma na gaya musu ina son Prince?" Sai kuma ta sake fashewa da wani kukan

Ƙarar saƙo ta ji a wayarta, a hankali ta share hawayenta, ta duba sai ta ga saƙon Najeeb kamar haka:
'Amincin Allah ya tabbata a gare ki tauraruwar mata, Amarya a gidan Prince, kin tafi kin bar ni da ciwon da ba wanda zai iya warkar da ni idan ba ke ba, amma farincikinki ya fi mun komai, tun da har kina jin daɗin zamanki da Prince wannan ma is enough...but i'm still with u, if u need my assistance, i'm always ready to help, I like u Cutie'

Tana gama karanta saƙon ta ji zuciyarta ta ƙara bugawa, jikinta yayi sanyi, ta ce "Allah sarki Najeeb, forgive me please" sai kuma ta ci gaba da kukanta

Su Anty Sadiya kuwa gidan Safwan suka wuce, ita da Sultana, Salma, Sajeeda da Safna, suka bar Anty Sameera ta zauna da Anty Saudat, sai dai ba ya nan. Tarbar arziki Nasreen ta musu duk da dai sun tarar da wasu ƙawayenta a gidan, fira suke yi sosai har ƙawayenta suka wuce suka bar su

Nasreen ta ce "Anty Sadiya ni ban san laifin da nayi wa Sunaiha ba, ɗazu na kira ta dan mu gaisa amma bata ɗaga ba, daga baya kuma da ta ɗaga sai ta mun kamar ba ta san wacece ba"

Kafin Anty Sadiya tayi magana, Salma tayi dariya ta ce "to ke ma Anty Nasreen wa ya aike ki kiranta?"

Sultana ta ce "ƙaddara mana da rabon ayi"

Anty Sadiya ta ce "zan ɓata ranku wallahi...kin ga Nasreen, ba abunda kika yi mata, ina sa ran gajiya ce ba wani abu ba, amma zan mata magana , saboda gobe zan koma gida na, nima mijina yayi kewa ta, amma zan fara zuwa wurinta kafin in wuce"

Dariya Nasreen tayi, ta ce "Anty Sadiya har da ku mazajenku na kewarku? Na ga kun tsufa ai"

Harararta tayi, ta ce "wane irin tsufa? Yara biyu ne za ki ce na tsufa? Zan ɓalla ki ne ni"

Sajeeda ta ce "tab, za ki ɓalla ta? To tun yanzu ki nemo lauyan da zai tsaya miki a kotu"

Dariya suka yi gaba ɗaya. Sun jima a gidan, sai da suka yi magrib kafin suka wuce

A hanya Salma na driving, ta ce "wallahi ni na ma rasa me Abba ya gani a jikin Anty Sunaiha da

har ya nace sai da Ya Sadeeq ya aure ta"

Sultana ta ce "bari kawai Salma, ni a rayuwa na daɗe ban ji na tsani mutum irin ta ba, haushi take ba ni"

Sajeeda ta ce "ni kuwa ban san meyasa kuke jin haushin ta har haka ba, ni ina sonta wallahi"

Sultana ta ce "har yanzu ba tayi miki abunda ta mana bane shiyasa, in da ma Ya Sadeeq ɗin yana sonta ne, da sai in ɗan so ta ko kaɗan ne"

Tsaki Anty Sadiya tayi ta ce "dan Allah ku mana shiru, haba! Wannan wane irin jaraba ne? Ku kenan kullum zance ɗaya? To da Sadeeq ɗin ba ya sonta ai bai ce ku zage ta ba ko!? Kar wscce na sake samun labarin ta zagi Sunaiha, kuma ku shirya dole gobe da ku za mu tafi gidanta"

Ɓata rai suka yi, ta ƙara da cewa "ni ki fara tsayawa wurinsu Grandpa mu duba shi, dan ƙafarshi ta tashi ɗazu"

Ba tare da ta ce komai ba ta ɗauki hanyar gidan su Grandpa, suna shiga harabar gidan suka ga motocin su Safwan da Sadeeq, ku sa da su tayi parking kafin suka fita

Da sallama suka shiga gidan, suka gaishe su, tare da yi wa Grandpa ya jiki, yana zaune kan resting chair ɗinshi ya miƙe ƙafa, Grandama na gefe

Anty Sadiya ta ce "ɗazu Alhaji ke gaya mun wai jikin ya tashi kuma"

"Wallahi kuwa Sadiya, yau gaba ɗaya a gida na wuni, ko masallaci ban iya zuwa ba"

"Allah sarki, sannu, Allah ya ɗauke wahala"

"Ameen"

Tiger na zaune yana duba magungunan da yake sha, kafin ya ce "waɗannan magungunan ba su ya kamata ka dinga sha ba yanzu Grandpa, ya haka? Kawu Ƙarami bai gan su bane?"

Grandama ta ce "bai gani ba, ai kasan halin Kakan naku, duk yanda Aliyu ya ce ya kawo maganin ya gani ko za'a canza, sai ya ce ba su ƙare ba"

Girgiza kai Sadeeq yayi, ya ce "waɗannan ba abunda za su rage mishi....to ya soft drinks ɗin da na ce ya daina sha, yana sha ko?"

Nuna mishi wata gora tayi na Fearless drink, ta ce "ka ga jarabar can, kafin magrib ɗin nan ya sha, bai daina ba"

Kallonshi yayi ya ce "meyasa ba za ka daina ba Grandpa? Na sha gaya maka drinks ɗin nan suna da matsala sosai wallahi, suna kashe ƙafa"

"Ƙyale ta Abubakar, yau ne fa kawai na ɗan sha, ka san abunda mutum ya saba, i'm so addicted to it"

"But it's affecting your health Grandpa"

Safwan ya ce "ni na ce ma ya bari a fitar da shi waje amma ya ce wani wai in ƙyale shi" yayi maganar yana mishi wani kallo

"Ba in da zan tafi fa, ni nayi sallama da abroad kuma yanzu ai" cewar Grandpa

Sadeeq ya ce "maganar Safwan gaskiya ne ai, sun fi mu kwararrun likitoci"

"Kai ma ai kwararren ne Abubakar, idan kuma ka gaji da duba ni ka gaya mun, ni ba wata ƙasa da zan tafi, in har Allah ya ƙaddara zan warke kafin mutuwa ta to zan warke, idan kuma da ciwon zan tafi, Allah ya bamu ikon cika wa da imani"

Sadeeq ya ce "ni ban gaji da duba ka ba Grandpa, Allah ya baka haƙuri, amma dan Allah ka kiyaye abubuwan da nake gaya maka"

"To My Doctor, an gama, zan kiyaye" yayi maganar yana murmushi

Shi ma murmushin yayi, ya ce "gobe dan kawo maka wasu magungunan"

"Allah ya kai mu...yanzu dai ku tashi ku wuce gida kun bar ƴaƴan mutane su kaɗai, ke ma Sadiya ku tashi, dare nayi, ba so nake kuna night driving ba"

Salma ta ce "Grandpa ni ke driving ai, idanu na ƙal suke"

Granda ya ce "ke dalla ware, ai gwara Sadiya ma tayi driving ɗin dan na fi yarda da hankalinta, amma ke da Sultana kam, Allah ya kyauta"

Sultana ta ce "yanzu matayen na ka ne marasa hankali? Haba mana Habibi" ta ƙarasa tana dariya

Anty Sadiya ma dariyar take, ta ce "Allah ya shirye ki"

Grandama ta ce "bar ni da ita Sadiya, a gaba na ake cewa mijina Habibi tsabar rashin ta ido"

Sajeeda ta ce "to Grandama ke kishin me za kiyi akan tsoho?"

"Ai soyayya ba ta tsufa"

Safwan ya ce "oh ni Safwan, su tsohuwa an san soyayya"

Dariya suka yi gaba ɗaya banda Sadeeq da murmushi kawai yayi, ya musu sallama ya wuce, kafin Safwan ya bi bayanshi, sannan su Anty Sadiya

Salma ta kalli Grandma, ta ce "kishiyas sai da safe" ta fita tana dariya

"Maganinku zan yi, ja'iran yara kawai"

Washe gari da safe kusan ƙarfe goma, Momi na parlourn ta, tare da Sarah

"Anty Baseera gani, kin kira ni ba ki ce komai ba, kuma na gaya miki makaranta zan tafi" cewar Sarah

"Hmm, tambayarki zan yi, kuma kar ki ɓoye mun komai"

"To ina jinki"

"Ina so ki gaya mun, shin har yanzu kina son Sadeeq?"

"Kai Anty Baseera, meyasa kike son tada tsohon zance ne? Wannan ya riga da ya wuce a wuri na ni"

"Na sani Sarah, ki amsa mun dai, kina son shi?"

Shiru ta ɗan yi kafin ta ce "har yanzu ina jin son shi a raina, amma kullum ina roƙon Allah ya cire mun shi a raina ya bani wani da ya fi mun shi alkhairi a rayuwata"

Jinjina kai Momi tayi, ta ce "that's good"

"Lafiya?" Sarah ta tambaye ta

"A'a ba komai, amma dai very soon za ki samu Sadeeq"

"As how?"

"Ba dai kina son shi ba!? Don't worry, tafi ki tafi makarantar, Allah ya kiyaye"

Maganganun Momi sun ɗaure wa Sarah kai, amma haka ta tashi ta wuce, sai da ta biya tayi wa

su Hajiya da Umma sallama, kafin ta wuce

Sadeeq kuwa ya gama shirin fita, yana parlour yana shan tea, Sunaiha na gefe tana danna wayarta, ba komai take kallo ba sai saƙon Najeeb na jiya ta ke ta nanata wa tana ƙoƙarin danne hawayenta musamman idan ta tuna wayar da Sadeeq ɗin yayi jiya

Muryarshi ta ji yana cewa "tun yaushe rabon da ki kira Mummy?"

A hankali ta ce "ban kira ta ba"

"Daddy fa?"

"Na kira shi ɗazu amma bai yi picking ba, may be yana aiki"

"Kin kyauta wa kanki kenan? Kalar soyayyar da kike yi wa mahaifiyarki kenan? Kwana biyu ba ki iya kira kin ji lafiyarta ba?"

"Ai ita ma ba ta kira ni ba ta ji yanda nake" ta faɗa tana turo baki

Cike da ɓacin rai ya ce "idan na mare ki sai haƙoranki sun zube wallahi, ita kike ji ta fara kiranki ke ba za ki iya kiranta ba? Shi Daddy da kika kira shi, kiranki yayi?"

Girgiza mishi kai tayi, ya ce "ok, so kike ki nuna mun kin fi son mahaifinki fiye da mahaifiyarki!"

"Ai ya fi so na, ita Mummy kullum sai ta mun faɗa,duk abunda zan yi ba zan burge ta ba, ta fi fifita masu aiki fiye da ni"

"Ka ji wata maganar banza, mahaukaciyar ina ce ke? Kin san me ake nufi da kalmar mahaifiya kuwa? Kin san girman son da uwa ke yi wa ɣaɣan ta? To ba Daddy ba, ko ke kanki, mahaifiyarki ta fi ki son kanki, duk faɗan da take miki so ne take nuna miki, amma dan kina wawuya ki ce ba ta son ki....to ki buɗe kunnenki da kyau ki saurare ni, kullum sai kin kira ta da safe da daddare kuma, ki sa wannan a daily schedule ɗinki, kuma cikin girmamawa nake so ki gaishe ta, kin ji ni?"

Ɗaga kai tayi ta ce "eh"

"Ki kira ta yanzu"

Ba musu ba fara dailing numbern ta, bugu biyu ta ɗauka, ta ce "Hello Mummy"

A hankali ya ce mata "sallama za kiyi" kasancewar tana kallonshi

Sallamar tayi, kafin ta ce "ina kwana?"

Daga ɗayan ɓangaren Mummy ta ce "lafiya ƙalau, kun tashi lafiya?"

"Lafiya ƙalau"

"Yau kin tuna da ni kenan, tunda kin samu Prince ko?"

"A'a" ta faɗa a hankali

"A'a ko eh, amma shi Prince ɗin na ki ko jiya sai da ya kira ni"

Da mamaki Sunaiha ta kalle shi, tea ɗinshi kawai ya ke sha, ta ce "kiyi haƙuri to"

"Dole zan haƙura mana Sunaiha! Ya na iya da ke? Dama dai na ce ba zan kira ki ba sai na fa iya hankalinki"

Murmushi tayi, Mummy ta ci gaba "amma na ji ki a natse, lafiya?"

"Lafiya ƙalau Mummy"

"To Allah ya muku albarka, ya ƙara daidaita tsakanin ku"

A ranta ta ce 'in da ma a daidaicen muke da har za a ce Allah ya ƙara daidaita tsakanin mu', a zahiri kuwa ta ce "ameen, sai anjima"

"To ki gaishe shi" daga haka suka kashe wayar

Sadeeq ya ce "kamar haka kullum za ki kira ta ku gaisa, anjima ki sake kiranta, saura ki ce kin manta....kuma su Anty Sadiya za su zo, kiyi ƙoƙari ki wulaƙanta mun su" ya miƙe ya fita

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦

*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~

_Don’t be a parrot in life, be an Eagle. A parrot speaks but can’t fly high, but an Eagle is silent & has the willpower to touch the sky._

*PAGE 37-38*

Tun bayan fitar Tiger, Sunaiha ke zaune a wuri ɗaya, gaba ɗaya ta rasa wane tunanin za ta kama saboda abubuwa kala-kala ke zuwa mata a rai, a hankali take sa hannu tana share hawayen fuskarta

Kusan mintuna ashirin tana abu ɗaya, ta ji an danna door bell ɗin parlourn, sai da ta share hawayenta kafin ta miƙe ta je ta buɗe, kallonsu take da mamaki saboda ba ta ji motsin gate ba ma bare kuma ƙarar motarsu

Anty Sadiya na murmushi ta ce "amarya yi haƙuri mu shiga mana"

Ba tare da ta fe komai ba ta koma cikin parlourn, kau tsaye kitchen ta nufa, ta ɗauko musu ruwa da drinks ta ajiye musu. Salma, Sultana, Sajeeda, Safna da Sajeed, suka haɗa baki wurin gaishe ta, can ƙasan maƙoshinta ta amsa musu ba ma lallai idan sun ji ba, ta wuce ɗaki, su kuma ko ta kan ruwan ba su koma ba suka ci gaba da firarsu

Tsawon lokaci ba Sunaiha ba labarinta, hakan ya sa Anty Sadiya ta bi bayanta, tana shiga ɗakin ta tarar da ita kwance akan gado da littafi a hannunta duk da cewar ba karantawa take yi ba, bakin gadon, Anty Sadiya ta ƙaraso ta zauna tana kallonta da kyau, kafin ta ce

"Sunaiha! Ki tashi ina son magana da ke"
~~~~~~~~~~~~~~~

Ko motsi ba tayi ba, ta ce "ina jinki"

Girgiza kai tayi, ta ce "mai hali ba zai daina halinsa ba dama...Sunaiha magana nace nake so zan yi dake, za ki tashi ko sai na kira shi?"

Da sauri ta miƙe ta dawo ƙasa ta zauna, ta ce "dan Allah kar ki kira shi, ina jinki wallahi"

Ganin yanda ta tsorata daga cewa za ta kira shi, ba ƙaramin mamaki tayi ba, saboda ba ta yi tsammanin har Sadeeq ya cusawa Sunaiha tsoronsa har haka ba, nuna mata gadon tayi, ta ce "taso ki dawo nan"

Ba musu ta koma kan gadon, Anty Sadiya ta ce "Sunaiha zuwa na gidan nan yana da matuƙar muhimmanci a wurinki, amma fa idan kin sauke wannan ji da kan naki kin saurare ni...na san irin zaman da kuke yi da Sadeeq a gidan nan, kuma kap gidanmu ba wanda ya sani sai ni saboda ni da Sadeeq tube da tyre ne, bai taɓa ɓoye mun komai da ya shafe shi ba"

Sunaiha na kallonta ta ce "umm..umm"

"Anty Sadiya" abunda ta faɗa kenan dan ta lura sunan da za ta kira ta a shi take tunani

"Anty Sadiya!?" Sunaiha ta faɗa a hankali, dan ita kanta ta ji nauyin sunan dan bata taɓa kiran sunan kowa cikin ladabi irin haka ba, ta ci gaba "kin san abunda yake mun? Shi ya gaya miki? Ba ya so na, ban san me nayi mishi ba? Ni ce amarya ta farko da ta fara fuskantar wulaƙanci a wurin mijinta tun ranar farko, ina son Prince..um Tiger, amma ya tsane ni..." Kukan da ya ci ƙarfinta ne ya hana ta ƙarasa maganar da ke bakinta

Ba ƙaramin tausayinta Anty Sadiya ta ji ba, saboda daga yanayin yanda take magana ta fahimci abun yana damunta sosai amma ta rasa wanda za ta gaya wa, jan ta tayi jikinta tana shafa mata baya da sigar rarrashi, sai da ta tsagaita kukan kafin ta ɗaga ta

"Sunaiha, ba kuka nake so ki mun ba, na sani, it really hurts, amma laifinki ne ba na kowa ba, kin san meyasa?"

Girgiza kai tayi ta ce "a'a"

"Halayenki, su ne suka ja miki wannan wulaƙancin, Sadeeq b mugun mutum ba sai dai yana da zafin zuciya wanda hakan ya sa mutane da dama suke ganin yana da wuyar sha'ani, amma to be sincere, he so much value the people he loves, more especially, his family...sai ke kuma Allah ya yi ki mutum me girman kai da wulaƙanta mutane, kuna ba ki tsallake kowa ba, har ƴan uwanshi da sauran mutane ma baki ɗaya, ba Sadeeq kaɗai ba, kap ahalinmu ba wanda yake shiri da mutum mai irin halayyarki, shiyasa muka yi mamaki matuƙa da Abba ya nace sai ya aure ki, amma zan miki wani taimako idan kin ji kina buƙata, dan nima ba wai ina yinki bane,

kawai ina tausaya miki ne a matsayin ki na ƴa mace, saɓanin sauran ƴan uwa na, dan kin ga Sameera da Saudat ba sa ma buƙatar ganinki, bare su kuma Sameer da Sauban da ko zancenki ba sa tsayawa su yi"

Wasu zafafan hawaye suka sauko kan fuskarta, gaba ɗaya kalaman Anty Sadiya sun ɓata mata rai, yanzu dama ashe akwai waɗanda za su ji ba sa sonta har haka, duk da irin kyaunta da matsayinta?, Ta ce "su waye Sameera, Saudat, Sauban da Sameer?"

"Za ki san su a hankali idan har kika so hakan, bayan su ma akwai Sajeed, Armaan, Aryaan da Ilham...ki ajiye zancdn waɗannan a gefe, kina so in taimake ki ko kuwa?"

Share hawayenta ta yi, ta ce "ina so"

"Da farko za ki fara sauke wannan ji da kan naki da girman kai, ki saurare ni, zan ɗora ki akan wasu halayya waɗanda matuƙar kika bi su, za ki ji daɗi, ba zan baki tabbacin Sadeeq zai so ki ba saboda yana da wacce yake masifar so, amma tabbas za kiyi martaba da daraja a idanunsa, zai daina wulaƙanta ki...bayan kin ajiye girman kai, za ki daina wulaƙanta mutane, ina so ki sa a ranki da ke da sauran mutanen duniyar nan matsayinku ɗaya, dan Allah ya azurta ki, ba shi yake nuna Allah ya fi sonki akan sauran bayinsa ba ko kuma kin fi su ba, abu na uku, ki kasance mai son ƴan uwansa da iyayensa, na huɗu, ki kasance mai girmama naki iyayen, musamman mahaifiyarki, dan yana daraja duk wacce za'a kira da uwa, na biyar, ki zama mai ladabi da biyayya, ba wai a wurinshi kawai ba, a wurin kowa ma, sannan ki kasance mai kula da addini da al'amuran addininki, sannan abu na ƙarshe, ki zama mai iya girki da tsafta, na jiki da muhalli kuma ki iya ado...kin ga waɗannan, muddin kina da su, to tabbas za kiyi daraja a idon Sadeeq"

Cikin raunanniyar murya, Sunaiha ta ce "amma duk cikin abunda kika lissafa, ba wanda nake da shi in banda tsaftar jiki na da kuma iya ado, amma ya hana ni yin adon"

Numfashi Anty Sadiya ta sauke, ta ce "kenan ba kya son shi?"

"Ina matuƙar ƙaunarsa wallahi"

"Then, dole za ki koyi waɗannan abubuwan saboda shi, i'm here to support you, zan ɗora ki akan kowane daga cikinsu ta yanda har ƴan gidanmu sai kinyi martaba a idonsu, sun daina tsanarki, are you ready?"

"Yes of course" ta faɗa tana jin son Anty Sadiya na ratsa ta, abunda ba ta taɓa ji ba kenan, lokaci ɗaya ta ji tana son mutum, ya burge ta, Prince ɗin ta ne na farko, sai kuma Anty Sadiya

"To shikenan, amma yanzu girki za ki tashi mu je muyi, sauran za muyi su ta waya, yau zan koma gidan mijina, za mu dinga yin v-call ina nuna miki yanda ake girke-girke da wasu abubuwa kafin in sake dawowa"

Ba ƙaramin daɗi ta ji ba, godiya take har da hawaye, Anty Sadiya ta lallaɓa ta, ta tashi suka shiga kitchen ba tare da sun ce ma su Salma komai ba. Jollof rice suka dafa, sai da suka yi serving ma su Salma, sannan suka dawo suka ƙarasa tuwon semovita da suka ɗora da miyar egusi wanda Tiger zai ci da daddare, sannan suka gyara komai da suka ɓata, suka zuba na su abincin suka koma ɗakin Sunaiha suka ci tare, Anty Sadiya na janta da fira har suka gama, sannan Anty Sadiya ta dawo parlour ita kuma ta shiga toilet tayi wanka, ta fito sanye da doguwar rigar shadda sea green da aiki light pink, kayan sun mata kyau sosai

Tana fitowa ta tarar da ba kowa sai Anty Sadiya, ta ce "suna ina?"

"Sun fita, wucewa za muyi dan har sun fitar motar...kar ki manta da duk abubuwan da na gaya miki, kuma kar ki kuskura ki sanar da shi wannan taimakon da zan miki dan zai ji ba daɗi saboda zai yi tunanin ina so in taya ki yaƙar waccan budurwar ta shi"

"In sha Allah Anty Sadiya ba zan saɓa miki ba, kamar yanda nayi miki alƙawari, tun daga yanzu ma na fara sauyawa, ko ba dan kowa ba, dan in samu Prince ɗina, na ɗauki tsawon shekaru ina dakon soyayyarsa, i can't let it go so easily"

"Kiyi dan Allah, dan Sadeeq, kuma dan kanki, ba wai dan Sadeeq ɗin kawai ba....mun barki lafiya" daga haka Anty Sadiya ta fita

Komawa tayi kan kujera ta zauna tana jin farincikin da ta kwana biyu ba ta ji ba, ji take tana dab da fara sabuwar rayuwa da Prince ɗinta, da har ta fara karaya, amma zuwan Anty Sadiya sai ta ji ta samu ƙarfin gwuiwa, tana wurin a zaune kiran Daddy ya shigo wayarta, da murna ta ɗauka

"Hello Daddy na...au, Assalamu alaikum"

Murmushi yayi ya ce "yaushe Baby na ta fara sallama?"

"Ɗazu mana"

Murmushi yayi kafin suka ci gaba da gaisawa, kusan mintuna biyar sannan suka kashe, ta tashi tayi sallar la'asar sannan ta fara gyaran gida

Tun a hanya su Salma ke maganar yanda Anty Sadiya ta saki jikinta da Sunaiha, amma ba abu da ta ce mu su har suka zo gida, ta wuce ɗakinta kai tsaye ta fara haɗa kayansu dan su wuce gida, Anty Sameera ce ta shigo tana ɗauke da Aryaan

"To Anty babba, kun dawo?"

Tana ta ƙoƙarin haɗa kaya, ta ce "kin gan mu sai yanzu, sam ban so na kai wannan lokacin ba tare da na je gida ba, saboda na gaya mishi ƙarfe uku zan dawo"

"Ai kam, yanzu sai ki gaya mishi kin je gyara auren wasu ne"

Dakata wa tayi daga rufe akwatin, ta ce "gyara auren wasu? Ya aka yi kika sani?"

"Kin manta tare da repoter ɗin gidan nan kuka tafi? Sajeeda!"

"Amma ai su ma ba su san abunda yake faruwa ba"

"Haka ne, ba za su sani ba, amma kar ki manta hankali na da na su ba ɗaya ba, daga yanda ta bani labarin kin taya ta aiki, na fahimci akwai matsala, oga Tiger ne fa, kuma na san ba sonta yake yi ba"

Numfashi ta ja, ta ce "akwai matsala kaɗan, amma komai ya daidaita, dan Allah kar ki gaya wa su Hajiya"

"Bakina da zip, ni da zan bar gidan nan ma yanzu, ga yaronki dai, ya dame ni da kuma tun ɗazu har yayi bacci"

Karɓar shi tayi, ta ce "Allah sarki My love...wai Saudat fa, tun da muka dawo ban ganta ba"

"Tun ɗazu mijinta ya zo ya ɗauke ta ai"

"Oh ni Halimatu, ni wannan mutumin sai in rasa irin son da yake wa Saudat wallahi" ta ƙarasa tana dariya

Anty Sameera ma dariyar tayi, ta ce "na ku wasa ne, yanzu suka zo a auren shiyasa, ni kin ga bari in je in nemo Ilham da Armaan, ban ma san wane kusurwa suka shige ba a gidan nan"

"To je ki nemo su, yau dai hijira za muyi wa gidan nan kenan"

Anty Sameera na dariya ta fita, ita kuma ta ajiye Aryaan kan gado ta ci gaba da haɗa kayan

Momi na wurin wata ƙawarta Hajiya Ladi, ta gama bata labarin duk abunda ya kawo ta, Hajiya Ladi ta ce "to ai Hajiya Baseera maganin matsalarki a bayyana yake, wurin boka na kan tudu kawai za mu tafi, za ki ga aiki da cikawa"

"A'a Hajiya Ladi, ke kin san ni bana sha'awar ziyartar bokaye, kawai shawara nake so ki bani, a irin kisisinar mu na mata ai zan iya ɗaukar mataki"

Sai da Hajiya Lafi ta nisa, kafin ta ce "shikenan zan baki shawara, amma zai ɗan ɗauki lokaci abunda zan gaya miki saboda a hankali za mu bi komai, matuƙar muka ce za muyi garaje, Sadeeq ɗin nan na lura yana da basira, tsaf zai gano mu"

"Haka ne, Sadeeq akwai saurin fahimtar abu, ba damuwa, a hakan ma ina jinki"

Dalla-dalla Hajiya Ladi ke zayyana wa Momi yanda za suyi dan ganin Sadeeq ya auri Sarah ko yana so ko ba ya so, tana kai wa ƙarshe, suka sa shewa gami da tafa hannu, Momi ta ce "shiyasa nake yinki ƙawata, wannan ai mai sauƙi ne, na gode miki"

Daga haka suka ci gaba da fira har kusan magrib, kafin ta wuce gida

Ɓangaren Tiger kuwa, bayan ya taso daga wurin aiki, sai da ya fara zuwa wurin Grandpa ya duba lafiyarshi, ua ba shi magungunan da ya ɗauko mishi, sannan ya ƙarasa gidansu domin gaida iyayenshi, yau ma kamar kullum bai damu ya je part ɗin su Momi ba dan ya san ya bar Kawu Ƙarami a asibiti, Momi kuwa dama ba gaishe ta zai yi ba, yana fitowa ya wuce gida

Lokacin da ya shigo Sunaiha na zaune tana kallo, gaishe shi tayi, bai damu ya amsa ba, ya wuce cikin ɗakinshi, sai da yayi wanka kafin ya dawo parlour ya zauna, ta tashi ta ɗauko mishi abinci sannan ta koma ƙasa ta zauna tana roƙon Allah ya sa kar ya tambaye ta wa ya dafa abincin, ai kuwa har ya gama ci bai ce komai ba, ta miƙe ta kwashe kayan sannan ta dawo

Zamanta ke da wuya, ta ji ƙarar saƙo ya shigo wayarta, gyara zamanta tayi sannan ta buɗe, Najeeb da saƙonshi kamar haka:
'Kece kadara mafi daraja wacce farashinki ba ya taɓa faɗuwa a rayuwata, kullum hauhawa kike sama tamkar shekaruna! A kowane lokaci ina ƙoƙarin ganin na cire ki a raina domin kin zama matar wani, sai ko wace daƙiƙa zuciya ta gaya mun take ke tawa ce, kasancewar ki matar wani ba shi ke nuna na rasa ki ba, za ki dawo gare ni wata rana, kuma na yarda da zuciya ta, amma ina so ki amsa mun idan haka ne, kin ji My cutie pie, i will always be ur best lover Sweetie...Najeeb Hameed Namadina loves u'

Tana kaiwa ƙarshen saƙon, ta jiyo muryar Tiger a tsawace "ke ba magana nake miki ba?"

Sai da ta tsorata har wayar na faɗuwa daga hannunta, da sauri ta ɗauka, sannan ta ce "na'am, kayi haƙuri ban ji bane"

"Dama ta ya za ki ji bayan hankalinki na cikin waya!? Idan kika yi wasa zan kwace wayar nan wallahi"

"Kayi haƙuri" ta sake maimaitawa

"Ke kika san shi, ni ki tashi ki haɗa mun tea"

Ba tare da ta iya cewa komai ba, ta miƙe ta nufi kitchen da waya a hannunta, so take ta daina tunanin message ɗin Najeeb, amma duk yanda tayi sai ta ji kalaman a kunnenta tamkar shi ke karanta mata su, har ta kammala haɗa tea ta je ta kai mishi

Tarar da shi tayi yana waya, ko ba'a gaya mata ba, ta san da wannan budurwar ta shi yake wayar, ajiye tea ɗin tayi tana ƙoƙarin wucewa, ya mata alama da hannu ta dawo ta zauna, zama tayi tana jin zuciyarta na dukan uku-uku, tana ƙoƙarin mayar da hawayenta amma sai da suka zubo, sam ba za ta iya jure jin kalaman da yake gaya wa budurwarshi ba dan ji take tamkar yana watsa mata garwashi a zuciya, Allah ya sani tana matuƙar son Sadeeq kuma tana kishinsa sosai, amma tsabar wulaƙanci ba ya tashi yin wayarsa sai a gabanta kuma ya sai hana ta tafiya

Har ya gama wayar ya kashe, ba ta juya ta kalle shi ba sai dai tana ta share hawaye, yana gama shan tea ya tashi ya bar mata parlourn, ita ma ta miƙe ta kashe TVn sannan ta wuce na ta ɗakin ta kwanta, har kusan ƙarfe sha biyu bacci ya ƙi ɗaukanta, abu biyu ke mata yawo a zuciya, saƙon Najeeb, me yake nufi da ita ne wai? Duk da cewar tayi aure kuma ya sani amma yake bin ta da waɗannan kalaman haka? Abu na biyu kuma Sadeeq, me yasa yake wulaƙanta ta haka? Meyasa sai a gabanta sannan sai yi waya da budurwarshi har yake gaya mata wai ba ya son matarshi dan ba ta da abunda zai sa ya so ta, to me ta rasa da yake gaya mata wannan maganar? Fata take Allah ya haɗa ta wannan budurwar, sai ta yaba wa aya zaƙinta, za ta tabbatar mata da ita kaɗai ke da Prince. Da wannan tunanin bacci yayi awon gaba da ita..........

INA BA KU HAKURI NA RASHIN POSTING DIN DA NAYI KWANA BIYU, HAKAN YA FARU NE SAKAMAKON JINYAR DA NAYI BA WAI DA SON RAI NA BA, I'M REALLY SORRY... WAƊANDA SUKA NEME NI TA GROUPS, TA PRIVATE DA WAƊANDA SUKA KIRA NI DAN JIN LAFIYA TA, I REALLY APPRECIATE, ALLAH YA SAKA DA ALKHAIRI... SUNAIHA MA TAYI MISSING DINKU, HAKA MASOYAN TIGER SHI MA YAYI MISSING DINKU😁❤️

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_If you believe you can, you probably can. If you believe you won’t, you most assuredly won’t. Belief is the ignition switch that gets you off the launching pad._

*PAGE 39-40*

Yau kusan sati ɗaya kenan da zuwan su Anty Sadiya wurin Sunaiha, kullum sukan yi video call aƙalla sau biyar, Anty Sadiya tana koya mata abubuwa sosai, kuma Sunaiha tana ɗauka dai-dai gwargwado, sai dai wanda take yi saboda shi ko a jikinshi, dan bai ma taɓa tsayawa ya lura da al'amuran ta ba, abu ɗaya kawai zai iya ba da tabbacin ta iya, shi ne girki, duk abincin da za ta dafa yanzu yana jin daɗinsu, amma ko da wasa bai taɓa gaya mata abincin na da daɗi ba. Duk da cewar abun yana damunta, amma ba ta daina ba kullum ƙara dagewa take yi, sai dai shi mai gadi ya tabbatar da ta fara sauya wa saboda idan ta fito yin shara tana amsa gaisuwarshi, wani lokacin ma ita ke fara gaida shi kasancewar babba ne, kuma tana kai mishi abinci ko da yaushe ba fashi

Kamar yanda Tiger har yau bai daina kiran budurwar shi a gabanta ba, haka ma Najeeb ba abunda ya rage a saƙonin da yake tura mata, sai ma ƙaruwa da yayi, dan yanzu sau biyu yake turo wa a rana, tun abun na damunta, har ta saba, sai dai kawai ta karanta ta wuce, ba ta taɓa
~~~~~~~~~~~~~~~~

replying ba kuma ba ta taɓa goge wa ba. Haka ma ta karɓi numbern su Umma da Nasreen, tana kiransu suna gaisawa

Kamar kullum, yau ma da daddare suna parlour a zaune yana ta fira da budurwarshi ɗin har ya gama, yau ji tayi ba za ta iya ƙyale shi ba, sai ta kalle shi, ba annuri a fuskar nan sai ka ce ba yanzu ya gama dariya ba, amma ta dake, ta ce "Tiger ina so zan tambaye ka"

Kamar ba zai amsa mata ba, ba tare da ya kalle ta ba, ya ce "ina jinki"

"Dan Allah meyasa kullum a gidan nan burinka ka ɓata mun? Ina ƙoƙarin ganin na faranta maka fa amma ba ka gani, ka san ina sonka amma a gaba na matsayina na matarka kake fira da wata har..."

Katse ta yayi da "ki rufe mun baki, yaushe kika fara samun ƙarfin zuciyar da za ki mun wannan maganar? Kin fara raina ni ne ko me?"

Cikin muryar tausayi ta ce "a'a, ni ba raina ka nayi ba, amma kar ka manta ni matarka ce, ban cancanci hakan daga gare ka ba"

"Mata? Mata fa kika ce! Ke a haka kina kiran kanki da sunan mata? Ni har yanzu ban ga kina da qualities ɗin da zan kira ki da sunan mata ba, an cutar da ni kawai da ba'a bari na auri wacce ke da wannan qualities ɗin ba"

Hawayen da ke kwance cikin idanunta suka zubo, ta ce "waɗanne irin qualities kake buƙata a wurin mata wanda ba ni da shi? Idan ma bani da shi, i promise you zan gyara wallahi"

"Ba za ki iya gyarawa ba ai saboda ba abu ne wanda kika saba da shi ba, amma kin ga waccan ɗin ta haɗa komai, dan haka idan kina tunanin zan sauya ra'ayi, you're surely deceiving yourself" daga haka kawai ya miƙe ya bar mata parlourn

Kuka take yi sosai, ta rasa me za tayi wa bawan Allahn nan ta burge shi, gani take kullum ƙara tsanarta yake yi, a hankali ta ce "i'm sorry Mummy, ina tunanin maganar Anty Sadiya ne da ta ce duk wanda yake saɓawa mahaifiyarsa, ba ya ɗaukar ta da muhimmanci, sai ya fuskanci yanda ba ya so a rayuwa, na tabbata Mummy saboda ke ne Allah ya jarabce ni da son wanda ba ya sona har na aure yake mun wannan wulaƙancin, ba yanda ba ki so ɗora ni akan hanya ba tun tasowa ta, amma na ƙi saurarenki sai dai Daddy...i'm so sorry for disobeying you Mummy, i'm sorry" ta ƙarasa tana kuka mai cin rai, ta jingina jikin kujera tana ci gaba da kukanta har bacci yayi awon gaba da ita

Tun asuba da ya tashe ta dan tayi sallah, ba ta koma ba, tana gama sallah tayi azhkar ɗin da Anty Sadiya ke koya mata, baan ta kammala ta gyara ɗakinta dan yanzu kam ta iya gyaran gida sosai kamar ba ita tayi ba, sannan ta fito kitchen ta haɗa mishi breakfast ta jera kan center

table, ta ci gaba da gyaran sauran gidan

Ƙarfe bakwai da rabi ya fito cikin shirin ƙananan kaya, yayi kyau sosai, gaida shi tayi ya amsa, tana ƙoƙarin zuba mishi breakfast ɗin

Ya ce "sauri nake yi, ba zan ci ba...ki shirya 12pm zan aiko Sameer ya zo ya kai ki gida ki gaida Mummy, zuwa 4pm zan zo in ɗauke ki mu je ki gaida Grandpa da ƴan gidanmu, ki ƙoƙari kuma ki ɓata mana lokaci" bai jira amsawar ta ba ya fita

Ita kuwa daɗi ta ji sosai, saboda tun zuwanta gidan ko gate bata taɓa leƙawa ba, ita da ta saba kusan kullum tana wurin yawo, jin yau za ta fita ya sa ba ta wani damu da rashin cin abincinsa ba, tana gama aiki ta zauna ita ta ci

Tana cin abincin ne kiran Najeeb ya shigo wayarta, tana kallo har yayi kira biyu, sai a na ukun da daure ta ɗaga

"Haba My Cutie, daga yin aure sai ki share ni!? Kullum sai na turo miki da message amma ba kya replying kuma i'm very sure kina gani"

"Dama gaya maka aka yi ba na gani ne? Idan kai ka manta ni matar aure ce, to ni ban manta ba, Najeeb ba ka da gurbi a zuciya ta, ka ƙyale ni for Gid sake" ta ƙarasa cike da ɓacin rai

"Zan ƙyale ki amma idan na daina numfashi a duniya, Sunaiha i love you, i can't do without you..."

"But i'm married" ta katse shi

"And so what!!! All i know is I love you, and i can't stop loving you"

Yanayin maganar shi ya bata mamaki, ta ce "Najeeb, ina tunanin ka haukace"

"Eh na yarda, na haukace in dai a kanki ne, kuma zan iyayin komai saboda ke, ina nan ina jiranki, na san wata rana za ki fahimci na fi kowa sonki kuma za ki kawo kanki"

"God forbid" ta faɗa a hasale ta kashe wayar tana tsaki, ta ce "wannan wane irin jarababben mutum ne wai?" Ta sake yin wani tsakin a karo na biyu, ta ci gaba da cin abincin ta

Kamar yanda Tiger ya sanar da ita, ƙarfe sha biyu ta gama shirinta tsaf, tana jiran isowar Sameer, sai ga shi ya shigo parlourn da sallama, amsa mishi tayi suka gaisa kafin ta ce "ka zauna in kawo maka ruwa"

Da mamaki yake kallon ta dan ba haka yayi tsammani daga gare ta ba, ya ce "a'a na gode...Ya

Sadeeq ya ce in zo zan kai ki gida"

"Eh haka ne, ina zuwa"

Cikin ɗaki ta shiga ta ɗauko jakarta da mayafi ta fito suka wuce. Ita ke nuna mishi hanya har suka kai gidan, ya ajiye ta sannan ya wuce

Da gudu ta buɗe ƙofar gate ɗin kasancewar a waje ta ce ya ajiye ta, mai gadi na ganinta ya miƙe da sauri yana ƙoƙarin gaishe ta, sai ya ji ta riga shi yin gaisuwar, yayi mamaki sosai, ya ma kasa amsa gaisuwar sai bin ta yake da ido har ta wuce ciki, Mummy ta gani ta nufi hanyar kitchen ɗauke da bowl a hannunta, da gudu ta rungume ta tana faɗin "Mummy!!"

Cike da fara'a Mummy ke kallonta ta ce "Amarya manya, zuwa ba sanarwa?"

"Mummy ba ki ji daɗin ganina ba kenan"

"Wa ya gaya miki, na ji daɗi mana"

Murmushi tayi ta ce "Mummy i missed you alot"

"A'a Sunaiha ban son daɗin baki, kin yi missing ɗina ko dai Daddynki?"

"A'a Mummy ke dai"

"Hmm, Sunaiha kenan, yanzu dai ki zauna bari in kai bowl ɗin nan kitchen"

Ajiye jakarta tayi da mayafi, ta ce "Mummy da kanki? Ina masu aikin?"

"Gaba ɗaya ba sa nan, na aike su, Larai kuma ba ta da lafiya"

"Ayya, to kawo in kai miki" ta faɗa tan karɓar bowl ɗin ta wuce kitchen

Har ta fito Mummy na tsaya cike da mamakinta, dan tun iya saninta da Sunaiha ba ta taɓa ganinta da ko da cokali bane ta karɓar mata, sai da ta fito sannan suka zauna tare suka sake gaisawa

Mummy ta ce "Sunaiha ashe za kiyi hankali? Ni fa kallonki nake ta yi kamar ba ke ba, kin natsu"

Murmushi tayi ta ce "Mummy ai ina da hankali mana.... Mummy" ta kira sunanta

"Na'am Sunaiha?"

"Mummy na san na ɓata miki rai sosai a baya, na saɓa miki, bana jin maganar ki, Mummy dan

Allah kiyi haƙuri ki yafe mun, i'm so sorry Mummy, i'm sorry..." Kuka ne ya kwace mata, Mummy ta jawo ta a jiki tana rarrashinta, tayi matuƙar mamakin jin wannan maganar daga bakin Sunaiha

Ɗaga ta tayi tana kallon cikin idonta, ta ce "Sunaiha, lafiya kuwa? Me yasa kike neman gafara ta?"

Tana share hawaye ta ce "ba komai Mummy, kawai dai na fahimci abunda nake miki ban kyauta ba, ke mahaifiya ta ce, kin fi kowa muhimmanci a rayuwa ta, kiyi haƙuri"

"Hmm, Sunaiha, kamar yanda kika ce ni mahaifiyarki ce, haka ne, kin kuwa san na fi kowa sanin halinki ko! Ni na san akwai abunda ya sa kika yi saurin sauyawa haka, tun yaushe nake miki wa'azi amma ba kya ji, yau kwatsam sai ga shi kin fara gane gaskiya....ko dai Prince ɗin ki ne ya miki magana kika ji?" Ta ƙarasa tana murmushi

Tana ƙoƙarin danne damuwarta ta ce "eh, amma ba shi ne ya fahimtar da ni rayuwa ba, Yayarshi ce"

"Kin gani ko, shiyasa nake gaya miki ki san darajar ɗan adam, yanzu Yayarshi ita ce ta ja ki a jiki har take gaya miki gaskiya, bayan nan kika gama zaginsu kina cewa ba ruwanki da su"

Murmushin takaici tayi, a ranta ta ce "hmm ai na gane komai yanzu, wanda nake so, nayi shirin ba wa muhimmanci da kula, shi ne wanda yake wulaƙanta ni, wacce nake ganin ba ta da amfani a wuri na, sai ga shi ita ke nuna mun so na gaskiya" wasu hawaye suka biyo kumatunta

Mummy ta ce "meyasa ki kuka kuma?"

Share hawayen tayi ta ce "ba komai Mummy"

Tayi murmushi ta ce "to albishirinki"

Murmushin ita ma ta ƙirƙira, ta ce "goro"

"Gobe su Hajiyar London za su zo"

Cike da murna ta ce "da gaske Mummy? Har da su Shareef?"

"Eh, har da Najma, nima ɗazu take gaya mun, sai dai ba da Abbanku ba saboda aikinshi"

"Allah sarki, i missed them alot"

"Kuma za su jima kafin su koma"

"Allah ya kawo su lafiya to"

"Ameen"

Sunaiha na murna ta ce "Mummy kina so in dafa miki abinci?"

"Abinci kuma? Wane irin abinci? Sai dai jagwalo"

"Mummy na iya abinci wallahi, Anty Sadiya ce take koya mun"

Kallonta tayi sosai, kafin ta ce "to tashi je kiyi in gani"

Ta miƙe da sauri ta faɗa kitchen, Mummy kuwa mamakin duniya ya ishe ta, gani take kamar ba Sunaihar da ta sani ba ce wannan, ta ce "wannan sauyin da nake gani a wurin yarinyar nan Allah ya sa mai ɗorewa ne, da na fi kowa murna" ta ƙarasa tana ta farinciki

Tiger na office ɗinshi ya sa laptop a gaba, har Yarima Muhsin ya shigo bai sani ba, sai da ya rufe laptop ɗin sannan Tiger ya ɗago ya kalle shi

"Haba Muhsin, meye haka kuma? Yaushe ka fara shiga wuri ba sallama"

Zama Yarima yayi, ya ce "sannu ɗan rainin hankali, sau nawa nayi sallama amma hankalin ka yana nan...wai kai me ke damunka ne haka? Kusan kullum sai ka sa hoton nan a gabanka kana kallo? Sai nake ganin komai ya wuce tun da kayi aure"

Numfashi Sadeeq ya sauke, ya jingina jikin kujera ya ce "lallai Muhsin ba ka san yanda zuciya ta ke azabtuwa ba ko da yaushe shiyasa, auren da nayi ba zai taɓa canza komai a zuciya ta ba"

"Ai kuwa kana tattare da wahala Tiger"

"Ba zan ga laifinka ba dan har yau ba ka san girman so ba, amma a hankali za ka gane, ni na yarda da ƙarfin so tun lokacin da ya kama zuciya ta"

"Amma naka yayi yawa"

"Muhsin! Yanda na gaya maka, ba za ka gane ba, so a bar maganar kawai....what's wrong?"

"To Allah ya kyauta...kawai missing ɗinka nayi, shi ne na biyo"

Dariya Sadeeq yayi ya ce "missing fa?!"

"Eh mana" ya faɗa shi ma yana dariya

"To ga ni" dariya suka yi gaba ɗaya, suka yi ta firarsu kamar yanda suka saba cikin girmama juna

Ƙarfe huɗu saura ƴan mintuna kaɗan, Sunaiha ta gama komai suna fira da Mummy tana yi tana duba agogon hannunta, doorbell suka ji an danna, Larai ta zo ta buɗe, Sadeeq ne sai da suka gaisa kafin ya ƙarasa ciki

Cike da ladabi ya durƙusa ya gaida Mummy, ita ma ta amsa da fara'a tana tambayarshi aiki

"Alhamdulillah Mummy"

"To Allah ya bada sa'a"

"Ameen ameen"

"Ka zo ɗaukar matarka kenan, tun yanzu?"

Murmushi kawai yayi ya sunkuyar da kai, Mummy tayi murmushi ita ma, ta ce "to tashi ku tafi, Allah ya kiyaye, ku ci gaba da haƙuri, musamman kai Sadeeq, kullum ina gaya maka"

"In sha Allah Mummy, mun gode...ina gaida Alhaji idan ya dawo"

"Zai ji" daga haka ya fita, sai da Sunaiha ta sake yin sallama da Mummy kafin ta fita tana mamakin halin Sadeeq, saboda idan yana magana da wasu sai ta ga ya sha banban da yanda yake mata, ta rasa me ta tare mishi a rayuwa

Lokacin da ta fita yana cikin mota a zaune yana jiranta, ta buɗe gidan gaba ta zauna, ko kallonta bai yi ba ya tayar da motar suka nufi gidansu Grandpa

Shi ne a gaba tana bin shi a baya har cikin parlourn, Grandma ce kawai a zaune tana lazumi, da dukkan alamu yanzu ta gama sallah, cike da fara'a ta tarbe su, suka zauna ta sa mai aikinta ta kawo musu ruwa da drinks

Grandma ta ce "yau dai Allah ya cika nufi, an kawo mun kishiyar nan ta wa"

Sadeeq ya ce "ai ba wurinki ta zo ba, Grandpa ta zo gani, ko kin taɓa ganin kishiya ta zo wurin kishiyarta?"

"Ba laifinka ba ne, wurin zama na ba ku shiyasa, da kun jira shi Grandpa ɗin, shiyasa nake cewa Safwan ya fi ka mutunci, sau biyu yana kawo mun Nasreen"

"Whatever dai, bari in je inyi sallah"

"Oho dai, shi ma yana masallacin" ba tare da ya ce mata komai ba ya fita

Mayar da hankalinta tayi wurin Sunaiha ta ce "sannu kin ji"

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "ya mai jiki"

"Ya ji sauƙi ai, ga shi yau har ya fita masallaci ma"

"Allah ya ƙara sauƙi, Grandma zan yi sallah nima"

"Anko kuka yi kenan ko? Kuna makara a sallah"

Dariya kawai tayi, Grandma ta tashi ta nuna mata toilet tayi alwala sannan ta fito tayi sallah, su na zaune sai ga Grandpa da Sadeeq sun shigo

Gaisawa suka yi da Sunaiha, kafin Sadeeq ya sake duba jikin Grandpa Sannan suka yi musu sallama, ba yanda Grandma ba ta so Sadeeq ya bari Sunaiha ta kai bayan magrib ba, amma ya ce zai sake kawo ta, tayi haƙuri, ba dan ta so b suka wuce duk da ta lura Sunaiha ta kasa sakin jiki da ita, ba kamar yanda Nasreen ta sake da ita ba lokaci ɗaya

Kai tsaye gida suka nufa, babban parlour suka shiga, Hajiya, Umma da Momi ne kawai a parlourn

Hajiya ta ce "maraba da Amarya" ta faɗa tana janta kusa da ita

Ɗaya bayan ɗaya Sunaiha ke gaishe su, kallo ɗaya tayi wa Umma ta gane ita ce mahaifiyar Tiger saboda yanayinsu ɗaya

Hajiya ta ce "shi ne sai yau ko"

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "kuyi haƙuri"

Umma ta ce "ai ba laifinki bane na sani, laifin Sadeeq ne"

Momi ta ce "a'a wane Sadeeq kuma, ni fa ba so nake kina ɗora mishi laifi ba"

Wani irin kallon tuhuma Sadeeq ke yi wa Momi, shi ya san ba ta saba saka bakinta ba idan ana irin haka a kan shi ba, sai yau, ita kuwa ba ta ma san yana yi ba

Sajeed ne ya shigo parlourn, Umma ta ce ya je ya kira su Salma, ga Antynsu, da gudu ya sake

bi hanyar part ɗinsu, ita kuwa Sunaiha ji tayi gabanta ya faɗi jin an ambaci a kira su Salma, maganar Anty Sadiya kawai ta tuna da ta ce wai sun tsane ta, sai ta ji ina ma kar a kira su data fi jin daɗi, shi kuwa Sadeeq miƙe wa yayi ya nufi ƙofar part ɗinsu ya bar su a wurin, sai murnar ganin Sunaiha suke ta yi, banda Momi da ita kaɗai ta san abunda ke ranta......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_WORDS & HEARTS should be handle with care, because when words are spoken and when heart is broken, they're the hardest things to repair.... TAKE NOTE_

*PAGE 41-42*
~~~~~~~~~~~~~~~~

Lokacin da su Salma suka fito parlourn, Sajeeda da Safna kawai suka gaida Sunaiha, Salma da Sultana kuwa ko kallon gefenta ba su yi ba, Salma ta ƙarasa kusa da Umma ta ce "Umma ga mu"

Wani kallo Umma ta mata mai kama da harara, ta ce " ga ku kuma? Ba ku ga Antynku ba ne? Ko ba ku iya gaisuwa ba?"

Kwaɓe fuska tayi ta ce "au, ban ganta ba ne shiyasa...ina wuni!" Salma ta faɗa tana kallon Sunaiha

Ita ma Sunaiha ɗin kallonta tayi tana mamakin yau ita ce aka yi wa irin wannan gaisuwar, in da Sunaihar da ce, wa ya isa?, A hankali ta ce "lafiya ƙalau, sannu"

Umma ta juya dan ta ga idon Sultana, ita ba za ta iya gaishe ta ba ne ko me, sai ta ga ba ta wurin, dan tun lokacin da Salma tayi wa Umma magana, ta bi ta bayansu tayi part ɗin su Sameer, ganin ba ta nan ya sa Umma yin shiru, su Safna kuwa sai ƙoƙarin jan Sunaiha fira suke yi, amma in banda murmushi ba abunda take musu, roƙon Allah ta ke ya sa Tiger ya fito su wuce gida

Sunaiha kuwa tana haura stairs ɗin su Sameer tana ta faɗa ita kaɗai, ba ma a jin me take cewa, har ta kai ƙofar parlourn ta tura, sam ba tayi tsammanin Tiger na ciki ba, ganinshi ɗin da tayi ne ya sa ta yin sallama dan ta tsab zai kore ta

Ba tare da ya ɗaga kai ba ya amsa mata sallamar, zuwa tayi ta gaishe shi kafin ta ce "ashe tare ku ka zo"

"Da wa?" Ya sake amsawa ba tare da ya kalle ta ɗin ba

"Sunaiha mana"

Sai a lokacin ya mata wani wawan kallo, ya ce "tare da wa kika ce?"

Ba ta fahimci dalilin kallon ba, hakan ya sa hankali a kwance ta maimaita "Sunaiha"

Rai a ɓace ya ce "Sunaiha?! Kai tsaye Sunaiha? Yaushe kika fara rashin kunya ban sani ba? Shekarunki ɗaya da ita? Ai ko sa'ar ki ce, kya ce mata Anty saboda kasancewar ta mata ta"

Sultana ba tayi mamakin jin yayi mata wannan faɗan ba, dan ta san ya tsani ya ga ƙarami ya raina babba, yanzu ma mantawa tayi da Tiger take magana, shiyasa tayi suɓutar baki ta ce Sunaiha, kai a ƙasa ta ce "i'm sorry Ya Tiger, mantawa nayi ne, ka san ba wani saba wa nayi da ita ba shiyasa nake manta akwai Anty a farkon sunanta, ka ga Anty Nasreen ma wani lokacin mantawa nake yi sai in kira ta Nasreen" ta shirya mishi ƙarya dan kawai a wuce wurin

Ba abunda ya ce mata, ya ci gaba da haɗa takardun da ya ɗauko daga tsohon ɗakinshi, miƙewa tayi za ta wuce ya kira ta

"Ina za ki je?"

"Zan duba ne ko Ya Sameer yana nan"

"Zo nan"

Dawowa tayi ta zauna, kafin ya ce "ina Sunaiha"

"Tana parlour wurinsu Hajiya"

"Me kika ga tana yi?"

Sakin baki tayi tana kallonshi, kafin tayi saurin cewa "nima ban sani ba, kawai dai tana zaune tare da su"

Ƙyale ta kawai yayi, sai ta miƙe ta bar parlourn ma gaba ɗaya, dan shirun da yayi ne ya tabbatar mata da ya gama magana da ita, dan haka yake musu, ba ya ce wa mutum ya tafi, sai dai ya ƙyale ka idan ka gaji da zama ka tashi. Shi kuwa ɗaukar waya yayi ya kira wani Dr Abbas

Wannan ɓangaren kuwa Sarah ce tare da mahaifiyarta su na zaune, mahaifiyarta ta kalle ta, ta ce "Sarah"

"Na'am"

"Mun yi magana da Antynki kwana biyu da suka wuce, ta ce za ta kira ki kuyi magana, amma na ji har yanzu ba ki ce mun komai ba, ko ba ta kira ki ba?"

Ɗan ƙaramin tsaki tayi, ta ce "ta kira ni, amma akan maganar Sadeeq ne, ban san meyasa Anty Baseera ta nace akan Sadeeq ɗin nan ba wallahi, na gaya mata na haƙura da shi"

"Hmm, Sarah kalle ni nan, ni na san har yanzu kina son Sadeeq, ko ba haka ba?"

"Ina son shi Mama, amma..."

"Amma me?" Ta katse ta, "Sarah ina so ki yi rayuwar farinciki ne, ina so kiyi aure a gidan da za ki huta, gidan da za ki ji daɗi, kuma ki samu wanda kike so"

"Wanda nake so ɗin Mama idan shi kuma ba ya so na kuma fa?"

"Ke za ki sa ya so ki mana, ke fa mace ce,kuma kyakkyawa, duk namijin da kika yi ra'ayin ya so ki, ai dole sai ya so ki"

"Na sani Mama, amma fa kar ki manta, Sadeeq yayi aure, kuma ya daɗe da gaya mun yana da wacce yake so"

"To Sarah, bari in fito miki a mutum yanda za ki fahimce ni, Sadeeq yayi aure amma wacce ya aura kwata-kwata ba sonta yake yi ba, sannan waccan ɗin da yake so tayi aurenta ita ma tun lokacin da ta samu labarin yayi aure, kin ga kenan dole ya shafe ta a rayuwarshi, wannan matar ta shi kuma tun da ba sonta yake yi ba, tsab za ki iya karkato da hankalinsa zuwa wurinki, wataƙila ma ya sake ta sai ya aure ki"

Shiru Sarah tayi kafin ta ce "yanzu Mama kina nufin duk irin son da yake mata, aure ta je tayi?"

"To shi ma ba auren yayi ba?"

"Amma ai ba da son ranshi ba, na tausaya mishi dan na san yana jin ba daɗi, ya so ta fa sosai wallahi" ta faɗa cikin sigar tausayi

Mama ta ce "nima na tausaya mishi, to shiyasa muke so ke da kike sonshi, ke ce za ki iya gane halin da yake ciki har ki sa ya manta da wanna damuwar, ta hanyar dawo da soyayyarki a gare shi"

"Allah sarki, Anty Baseera ba ta mun bayani yanda zan fahimta ba ne...to amma Mama, ta ya zan dawo da hankalinshi wurina har in ba shi farincikin da yayi deserving?"

"Kyautatawa da kulawa, kin san shi Sadeeq juyayyen mutum ne wani zubin, ba kai tsaye za ki je mishi ba, a hankali za ki dinga kyautata mishi kina ɗan nuna kulawarki akanshi, da musamman mahaifiyarshi, ki kula da ita sosai, to za ki ga shi da kanshi ma zai kawo kanshi har komai ya daidaita tsakanin ku"

Wani irin farinciki ne ya ratsa zuciyarta, dama can har yanzu son Sadeeq bai barta ba, kullum ƙaruwa yake yi, musamman ma idan ta ganshi, jin wannan bayanin na mahaifiyarta ya sa ta ji tamkar ma ta same shi, ta ce "in dai haka ne, to tabbas Sadeeq ya gama zama na wa"

"Yawwa, ko ke fa, ana ta nusar da ke kina bijirewa"

"Ai yanzu na fahimta Mamana" ta ƙarasa tana murmushi

Ita ma murmushin tayi, ta ce "to bari in shiga ciki kafin a kira magrib"

"To" ta miƙe ta nufi ɗakinta

Tana shiga ta mayar da ƙofa ta rufe, ta zauna ta fara ƙoƙarin kiran Momi, ita kuwa ganin kiran Yayarta ya sa ta miƙe ta bar parlourn zuwa part ɗinta tana ɗaga wayar

"Hello Yaya" ta faɗa bayan ta zauna ka kujera

"Baseera na yi yanda kika ce"

"Ta amince?"

"Ƙwarai kuwa, ina gaya mata duk yanda kika tsara, ta amince ba tare da ta musanta mun ba"

Cike da murna Momi ta ce "yawwa, aikinki yayi kyau Yayata, kin ga yanzu mun gama da matsalar step one"

Murmushi tayi, ta ce "to sai step two, ya za'a yi?"

"Ki kwantar da hankalinki, step two Sarah ce za ta mana shi, wannan bayanin kawai da kika yi mata, shi zai sa tayi step two ɗin ba tare ma da ta san tana yi ba, kin ga kin yi step one, Sarah za tayi two, ni kuma zan yi three, step four kuwa wanda shi ne final, manyan family ɗin nan za suyi mana shi da kansu, ko su na so ko ba sa so"

Dariya Mama tayi, ta ce "kai Baseera, ba ki da dama, in dai kika ƙwallafa rai a abu to sai burinki ya cika, na ɗauka kina girma kina dainawa ne, ashe ƙara samun basira ma kike yi akan al'amuran ki, ba'a banza kika ci sunan Baseera ba, Baseera iyayen basira" ta ƙarasa tana dariya

Ita ma Momi dariyar take yi ta ce "Yaya kenan, to me za'a fasa? Mutuwa ko hisabi? Kin ga gwara ayi sha'ani kawai...yanzu dai sai anjima zan kira ki, zan koma wurin waɗancan kar su yi tunanin wani abu, saboda Sadeeq ɗin ya kawo mana matarshi"

"Kishiyar ƴata za ki ce" su na dariya suka kashe wayar

Momi tayi dariya ta ce "na fara ganin haske a shiri na, kuma sai buri na ya cika ko ta wake hali ne kuwa" ta miƙe ta koma parlourn

Sai da suka yi sallar magrib, kafin Sadeeq ya zo suka yi musu sallama suka koma gida, yana yin parking ya fita ya tafi masallaci, sai da yayi sallar isha'i kafin ya dawo gidan, lokacin ita kuma har tayi wanka tayi sallah ta ƙara turara ɗakin da turaren wuta, sannan ta dafa mishi coffee kamar yanda ya umarce ta

Ɗakinshi ya wuce, shi ma yayi wanka ya fito sanye da pyjamas baƙi, ya zauna ya fara shan coffee ɗin shi, lokacin ta fito daga kitchen da plate ɗin indomie ta zauna ta fara ci, jira take ta ji ya fara wayarshi da ya saba, amma har ta kammala ta kai plate da cup ɗin shi kitchen ta dawo

ba ta ga yana da alamar yin waya ba, wasu files kawai yake ta aikin cikawa

Sai da ta sauke ajiyar zuciya kafin ta ce "Ya Sadeeq" ta kira kamar yanda Anty Sadiya ta bata shawarar kiranshi

Da mamaki ya ɗaga ido ya kalle ta, kafin ya ce "ya aka yi?"

"Gobe su Hajiyar London za su zo"

"Ban san ta ba" ya faɗa bayan ya ci gaba da rubutun da yake yi

Ba tayi mamaki ba dan ya ce bai san su ba tun da bai taɓa ba ta lokacin shi ba ma bare ya san ƴan uwanta, ta ce "Hajiyar London matar Yayan Daddy ce, a London suke, wurinsu na zauna lokacin da nayi karatu a can, ita ce za ta zo da yaranta, Anty Najma da Shareef"

"Allah ya kawo su lafiya" ya faɗa ba yabo ba fallasa

Ta sake cewa "Ya Sadeeq ina so ne zan je gida ne gobe dan in gan su"

"Idan suka zo goben, ba kwana za suyi ba za su sake komawa ne?"

"A'a, za su daɗe a nan ma"

"To ba inda za ki je"

Ranta ya ɓaci amma ba ta nuna mishi ba, ta ce "sai jibi zan tafi?"

"A'a" ya amsa a taƙaice

"Sai yaushe to?"

A tsawace ya ce "ba za ki tafi ba na ce, sai ranar da na ga ya kamata"

Shiru tayi tana ji ranta yana ɓaci, sai kawai ta juya ta cigaba da kallonta duk da ba fahimta take yi ba, so take ta wuce ɗaki ta kwanta ko za ta ji sassauci, amma ta san ba bari zai yi ta wuce ba sai ya tashi, ita wannan hukuncin na shi mamaki yake ba ta, haka tayi haƙuri ta zauna har sai da ya gama ya tashi sannan ta tashi ita ma

Bayan shigarshi, ya gama abunda yake yi sannan ya kwanta, ya jawo bedside drawer ya ɗauko wani hoto, yana kallo yana murmushi kusan mintuna uku sannan ya ce "i'm sorry dear, but i still love u and i will love u till eternity, ba wani ko wata da suka isa su raba ni dake, i love u my Jewel, i'm coming to you very soon" ya sumbaci hoton sannan ya mayar da shi ya kwanta

Washe gari da safe ta gama haɗa breakfast, sai ta shiga gyara kitchen, tana fitowa ta tarar da ya gama yana shirin fita

Ya ce "kiyi abincinki ke kaɗai da rana sai mai gadi, ni sai da daddare zan dawo"

"Meyasa? Ina za ka tafi?" Ta tambaye shi cikin kulawa

Kallonta yayi kafin ya ce "wurin budurwa ta zan tafi, kwana biyu ban ganta ba"

Sauke idanunta kawai tayi, a hankali ta ce "Allah ya kiyaye"

Shi ma a hankali ya amsa mata da "ameen" sannan ya fita

Girgiza kai tayi ta koma ta ci gaba da gyaran da take yi sannan tayi wanka ta dawo parlour. Haka kawai zuciyarta ke raya mata ta tashi ta shiga ɗakinshi ta gani, meyasa yake rufe shi idan zai fita kuma tana da spare key na ko ina amma banda na ɗakinshi, miƙewa tayi kuwa ta tura ƙofar ɗakin a hankali, wani ƙamshi mai daɗi wanda ya gauraye da sanyin AC ya daki hancinta, sai da ta lumshe ido kafinta kutsa kai ciki

Yanda tsarin ɗakinta yake, haka wannan ɗin ma yake, sai da ta gama kallon ɗakin da kyau, sannan ta nufi wardrobe ta buɗe, kayanshi ne a jere sun sha guga har sun gaji, ta mayar ta rufe, nufi wurin dressing mirror, daga gefe set ɗin glasses ɗin shi ne, ta buɗe drawer ta jawo wani ƙaramin box ta buɗe, shi kuma set ɗin facemask ne a ciki, ta ce "shi wannan facemask ɗin da glass kamar abun dole, kullum sai ya sa su sai ka ce mai wani mugun abu a fuska...umm, kayi ta sakawa ma, ko ba komai kana ɓoye mun kyakkyawar fuskarka daga sauran mata"

Ta rufe ta mayar, ta koma kan gado ta zauna, ta buɗe bedside drawer shi ma, hotuna ta gani a watse za su kai guda goma, sai dai a kife suke, ba ta san ko hoton waye ba, hoton da ke sama, ta ga an rubuta PRINCESS JEWEL, sunan ya tabbatar mata da hoton budurwarshi ce, ta kai hannu za ta ɗauko, ta ji muryarshi

"Sannu da ƙoƙari"

Firgita tayi, ta juyo tana kallonshi, cikin tsoro ta ce "kayi haƙuri, na ga ka bar ƙofan a buɗe ne shiyasa na zo in gyara maka ɗakin, amma..."

Ɗaga mata hannu yayi, ya ce "kin ji na ce wani abu ne? Fita ki ba ni wuri kawai"

Jiki ba ƙwari ta fita, ya ɗauki abunda ya dawo da shi, sannan ya rufe ƙofar ya wuce.........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*

♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~~

_An Airoplane Is Always Safe At Ground. But It's Not Made For That. So Always Take Some Meaningful Risks In Life To Get Great Acheivement._

*PAGE 43-44*

Shirye-shirye Mummy ke yi ba kama hannun yaro na zuwan su Hajiyar London, ta sa an gyara musu part ɗin da za su sauka, sannan an girka musu abinci kusan kala biyar, da snacks da drinks, haka aka jera musu shi akan babban dinning table ɗin su, jiran isowarsu kawai ake yi

Ƙarfe uku da ƴan mintuna, jirginsu ya sauka, driver ya ɗauko su zuwa gidan Senator. Da sallama Suka shiga cikin parlourn, da murmushi ɗauke a fuskokinsu, Mummy miƙe wa tayi tana murmushi ta amsa sallamar sannan suka rungume juna ita da Hajiyar London cike da murna

Najma ita ma cikin murna ta rungume Mummy tana faɗin "i miss you Mumcy"
~~~~~~~~~~~~~~~~~

"Miss u too My dear" Mummy ta faɗa

Sharif na gefe yana kallonsu, ya ce "ina Daddy? Na san shi kam yayi missing ɗina, ke Mummy dama ba so na kike yi ba"

Dariya Mummy tayi, sannan ta miƙe mishi hannu suka yi musabaha, sannan ta rungume shi ta ce "haba Sharif, nayi missing ɗinka mana sosai ma, duk da cewar dai kai ba ɗana bane, kawai kara nake wa Hajiyarka"

"Ba komai dai" cewar Sharif yana ƙoƙarin zama kusa da Hajiyar London

Hajiyar London ta ce "ƙyale ta My boy, ni na san ta fi kowa missing ɗinka ma"

Dariya suka yi, kafin Sharif ya sake cewa "Mummy, Daddy fa?"

"Na san yanzu ma yana hanya in Allah ya yarda, ya so ya bi driver wurin ɗauko ku ai, amma meeting ya riƙe shi"

"Allah sarki, Allah ya dawo da shi lafiya"

"Ameen" cewar Hajiyar London

Najma ta ce "kowa da abunda ya dame shi dai, ni kam Mummy ina Hajiyata? Ƙawar faɗa na"

Hajiyar London ta ce "kin riga ni ne kawai ai, ina so in tambaya nima, ina Baby?"

Murmushi Mummy tayi ta ce "tana gidanta, ita ma sai jiya nake gaya mata zuwanku"

Hajiyar London ta ce "ai na ɗauka ko za ta zo"

Mummy ta ce "ni ma haka nayi tsammani, sai dai ɗazu mijinta ya kira ni yana ba ni haƙuri, ba za su samu zuwa yau ba"

Hajiyar London ta ce "Allah sarki, ba komai ai"

Najma ta ce "no wahala, Allah ya kai mu goben lafiya....amma Mummy nayi mamaki yanda aka ce Sunaiha Prince ɗin nan na ta ne ta aura"

Mummy ta ce "ai ba'a mamaki da lamarin Ubangiji, ni kai na ban taɓa tsammanin akwai wannan Prince ɗin a duniya ba"

Dariya suka yi baki ɗaya, Sharif na ɓata fuska ya ce "Mummy wai ba'a gama abinci bane? Yunwa fa nake ji"

Mummy ta ce "sarkin ci, tashi ga shi nan a dinning...Hajiya mu je ku ci abinci"

"A'a sai nayi wanka tukunna"

Najma ta ce "nima dai kam, wankan nan first, sannan abinci, ƙyale wannan ƙazamin acicin ya fara ci"

"Oho dai" cewar Sharif yana nufa hanyar dinning

Hajiyar London da Najma kuwa suka nufi hanyar part ɗinsu, Mummy ta raka su. Shigar su ke da wuya sai ga Daddy ya turo ƙofa da sallama, kai tsaye wurin Sharif ya nufa yana ta fara'a, shi ma miƙewa yayi suka rungume juna

Daddy ya ce "Malam Sharif"

"Yes Daddy, ina wuni"

"Lafiya ƙalau, how was your flight?"

"Good and fine, alhamdulillah"

"Masha Allah....ina Najma da Ummanku?"

"Sun shiga ciki"

"Sai kai aka bari sarkin ci ko?"

Dariya Sharif yayi, dan in dai abinci ne kowa ya san Sharif ba ya wasa, Daddy ya ce "to zauna ka ci gaba, nima zan shiga in yi freshen-up kafin su fito"

"Alright Daddy, a fito lafiya"

Daga haka ya ci gaba da cin abincin shi, Daddy kuwa ya wuce

Sunaiha na kwance a parlour tunanin duniya ya dame ta, gaba ɗaya ta rasa me ke mata daɗi, kiran Ikram ya shigo wayarta

"Amaryar Prince"

Tattaro murmushin ƙarfin hali tayi ta ce "Hajiya Ikram, ya gida?"

"Normal, ya kike ya Prince?"

"Ba ruwanki, Ikram shikenan daga kawai nayi aure sai ki share ni? Sau nawa kika zo gidan nan?"

Dariya Ikram tayi ta ce "ke ma sau nawa kika zo gidanmu tun lokacin da kika yi aure? Ko sau ɗaya fa ba ki zo ba"

"Amma ya kamata ki gane yanzu fa ba da bane, dole sai da izinin mijina"

"Su miji manya, to ban ga daman zuwa ba"

"Kar Allah ya sa ki zo ɗin to" ta faɗa rai a ɓace

"Haba Habibiya, daga magana kuma, calm down zan zo"

"Matsalarki ce yanzu ai" ji tayi an danna doorbell, hakan ya sa ta ce "ina zuwa, i'll call u back" ta katse wayar sannan ta miƙe ta nufi ƙofar

Anty Sadiya ce a tsaye, cike da murna ta tarbe ta suka ƙarasa ciki, sai da ta kawo mata ruwa da abinci da wani watermelon juice da tayi sannan ta zauna suka gaisa

"Ina su Armaan?"

"Suna wurin kakarsu, Mahaifiyar Abbansu"

"Ayya, ashe yau za ta kwashi rigima"

Dariya tayi ta ce "Laila dai za ta yi fama, ai kakarsu rigimammiyar tsohuwa ce"

Dariya Sunaiha tayi, ta ce "ke dai kika faɗa ba ni ba"

Anty Sadiya ta sake yin dariya, kafin ta kalli abincin ta ce "Sunaiha sai kace kina jiran zuwa na, wannan abinci haka?"

"Na ji daɗin ganinki ne dai kawai"

"Kin ji daɗin ganina ko dai so kike ki nuna mun ba lectures ɗin banza nake miki ba, kina ganewa" ta ƙarasa tana murmushi

"Ashe dai kin fahimta" ita ma ta amsa tana murmushi

"Yayi kyau, daga ido ma mutum zai san abincin nan yayi daɗi ai"

"Na gode"

Sauka tayi ta fara cin abincin suna fira, sai da ta kammala, Sunaiha ta kwashe kayan sannan ta dawo ta zauna, Anty Sadiya ta ce "komai yayi daɗi Sunaiha, kina ƙoƙari"

"Thanks once again....yawwa Anty Sadiya"

"Na'am"

"Dama ina tunanin kiranki sai ga ki, kin ga Ya Sadeeq yana jin maganar ki, dan Allah ki gaya mishi ya bari in tafi gida"

"Gida kuma? Me za kiyi a gida bayan ya gaya mun jiya ya kai ki"

"Eh haka ne, amma yau su Sharif da Anty Najma suka zo, ina so zan gansu amma ya hana"

"Su waye haka kuma?"

"Cousins ɗina ne"

"Ayya, ko su ne Mummy ta ce su na London?"

"Eh su ne"

"Ai kuwa bai kyauta ba, zan mishi magana, zai bari ki tafi"

"Nagode sosai Anty Sadiya"

"Kar ki damu..ina so ma zan kawo miki su Sameera da Saudat, dama Saudat ce tayi delaying ɗinmu saboda ba ta jin daɗi"

"Allah ya ba ta lafiya"

"Ameen" daga haka suka ci gaba da fira, sai bayan Magrib sannan Anty Sadiya ta wuce

Tana kitchen tana haɗa abinci, ta ji ƙarar shigowar saƙo a wayarta, tayi zaton Najeeb ne shiyasa ba ta koma ta kan wayar ba ta ci ga da aikinta, sai da ta kammala sannan ta ɗauki wayar ta fito tana duba saƙon

Sabuwar number ce, abun da aka turo shi ne
'ki shirya kafin in dawo za mu fita'

Tana gama karantawa zuciyarta ta bata wannan Tiger ne, amma tunanin da take yi, dama yana da numbern ta ne? Ita dai ta san ba ta da numbern shi, kuma ta kasa tambayarshi saboda tsoron wulaƙancin shi, tana kuma jin nauyin yanda za ta tambayi Anty Sadiya, dan akwai kunya ta ce wai ba ta da numbern shi

Ajiyar zuciya ta sauke kuma, cikin farinciki ta ce "whatever dai, bari in shirya kafin fitinannen Prince ya dawo ya ce ya fasa, na tabbata Anty Sadiya ta mishi magana"

Da sauri ta shiga ɗaki, ta je tayi wanka, ta saka atamfa ɗinkin riga da skirt, colour brown da peach, tayi kyau sosai, ta ɗauko hijab ɗinta peach colour ta saka, ba ƙaramin kyau tayi ba

Tana fitowa parlour sai ga shi ya shigo, kallonta yake daga sama har ƙasa, jira take ta ji ya zage ta ko ya ce tayi wani abu ba dai-dai ba, sai kawai ta ga ya shige ɗakinshi, bai fi mintuna goma sha biyar ba ya fito, kallo ɗaya ta mishi ta fahimci wanka yayi dan ya sauya kayan jikinshi da madubi, sai dai bai saka facemask ba, ba tare da ya ce mata komai ba ya fita, da sauri ta ɗauki wayarta da makullin parlourn da ke kan center table ta bi bayanshi

Sai da ta rufe ƙofa sannan ta wuce, zuwa lokacin har ya kai waje, dama bai shigo da motar ba, mai gadi ya ce "Hajiya a sauka lafiya, sai kun dawo"

"Yawwa, sannu" ta amsa mishi, sannan ta fita

Yana tsaye jikin mota yana waya, tsayawa tayi sai da ya gama sannan ya buɗe suka shiga, sai da ya hau titi, sannan ya ce "ɗazu me kika gaya wa Anty Sadiya?"

Gabanta ta ji ya faɗi, ta dake ta ce "ba komai"

"Ba komai? In kira ta?"

"A'a"

"To meyasa za ki mun ƙarya, ina so duk abunda za ki gaya mun ya kasance gaskiya ko da kuwa yanka ki zan yi"

"Yanka ni?" Ta faɗa ba tare da ta san tambayar ta fito fili ba

Kallonta kawai yayi, ya mayar da hankalinshi kan titi, ita ma ba ta sake cewa komai ba, ita burinta kawai ta ganta a gidansu. Sai dai abunda ya ɗaure kanta shi ne, da ta ga sam ba hanyar gidansu ya bi ba, tana so tayi magana amma ta kasa dan ta gaji da faɗanshi, haka ta sa wa sarautar Allah ido

Gaban wani gida ta ga yayi horn aka buɗe, gidan babba ne ba laifi, yayi kyau, gashi an zagaye shi da wasu glubs da suka haske wurin, wurin da aka tanada dan aje motoci ya ajiye na shi

sannan ya fito, ita ma buɗe ƙofa tayi ta fita, sannan ya shiga gaba suka wuce

Danna doorbell yayi, sai ga Nasreen ta buɗe, murmushi tayi, ta ce "ikon Allah, Oga Tiger ku ne cikin daren nan ba sanarwa?"

"Mu koma kenan"

"Ni!!! Ai ko zan kori kowa banda Oga Tiger, bisimillah" ta faɗa tana matsawa gefe

Yana wuce wa, ta rungume Sunaiha, suna farincikin ganin juna, duk da cewar Sunaiha a can ƙasar zuciyarta tana jin haushin ganinta a gidan ba wai gidansu ba, amma tabbas tayi murnar ganin Nasreen

Ƙarasawa suka yi ciki, san Sunaiha ba tayi tsammanin Safwan na ciki ba, sai ta gansu a parlourn shi da Tiger suna magana, sunkuyar da kai tayi dan sai yanzu take jin kunyar abubuwan da suka taɓa faruwa tsakaninta da Safwan

Sai da suka zauna sannan tayi ƙoƙarin gaida shi, ba tare da ya nuna mata wani abu ba ya amsa mata, sannan ya ce "ya kike?"

"Lafiya ƙalau" ta amsa still kanta a ƙasa

Nasreen ta kawo ruwa da abinci ta ajiye musu, sannan ta ce "ko kan dinning zan kai muku?"

Tiger ya ce "wa kika kawo wa abinci?"

Nasreen ta ce "ban gane wa na kawo wa ba, Tiger kana da matsala fa, idan ba ka so surutu ba ka share mutane, idan kuma ka so magana har na banza kake yi"

Dariya suka yi banda Sunaiha da tayi murmushi, shi kanshi Tiger dariyar mai kama da murmushi ne

Safwan ya ce "Baby love manta da shi... cushion ɗin nan ta kawo wa" ya ƙarasa yana hararar Tiger

Nasreen ta ce "Sunaiha bari in zuba miki ke kam ki ci"

Kafin ma tayi magana, Tiger ya ce "akan me za ki ɗura mata abinci?"

"Ai dai ba kai na ce ba"

"To ba ki san yanzu idan ta ci ta ƙoshi ba ni kika yi wa, dan ba zan iya cin abinci ba sai tare da ita"

Wani kallon mamaki Safwan da Sunaiha suka yi mishi, Nasreen kuwa dariya tayi, ta ce "iyeee, soyayya manya"

Kallon Sunaiha yayi dake kallonshi, ya ce "ya dai? Ko kina so ki ci ne?" Ya tambaye ta cike da kulawa

A hankali ta sauke idanunta daga kanshi ta girgiza kai, Nasreen ta ce "ko da tana so ai, ka hana ta tunda ka zama bakinta"

Tiger ya ce "wai ke dole sai kin shiga tsakanin mata da miji ne?"

"Ni ɗin banza, Allah ya ba ku haƙuri, Sunaiha tashi mu shiga ciki dan mijin nan na ki ba bari zai yi hankali na ya kwanta ba tunda yau yana son surutun"

Miƙe wa Sunaiha tayi ta bi ta tana ta mamakin Tiger. Safwan kuwa tun ɗazu kallon Sadeeq yake ya kasa magana, gaba ɗaya ya ɗaure mishi kai

Sadeeq ya ce "meye wai kake ta kallo na?"

"Mamakinka nake yi"

"Da aka yi me?"

"Yaushe ka fara son yarinyar nan har haka?"

"Ranar da ka fara sake mata fuska"

"To ai yau ne"

"Really!?" Sadeeq ya mishi tambayar cikin salon rainin hankali

"Eh mana, shi ma kawai tunanin nayi she's now your wife, to meye kuma amfanin faɗan? Allah ya shirya ta kawai, although na ga ta ɗan natsu, ko iya yau ne? ban sani ba"

"Hmm, ta natsu ka ce?"

"Sosai ma, sai na ganta kamar ba ainihin Sunaihar da na sani a baya ba"

"Yayi kyau...wai ya labarin case matar nan?" Ya tambaye shi dan kawai su canza topic ɗin, ba so yake ana yawan magana da shi a kanta ba, Safwan ba tare da ya game manufarsa ba, ya biye shi suka ci gaba da firar da ya ɗauko

A ɗaki kuwa Sunaiha ji take kamar ta fito, Fira suke yi amma san ba dadinshi take ji ba, a tunaninta bayan sallar isha'i zai ce ta fito su tafi gidan na su, amma har suka je masallaci suka dawo, shiru kake ji har kusan ƙarfe tara da rabi, sannan Safwan ya kira Nasreen akan su fito haka nan, sallama suka yi musu sannan suka wuce gida

Tun a hanya take ji kamar tayi ta kapta mishi mari saboda haushin da ya ba ta, amma ba zai yiwu ba, suna dawo wa gida ta ajiye mishi abincin shi kan table sannan ta shiga ɗakinta ta mayar da ƙofa ta rufe, yau ba za ta zauna ba sai dai duk abunda zai faru ya faru, yana kallonta shi kuma, tsab ya gane haushinsa take ji, amma yayi banza da ita kamar bai san tana yi ba

Sai da ta sauya kayanta zuwa na bacci sannan ta kwanta ta sake kiran layin Najma amma a kashe, na Sharif ma haka, na Hajiya ma, ta san har yanzu ba su mayar da layinsu na Nigeria kan wayoyinsu ba kenan, haka ya sa yanke shawarar kiran Mummy kawai, ita kuma ba ta ɗaga ba, bata ma yi wahalar kiran Daddy ba dan ta san ba samunshi za tayi ba yanzu, haka ta haƙura tayi baccin baƙin cikin rashin ganin su Sharif........

DAN ALLAH KUYI WA TIGER HAƘURI, YANA TA SHAN ZAGI😂🤣 NI FA BA RUWA NA, ABUNDA YAYI NE NAKE FAƊA, NIMA KU DAINA ƊORA MUN LAIFI, AMMA DAI ZAN JA MISHI KUNNE DAN YA SAN SUNAIHA TA TARA SUPPORTERS YANZU😻😂

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Greatness is more than potential. It is the execution of that potential. Beyond the raw talent, one needs the appropriate training, discipline, inspiration & drive._

*PAGE 45-46*

Washe gari da safe, Sunaiha tana kammala aikinta ta koma ɗakinta ta kwanta, ba ta fito ba sai ƙarfe goma, tsayawa tayi ganin Tiger kwance a doguwar kujera yana chatting, sam ba tayi zaton yana gidan ba, dama ba so take yi su haɗu yau ɗin ba. Ba tare da ta sake kallonshi ba ta nufi hanyar kitchen dan yunwa take ji, shi kuwa yi yayi kamar bai ganta ba.

Dawowa tayi parlourn ta zauna ta fara shan tea, sannan ta ɗauki wayarta ta kira Mummy, bugu ɗaya ta ɗauka, gaisawa suka yi kafin ta ce

"Mummy nayi fushi"

Murmushi Mummy tayi dan ta fahimci in da ta dosa, ta ce "kiyi haƙuri mana Babyn Daddynta, jiya kin san su Hajiyar London na nan shiyasa ban da lokacin waya tana ɗaki"

"Amma ai kin ga missed calls ɗina kuma ba ki kira ni ba" ta faɗa cikin sigar shagwaɓa

"Kusan ƙarfe sha ɗaya fa na dawo daga part ɗinsu, lokacin kuwa na san kinyi bacci"

"To shikenan, yanzu ina suke?"

"Hajiyar London yanzu ta bar nan ta je ta kwanta, amma ga Sharif"

Kafin Sharif ya tashi daga wurin da yake ya karɓi wayar, Najma ta riga shi saboda tana bayan Mummy
~~~~~~~~~~~~~~~~

"Haba Amarya, nayi tsammanin ke ce a gaba zuwa airport ɗauko mu, sai na ga Prince ya fi mu yanzu" ta faɗa tana ƴar dariya

"Don't say so Anty Najma, ba wanda ya fi ku ai"

"Hmm, kamar gaske.....but wait, me naji kin ce?" Ta ƙarasa maganar tana zama kusa da Sharif da ke ta zabga mata harara

Sunaiha ta ce "na ce ba wanda ya fi ku"

"A'a ba haka ba, me na ji kin kira ni?"

"Anty Najma?"

Wani murmushin mamaki Najma tayi, ta ce "yaushe kika fara ba ni wannan girman?"

"Haba Sis, sai an ji mu da ke ne?"

Dariya tayi ta ce "to shikenan dai, yanzu yaushe za ki zo? Yaushe Prince ɗin zai bari mu ganki?"

Satar kallon Tiger tayi, kafin ta ce "za ki ganni dai"

"Ke ni fa ba ma ke nake son gani ba, Prince ɗin nan nake so in gani, ya yake? Ya kamanninsa suke? Da me ya fi sauran samarin da kika yi ta wulaƙantawa saboda shi, i just wanna see him" ta ƙarasa cikin zumuɗi

"Hmm, very soon za ki gane wa idonki"

Kafin Najma tayi wata magana, Sharif ya ƙwace wayar, ya ce "ki kirata da na ki....Hello Partner" ya kira ta da sunan suke kiran junansu kasancewar sa'anni ne

Murmushi tayi ta ce "Hi Partner, ya kake?"

"So good but i miss you"

"I miss you too Partner, amma zan zo ko saboda kai"

Daɗi ya ji sosai, ya ce "idan ma ba ki zo ba, ni zan zo ne kin sani, saboda na kawo miki labarai sosai, musamman na wannan ƙawar ta ki, Aliana"

"Oooo... Allah sarki Aliana, tayi auren? Saboda mun yi chat da ita last month ta ce ita ma auren ya kusa, amma yanzu ko na kira wayanta ba ya zuwa, kuma ko wane account ɗinta it's off" ta

ƙarasa maganar cikin alamar damuwa

"Ban san meyasa ba nima, kusan two weeks back, da na ganta lokacin da na shiga school, sai dai ban gaya mata za mu zo Nigeria ba"

Mummy ta ce "oh ni, ku ba ni waya na haka nan, idan ta zo ku ƙarasa"

Najma ta ce "ka ba ta wayanta, kai ma ka kira da na ka"

Sharif ya ce "kai!!!.... Partner ba za su bari in miki magana cikin kwanciyar hankali ba, sai kin zo kawai"

Ƴar dariya tayi ta ce "shikenan, idan Hajiyar London ta tashi ka miƙa mun saƙon gaisuwa kafin zuwa na"

"In sha Allah, ki gaida Prince"

"Zai ji" daga haka suka kashe wayar

Najma ta ce "Mummy yau za ta zo?"

"Najma ta ya zan sani? Meyesa ba ki tambaye ta ba?"

"Ta ce mun dai zan ganta, to yau take nufi ko gobe ban sani ba"

"To ki jira ki gani...ni dai bari in duba yaran can, ya aikin ke tafiya"

Gyara zama Najma tayi kan kujera tana faɗin "ke ai Mummy ba za ki bari ki huta ba, kullum sai ki wani shiga kitchen wai kin je duba aikin da suke yi, kuma ni na ga dai-dai gwargwado dai masu aikin nan su na ƙoƙari"

"Haka ne, amma dai na fi so in gane wa idona abunda suke yi" ba ta tsaya jin me za ta ce ba, ta nufi kitchen ɗin

Sunaiha kuwa bayan sun gama wayar ta ci gaba da breakfast ɗinta, Sadeeq na jinta amma ko ɗaga ido bai yi ya kalle ta ba, sai da ta gama sannan ta kai kwanonin kitchen ta shiga ɗaki tayi wanka, ta shirya cikin abaya army green, sannan ta sake dawowa parlourn

Yanda ta bar shi yana nan bai tashi ba, ta ce "Ya Sadeeq"

"Meye?"

"Ina so zan je ganin su Hajiyar London, ka ga jiya ban tafi ba, yau ka bari in tafi"

Kamar ba zai yi magana ba, sai kuma ya ce "yau ma ba za ki tafi ba"

Da mamaki tale kallonshi ta ce "kamar ya!?"

"Kamar yanda kika ji"

"Ya Sadeeq dan Allah mana" ta faɗa kamar za tayi kuka, dan ta fahimci idan ta ƙyale shi ma a banza, dan ba gane zai yi ranta ya ɓaci ba har ya tausaya mata ya ce ta tafi

Kafin yayi magana aka danna doorbell, kallon ƙofar yayi yana nazarin ko waye, ba ɓata lokaci ita kam ta miƙe ta je ta buɗe, Sarah ce a tsaye ta sha make up ɗin ta mai kyau

Murmushi tayi ta ce "amarya"

Ita m Sunaiha murmushin ta ƙirƙira saboda ba ta san ta ba, sau ɗaya ta taɓa ganinta, shi ma a wurin walimarsu ne da ta zo suka yi hoto, ta ce "sannu da zuwa...shigo mana"

"Yawwa, Nagode" ta faɗa tana ƙoƙarin kutsa kai cikin parlourn

Kujera ta samu ta zauna kafin ta fara gaida Sadeeq da ya tashi ta zauna, dai-dai lokacin da Sunaiha ta ajiye mata ruwa

"Sarah ya gida?" Cewar Sadeeq

"Lafiya ƙalau, nayi mamakin samunka da nayi a gida ma yanzu, amarya ta riƙe ka kenan"

"Kamar yanda nayi mamakin ganinki yanzu da wannan safiyar" ya amsa mata

"Oh sorry, gidansu wata ƙawata na zo, gidansu na nan farkon layi ina so zan karɓi wasu litattafai ne a wurinta kafin in wuce makaranta, shi ne ma ce bari in biyo ta nan in ga amarya saboda tun ranar da aka kawo ta ban dawo ba"

Jinjina kai kawai yayi sannan ya miƙe ya nufi cikin ɗaki, sai a lokacin ta mayar da hankalinta kan Sunaiha da tayi shiru tana bin su da ido, kusan mintuna goma su na ƴar fira kaɗan-kaɗan

Tiger ne ya fito cikin shirin manyan kaya, Shadda ce mai tsadar gaske Navy blue, ɗinkin rigar iya gwiwa haka ma hannun rigar ba mai tsayi ba ne, hular kanshi ma Navy blue ce da ratsin sky blue da fari kaɗan, agogon hanunshi blue black da takalmi Navy blue, ga baƙin glass ɗinshi ƙirar Versace, yayi matuƙar kyau sosai, dan kayan sun ƙara haska mishi farar fatarshi, kyaunshi ya ƙara bayyana a fili

Kallo ɗaya Sunaiha ta mishi ta sauke idonta saboda wani abu da ta ji a zuciyarta, Sarah kuwa kallonshi take yi ta kasa ɗauke idanunta, yana ganin irin kallon da take mishi sai dai ita ba ta ganin ƙwayar idonshi saboda baƙin madubin, hakan ya sa ya ji tamkar ya koma ya saka facemask dan ya tsani irin wannan kallon, amma hakan ba zai yiwu ba dan facemask ba zai yiwu a wurin da zai tafi ba

Ƙarasa wa yayi cikin parlourn ya ɗauki makullin motarshi, sannan ya ce "i'm going out" ya faɗa yana kallon Sunaiha

"Allah ya kiyaye" ta amsa tana ƙoƙarin sake kallonshi

Sarah ma miƙe wa tayi ta ce "bari in biyo ka, ka rage mun hanya dan Allah"

Ba abunda ya ce, ya fita, Sunaiha kuwa wani wawan kallo take yi wa Sarah har tayi mata sallama ta fita ba ta iya amsa mata ba, gaba ɗaya zuciyarta ta kasa natsuwa, sai harbawa take yi, a hankali ta zauna tana dafe kai, ta ce "Allah ya tsare mun kai daga sharrin ko wace mace Prince, irin wannan kyau yau ban san adadin matan da za su kalle ka ba"

Hawaye ya cika idonta lokacin da ta tuna da budurwarshi, wataƙila ma gidansu zai tafi dan wannan kayan da ya saka yau akwai alamar tambaya, tana ƙoƙarin mayar da hawayen ta ce "Allah ya kashe wannan shegiyar ko ma wacece, idan ta mutu ai zan ga ƙarshen soyayya...aikin banza kawai" ta sauke numfashi ta miƙe ta kwashe ruwan da ta ajiye wa Sarah dan ba ta sha ba

Sarah kuwa lokacin da ta fito yana cikin mota yana jiran ta, ta buɗe ta shiga suka wuce, tun da suka hau hanya ba wanda ya ce komai har ya ajiye ta ƙofar makaranta

Ta ce "na gode sosai Sadeeq, kayi haƙuri na canza maka hanya"

"Ba damuwa, kan hanya ta nake shiyasa har na ɗauko ki"

Godiya ta sake yi sannan ta fita, ya ja motar yayi gaba

Ƙawarta da ke bakin gate ɗin makarantar tare da wani, ta kalli Sarah bayan isowarta, ta ce "Sarah yau wa ya kawo ki?"

Murmushi tayi ta ce "Hmm, Jamima kenan...kin san Sadeeq?"

"Wane Sadeeq kuma?"

"Dr Sadeeq Usman Saraki"

"Ba dai wannan da kike so ba?"

"Shi fa"

"To yaushe kuma ya fara sonki? Ba kin ce ya gaya miki yana da wata ba?"

"Haka ne, kin san ance opportunity comes at once, yanzu lokaci ne da zan dawo da hankalinshi kai na, shiyasa kika ganmu tare"

"Ni fa kin ɗaure mun kai, gida ya je ɗauko ki?"

"A'a, gidansu Aisha na je, layinsu ɗaya shi ne na bi ta gidanshi, sai na ga zai fita, ai kuwa da gangan na bar mota na a gidan su Aisha na ce ya kawo"

"Lallai ma matar nan, to ya kika yi da matarshi?"

"Ya zan yi da ita kuwa? Ai ba sonta yake yi ba shiyasa na ga lokaci na ne yanzu"

Ƴar dariya Jamima tayi, ta ce "to Allah ya taimaka, zo mu shiga ciki"

"Ameen dai" daga haka suka ƙarasa cikin makarantar

Sadeeq kuwa bai tsaya ko ina ba sai gidan Senator, a parking lot ya ajiye motarsa, ya cire madubin fuskarsa ya ajiye kafin ya ƙarasa ciki

Kasancewar yayi waya da Daddy kafin zuwansa kuma ya tabbatar mishi da zai same shi a gida, doorbell kawai ya danna, ɗaya daga cikin mai aikinsu ce ta zo ta buɗe, cikin girmamawa ta gaishe shi sannan ya shiga ciki

Dadday na zaune a parlour, ya ƙarasa kusa da shi ya zauna a ƙasa ya gaida shi

"A'a, haba takwara na, miƙe ka zauna kan cushion"

"A'a nan ma yayi, ya aiki?"

"Alhamdulillah, ina shirin fita ne ma ka kira ni ai...ga Mummynku nan zuwa ta shiga kiran baƙin"

Rufe bakinshi ke da wuya, sai ga Hajiyar London da Mummy sun shigo, sai Najma dake bayansu, cikin girmamawa ya gaida su, sannan suka gaisa da Najma da tun shigowarta take yaba irin wannan halittar Ubangiji

'haƙika Allah gwanin iya halitta ne, mutumin nan akwai kyau, dole Sunaiha ta nace akan lallai sai shi za ta aura' abunda take faɗa a ranta kenan, a zahiri kuma ta ce "Malam Prince, ka san

sunan Daddy ne da kai, sunanka akwai nauyi dole zan ari sunan Prince, ina Sunaiha? I thought tare za ku zo"

Murmushi yayi ya ce "tana gida, baƙi ta yi, shi ne na zo a madadin ni da ita ɗin kafin ita ta zo, saboda kar ku ci mu tara"

Najma ta ce "har da kai kana tsoron biyan tara?" Ta ƙarasa tana murmushi

"Me zai hana?"

Hajiyar London ta ce "Sadeeq ƙyale ta, idan ka biye ta sai ka sha mamakin surutun ta, yanzu yaushe za ka kawo ta?"

"Gobe da safe in Allah ya yarda" ya amsa mata cike da girmamawa

"To Allah ya kai mu"

"Ameen"

Miƙewa yayi, Mummy ta ce "ba dai tafiya za kayi ba ko ruwa ba'a kawo maka ba"

Ɗan murmushi yayi ya ce "eh Mummy, akwai wurin da nake so zan tafi"

Daddy ya ce "ai ke ma kin san Sadeeq ba son zama yake yi ba idan ya zo, sai ka ce ana korarshi"

Kafin Sadeeq yayi magana sai ga Sharif ya sauko daga kan stairs, ƙarasa wa yayi kusa da Sadeeq suka yi musabaha, ya ce "ina wuni"

"Lafiya ƙalau ya gajiyar tafiya"

"Alhamdulillah, kenan da ban sauko ba tafiya za kayi ba mu gaisa ba ko!?"

Ɗan murmushi yayi, ya ja Sharif suka fita bayan ya sake yi wa su Mummy sallama

Anty Sadiya ce ke waya da Anty Saudat, ta ce "wai Saudat sai yaushe za ki shirya mu tafi gidan Tiger?"

Anty Saudat ta ce "wane Tiger ɗin?"

"Ke fa kin iya tambayar rainin hankali, wane Tiger kika sani?"

"Anty Sadiya na gaya miki ba abunda zai kai ni gidan Sadeeq, idan ina son ganinshi na san yanda zan yi"

"Saudat kina da daurin kai wallahi, da ke da Sultana halinku ɗaya, na gaya miki wannan ƙiyayyar ki ajiye ta gefe, wallahi yarinyar nan ta sauya ba kamar yanda kika sani ba"

"Ai ke dama kina sonta, ba yanda za'a yi ki ga laifinta, ni fa ba ta mun ba"

"Saudat... Wai ma tsaya, na isa da ke?"

"Eh kin isa, amma dai...."

Katse ta tayi da "ban son wani bayani kuma, anjima bayan la'asar zan zo in ɗauke ki, mu biya gidan Sameera ita ma, nayi mata magana, sai mu tafi"

"Anty Sadiya...."

"Saudat, na gama magana, idan kuma kika ƙi, zan kira Alhaji in gaya mishi"

Shiru ta ɗan yi kafin ta ce "shikenan, Allah ya kai mu"

"Ameen" daga haka ta kashe wayar, sai da ta kira Sunaiha ta gaya mata kafin ta je ta ci gaba da aikinta.......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Good Relations are just like WATER, No Colour, No Shape, No Smell, NO Taste. But Still Very Very IMPORTANT For Life._

*PAGE 47-48*

Kamar yanda Anty Sadiya ta tsara fitarsu, haka aka yi, ƙarfe huɗu da kusan rabi ta fito daga gidanta zuwa gidan Anty Sameera, sannan suka biya gidan Anty Saudat, daga nan suka wuce gidan Sadeeq

Sunaiha ta gama shirya musu komai jiran zuwansu kawai take yi, fitowar ta daga ɗaki kenan ta ji an danna doorbell, kai tsaye ta je ta buɗe ƙofar, cike da murnar ganinsu take fara'a ta musu iso zuwa ciki

Zama suka yi ta fara gaida su, suka amsa mata da fara'a, banda Anty Saudat da ta amsa ba yabo ba fallasa, har snacks da drinks ɗin da ta ajiye musu Anty Saudat ko kallonsu ba ta yi ba

Sun fi mintuna talatin a gidan, su na ta fira su uku, Anty Saudat chatting ɗinta kawai take yi, door bell aka danna, Sunaiha ta je ta buɗe. Ba ta yu tsammanin Sadeeq ba ne saboda yana da makullin da yake buɗe wa, sai ganinshi kawai tayi a tsaye, gaida shi tayi ya amsa kafin ya ƙarasa ciki

Zauna wa yayi suka gaisa, sannan ya ce "zuwa ba sanarwa?"

Murmushi Anty Sameera tayi ta ce "ka san halin Anty babba ai, ɗazu kawai ta kira ni wai in nemi izini za mu fita"

Anty Sadiya ta ce "nayi laifi kenan"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Tiger ya ce "wa ya isa ya ce kin yi laifi?

Anty Saudat ta ce "Sadeeq ni nemanka ma nake yi"

Anty Sadiya ta ce "mu tashi kenan?"

Anty Sameera ta ce "su tafi su ba mu wuri dai"

"Ni ban ce kowa ya tashi ba saboda ba sirri ba ne"cewar Anty Saudat

Tiger ya kalle ta ya ce "ina jinki to"

"Sadeeq ina budurwarka wacce kake so? Sai yaushe za ka bayyana mana ita?"

Tambayar da tayi ta ba kowa mamaki musamman Sunaiha, Sadeeq ya ce "tana nan, amma meyasa kike tambaya?"

"Saboda ina so in san ta haka nan, na tabbata ita ta san darajar ɗan adam, ka bayyana mana ita ayi auren nan kowa ya huta, dan ka ga ni zan huta zuwa gidan da ba'a san daraja ta ba, gidanka dai ake so in tafi ko!? To ka ga idan ka auro ta na samu gidan zuwa, ba wanda zai ce ban tafi gidan Sadeeq ba, ni kai na ina son zuwa, amma ban ga abunda zai kawo ni wannan gidan ba, na fi so in tafi gidan Safwan, ko ba komai za'a mutunta ni"

Tun da ta fara maganar suke kallonta da mamaki, sun dan halin Saudat, amma ba su yi tsammanin za ta iya wannan maganar a gaban Sunaiha ba. Sunaiha kuwa hawaye ne tap a idonta, rai a ɓace Anty Sadiya ta ce "Saudat wai lafiya kike kuwa? Wannan wane irin magana ne haka? Kina magana akan wacce ta san darajar ɗan adam, to ki gaya mun gidan nan wa ya wulaƙanta ki?"

"Ba'a wulaƙanta ni ɗin ba, amma matuƙar ban kama kai na ba, na san ana kan hanya" ta ƙarasa tana yi wa Sunaiha wani kallo

Hawayen idonta na shirin zubo wa ta juya da sauri ta nufi ɗakinta, bin ta suka yi da ido har ta shige, sannan Anty Sadiya ta ce "Saudat kin ba ni mamaki, ban yi zaton za ki iya gaya wa mutum maganar da za ta ƙona mishi rai ba har haka, yanzu me ye laifin yarinyar nan? Tun zuwanki me tayi miki wanda ba dai-dai ba ban da gimama ki ɗin da take yi?"

"Ai dama ke ba za ki ga laifinta ba tunda har kina sonta, halinku ɗaya ke da Umma, ba kwa taɓa gane masoyin gaskiya, ke yanzu har kin ga abun so da tausayi a jikin yarinyar da ba ta san darajar ɗan adam ba?"

Anty Sameera ta ce "Saudat dan Allah kiyi shiru mana, meye haka? Kin san ni kai na bana supporting ɗin duk wani mutum mai wulaƙanci, wanda bai san darajar mutum ba, ba ma ni ba,

kap ilahirin mu kusan haka ne, amma tunda na fara ganinta na ga halayenta ba kamar yanda su Salma suka faɗa ba ne, sai na tattara zancen ƙiyayya na zubar, to ke ma meyasa ba za ki sauya ba tunda ta sauya?"

"Oh, ke ma kenan kin bi bayan Anty Sadiya?"

"Ba bayanta na bi ba, bayan gaskiya na bi"

Anty Sadiya ta ce "Kyale ta Sameera, nayi dana sanin ɗauko ki ɗin da nayi na kawo ki har gidan yarinyar nan kika ci mata mutunci haka, ke da kika san darajar ɗan adam ɗin me kenan kika yi?"

"Abunda ya kamata shi nayi, kuma wallahi ko gobe kika dawo da ni gidan nan sai nayi abunda ya fi haka" ta ƙarasa rai a ɓace

Sadeeq dake gefe ya naɗe hannu yana kallonsu, sai yanzu ya samu bakin magana, "Anty Saudat kiyi shiru haka nan mana, Anty Sadiya ce fa kike gaya wa magana son ranki"

A tsawace ta ce "dalla rufe mun baki, wa nake wa fadan idan ba kai ba? Ai tana sane ta bari aka ɗaura maka aure da wacce ba ka so, ku ka ƙi gaya mun, lokacin da na sani kuma nace zan yi wa Abba magana a dakatar da auren, ta ce wai a'a, a ƙyale ka kayi wa mahaifinka biyayya.... to shikenan, ai kayi biyayyar, amma wallahi daga yau ba za ka sake gani na a gidan nan ba, in har kana son ganina, ka same ni a gidana ko kuma mi haɗu a gida, in har ka ganni a gidanka, to tabbas ka auri wacce zan iya zama da ita muyi fira cikin mutunci" tana kai wa ƙarshen maganar, ta figi jakarta ta fita tana huci

Sai da Sadeeq ya kalli su Anty Sadiya, kafin ya juya ya bi bayanta da sauri, har ta kusan kai wa gate, ya riƙe hannunta

Cikin tattausar murya ya ce "haba my beloved sister, the best sister ever, my pride and happiness, meyasa za ki ɓata ranki akan abunda bai kai ya kawo ba? Kin fi kowa sanin na tsani abunda zai ɓata ranki, burinki dai shi ne in auri wacce nake so, ko!?"

Kallonshi tayi, sai kuma ta ɗaga kai, ya ce "to ki kwantar da hankalinki, very soon za ki ganta, kuma burinki zai cika"

"But when? Sadeeq i only need your happiness (amma yaushe? Sadeeq farincikin ka kawai nake buƙata)"

"But i will be happy only if you're happy (amma zan yi farinciki ne kawai idan kina farinciki), My Sis, wannan ɓacin ran, ki ajiye shi pls" ta ƙarasa yana kwaɓe fuska yana kallonta

A hankali ta sauke numfashi ta ce "shikenan, na daina...zan wuce"

"Zuwa ina kuma? Ki jira su ku wuce tare dai"

"A'a, zan je in shiga napep"

Ɗan buɗe ido yayi, ya ce "napep kuma? So kike ki kashe mana yaro? Kin san kuwa da mun yi shari'a da ke"

Ƴar dariya tayi, ta ce "ni da nake da Safwan a hannu"

"Ok to shikenan, ba zan bari ki tafi ba, dan girman Allah ki bari ku tafi tare"

"To na ji, amma ba zan koma ciki ba, zan jira su wurin mota, su fito mu tafi"

"Ba komai, zan kira miki su yanzu" daga haka ya koma ciki

Anty Sadiya na ta faman knocking ƙofar ɗakin Sunaiha amma ta ƙi buɗewa, ganin shigowar Sadeeq ya sa ta dawo, ta ce "Sadeeq ta ƙi buɗe wa, ina so zan ba ta haƙuri ne"

Anty Sameera ta ce "kayi mata magana, wataƙila za ta ji"

Kallon ƙofar yayi kafin ya ce "ita dai ta rufe ƙofar ai ko, to ku ƙyale ta za ta buɗe"

"Kamar ya a ƙyale ta? Kana jin irin maganar da Saudat ta gaya mata, shi ne za ka ce a ƙyale ta?" Cewar Anty Sadiya

"Na ji....Anty Sadiya ban san meyasa ma kika biye Anty Saudat ba, ke kin san matsalarta, kin san ciwon da take fama da shi, to meye abunda ya sa kika biye ta?"

Numfashi Anty Sadiya ta sauke, ta ce "haushi ta bani ne wallahi shiyasa nayi magana, amma ai ka ga daga baya kuma ƙyale ta nayi, sai a lokacin abun ya zo kaina"

Anty Sameera ta ce "yanzu dai tana ina?"

"Tana waje tana jiranku"

Anty Sameera ta kalli Anty Sadiya ta ce "ya kamata mu wuce, saboda za ta iya wucewa"

"Haka ne, amma ina so inyi magana da Sunaiha"

Tiger ya ce "ku wuce, zan mata magana"

Anty Sameera ta ce "kina da numbern ta ai, mu tafi ma sai ki kirata daga baya"

"Hmm, shikenan, mu tafi"

Sai lokacin da za su wuce sannan Tiger ya ce "wai ina yarana? Ke dai Anty Sadiya har yanzu kin ƙi ɗauko su gidan Kakarsu, to ke Anty Sameera ina Ilham?"

Murmushi tayi ta ce "ita ma tana gidansu Babanta"

"Hmm, Allah ya shirya ku to"

"Ameen" suka amsa mishi kafin suka fita

Zama yayi kan cushion ya dafa kai kusan mintuna ashirin, kafin ya miƙe ya shiga ɗakinshi, wanka yayi ya canza kaya, sannan yayi alwala saboda an kusa yin sallar magrib. Har ya kai ƙofa, sai kuma ya dawo ya nufi ƙofar ɗakin Sunaiha, knocking yayi kusan sau biyu bata buɗe ba, sannan ya ce "za ki buɗe ne ko sai na ɓalla ƙofar?"

Shiru har yanzu bata ce komai ba, a tsawace ya ce "ba magana nake yi ba?"

A hankali ta buɗe ƙofar, ba tare da ta ce komai ba ta juya ta koma ciki, tsayawa yayi yana nazarin shiga, sai kuma ya ɗan tura ƙofar ya tsaya yana kallonta a zaune kan gado, ba sai an gaya maka ba, kallo ɗaya za ka mata ka fahimci tayi kuka sosai kasancewar idanunta sun yi ja sosai, kallo ɗaya yayi mata ya ɗauke idanunshi daga kanta, ya ce "ki shirya gobe da safe za ki je gaida su Sharif" bai jira jin amsarta ba ya wuce masallaci

Wani sabon kuka ne ya sake ƙwace mata, a tunaninta zai ba ta haƙuri ne akan irin cin mutuncin da Yayarshi ta mata, amma sai ta ga ko a jikinsa, sam bai ma nuna ya san wani abu ya faru ba. Duk da cewar abunda ya faɗa ta daɗe tana so ta ji hakan, amma sam ta kasa yin farinciki, sai tunani take wannan wane irin miji ne Allah ya haɗa ta da shi? Wane abu tayi da tayi deserving irin wannan jarabawar? Ko ma dai me ta aikata, ai ta gyara halayenta, amma meyasa har yanzu Sadeeq ya kasa ganewa

Ta daɗe zaune a wurin, har aka kammala sallah, sannan ta iya miƙe wa ta je tayi alwala tayi sallah, t jira aka kira isha'i, shi ma ta miƙe tayi sannan ta je tayi wanka ta fito ta kwanta. Gaba ɗaya ba ta jin daɗin jikinta, ta rasa me ke mata daɗi a duniya, sai juyi take tayi, tana jin lokacin da Sadeeq ya shigo, har ya gama abunda yake yi a cikin parlourn ya shiga ɗakinshi tana ji ta ƙyale shi

Kusan ƙarfe goma har ta fara bacci ta ji wayarta tayi ƙara, sai a lokacin ta tashi ta ɗauko ta daga kan mirror da ta ajiye tun ɗazu, ganin kiran na Najeeb ne ya sa tayi tsaki ta ajiye ta sake kwantawa, wani kiran ne ya sake shigowa, sai da ta zauna kafin ta ɗaga

"Sunaiha" abunda ya fara faɗa kenan bayan ta ɗaga

Cikin ɓacin rai ta ce "wai Najeeb meye matsalarka ne? Meyasa ka cika naci ne? Najeeb ka ƙyale ni"

"I'm sorry Cutie, amma na kasa yin bacci ne, wallahi tunanin nake tayi, na san kina jin haushi na, amma ya kamata ki fahimci irin son da nake miki, i want you to be with me for ever, i promise to make you happy for the rest of your life, i so much love you more than you think"

Kalamansa sun shige ta, har ta ji tausayinsa, amma ta ce "and then!? Me kake so in maka? Ni matar aure ce Najeeb, I'm already married, i can't do anything, so just let me go, leave me alone for God sake Najeeb, pls" ta ƙarasa wasu hawaye na biyo fuskarta, ba ta jira amsarsa ba ta kashe wayar

Ba'a fi mintuna uku ba, sai ga saƙonshi ya shigo, yana ba ta haƙuri tare da ƙara jaddada mata irin son da yake mata, sannan yayi mata fatan alkhairi, haka kawai ta tsinci kanta da shiga wani yanayi da yayi mata wuyar fassara, ta san dai tana jin wani iri a zuciyarta, ta daɗe zaune tana share hawaye jifa-jifa, daga bisani ma tashi tayi, tayi alwala ta zo tayi sallah raka'a biyu ta roƙi Ubangiji sassauci kamar yanda Anty Sadiya ta bata shawarar yin nafila a duk lokacin da take jin ba daɗi

Washe gari da safe, ƙarfe tara har ta gama komai har breakfast tayi, tea kawai ta sha, ta shirya tsaf cikin ɗinkin riga da skirt na material dark purple, da hijab ɗinta light purple, ba make up a fuskarta, amma tayi kyau sosai, jiran fitowar Sadeeq kawai take yi. Karfe tara da ashirin sai ga shi, shi ma ya shirya cikin ƙananan kaya, wando baƙi da riga maroon, sai glass baƙi da facemask baƙi

Kallonshi tayi ta sauke ido, ta rasa dalilin da yasa duk irin shigar da Sadeeq zai yi dai ta ga yayi matuƙar kyau, har ta facemask ɗinshi yana burge ta dan ta tabbata wannan facemasks ɗin da yake saka wa ba na Nigeria bane, ko wane facemask da irin design ɗinshi, a hankali ta gaida shi, ya amsa da "lafiya" sannan suka fita

A ƙofar gidansu ya ajiye ta, ko gate bai shiga ba, ya ce "ki gaishe su"

Kamar ba za ta tanka mishi ba, sai kuma ta ce "kai kuma fa? Ba za ka iya shiga ka gaida su ba kenan"

"Eh" ya amsa mata yana gyara zaman madubinshi tare da duba agogon hannunshi

Wani kallon mamaki take bin sa da shi, ya ce "malama ki fita, i'm late, ina da aiki a gaba na"

Ba ta iya cewa komai ba ta buɗe ƙofar ta fita, har sai da ta shiga cikin gidan kafin iya jan motar ya wuce.........

MANAGE THIS PLS❤️

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Never give up on something you really want. It's difficult to wait, but more difficult to regret...!_

*PAGE 49-50*

A parlour ta tarar da Hajiyar London na saukowa daga dinning area, hannunta riƙe da gorar ruwa, da gudu Sunaiha ta ƙarasa ta rungume ta, ta ce "i miss you Hajiyata"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Ita ma rungume ta ɗin tayi ta ce "i miss you too My Baby" jan ta tayi suka zauna kafin ta ce "amma kin yi missing ɗina shi ne sai da nayi kwana biyu a ƙasar nan sannan za ki zo ko?"

Kafin Sunaiha ta ba ta amsa, Mummy ta shigo, har sai da ta zauna kafin ta Sunaiha ta gaishe ta, "yau kin samu shigowa kenan" cewar Mummy

Hajiyar London ta ce "sai yau, ai ni fushi ma nake da ita"

Sunaiha ta shagwaɓe fuska ta ce "haba Hajiyata, kiyi haƙuri ai ga ni na zo kuma sai dare zan tafi"

Hajiya ta nisa ta ce "shikenan zan haƙura amma saboda mijinki"

Sunaiha ba ta damu ta fahimci me Hajiya ke nufi ba, ita dai tayi murna, sai ta ce "Daddy dai na san ya fita amma za mu haɗu anjima, to ina Sharif da Anty Najma?"

Hajiyar London ta ce "yaushe kuma kika fara ganin girman Najma har ta samu Anty?"

Mummy tayi ƴar dariya ta ce "ba na gaya miki ashe aure zai sa yarinyar nan tayi hankali ba!"

"Ai kuwa na ga zahiri"

Sunaiha ta ce "wai meyasa kuke cewa ba na a hankali? Amma ba komai... yanzu dai ina suke?"

Mummy ta ce "Sharif ya je yawo, kin san bai iya zaman gida ba, Najma kuma dama halinku ɗaya, yanzu ta gama breakfast ta wuce ɗaki"

Miƙewa Sunaiha tayi cike da murna ta cire hijab ɗinta, ta ce "bari in je" da gudu ta ke haura stairs ɗin

Najma na kan gado tana kallo cikin laptop ɗinta, Sunaiha ta shiga ɗakin da gudu, sai kan gadon ta sauka, ta rungume ta, ta ce "My Sis"

Ita ma Najma rungume ta tayi kafin ta janye ta daga jikinta tana ƙare mata kallo, ta ce "ni matsa ma nayi fushi dake ai"

"Oh God, Anty Najma i'm sorry, yanzu ma Hajiya fa cewa tayi tana fushi da ni, ke ma haka, ya kuke so in yi, inda Sharif ne na san he will surely understand me" ta ƙarasa tana turo baki

Murmushi Najma tayi ta ce "i also understand you dear....but wait, me na ji kin ce?"

Haɗe gira Sunaiha tayi alamun rashin fahimta ta ce "me kike nufi?"

"Na ji kamar kin ce Anty"

"Yes, Anty Najma"

"Yaushe kika fara kuma? Oh, na manta yanzu you're married, kin fara hankali"

"Dama can ina da hankali ai"

"A'a, Prince dai yayi ƙoƙarin gyara mana ke, dama yanda kike son shi ɗin nan na san tsab zai saita ki....gaskiya Sunaiha kinyi dacen miji, ga kyau, ga iya kwalliya, ga class, he's perfect, no wonder kika yi rejecting ɗin kowa sai Prince"

Da mamaki Sunaiha ta ce "a ina kika ganshi to?"

"Ji ki da zancen banza, ba jiya ya zo nan ba har ya ce kina da baƙi shiyasa ba ku zo tare ba? A nan na ga haɗu, kuma da alama yana sonki"

Numfashi ta sauke, ta ce "hmm, na so yanda kike tsammani ɗin haka ne, da na ji daɗi"

Kallon tsab Najma tayi mata, kafin ta zauna da kyau ta ce "ban gane ba, me kike nufi?"

Hawaye ne ya biyo fuskarta, ta ce "Anty Najma ke kaɗai ce wacce zan iya gaya wa matsala ta yanzu, na so gaya wa Sharif, amma na fasa, ke ce mace na san za ki fi shi fahimtar halin a nake ciki....Anty Najma, Prince ba ya so na, ni kaɗai ce ke hauka akan shi"

"Sunaiha ki mun bayani yanda zan gane"

Share hawayenta tayi kafin ta fara bata labari, tun farkon aurensu har zuwa yanzu, ba abunda ta ɓoye mata, ta kai ƙarshe tana kuka, ta ce "Anty Najma abun nan ya damu na kullum, ya hana ni gaya wa kowa, da farko tsoronshi ya hana ni faɗawa kowa, amma daga baya na yanke shawarar gaya wa Mummy, amma na san za ta ji haushinsa ne kawai, Ikram kuwa bana so ta fahimci halin da nake ciki, ke kaɗai na ji za ki iya fahimta ta"

Gaba ɗaya mamaki ne da takaicin Prince ya gama cika Najma, ta ce "tabɗijam, wai wannan maganar da gaske kike yi Sunaiha?"

"Wallahi Anty Najma ba abunda na faɗa wanda yake ƙarya ne, ba zan miki ƙarya ba ke kin san halina"

A fusace ta ce "to wallahi da sake! Sunaiha da gatanki a grin nan, wani banzan namiji ya mayar da ke baiwarsa! Shiyasa gaba ɗaya kin sauya, i thought hankali kika yi, ashe na dole ne? To wallahi bari ki ji, wannan iskancin na shi dole ne ya zo ƙarshe a yau ɗin nan, saboda ki a son shi ba shi zai sa ya dinga miki wannan wulaƙancin ba, yanzu zan je in gaya wa Mummy, dole ne ku

rabu, haka kawai! Hauka ake yi? Zai wani wulaƙanta ki! To yau za ku rabu, ya je ya auri wacce yake so ɗin, ke kuma Allah ya ba ki wanda ya fi shi alkhairi" ta ƙarasa rai a ɓace tana miƙe wa

Har ta kai ƙofa, da gudu Sunaiha ta jawo ta, tana share hawaye, ta ce "dan Allah Anty Najma ki tausaya mun, ba wai na gaya miki ba ne saboda ki gaya wa Mummy ba, kawai na gaya miki ne saboda matsayinki a wuri na"

"Kar a gaya wa Mummy? Ai wanda ya gaya mata kawai ya riga ni, ki ƙyale ni"

Cikin kuka ta ce "Anty Najma dan Allah kar ki je, ba na so a raba ni da Prince ɗina, i still love him wallahi, na tabbata wata rana zai gane na fi kowa sonshi a duniyar nan, i can't leave without him...amma idan kika ce sai kin gaya mata, ba zan sake gaya miki komai da ya shafe ni ba, sannan ba za ki sake ganina cikin farinciki ba"

Jikin Najma ya gama mutuwa ganin yanda Sunaiha ke kuka akan wanda ya wulaƙanta ta, saboda kawai tana sonshi, ba ta taɓa tunanin za ta ga Sunaiha haka a rayuwarta ba, jan hannunta tayi suka koma kan gadon suka zauna, ta ce "Sunaiha!"

Ba ta iya amsa mata ba, sai kallonta kawai da take yi da jajayen idanunta

"Yanzu Sunaiha kina nufin har yanzu kina son wannan mutumin?"

Da ƙyar Sunaiha ta iya dai-dai kata, ta ce "Anty Najma i truly love him, duk abunda ya mun ba na ganin laifinsa, laifina ne"

"Me kika yi da kika yi deserving wannan?"

"Ke ma kin sani Anty Najma, halina ya ja mun wannan, na wulaƙanta mutane ban san adadinsu ba, na ci zarafin mutane da yawa, ban san darajar ɗan adam ba a rayuwa ta, bana jin maganar mahaifiyata, na fifita Daddy da dukiya fiye da komai, na manta cewa Allah da ya azurta mu ba wai mun fi sauran bayinsa ba ne, Anty Najma, duk wannan laifin Daddy ya fi na wa,  yana so na, amma ya kasa nuna mun hanyar da zan iya gyara rayuwata ta lahira, Daddy bai damu da karatuna na addini ba, bai damu da yanda nake tafiyar da mu'amalata da mahalicci na ba, shi dai kawai duniya ya sa a gaba, hakan ya sa nake jin tamkar na fi kowa....amma kin san me Anty Najma, auren Prince alkhairi ne a wurina, saboda shi ne na haɗu da Yayarsa da ta sauya ni completely, da farko na sauya ne saboda son Prince, amma yanzu ko ba da shi ba zan iya ci gaba da gudanar da rayuwata a haka"

"Hmm, Sunaiha wannan duk ba dalili ba ne da za ki ci gaba da zama da shi"

Sake share hawayenta tayi a karo na ba adadi, ta ce "a cikin karatun da Anty Sadiya ke mun, ta gaya mun ko wane mutum yana da kalar na shi ƙaddara, akwai hanyoyi kala-kala da Allah ke jarabtar bawansa, na tabbata son Prince shi ne nawa ƙaddarar rayuwar, soyayya ita ce jarabta

ta....Anty Najma dan Allah kar ki hana ni cin wannan jarabawar, zan jure komai da Prince zai mun har zuwa lokacin da Allah zai karɓi addu'a ta"

Anty Najma ta tausaya wa Sunaiha sosai ba kaɗan ba, ta yarda so yana iya juya mutum ko mai girmansa ko matsayinsa, dan ga zahiri ta gani a wurin ƴar uwarta, yarinya me ji da kanta, ga aji, ga izza, ga kyau, ga matsayi, kusan komai ta haɗa, amma ta iya jure wannan rayuwar da Prince saboda SO, kuma har yanzu ba ta karaya ba.

Jawo ta tayi tana rarrashinta, ta ce "shikenan ya isa, kiyi shiru, ba zan gaya wa kowa ba, amma idan hakan na ga ya fara wuce hankali, to tabbas sai dai kiyi haƙuri, dan zan faɗa ne, ba zan ƙyale ki ki ci gaba da zama cikin gidan da ba'a sonki ba'a girmama ki, har ita Yayar ta shi ba wai na yarda tana ƙaunarki bame, saboda da ace ƴar uwarta ce ke cikin wannan halin a gidan miji, sai tayi duk yanda za tayi an raba auren, ba wai ta ce ta ci gaba da zama ana wulaƙanta ta ba"

Sunaiha kuka kawai take yi, ta kasa cewa komai, kusan mintuna biyar su na haka, sannan Sunaiha ta miƙe ta shiga toilet dan ta wanke fuskarta, kira ne ya shigo wayarta, har ya tsinke Anty Najma na kallo, sai da kira na biyu ya shigo sannan Sunaiha ta fito ta ɗauki wayar, ganin Najeeb ne ya sa tayi tsaki ta ajiye

Anty Najma ta ce "waye kika yi saving contact ɗin shi da NAJEEB DEAR?"

"Wani ne"

"Na san wani ne ai, waye shi na ce"

Zama tayi ta ba ta labarin Najeeb kasancewar bata gaya mata labarinshi ba tun farko, Anty Najma ta ce "shi ne har yanzu yake bibiyarki kuma?"

"Eh, daga aure na zuwa yanzu ya tura mun saƙo ya fi guda talatin, bari ki gani"

Miƙa mata wayar tayi wurin da saƙonnin Najeeb suke, saƙonnin sun yi yawa, hakan ya sa ba ko wane take karanta wa ba, amma daga cikin waɗanda ta karanta, ta fahimci Najeeb na matuƙar son Sunaiha, kawai dai idonta ya rufe ne akan wannan Sadeeq ɗin

Numfashi ta sauke ta ce "Allah ya kyauta....yanzu ki ɗan zauna, idan kin natsu sai mu sauka wurinsu Mummy dan kar su fahimci wani abu"

Jinjina kai tayi, sannan ta zauna

Ɓangaren Sarah kuwa, ƙarfe biyu ta fito daga makaranta, kai tsaye ta nufi gidansu Tiger, ta daɗe a ɓangaren Umma suna ta fira kafin ta koma ɓangaren Momi kasancewar yau Hajiya ba ta

nan, sun fita da su Sultana

"Sarah ba dai har kun gana firar ba" cewar Momi

"Mun gama, to Anty Basira kin san ba wani saba wa nayi da ita haka nan ba, ina jin nauyinta sosai, amma ai na daɗe"

"Haka ne kuma kin yi ƙoƙari, amma ki ƙara matuƙar kina son samun Sadeeq, kamr yanda na gaya miki, ya fi sonta fiye da kowa"

"Ai ban manta ba Anty na, in sha Allah sai na mallaki Sadeeq, ni ba sai ma ya saki waccan ɗin ba, in aure shi, shi ne babban burina yanzu"

"Burinki zai cika kuwa, amma dai idan kina ke kaɗai za ki fi jin daɗi"

"To shikenan, amma banda matsala da matarsa, kowa da halinshi yake zama ai"

"Ba za ki gane ba, amma ba komai"

Murmushi tayi ta ce "ni dai zan koma babban parlour, na ga ba kowa a can, zan yi kallo"

"Bari in biyo ki ai, nima yanzu nake shirin fita sai ga ki"

Tare suka dawo babban parlourn gidan suka zauna, kallo suke yi suna fira kaɗan-kaɗan

Ƙofar parlourn Sadeeq ya turo ya shigo, ganin Momi ya sa annurin fuskarshi ɗauke wa, kasancewar sun ba ƙofar baya, kuma sun da nisa da ƙofar, ya sa ba su ji shigowarsa ba, har ya haura sama ba su ganshi ba, bai tsaya ko ina ba sai ɗakin Umma

Fitowarta kenan daga cikin ɗaki, ta ce "Saddikul Akbar ɗan Ummanshi"

Murmushi yayi, ya ƙarasa kusa da ita, ya ce "Maa, kin wuni lafiya?"

"Alhamdulillah Siddiku na, ya aiki ya matar gidan"

Wani murmushin ya sake yi, ya ce "Maa, yau na ga sai farinciki kike ta yi, lafiya kuwa? Har wata sabuwar soyayyar ɗanki kike ji"

Ƴar dariya tayi ta ce "shikenan sai wani abu ya faru zan yi farinciki?"

"Ai na san halinki ne Maa, shiyasa"

"To ba komai, haka kawai nake jin farinciki, kuma Hajiya ba ta nan yau, Sarah ta zo nan part ɗin

ta taya ni fira, ba ta jima da fita ba ma"

"Sarah dai?"

"Ƙwarai, nayi tunanin Sarah za ta daina zuwa gidan nan bayan kayi rejecting ɗinta, sai na ga ko a jikinta, ta fahimce ka ta ajiye komai, gaskiya tana da hankali, na so ka auri yarinyar nan, amma Allah shi ne mafi sani akan komai, Allah ya sa Sunaiha ita ce alkhairi a rayuwarka"

Shiru ya ɗan yi, kafin ya ce "Maa yunwa fa nake ji" ya kawar da zancen

"Matarka fa? Ka je wurin ta ka ci"

"Tana gida ne ai...ni dai muje ki san yanda za kiyi da ni, i'm hungry"

"To Abbakar, ka cinye ni"

Murmushi ya suɓuce mishi, ya ce "Maa idan na cinye ki gobe wurin wa zan zo in ji daɗi?"

"Hajiya mana"

"Ai ba za ta iya maye gurbin ki ba Maa,...to amma na ji, shi kuma Abba wa zai kalla ya ji sanyi a zuciyarsa idan na cinye Habibiyarsa?" Ya ƙarasa yana ƙumshe dariya

Dukanshi Umma tayi ta ce "ashe ba ka da kunya ban sani ba ko! Ana maka kallon salihi idan ka shiga mutane ka ɗaure fuska, nan kuwa ni mahaifiyarka kake sauke wa rashin kunyarka"

Dariya yayi ya koma ta bayanta ya rungume ta, ya ce "i love you My World best"

Shafa fuskarshi tayi ta ce "love you too dear....mu je ka ci abincin"

Parlour suka koma, sai a lokacin Momi ta ganshi, ta ce "Sadeeq yaushe ka shigo?"

Umma ta ce "ba ku ganshi ba kenan"

"Series ɗin nan ya ɗauke mana hankali"

Murmushi kawai yayi ya wuce dinning area, Umma ta ce "Sarah dan Allah zo in sa ki wani aiki"

"To Umma" ta faɗa cike da girmamawa tana miƙe wa

"Ki je ki gaya wa ma su aikin nan a samu wacce za ta kawo ma Sadeeq abinci"

"To Umma, zan kai mishi m, ba komai"

"Sarah kenan, to nagode"

"Ba komai" daga haka ta wuce kitchen

A dinning area ta same shi, tayi serving ɗin shi, sannan ta zauna, ta ce "kana buƙatar wani abu?"

"No it's ok, thank you" ya faɗa kafin ya fara ci

Kallonshi kawai take yi tana saƙa abubuwa a ranta, ɗaga ido yayi ya kalle ta, ya ce "ya dai?"

"Ba komai" ta amsa tana murmushi

"Nagode" ya faɗa bayan ya kawar da idanunsa daga kanta

"Da me?"

"Da kika taya Maa fira yau"

"Haba ba komai, ai nima mahaifiya ta ce"

Kallonta ya sake yi kafin ya jinjina kai, ta ce "yawwa Sadeeq in tambaye ka mana"

"Ina jinki"

"Umm... shikenan ma, manta kawai"

Ɗaga kafaɗa yayi, ya ce "ok" haka suka ci gaba da zama har ya kammala cin abincinsa, sai da yayi kusan mintuna goma sannan ya miƙe yayi mata sallama, ya koma cikin parlourn yayi wa Umma sallama sannan ya fita.......

KUYI HKR DA WANNAN YAU MA DAN ALLAH, SABODA MA NACE YAU ZAN YI POSTING SHIYASA NAYI SQUEEZING TIME NAYI, I'M SORRY🥰

INA JIN DAƊIN COMMENTS ƊINKU SOSAI, YANA BANI NISHAƊI, TNX🤗❤️

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Always focus on everything you love about yourself each and everyday. Tell yourself how proud you are for how hard you are trying. See everything with love and compassion then you will see your world so differently._

*PAGE 51-52*

Kwanaki bakwai kenan da zuwan Sunaiha gida, ba abunda ya sauya daga zamantakewarsu da Tiger, tana iya ƙoƙarin ta kullum kamar yanda ta saba, sai dai shi ma as usual, ba ruwanshi da ita. Haka ma Najeeb, ba abunda ya rage daga kira ko saƙon da yake tura mata, har ta daina damuwa da shi, wani lokacin ta kan ɗauki wayar, wani lokacin kuma ta ƙyale shi. Sarah ma tana yawan kyautata ma Umma sosai, kusan kullum sai ta biya ta gidan idan ta tashi daga makaranta, za ta zauna tare da su Sultana da Salma suyi ta fira, wani lokacin ma sai dare take wucewa, Momi na jin daɗin hakan sosai saboda tana ganin alamun nasara a plan ɗinta, shi kan shi Sadeeq yana jin daɗi idan Umma tana gaya mishi yanda Sarah ke mata, har yana jin
~~~~~~~~~~~~~~~~

haushin meyasa tun farko da ta ce tana sonshi ya dinga share ta, madadin ya lallaɓa ta su rabu lafiya, hakan ya sa na ɗan fara sake mata fuska idan ya ga dama, sai dai ba can-can ba

Sadeeq na wurin wani shaƙatawa tare da Muhsin, suna fira, Sadeeq ya ce, "Yarima ka san me?"

"Ina jinka dai, sai ka faɗa"

"Ina tunanin bayyana wa duniya Jewel, i'm tired of all this"

"Hmm, Tiger kenan, to ai ni tun lokacin da ka gaya mun abunda Anty Saudat tayi, na so in gaya maka ko da baka nuna wa kowa ita ba, to ka nuna wa Anty Saudat may be za ta ji daɗi...to amma na san kai juyayyen mutum ne, tsab za ka ce a'a"

Murmushi Tiger yayi, ya ce "ai da ka gaya mun, ba dan ce a'a ba...amma zan yi magana da Anty Sadiya anjima"

Kafin Muhsin yayi magana, sai ga Safwan ya ja ɗaya daga cikin kujerun da ke wurin ya zauna, dama jiranshi suke yi, ya ce "wace magana za'a yi da Anty Sadiya kuma?"

Muhsin ya ce "Safwan akwai ka da gulma"

"Eh ba komai dai, a gaya mun"

Muhsin ne ya gaya mishi zancen da suke yi, Safwan ya ce "wai kai har yanzu dama ba ka daina zancen wannan Jewel ɗin ba"

Kallon mamaki Sadeeq ya bi shi da shi, kafin ya ce "in daina zancenta fa ka ce, Safwan kai kanka ka san tsawon shekarun da nayi ina son Jewel, kai tsaye sai ka ce in manta da ita? Saboda me?"

"Saboda kayi aure mana Tiger"

"Shikenan kuma dan nayi aure sai aka ce ba zan sake auren wata ba? Mata huɗu fa nake da ikon aura"

"Amma ai ba ka da ra'ayin auren ko da mata biyu ke bare kuma huɗu" cewar Safwan

"Zan iya sauya ra'ayi ai, in dai akan Jewel ne"

"Amma ka san idan ka auri Jewel za ka cutar da Sunaiha"

"Nima ta cutar da ni ai"

Safwan ya buɗe baki zai yi magana, Muhsin ya katse shi, "come on!! It's okay mana, ya isa haka, ni kun dame ni da magana ɗaya, sai na ga da Sunaiha da Jewel ɗin duk ɗaya ne"

Sadeeq ya ce "ba ɗaya ba ne, akwai banbanci"

Safwan ya ce "ka ji ko!? Wanda bai ɗauke su matsayin abu ɗaya ba, ta ya kake tunanin zai yi adalci?"

"Dama ai zai ji suna da banbanci a zuciyarshi, amma zai yi adalci" cewar Muhsin

Safwan ya ce "seems like har yanzu ba ka gama gane waye Tiger ba, amma...." Ƙarar da wayarshi yayi ne ya katse shi

Ɗauka yayi bayan ya ga Kawu Ƙarami ne, sai da suka gaisa kafin Kawu Ƙarami ya ce "Safwan kuma tare da Sadeeq ne?"

"Eh Kawu" ya amsa

"Ba shi wayar"

Miƙa mishi yayi tare da gaya mishi ko waye, sallama Sadeeq yayi, Kawu Ƙarami ya ce "Sadeeq ina ka ajiye wayarka nake ta kiranka ba ka ɗaga ba?"

"Kayi haƙuri Kawu, wayar na mota ne"

"Allah ya shirya mun kai Sadeeq, tun ɗazu ake kiranka daga ɗayan asibitin akwai emergency ba ka ɗauka ba, sai da suka kira ni, ina nan ina da wani aiki a wannan asibitin, dole Dr Abbas na nema"

"Kayi haƙuri, ban san za'a samu emergency yanzu ba shiyasa, yanzu na bar asibitin ma"

Ƴar dariya Kawu yayi, ya ce "Sadeeq kenan, idan emergency ɗin zai samu gaya maka ake yi? Ai kwatsam yake zuwa, ka san yanayin aikinka, ka dinga ajiye wayarka a kusa"

"In sha Allah, zan kiyaye"

"Yawwa....yanzu ma duk ba wannan ba, Hajiya ce ta kira ni, wai jikin Baba (Grandpa) ya tashi, shi ne nake so ka je ka duba shi ka gani, yanzu akwai operation ɗin da za mu shiga"

"To, yanzu zan tafi" daga haka ya kashe wayar ya miƙe

Safwan ya ce "lafiya?"

"Jikin Grandpa ne ya tashi" ya faɗa yana miƙa mishi wayar

Miƙewa suka yi, Muhsin ya ce "Subhanallah...da sauƙi?"

"Ban sani ba ga gaskiya, sai na je zan gani"

"To mu tafi"

Murmushi Sadeeq yayi ya ce "a'a Muhsin, tun ɗazu mai martaba ya kira ka fa ka ce mishi kana zuwa, ya kamata ka tafi ka ji menene"

"I know it's nothing important, mu je in ga Grandpa"

Safwan ya ce "Muhsin kana gaya wa mutane su dinga bin iyayensu fa, yau kai ne mai martaba ya kira ka kayi jinkirin zuwa?... Kayi haƙuri ka tafi, ko menene zan kira ka"

Ssdeeq ya ce "zancen aure zai mishi ne shiyasa yake zillewa"

Dariya Safwan yayi ya ce "ka tafi, Allah ya sa kai ma irin na wani za'a yi maka"

Hararar Safwan suka yi kafin Sadeeq ya ce "ka ji da shi dai"

Daga haka suka wuce kowa ya shiga motarsa, Muhsin ya wuce fada, su Sadeeq suka nufi gidansu Grandpa. Tare suka shiga gidan da Safwan, Hajiya, Umma da Momi duk suna cikin parlourn, sai Grandma dake gefe, Grandpa kuwa na kwance kan kujera

Gaida su suka yi baki ɗaya kafin Sadeeq ya ƙarasa kusa da shi ya taɓa shi, jikinshi yayi zafi sosai, da ƙyar yake  iya buɗe ido, Sadeeq ya ce "kaii!! Haka jikinshi yayi zafi?"

Hajiya ta ce "haka muka same shu, mu ma Mama (Grandma) ta kira take gaya mana kuma nayi ta kiranka ba ka ɗaga ba"

Kallon Safwan yayi, ya ce "Safwan tayani ɗaga shi, sai mun tafi asibiti"

Kama shi suka yi zuwa motar Sadeeq, Safwan ya ja motar, su Hajiya kuwa Momi ta ja ta su motar. Kai tsaye asibitin su suka nufa, ba tare da ɓata lokaci ba aka yi admitting ɗinshi, Sadeeq ya shiga ya duba shi ya mishi allurar da ya kamata, ya sa mishi ruwa sannan ya fito, su Hajiya suka shiga

Fitarshi ke da wuya, sai ga Kawu, ya ce "Sadeeq ya jikin na shi?"

"Da sauƙi dai, amma BP ɗin shi ya hau sosai"

"How comes? Ya gaya mun ka sauya mishi magani, kuma na ga har da na BP, to amma ya aka yi bai rage ba sai ma ya hau?"

"Abu ɗaya ne Kawu, Grandpa ba ya son sha magani ko kaɗan, sannan magana nake kullum akan shan drinks ɗin nan amma ba ya ji, drinks ɗin nan suna da matsala sosai wallahi, har da shi ke ƙara mishi wannan ciwon ƙafan"

"To ai kai yana jin maganarka ma, kuma bai daina ba...amma ka san yanda za'a yi, yanzu mu barshi a nan, sai ka dinga kula da shan maganinshi kar a tsallake, sannan kar kowa ya kawo drinks asibitin nan, a hana shi sha, yayi ko da sayi ɗaya ne, sai mu ga wane canji za'a samu"

"Shikenan, in sha Allah zan yi haka"

"Bari in shiga in ganshi, Abbanku yana nan zuwa, amma kar ka kira Alhaji tun da ba ya ƙasar kar a ɗaga mishi hankali"

"To Kawu, bari in je office, zan cika wasu files"

"To" Kawu ya faɗa sannan ya shiga ɗakin, Sadeeq kuma ya wuce office

Ya kai mintuna goma yana aiki, sai ga Safwan ya shigo, bayani ya mishi akan abunda suka tattauna da Kawu, Safwan ya ce "wallahi matsalar Grandpa taurin kai, amma sau nawa ake cewa ya bari a kai shi abroad, ya ce a'a.....Allah ya ba shi lafiya to"

"Ameen, amma Grandpa idan ya tsaya kan magana ɗaya ba ya sauyawa"

"Halinku ɗaya ai, tun da ga shi ɗazu ka ƙara nuna mun"

"Hmm, Safwan ba za ka gane ba ne"

"Ai ba zan gane ba, yanzu dai dole dai ba za ka rabu da Jewel ba"

"Impossible"

Numfashi Safwan ya sauke ya ce "to yaushe za ka bayyana ta ɗin? Kayi wa Anty Sadiya magana, mu ma dai mu ganta kowa ya huta"

Murmushi yayi, ya ce "za ka ganta, amma yanzu ka ga ciwon Grandpa ɗin nan shi zai dakatar da ni, na fi so hankalin kowa yana wuri ɗaya sannan zan bayyana ta dan ta samu kula ta musamman, dan hak sai Grandpa ya warke zan bayyana ta"

"Wannan jan class ɗin dai yayi yawa, to Allah ya ba shi lafiya"

"Ameen" ya faɗa yana ci gaba da rubutun da yake yi

Sharif ya je wurin Sunaiha ya kai sau biyu, amma Najma sai yau ta zo, shi ma saboda Hajiyar London ta matsa mata, dan ita haushin zuwa gidan Sadeeq take ji

Suna zaune suna ta fira, Najma ta ce "wai Sunaiha ya mutumin naki? Ya sauya?"

"Hmm, Anty Najma kenan" abunda kawai ta faɗa kenan

"Bai sauya ba ko!? Wallahi Sunaiha kina ba ni mamaki, wai kyaun Sadeeq ne ke ruɗarki ko me? Sunaiha ban ga amfanin kyaun miji ba in dai ba zai daraja ki ba, kin ga miji me kyau da miji me kuɗi, wallahi aikin banza ne idan babu soyayya, duk kin wani sauya kamar ba ƳAR SENATOR ɗin da na sani ba!? Sunaiha, Najeeb yana sonki, ban san shi ba, ban taɓa ganinshi ba, amma wallahi daga kalaman shi zuciyata ke gaya mun shi ne mai sonki amma idonki ya rufe akan wannan Prince ɗin...to wallahi bari in gaya miki gaskiya, rabuwa da Sadeeq shi ne alkhairi a wurinki, ki dawo wa mai sonki, kar ki yi biyu babu, kar lokacin da kika fahimci Sadeeq ba abokin rayuwarki ba ne, ko ya sake ki, ki zo kuma Najeeb ya haƙura da ke, wallahi you will regret it"

Tun da Najma ta fara magana, Sunaiha ke kallonta, tana so ta ɗauki zancen amma zuciyarta na hana ta, ita ta san ba za ta iya rayuwa da kowa ba idan ba Sadeeq, ta san tabbas Najeeb na sonta sosai, amma ita kuma tana son Sadeeq, hawaye ne ya biyo fuskarta

Anty Najma ta kalle ta, ta ce "Sunaiha kina wahalar da rayuwarki, na yarda Allah yana jarabtar bayinsa, kuma ya jarabce ki wallahi, dan ko a mafarki aka gaya mun za kiyi haka, zan ƙaryata, amma a matsayina na ƴar uwarki, ina gaya miki abunda zai amfane ki ne, amma yanzu so ya rufe miki ido ba za ki gane ba, sai dai ina so ko da rana ɗaya ne, ki natsu kiyi nazarin abunda na gaya miki, duk ranar da kika auri wanda yake sonki, to za ki gane wannan gidan a matsayin ƴar aiki kike, ba matar gida ba"

Daga haka ba ta sake ce mata komai ba, ita ma Sunaiha shiru tayi, suna a haka, aka danna door bell, ta je ta buɗe, Ikram ce, ta ji daɗin ganinta sosai, amma sai da suka zauna kafin ta ce "ai dama ba ki zo ba, ni kayi fushi"

Ikram ta ce " kin gani ko Sis Naj, sai da na gaya miki ko zuwa nayi ba za tayi appreciating ba"

Murmushi Najma tayi ta ce "na gani kuwa, ai saboda ni kika zo, ƙyale ta kawai"

Sunaiha ta ce "oh, kenan ma ba zuwa na ba ne"

"Eh, Sis Naj ce ta kira ni ta ce in zo, ai in dai saboda ke ne ba za ki ganni ba sai ranar da kika

zo gidanmu" cewar Ikram

"To shikenan, ba komai"

Ikram ta ce "ni je ki kawo mun ruwa"

Hararta tayi, ta ce "Anty Najma ta ɗauko miki ai wurinta kika zo"

Suka yi dariya, Ikram ta ce "ai dai gidan ba baƙo na ba ne" sai ta miƙe ta je ɗaukowa

Najeeb na office tare da abokinshi, yake tambayarshi "wai Najeeb ina mutumiyarka?"

"Sunaiha?"

"Eh"

"Tana nan, meyasa ka tambaya?"

"Ina so ne in sani idan kayi hankalin ƙyale matar mutane ko kuma har yanzu kana bibiyarta"

"Bash kenan, ai duk abunda zai sa in ƙyale Cutie to ba ƙarami ba ne, musamman ma yanzu da nake ganin canji a tattare da ita"

"Ban gane ba"

"Yanzu fa idan na kirata, ta kan natsu ta saurare ni mu gaisa, wani lokacin ma sai ta saurari abunda nake faɗa kawai idan na gama ta kashe, saɓanin da, da idan na kira tana ɗauka za ta fara masifa sannan ta kashe ba tare da na ce komai ba"

"Lallai Najeeb...anya kuwa mijinta na sonta?"

"Meyasa ka ce haka?"

"A tunani na, ida mijinta yana sonta dole ne yana da lokacinta, idan yana da lokacinta dole wata rana zai ga kiranka a wayarta, amma kullum kan cin karenka ba babbaka!"

Dariya Najeeb yayi, ya ce "nima ban sani ba kam, amma dai na san tana matuƙar ƙaunarshi, sai dai zan cire wannan son na shi daga zuciyarta in sa nawa, kai ka san waye Najeeb"

Shi ma Bash dariyar yayi ya ce "tsab kuwa na san Najeeb musamman akan mace" suka sake yin dariya baki ɗaya

Sai bayan sallar isha'i sannan Tiger ya dawo gida, tana zaune a parlour ita kaɗai, sallama kawai yayi ya wuce ciki ba tare da ya kalle ta ba bare kuma ya amsa gaisuwarta, ya shiga ɗaki

Bai tsaya ɓata lokaci ba ya faɗa toilet saboda jikinshi ba daɗi, yau yayi aiki sosai a asibiti, gaba ɗaya a gajiye yake, wanka yayi sannan ya fito ya bi jikinshi da body sprays, ko mai ya kasa shafa wa, ya koma bakin gado ya zauna, sannan ya jawo drawer ya ɗauko hoton Jewel ɗin shi yana kallo, abubuwa da yawa ne ke zuwa mishi a rai akanta, a hankali yake fitar da wani kyakkyawan murmushi, ya kai tsawon minti goma sha biyar, sannan ya iya mayar da hoton ya tashi ya dawo parlourn ya zauna

Sunaiha na ganinshi ta je ta ɗauko mishi abinci ta ajiye, sannan ta fuskance shi, ta ce "sannu da aiki"

"Yawwa" ya amsa yana duba wayarshi

Girgiza kai tayi kafin ta ce "yau ba ka dawo da rana ba, lafiya?"

"Aiki nake yi" ya sake amsa mata a gajarce

"Aiki kuma?"

Ya ce "um"

"Amma ai na kira ka, meyasa ba ka ɗaga kira na ba?"

"Ba na kusa"

"To meyasa ba ka kir...."

A tsawace ya katse ta "Haba mana dan Allah!!! Wai yaushe kika fara aikin jarida ne? Waɗannan tambayoyin sun ishe ni"

Ta razana sosai, hakan ya sa tayi shiru, sai da ya ci gaba da danna wayarshi kafin cikin sanyin murya ta ce "Amma laifi ne dan na tambaye ka? Ni fa matarka ce"

Wani kallo ya mata, ya ce "Au haba!!? Haka ne kuma, na manta ai....ji wani bakinta, wai mata, mtsww" yayi tsaki

Ƙoƙarin mayar a hawayenta tayi, ta ce "na sani ai, ba sai ka faɗa ba, ba ka taɓa kallo na a matsayin matarka ba ko? Ka fi son Princess Jewel fiye da ni, i already knew it"

"Good" ya faɗa yana kallon cikin idonta, "it's better da kika fahimci haka da kanki, yanzu kin fara gane matsayin Jewel kenan"

Numfashi ta sauke mai cike da takaici, ta ce "Hmmm, Ya Sadeeq kenan, Allah ya ganar da kai mai sonka da gaskiya kafin lokaci ya ƙure maka"

Sake kallonta yayi, ya ce "what do you mean?"

"I mean nothing" ta miƙe kawai za ta wuce

Ya ce "for your own information, Grandpa ba ya jin daɗi, yana asibiti, da safe idan kin ji za ki iya, ki shirya mu tafi ki ganshi, idan kuma ba za ki iya ba, it's your own cup of tea"

Ba tare da ta ce mishi komai ba ta wuce ciki, tana shiga ta faɗa kan gado tana kuka, gaba ɗaya ta kasa gane kan Sadeeq, shi sam a rayuwarshi bai san kyautatawa bane ko me? Duk abunda za tayi laifi ne a wurinshi? Nan kalaman Najma suka fara dawowa kunnenta, ta rasa wa za ta saurara, kalaman Anty Najma ko kuma zuciyarta? Haka kawai ta tsinci kanta da rokon Allah ya sa Najeeb ya kirata ko ya turo mata da saƙo, wataƙila idan ta ji kalaman shi za ta ji sassauci, amma har bacci yayi awon gaba da ita, yau Najeeb ba kira ba saƙo tun na safe da yayi........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*

_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Always focus on everything you love about yourself each and everyday. Tell yourself how proud you are for how hard you are trying. See everything with love and compassion then you will see your world so differently._

*PAGE 51-52*

Kwanaki bakwai kenan da zuwan Sunaiha gida, ba abunda ya sauya daga zamantakewarsu da Tiger, tana iya ƙoƙarin ta kullum kamar yanda ta saba, sai dai shi ma as usual, ba ruwanshi da ita. Haka ma Najeeb, ba abunda ya rage daga kira ko saƙon da yake tura mata, har ta daina damuwa da shi, wani lokacin ta kan ɗauki wayar, wani lokacin kuma ta ƙyale shi. Sarah ma tana yawan kyautata ma Umma sosai, kusan kullum sai ta biya ta gidan idan ta tashi daga makaranta, za ta zauna tare da su Sultana da Salma suyi ta fira, wani lokacin ma sai dare take wucewa, Momi na jin daɗin hakan sosai saboda tana ganin alamun nasara a plan ɗinta, shi kan shi Sadeeq yana jin daɗi idan Umma tana gaya mishi yanda Sarah ke mata, har yana jin haushin meyasa tun farko da ta ce tana sonshi ya dinga share ta, madadin ya lallaɓa ta su rabu lafiya, hakan ya sa na ɗan fara sake mata fuska idan ya ga dama, sai dai ba can-can ba

Sadeeq na wurin wani shaƙatawa tare da Muhsin, suna fira, Sadeeq ya ce, "Yarima ka san me?"

"Ina jinka dai, sai ka faɗa"

"Ina tunanin bayyana wa duniya Jewel, i'm tired of all this"

"Hmm, Tiger kenan, to ai ni tun lokacin da ka gaya mun abunda Anty Saudat tayi, na so in gaya maka ko da baka nuna wa kowa ita ba, to ka nuna wa Anty Saudat may be za ta ji daɗi...to amma na san kai juyayyen mutum ne, tsab za ka ce a'a"

Murmushi Tiger yayi, ya ce "ai da ka gaya mun, ba dan ce a'a ba...amma zan yi magana da Anty Sadiya anjima"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Kafin Muhsin yayi magana, sai ga Safwan ya ja ɗaya daga cikin kujerun da ke wurin ya zauna, dama jiranshi suke yi, ya ce "wace magana za'a yi da Anty Sadiya kuma?"

Muhsin ya ce "Safwan akwai ka da gulma"

"Eh ba komai dai, a gaya mun"

Muhsin ne ya gaya mishi zancen da suke yi, Safwan ya ce "wai kai har yanzu dama ba ka daina zancen wannan Jewel ɗin ba"

Kallon mamaki Sadeeq ya bi shi da shi, kafin ya ce "in daina zancenta fa ka ce, Safwan kai kanka ka san tsawon shekarun da nayi ina son Jewel, kai tsaye sai ka ce in manta da ita? Saboda me?"

"Saboda kayi aure mana Tiger"

"Shikenan kuma dan nayi aure sai aka ce ba zan sake auren wata ba? Mata huɗu fa nake da ikon aura"

"Amma ai ba ka da ra'ayin auren ko da mata biyu ke bare kuma huɗu" cewar Safwan

"Zan iya sauya ra'ayi ai, in dai akan Jewel ne"

"Amma ka san idan ka auri Jewel za ka cutar da Sunaiha"

"Nima ta cutar da ni ai"

Safwan ya buɗe baki zai yi magana, Muhsin ya katse shi, "come on!! It's okay mana, ya isa haka, ni kun dame ni da magana ɗaya, sai na ga da Sunaiha da Jewel ɗin duk ɗaya ne"

Sadeeq ya ce "ba ɗaya ba ne, akwai banbanci"

Safwan ya ce "ka ji ko!? Wanda bai ɗauke su matsayin abu ɗaya ba, ta ya kake tunanin zai yi adalci?"

"Dama ai zai ji suna da banbanci a zuciyarshi, amma zai yi adalci" cewar Muhsin

Safwan ya ce "seems like har yanzu ba ka gama gane waye Tiger ba, amma...." Karar da wayarshi yayi ne ya katse shi

Ɗauka yayi bayan ya ga Kawu Karami ne, sai da suka gaisa kafin Kawu Karami ya ce "Safwan kuma tare da Sadeeq ne?"

"Eh Kawu" ya amsa

"Ba shi wayar"

Miƙa mishi yayi tare da gaya mishi ko waye, sallama Sadeeq yayi, Kawu Ƙarami ya ce "Sadeeq ina ka ajiye wayarka nake ta kiranka ba ka ɗaga ba?"

"Kayi haƙuri Kawu, wayar na mota ne"

"Allah ya shirya mun kai Sadeeq, tun ɗazu ake kiranka daga ɗayan asibitin akwai emergency ba ka ɗauka ba, sai da suka kira ni, ina nan ina da wani aiki a wannan asibitin, dole Dr Abbas na nema"

"Kayi haƙuri, ban san za'a samu emergency yanzu ba shiyasa, yanzu na bar asibitin ma"

Ƴar dariya Kawu yayi, ya ce "Sadeeq kenan, idan emergency ɗin zai samu gaya maka ake yi? Ai kwatsam yake zuwa, ka san yanayin aikinka, ka dinga ajiye wayarka a kusa"

"In sha Allah, zan kiyaye"

"Yawwa....yanzu ma duk ba wannan ba, Hajiya ce ta kira ni, wai jikin Baba (Grandpa) ya tashi, shi ne nake so ka je ka duba shi ka gani, yanzu akwai operation ɗin da za mu shiga"

"To, yanzu zan tafi" daga haka ya kashe wayar ya miƙe

Safwan ya ce "lafiya?"

"Jikin Grandpa ne ya tashi" ya faɗa yana miƙa mishi wayar

Miƙewa suka yi, Muhsin ya ce "Subhanallah...da sauƙi?"

"Ban sani ba gaskiya, sai na je zan gani"

"To mu tafi"

Murmushi Sadeeq yayi ya ce "a'a Muhsin, tun ɗazu mai martaba ya kira ka fa ka ce mishi kana zuwa, ya kamata ka tafi ka ji menene"

"I know it's nothing important, mu je in ga Grandpa"

Safwan ya ce "Muhsin kana gaya wa mutane su dinga bin iyayensu fa, yau kai ne mai martaba ya kira ka kayi jinkirin zuwa?... Kayi haƙuri ka tafi, ko menene zan kira ka"

Ssdeeq ya ce "zancen aure zai mishi ne shiyasa yake zillewa"

Dariya Safwan yayi ya ce "ka tafi, Allah ya sa kai ma irin na wani za'a yi maka"

Hararar Safwan suka yi kafin Sadeeq ya ce "ka ji da shi dai"

Daga haka suka wuce kowa ya shiga motarsa, Muhsin ya wuce fada, su Sadeeq suka nufi gidansu Grandpa. Tare suka shiga gidan da Safwan, Hajiya, Umma da Momi duk suna cikin parlourn, sai Grandma dake gefe, Grandpa kuwa na kwance kan kujera

Gaida su suka yi baki ɗaya kafin Sadeeq ya ƙarasa kusa da shi ya taɓa shi, jikinshi yayi zafi sosai, da ƙyar yake  iya buɗe ido, Sadeeq ya ce "kaii!! Haka jikinshi yayi zafi?"

Hajiya ta ce "haka muka same shu, mu ma Mama (Grandma) ta kira take gaya mana kuma nayi ta kiranka ba ka ɗaga ba"

Kallon Safwan yayi, ya ce "Safwan tayani ɗaga shi, sai mun tafi asibiti"

Kama shi suka yi zuwa motar Sadeeq, Safwan ya ja motar, su Hajiya kuwa Momi ta ja ta su motar. Kai tsaye asibitin su suka nufa, ba tare da ɓata lokaci ba aka yi admitting ɗinshi, Sadeeq ya shiga ya duba shi ya mishi allurar da ya kamata, ya sa mishi ruwa sannan ya fito, su Hajiya suka shiga

Fitarshi ke da wuya, sai ga Kawu, ya ce "Sadeeq ya jikin na shi?"

"Da sauƙi dai, amma BP ɗin shi ya hau sosai"

"How comes? Ya gaya mun ka sauya mishi magani, kuma na ga har da na BP, to amma ya aka yi bai rage ba sai ma ya hau?"

"Abu ɗaya ne Kawu, Grandpa ba ya son sha magani ko kaɗan, sannan magana nake kullum akan shan drinks ɗin nan amma ba ya ji, drinks ɗin nan suna da matsala sosai wallahi, har da shi ke ƙara mishi wannan ciwon ƙafan"

"To ai kai yana jin maganarka ma, kuma bai daina ba...amma ka san yanda za'a yi, yanzu mu barshi a nan, sai ka dinga kula da shan maganinshi kar a tsallake, sannan kar kowa ya kawo drinks asibitin nan, a hana shi sha, yayi ko da sayi ɗaya ne, sai mu ga wane canji za'a samu"

"Shikenan, in sha Allah zan yi haka"

"Bari in shiga in ganshi, Abbanku yana nan zuwa, amma kar ka kira Alhaji tun da ba ya ƙasar kar a ɗaga mishi hankali"

"To Kawu, bari in je office, zan cika wasu files"

"To" Kawu ya faɗa sannan ya shiga ɗakin, Sadeeq kuma ya wuce office

Ya kai mintuna goma yana aiki, sai ga Safwan ya shigo, bayani ya mishi akan abunda suka tattauna da Kawu, Safwan ya ce "wallahi matsalar Grandpa taurin kai, amma sau nawa ake cewa ya bari a kai shi abroad, ya ce a'a.....Allah ya ba shi lafiya to"

"Ameen, amma Grandpa idan ya tsaya kan magana ɗaya ba ya sauyawa"

"Halinku ɗaya ai, tun da ga shi ɗazu ka ƙara nuna mun"

"Hmm, Safwan ba za ka gane ba ne"

"Ai ba zan gane ba, yanzu dai dole dai ba za ka rabu da Jewel ba"

"Impossible"

Numfashi Safwan ya sauke ya ce "to yaushe za ka bayyana ta ɗin? Kayi wa Anty Sadiya magana, mu ma dai mu ganta kowa ya huta"

Murmushi yayi, ya ce "za ka ganta, amma yanzu ka ga ciwon Grandpa ɗin nan shi zai dakatar da ni, na fi so hankalin kowa yana wuri ɗaya sannan zan bayyana ta dan ta samu kula ta musamman, dan hak sai Grandpa ya warke zan bayyana ta"

"Wannan jan class ɗin dai yayi yawa, to Allah ya ba shi lafiya"

"Ameen" ya faɗa yana ci gaba da rubutun da yake yi

Sharif ya je wurin Sunaiha ya kai sau biyu, amma Najma sai yau ta zo, shi ma saboda Hajiyar London ta matsa mata, dan ita haushin zuwa gidan Sadeeq take ji

Suna zaune suna ta fira, Najma ta ce "wai Sunaiha ya mutumin naki? Ya sauya?"

"Hmm, Anty Najma kenan" abunda kawai ta faɗa kenan

"Bai sauya ba ko!? Wallahi Sunaiha kina ba ni mamaki, wai kyaun Sadeeq ne ke ruɗarki ko me? Sunaiha ban ga amfanin kyaun miji ba in dai ba zai daraja ki ba, kin ga miji me kyau da miji me kuɗi, wallahi aikin banza ne idan babu soyayya, duk kin wani sauya kamar ba ƳAR SENATOR ɗin da na sani ba!? Sunaiha, Najeeb yana sonki, ban san shi ba, ban taɓa ganinshi ba, amma wallahi daga kalaman shi zuciyata ke gaya mun shi ne mai sonki amma idonki ya rufe akan

wannan Prince ɗin...to wallahi bari in gaya miki gaskiya, rabuwa da Sadeeq shi ne alkhairi a wurinki, ki dawo wa mai sonki, kar ki yi biyu babu, kar lokacin da kika fahimci Sadeeq ba abokin rayuwarki ba ne, ko ya sake ki, ki zo kuma Najeeb ya haƙura da ke, wallahi you will regret it"

Tun da Najma ta fara magana, Sunaiha ke kallonta, tana so ta ɗauki zancen amma zuciyarta na hana ta, ita ta san ba za ta iya rayuwa da kowa ba idan ba Sadeeq, ta san tabbas Najeeb na sonta sosai, amma ita kuma tana son Sadeeq, hawaye ne ya biyo fuskarta

Anty Najma ta kalle ta, ta ce "Sunaiha kina wahalar da rayuwarki, na yarda Allah yana jarabtar bayinsa, kuma ya jarabce ki wallahi, dan ko a mafarki aka gaya mun za kiyi haka, zan ƙaryata, amma a matsayina na ƴar uwarki, ina gaya miki abunda zai amfane ki ne, amma yanzu so ya rufe miki ido ba za ki gane ba, sai dai ina so ko da rana ɗaya ne, ki natsu kiyi nazarin abunda na gaya miki, duk ranar da kika auri wanda yake sonki, to za ki gane wannan gidan a matsayin ƴar aiki kike, ba matar gida ba"

Daga haka ba ta sake ce mata komai ba, ita ma Sunaiha shiru tayi, suna a haka, aka danna door bell, ta je ta buɗe, Ikram ce, ta ji daɗin ganinta sosai, amma sai da suka zauna kafin ta ce "ai dama ba ki zo ba, ni kayi fushi"

Ikram ta ce " kin gani ko Sis Naj, sai da na gaya miki ko zuwa nayi ba za tayi appreciating ba"

Murmushi Najma tayi ta ce "na gani kuwa, ai saboda ni kika zo, ƙyale ta kawai"

Sunaiha ta ce "oh, kenan ma ba zuwa na ba ne"

"Eh, Sis Naj ce ta kira ni ta ce in zo, ai in dai saboda ke ne ba za ki ganni ba sai ranar da kika zo gidanmu" cewar Ikram

"To shikenan, ba komai"

Ikram ta ce "ni je ki kawo mun ruwa"

Harararta tayi, ta ce "Anty Najma ta ɗauko miki ai wurinta kika zo"

Suka yi dariya, Ikram ta ce "ai dai gidan ba baƙo na ba ne" sai ta miƙe ta je ɗaukowa

Najeeb na office tare da abokinshi, yake tambayarshi "wai Najeeb ina mutumiyarka?"

"Sunaiha?"

"Eh"

"Tana nan, meyasa ka tambaya?"

"Ina so ne in sani idan kayi hankalin ƙyale matar mutane ko kuma har yanzu kana bibiyarta"

"Bash kenan, ai duk abunda zai sa in ƙyale Cutie to ba ƙarami ba ne, musamman ma yanzu da nake ganin canji a tattare da ita"

"Ban gane ba"

"Yanzu fa idan na kirata, ta kan natsu ta saurare ni mu gaisa, wani lokacin ma sai ta saurari abunda nake faɗa kawai idan na gama ta kashe, saɓanin da, da idan na kira tana ɗauka za ta fara masifa sannan ta kashe ba tare da na ce komai ba"

"Lallai Najeeb...anya kuwa mijinta na sonta?"

"Meyasa ka ce haka?"

"A tunani na, ida mijinta yana sonta dole ne yana da lokacinta, idan yana da lokacinta dole wata rana zai ga kiranka a wayarta, amma kullum kan cin karenka ba babbaka!"

Dariya Najeeb yayi, ya ce "nima ban sani ba kam, amma dai na san tana matuƙar ƙaunarshi, sai dai zan cire wannan son na shi daga zuciyarta in sa nawa, kai ka san waye Najeeb"

Shi ma Bash dariyar yayi ya ce "tsab kuwa na san Najeeb musamman akan mace" suka sake yin dariya baki ɗaya

Sai bayan sallar isha'i sannan Tiger ya dawo gida, tana zaune a parlour ita kaɗai, sallama kawai yayi ya wuce ciki ba tare da ya kalle ta ba bare kuma ya amsa gaisuwarta, ya shiga ɗaki

Bai tsaya ɓata lokaci ba ya faɗa toilet saboda jikinshi ba daɗi, yau yayi aiki sosai a asibiti, gaba ɗaya a gajiye yake, wanka yayi sannan ya fito ya bi jikinshi da body sprays, ko mai ya kasa shafa wa, ya koma bakin gado ya zauna, sannan ya jawo drawer ya ɗauko hoton Jewel ɗin shi yana kallo, abubuwa da yawa ne ke zuwa mishi a rai akanta, a hankali yake fitar da wani kyakkyawan murmushi, ya kai tsawon minti goma sha biyar, sannan ya iya mayar da hoton ya tashi ya dawo parlourn ya zauna

Sunaiha na ganinshi ta je ta ɗauko mishi abinci ta ajiye, sannan ta fuskance shi, ta ce "sannu da aiki"

"Yawwa" ya amsa yana duba wayarshi

Girgiza kai tayi kafin ta ce "yau ba ka dawo da rana ba, lafiya?"

"Aiki nake yi" ya sake amsa mata a gajarce

"Aiki kuma?"

Ya ce "um"

"Amma ai na kira ka, meyasa ba ka ɗaga kira na ba?"

"Ba na kusa"

"To meyasa ba ka kir...."

A tsawace ya katse ta "Haba mana dan Allah!!! Wai yaushe kika fara aikin jarida ne? Waɗannan tambayoyin sun ishe ni"

Ta razana sosai, hakan ya sa tayi shiru, sai da ya ci gaba da danna wayarshi kafin cikin sanyin murya ta ce "Amma laifi ne dan na tambaye ka? Ni fa matarka ce"

Wani kallo ya mata, ya ce "Au haba!!? Haka ne kuma, na manta ai....ji wani bakinta, wai mata, mtsww" yayi tsaki

Ƙoƙarin mayar a hawayenta tayi, ta ce "na sani ai, ba sai ka faɗa ba, ba ka taɓa kallo na a matsayin matarka ba ko? Ka fi son Princess Jewel fiye da ni, i already knew it"

"Good" ya faɗa yana kallon cikin idonta, "it's better da kika fahimci haka da kanki, yanzu kin fara gane matsayin Jewel kenan"

Numfashi ta sauke mai cike da takaici, ta ce "Hmmm, Ya Sadeeq kenan, Allah ya ganar da kai mai sonka da gaskiya kafin lokaci ya ƙure maka"

Sake kallonta yayi, ya ce "what do you mean?"

"I mean nothing" ta miƙe kawai za ta wuce

Ya ce "for your own information, Grandpa ba ya jin daɗi, yana asibiti, da safe idan kin ji za ki iya, ki shirya mu tafi ki ganshi, idan kuma ba za ki iya ba, it's your own cup of tea"

Ba tare da ta ce mishi komai ba ta wuce ciki, tana shiga ta faɗa kan gado tana kuka, gaba ɗaya ta kasa gane kan Sadeeq, shi sam a rayuwarshi bai san kyautatawa bane ko me? Duk abunda za tayi laifi ne a wurinshi? Nan kalaman Najma suka fara dawowa kunnenta, ta rasa wa za ta saurara, kalaman Anty Najma ko kuma zuciyarta? Haka kawai ta tsinci kanta da rokon Allah ya

sa Najeeb ya kirata ko ya turo mata da saƙo, wataƙila idan ta ji kalaman shi za ta ji sassauci, amma har bacci yayi awon gaba da ita, yau Najeeb ba kira ba saƙo tun na safe da yayi........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Do not judge a person by their looks or the things they have. You do not love some one for their appearance or their nice cloths but because of their personality, their thoughts, their mind and most importantly for their heart and soul._

*PAGE 53-54*
~~~~~~~~~~~~~~~~

Washe gari kusan lokaci ɗaya suka gama shiri, ba ɓata lokaci suka nufi asibitin. Office ɗin shi suka fara shiga, ya zauna ya fara aikin da zai yi, tana zaune gefe tana kallonshi

Da sallama Dr Suhail ya shigo office ɗin, sai da suka gaisa kafin Tiger ya ce "Ya patients ɗin da aka kwana da su?"

"Na duba su ɗazu da asuba, da sauƙi gaba ɗayansu, sai dai wannan mutumin da ke ward C, ina tunanin sai ka duba shi da kanka, dan da ƙyar muka kai safe"

Girgiza kai yayi ya ce "mutanenmu suna ba ni mamaki wallahi, idan mutum ba ya da lafiya ba za'a kawo shi asibiti da wuri ba sai ciwo yayi tsanani ya zo yayi ta wahala"

"Bari kawai, kullum ana wayar da kai amma a banza, Allah dai ya ƙara mana lafiya baki ɗaya"

"Ameen...bari in ƙarasa wannan aikin sai in fita gaba ɗaya, jiya na gaji ne wallahi kuma jiya ya kamata a ce na kammala shiyasa ko wurin Grandpa ban biya ba na zo nan...ya jikin na shi?"

"Shi ma da sauƙi, sai dai har yanzu BP ɗin na shi bai dawo normal ba, amma ya sauka ba kamar jiya ba"

"Ka ba shi magani?"

"Eh na ba shi ɗazu"

"Abinci fa?"

"Ya sha tea da asuba ɗin dai"

"To shikenan ba damuwa, a hankali zai sauka"

"Allah ya sa"

"Ameen" ya ci gaba da abunda yake yi

Juyawa Dr Suhail yayi zai fita, sai a lokacin ya tuna ya ga Sunaiha, surutun da Tiger ke mishi ne ya sa shi mantawa, sai ya ce "Oga wannan fa?"

Ba tare da ya kalle shi ba,  ya ce "she's part of our family"

"Allah sarki" cewar Suhail, ya kalli Sunaiha ya ce "shi ne kika biyo shi nan, ai da kin tafi wurin Grandpa ɗin, Sauban da Sameer suna can, ko in raka ki?"

Ɗan murmushi tayi ta girgiza kai, ta ce "a'a, zan jira shi"

Ƴar dariya yayi ya ce "ba fa sace ki zan yi ba, ki zo in raka ki"

"A'a na gode, ba komai"

"Ikon Allah, tsoron mutane kike ji ne? Raka ki zan yi kin ga ma har fira zan taya ki, ya fi wannan zaman shirun da kike yi"

Kafin Sunaiha tayi magana, Tiger ya daka mishi wata tsawa, "Suhail!!! Back to your senses, she's my wife"

Ba Suhail ba, har Sunaiha tayi mamakin jin ya kirata da matarshi, ta ji daɗi sosai a ranta amma a fuska ba ta nuna ba, Suhail ya ce "i'm so sorry Sir, wallahi ban san matarka ba ce, na ji ka ce she's part of your family ne"

Cikin bacin rai Sadeeq ya ce "is she your own family?? Idan ban ce wa matata family ɗin gidanmu ba, na gidanku zan ce?"

Suhail ya san Sadeeq yana da faɗa wani lokacin, amma bai taɓa mishi magana irin haka ba, ya ce "kayi haƙuri, in sha Allah ba zan sake ba...i'm so sorry Madam" ya ƙarasa yana kallon Sunaiha

Ɗan murmushi tayi ta ce "ba komai" daga haka ya bar office ɗin

Sunaiha sai wani kallon Sadeeq take saboda ya bata mamaki, ɗaga ido yayi ya ga yanda take ta kallonshi, ya ce "ya dai!? Bin shi za kiyi?"

Girgiza mishi kai kawai tayi, ya ce "ki ma bi shi ɗin" ya faɗa yana mata wani kallo kafin ya ci gaba da aikinshi. Bai fi mintuna goma ba ya miƙe, ya ce "tashi mu tafi"

Ba musu ta miƙe, sai ga wata nurse ta shigo da sallama, cikin girmamawa ta gaida shi ya amsa, ta ce "Sir, wannan patient ɗin na ward C fa ya kamata ka zo ka ga halin da yake ciki"

"Wai har yanzu? I thought da sauƙi ne ai"

"Da sauƙi ɗazu, yanzu kuma jikin ya sake rikicewa"

"Oh Allah, shikenan gani nan zuwa"

Sai a lokacin ta kalli Sunaiha ta ce "sannu Matar Oga"

Murmushi tayi ba tare da ta ce komai ba, kallonta Sadeeq yayi ya ce "kin san ta ne?"

"A'a, Anty Sameera na ga ta ɗora hoton bikin a status, ka san lokacin da aka yi ba na gari"

Bai ce mata komai ba ya koma ɗaukar wayarshi, ta kalli Sunaiha ta ce "Congrats Amarya, gaskiya kin yi sa'ar samun miji irin Dr Sadeeq, duk wata mace mai hankali za tayi burin samunshi a matsayin abokin rayuwarta...shi ma yayi dacen mace kyakkyawa, kuma da alama kina da natsuwa abunki, you're such a perfect couples...Allah ya nuna mana yaranku"

Sadeeq da ke tsaye bayan Sunaiha yana ta kallon Nurse ɗin tana zuba kamar ƴaƴan kanya, ya ce "Malama idan kin gama mu tafi ko! Surutu kamar wata aku"

Dariya tayi ta ce "i'm sorry, amma faɗar gaskiya ai dole ne" tana gama faɗar haka ta juya ta fita, shi ma ya bi bayanta sannan Sunaiha, tafiya suke amma tunani kawai take yi

Har suka ƙarasa ɗakin da Grandpa yake, ya nuna mata ɗakin ya ce "ki shiga, ina zuwa" bai jira cewarta ba suka wuce shi da Nurse ɗin

Da sallama ta shiga ɗakin, Sauban da Sameer ne kawai a ciki, Grandpa na kwance da alama bacci yake yi, gaisawa suka yi da Sameer, sannan Sauban ya gaishe ta, ta amsa mishi da fara'a a fuskarta

Sunaiha ta ce "ya jikin Grandpa?"

Sameer ya ce "da sauƙi alhamdulillah"

"Allah ya ƙara mishi lafiya"

"Ameen" suka amsa tare

Sameer ya ce "tare da Oga Tiger ku ka zo?"

Ta ce "eh, ya je ya dawo"

Sauban ya ce "ai kai ma tun da ka ganta yanzu da safen nan ka san aikin Ya Tiger ne, madadin ya bari ta ɗan huta zuwa tara ko goma ta zo, amma ya ɗauko ta"

Dariya Sameer yayi, ya ce "ya fi son ƙafarsa, ƙafarta"

Ɗan murmushi tayi wanda yanzu ya zame mata jiki, ta ce "ku kaɗai ne?"

Sauban ya ce "eh, amma yanzu muka yi waya da su Umma, ta ce suna hanya"

"Allah ya kawo su lafiya, su Anty Sadiya fa da Nasreen?"

"Su ma na san suna nan zuwa"

Jinjina kai tayi ta ɗauki wayarta ta ci gaba da chatting, kusan mintuna goma sha biyar sai ga su Umma sun shigo tare da Tiger, nan suka tsaya gaisawa, Tiger kuwa ya wuce duba Grandpa dake ta bacci har yanzu, Sauban da Sameer kuwa suka wuce gida

Suna nan, Anty Sadiya ta fara isowa da sauran ƙannensu, kafin daga bisani Anty Saudat da Anty Sameera suka zo

Haka suka yi ta zaman asibitin suna fira, Tiger yakan shigo ya duba shi jifa-jifa, kasancewar VIP ward yake, babban ɗaki ne sosai, yana da Cushion daga can gefe, bayan arm chairs guda biyu da folding chair guda biyu, hakan ya sa kusan group uku suka yi a ɗakin, suna ta fira sai dai ba sa takura wa kowa dan ba hayaniya suke yi ba

Anty Sameera, Anty Sadiya, Nasreen da Sunaiha wuri ɗaya suka zauna, Anty Sadiya ta miƙe ta kalli Salma da Sultana, ta ce "ku zo nan" sai kawai ta fita

Bin bayanta suka yi har zuwa reception, suka samu wuri suka zauna, ta ce "Salma"

"Na'am"

"Sultana"

Ita ta amsa "Na'am"

"Wai sai yashe za kuyi hankali?"

Kallon juna suka yi, kafin Salma ta ce "Anty Sadiya me muka yi?"

"Yanzu a tunaninku abunda kuke yi wa Sunaiha kuna kyautawa? Ku manta da cewar matar Yayanku ce, ita musulma ce, kuma aƙalla ba ta ku shekara ko da ɗaya da rabi ne, kuma tana ƙoƙarin ganin ta kyautata muku, amma ba kwa da aiki sai na mata rashin kunya yanda ku ka ga dama!? Haba dan Allah"

Sultana ta ce "Anty Sadiya kenan kin manta ita abunda tayi mana?"

"Ina sane ban manta ba, amma wannan ai ya wuce, kuma idan ku ka lura yanzu tayi nadamar halayenta na baya, yanzu ta sauya sosai ba kamar waccan Sunaihar da ku ka sani ba ce....duk wanda ya san Saraki's Family ya san ba mutane bane masu wulaƙanta ɗan adam, amma ku yanzu me kenan kuke yi wa matar Yayanku? Kuna so ku ɓata mana suna ne ko me?...yanzu yanda kuka gaida ita da yanda kuka gaida Nasreen akwai banbanci, kuma duk matsayinsu ɗaya idan kuna da hankali"

Salma ta ce "Anty Sadiya...."

Dakatar da ita tayi, ta ce "ban son jin komai, ina so ku ƙaddara ku ne a matsayin ta, sai ƴan uwan mazajenku suna muku irin haka, how will you feel? Duk abunda za kayi wa mutum, ka dinga sa kanka a matsayin sa ka ji yanda kai za ka ji abun, kafin ka aikata...na gaya muku she has changed alot kuma wallahi idan ku ka saki jiki da ita kamar yanda ku ka yi da Nasreen, ina tabbata muku sai kun fi jin daɗin zama da ita akan ita Nasreen ɗin, sannan yanzu idan Abba ya ji irin zama da kuke yi da ita zai ji daɗi ne?"

Shiru suka yi ba wanda ya iya cewa komai, ta ce "ni ban ce dole sai kun sauya mata ba, amma shawara ce na baki, kuyi tunani da kanku" tana gama faɗar hakan ta miƙe ta wuce ya bar su wurin

Numfashi Salma ta sauke ta ce "Sultana gaskiya fa Anty Sadiya ta gaya mana, wallahi idan mu ne ake wa haka kin san ba za mu ji daɗi ba, sannan ba Abba ba, ko su Hajiya ko Grandpa suka samu labarin haka, wallahi sai mun faɗi wanda ya aike mu"

Ɗan rufe ido Sultana tayi ta ce "haka ne, ni fa kin san me Salma, tun ranar da na fara ganinta wallahi kawai na ji ina sonta, amma yanda ta mana ne ya ɓata mun rai wanda har yanzu idan na tuna haushi nake ji...amma tunda har Anty Sadiya ta ce ta sauya halayenta, mu gwada shiryawa da ita mu gani, ko ya kika ce?"

"Haka ne, in sha Allah daa yau za mu koma normal da ita" shiru suka yi na ƴan mintuna sannan suka koma ciki

Sai da yamma, sannan manyan suka bar asibitin, ya rage daga Sultana sai Salma sai Sajeeda, Sunaiha da Nasreen, kasancewar ita ma Safwan ya ce ta jira idan ya sake dawowa, sai su wuce tare, jikin Grandpa da sauƙi sosai, har ya samu yayi fira ɗazu, sai ai yanzu ya koma bacci

Fira suke su biyar gwanin burgewa, Sunaiha tayi matuƙar mamakin yanda su Salma suka sake mata, ta ji daɗi sosai hakan ya sa ita ma ta saki jiki da su. Sai da suka yi sallar Magrib kafin Safwan ya shigo ɗakin tare da Sadeeq, gaida Grandpa suka yi tare da tambayarshi jikinshi, wanda idar da sallarsa kenan

Kallon Sadeeq yake yana murmushi, ya ce "ai in dai ina ƙarƙashin kulawar Sadeeq, jikina zai dinga yin sauƙi ne da taimakon Ubangiji"

Murmushi suka yi gaba ɗaya, Safwan ya ce "ai in da ni ne Dr ɗin ma, ina gaya maka ko asibitin nan ba za ka zo ba sai dai ƙaddara"

Dariya ya ba su yanayin yanda yayi maganar, Salma ta ce "ai da sauƙi Ya Safwan tun da ka san ƙaddara ce za ta iya kawo shi asibiti, to yanzu ma ƙaddarar ce"

Grandpa ya ce "na dai gode miki Amarya, wani lokacin kina da hankali kaɗan, amma kin fi waccan mai idanun mujiya" ya ƙarasa yana kallon Sultana da ke kusa a Sunaiha

Shagwaɓe fuska tayi ta ce "ni ce mai idanun mujiya yau kuma?"

"Eh mana, Amarya Salma ta fi ki hankali ke da wannan yayan na ki, Safwan"

Juyawa tayi ta kalli Sunaiha, ta ce "Anty Sunaiha dan Allah ni da Salamatu wa ya fi hankali?"

Murmushi tayi ta ce "gaba ɗaya kuna da hankali ai Sultana"

Salma ta ce "Anty Nasreen ki gaya mata ta daina kira na Salamatu" ta faɗa tana kallon Nasreen

Nasreen ta ce "Salma sunanta ba Salamatu ba, ki kiyaye, kin ji ko Sultana"

Sunaiha ta ce "a'a Nasreen, kar ki buɗe mata ido fa, ai Salamatu shi ne sunanta, Salma kawai gayu ne"

Ƙara kwaɓe fuska Salma tayi ta ce "Grandpa kana jin matan nan ko"

Dariya yayi, ya ce "idan na biye ku ai sai kun ƙara mun ciwo, amma ga Safwan nan"

Safwan ya ce "wannan hukuncin ai sai Tiger"

Kallonsu kawai yayi, yayi murmushi ya ce "Grandpa ga maganinka, ka sha ka kwanta zai fi" ya faɗa yana miƙa mishi magani

Safwan ya ce "To shikenan, Grandpa Allah ya ƙara sauƙi, mu bari mu tafi, ina so zan kai Nasreen gidan su, may be zan dawo zuwa dare"

"To, Allah ya kiyaye, Nasreen ki gaida mutanen gida" cewar Grandpa

Daga haka ya suka fita, Sadeeq shi ma ya wuce ya zagaya sauran patients ɗin, ya rage daga Sunaiha sai su Salma, zaman asibitin ya ishe ta, amma dole ta zauna tun da Oga Tiger bai ba ta izinin tafiya ba

Kusan ƙarfe shida da rabi, sai ga su Hajiya sun sake dawowa su huɗu, tare da Sarah, su za su zauna kuma har sai dare idan su Sameer sun zo. Zama suka yi suka gaisa,Grandpa ya sake samun bacci, Sunaiha daga gaisawar da suka yi da Sarah, ba ta sake magana ba saboda haushinta take ji

Hajiya ta ce "wai Sunaiha dawowa kika yi? Ba ki zauna ki huta ba?"

Kafin tayi magana Salma ta ce "ai tun ɗazu ma ba ta koma gida ba"

Umma ta ce "kar dai Sadeeq yana nufin da gaske kuwa yake yi tare za ku koma?"

Hajiya ta ce "ƙaramin aikin Sadeeq ne wallahi, wannan ai ya wahalar da ita ne, tun safe har yanzu!?"

Sunaiha ta ce "a'a Hajiya, ba komai ai, ban gaji ba"

"Dama ta ya za ki ce kin gaji tunda zaman dole ne kike yi...zai shigo ya same ni ai" cewar Umma cikin ɓacin rai

Hajiya ta ce "a'a, kin ga ki bari zan mishi magana cikin natsuwa"

"Ke kike lalata shi ai, dai ki ce ba za'a yi mishi faɗa ba"

Momi dai na jinsu ya ƙyale su, wayar Sarah ce tayi ƙara, sai kawai ta tashi ta fita. Sun daɗe a zaune har aka fara kiran sallar magrib, suka shiga toilet suka fara alwala, suka yi sallah, amma Sadeeq bai shigo ba, Hajiya ta ce "Sultana je ki duba mun Sadeeq, ki kira mun shi, ke kuma Sunaiha ki zuba abinci ki ci karin ya zo ku wuce"

"A'a Hajiya, na ƙoshi ai, ba mu jima da muka ci ba"

Hajiya ta ce "na fahimci ba kya son cin abinci, ko dai na mu ne ba kya so ban sani ba....wai Sultana ba aikenki nayi ba!?" Ta ƙarasa tana kallon Sunaiha da ko motsawa ba tayi ba

Sunaiha ta ce "Hajiya bari Salma ta idar da sallah ta je, kin san wallahi ba son zagayen asibiti nake yi ba"

"Hmm, Allah ya shirye ki...Sunaiha tun da ba za ki ci abincin ba, je ki kira mun mijinki"

Kai a ƙasa ta miƙe ta fita, a hankali take tafiya har ta kai bakin ƙofar office ɗin, ta kai hannu za ta buɗe sai ta ji muryar Sadeeq yana cewa "to ai ke ma duk wanda ya same ki yayi sa'a, saboda kina da hankali, da natsuwa"

Mamaki take da wa Sadeeq ke fira kuma? Sai ta jiyo muryar Sarah tana faɗin "na ji, amma ba zai kai wacce ta same ka sa'a ba"

"Haka dai kike gani, amma ina tabbata miki da ace kin yi confessing love ɗinki tun kafin in ga Jewel har in fara sonta, to tabbas da zan iya aurenki, amma yanzu lokaci ya ƙure"

Murmushi tayi ta ce "wai wannan Jewel ɗin wane irin matsayi take da shi da har ya sa ba na jin

kana magana akan Sunaiha ita da take matarka, sai dai Jewel, always"

Wani ƙayataccen murmushi yayi, sannan ya ce "ina so ki sa a ranki cewa, duk lokacin da kika ji na ce Sunaiha, to ki ɗauka mace ce wacce matsayinta ya kai a kira ta da Matar Sadeeq ko Matar Tiger, wacce kowa ya santa, kowa zai iya faɗar maganar da ya ga dama akanta, it's left to me, ko in ɗauka ko in watsar, amma idan na ce Jewel, to ki sa a ranki wannan macen, ita ce kaɗai wacce ta mallaki komai na Sadeeq, ta mallaki zuciyarsa gaba ɗaya, ta mallaki hankalinsa, tunaninsa, natsuwarsa, ta mallaki Sadeeq ɗin ma baki ɗaya, i can be call a Tiger, amma a gaban Jewel, i'm nothing rather than a little cat that can be control so easily by her, kuma ba kowa ya santa ba, amma very soon zan bayyana ta, so ko bayan na bayyana ta ɗin, duk abunda za'a gaya mun a kanta ko kunne na ba zai shiga ba, bare in yi shawarar ɗauka ko watsarwa, I so much love her"

Sosai Sarah ke kallonshi dan ya ba ta mamaki matuƙa, irin wannan so haka? A ranta take cewa" wai har haka yake son wannan Jewel ɗin amma shi ne ta je tayi aurenta? Allah sarki Sadeeq, ina tausayin ranar da za ka ji labarin tayi aure ita ma, you'll be shattered, amma i won't let that happen, i'll make sure to keep you happy dear, shiyasa na dawo rayuwarka"

A zahiri kuma murmushi tayi ta ce "tab, lallai Jewel ta ciri tuta"

Kafin Sadeeq yayi magana, Sunaiha ta turo ƙofa wacce idanunta suka cika tab da hawaye, duk da cewar ta share hawayen kafin ta turo ƙofar, amma hakan bai hana wasu hawayen zubowa ba

Ko kallon cikin idanunshi ba tayi ba, ta ce "Hajiya na kiranka" sai kawai ta juya ta fita

Sarah ta kalle shi, sai ta ga ya miƙe ya fita ba tare da ya ce mata komai ba. Sauri Sunaiha ke yi, yana bayanta amma akwai tazara sosai a tsakaninsu, maimakon ta shiga ɗakin sai ta miƙe tayi bayan ɗakunan ta zauna

Lokacin da Sadeeq ya ƙarasa ɗakin yayi tsammanin ta shiga, sai bai ganta ba, ya ce "Hajiya ga ni, ko jikin Grandpa ne?"

"Wane jikin Grandpa kuma? Ashe ba Ummanku ta ce ka kai yarinyar nan gida ba tun ɗazu?" Cewar Hajiya

"Kuyi haƙuri wallahi aiki ne ya hana ni kai ta"

Umma ta ce "ai ba dole sai kai ba, ka tura wani ya kai ta mana, ba akwai drivers ba, ko ka kira Sameer ko Sauban, kuma ga su Salma nan, idan ma duk hakan bai maka ba, ka bata makullin ta tafi da kanta"

"Maa, i'm so sorry, yanzu zan kai ta, kiyi haƙuri"

Hajiya ta ce "Sunaiha ɗin fa?"

Abunda yake so ya tambaye ta kenan sai ta riga shi, yana nazarin abunda zai ce, sai ga ta, ta turo ƙofar, Umma ta ce "yawwa, Sunaiha zo ki tafi gida haka nan ke ma ki huta kin ji, kiyi haƙuri, Allah ya miki albarka"

Ƙirƙirar murmushi tayi ta ce "ameen Umma, ba komai ai"

Sallama tayi da Hajiya da Momi, Salma da Sultana suka miƙe za su raka ta, Sadeeq ya fara fita sannan suka bi bayanshi, a bakin mota suka yi sallama da ita sannan suka koma cikin asibitin, Ssdeeq kuma ya ja motar suka wuce

Tun da suka fara tafiya take share hawayenta a hankali saboda ba ta so ya lura da kuka take yi, ita kanta ba son kukan take yi ba, amma ba ta sanin lokacin da hawayen ke zuba musamman idan ta tuna maganganunsa, sai dai ba ta san Tiger na lura da ita ba, ƙyale ta kawai yayi

Har sai da suka kai bakin gate ɗin gidan, ya tsayar da motar, sannan ya kalle ta, ya ce "lafiya?"

Ba tare da ta kalle shi ba, ta ce "me ka gani?"

"Kin fi ni sani ai, ba ki so dawowa bane ko me?"

Numfashi ta sauke a hankali, ta ce "i'm ok... unlock the door, ina so zan fita"

Shi ma numfashin ya sauke, ya ce "well! Nima I'll never be ok idan na ci gaba da kallonki a nan...zan koma dan ban ƙarasa aiki na ba aka taso ni, sai na dawo" ya faɗa sannan yayi unlocking ƙofar

Sai da ta buɗe kafin ta ce "you can sleep there if you wish" ita kanta ba ta san maganar ta fito ba, ta fita ta rufe mishi ƙofar sannan ta shige cikin gida

Shiru yayi yana so ya gane idan abunda kunnuwansa suka ji haka ta faɗa, ɗan ƙaramin tsaki yayi, ya tada motar yana faɗin "she can't say that, ban ji da kyau ba ne may be" ya  ba motar wuta sannan ya wuce.........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_A Pure heart person can have a wonderful smile that even make his Enemy to feel Guilty for being his enemy. Keep smiling forever….._

*PAGE 55-56*

Sunaiha kuwa tana shiga cikin gidan, parlour ta zauna, duk yanda ta so kar ta tuna komai daga abunda Sadeeq ya faɗa, hakan bai yiwu ba, saboda ji take kamar yanzu ke ma yake maganar

Kuka take yi sosai, ta ce "Astaghfirullah, Astaghfirullah, Astaghfirullah...Ya Allah na san na saɓa maka a baya wataƙila shiyasa ka hukunta ni ta hanyar son wannan mutumin, Ya Allah kai shaida ke akan irin haƙurin da nayi da shi, kuma ka san irin son da nake mishi, Ya Allah ka bani ladar wannan jarabawar Ya Allah...Amma na gaji, na gaji wallahi, Prince dole zan haƙura da kai ko da kuwa hakan shi zai yi sanadiyar mutuwa ta, na gwammaci rabuwa da kai a halin yanzu
~~~~~~~~~~~~~~~~

saboda ka samu peace of mind, nima ka daina zubar mun da girma haka nan, ka je ka auri Jewel ɗin, nima in auri wanda yake so na ba wai dan ina son shi ba, kai kaɗai nake so Prince, tun ban sanka ba a zahiri nake matuƙar sonka, kuma har yanzu ina sonka, and i'll love you till eternity" ta sake fashewa da wani kukan, abun tausayi

Ta ɗauki tsawon lokaci tana kukanta kafin ta miƙe ta shiga ɗaki, wanka tayi ta fito tayi sallar isha'i sannan tayi kwanciyarta, ba ta damu ta ci abinci ba

A asibiti kuwa, sai ƙarfe tara sannan su Sauban suka zo asibitin, Grandpa ya takurawa Sadeeq akan ya wuce gida sabida ya bar matarsa ita kaɗai, haka ya musu sallama

Hajiya ta ce "Sadeeq ka wuce mana da su Salma gida saboda mu ba yanzu ba sai kamar ƙarfe goma"

Tiger ya ce "goma kuma?  Bayan ga su Sauban me za kuyi kuma?"

Grandma ta ce "ni ce ban ga damar tafiya yanzu ba"

Murmushi kawai yayi, Sultana ta ce "wai tsohuwa ta san daɗin miji,  to bari in gaya miki ko nan kika kwana dai mu yake yayi yanzu,  ke kin yi condemn"

Umma ta ce "yarinyar nan ba kya da ta ido wallahi, yanzu a gabanmu kike cewa uwarmu tayi condemn?"

Momi ta ce "ai Sultana kam Allah dai ya shirye ta"

Ta amsa da "ameen" tana dariya

Grandma ta ce "idan na zubar miki da haƙori ai za ki gane,  masu ƙwacen miji kawai,  kar ku fitar da mazajenku,  ku bari sai sun ƙare ku koma auren na mutane"

Salma ta ce "ka ji mun matar nan"

Sultana ta ce "ƙyale ta, mu mazajen mu in gaya miki ba ma ƴan Nigeria bane"

Hajiya ta buɗe baki,  ta ce "ashe ba ku da kunya ban sani ba? "

Sameer ya ce "Hajiya ai ke ce kike tunanin yaran nan suna da kunya... Za ku wuce ne ko kuwa? " ya ƙarasa yana yi ma Sultana wani kallo mai kama da harara

Sadeeq dake ƙara auna BP ɗin Grandpa ya ce "Sameer ƙyale su, idan ku ka bari na gama kuna ɗakin nan sai na ɓalla ku"

Kafin ma ya ƙarasa rufe baki har sun fita,  yana gamawa ya ƙara musu sallama sannan ya fita. A bakin mota ya tarar da su suna jiransa, buɗewa yayi,  Salma ta shiga gaba,  Sultana kuma baya,  sai da suka ɗauki hanya kafin Salma ta ce  "Ya Tiger ka san me? "

Ba tare da ya kalle ta ba ya ce "um um"

"Wallahi ban taɓa tsammanin zan ji daɗin zama da Anty Sunaiha ba sai yau"

A hankali ya kalle ta,  ya ce "ban fahimta ba"

"Ka san fa tun aurenku ba mu taɓa tsayawa yin wani dogon fira da ita ba saboda halayyenta na jin kai,  amma yau ka ga irin yanda ta sake mana muka yi ta fira,  sai na ji ta masifar shiga raina"

Sultana ta ce "wallahi kuwa Ya Sadeeq,  yanzu Anty Sunaiha ba ruwanta, ta ajiye wannan jin kan nata,  sai ka ga yanda muka yi da ita yau, i really like her for sure"

Ba abunda yq ce musu,  kamar ma ba da shi suke magana ba, wani tunanin ne a ranshi na daban, Salma ta kalle shi,  ta ce "Ya Sadeeq stop thinking, kai ma ka bata fuska ko kaɗan ne, za ka ga abunda muke gaya maka, ta gyara halayenta sosai, saboda akwai ranar da na ji Anty Sadiya tana magana a waya tana cewa har yau ba ka sake wa Anty Sunaiha fuska ba saboda ba ka sonta, amma ina ji a jikina idan ka ba ta chance za ku ji daɗin zama da juna"

Har yanzu ba abunda ya ce mata,  hakan ya sa tayi shiru saboda ta san idan ta ci gaba sai iya mata faɗa,  shirun da yayi ya nuna mata bai da ra'ayin zancen,  ita kanta Sultana ta so tayi magana su yi convincing ɗin shi, amma ganin Salma tayi shiru ya sa ita ma ta kama bakinta. Suna kai wa bakin gate,  ya tsayar da motar, har za su fita, ya kira sunan Salma,  gaba ɗaya suka tsaya

"Ku ka ce kuna son Sunaiha? "

Salma ta ce "Ya Sadeeq ai Anty Sunaiha mace ce da duk wanda ya ganta dole zai so ta, duk wanda za ka ji ya ce ba ya sonta, to tabbas halayenta ne ba ya so ba wai ita ba, amma yanzu ta sauya"

"Yanzu for example, idan  na ce ki zaɓa ɗaya tsakanin Sunaiha da Jewel,  wa za ki ɗauka?"

"Ni da ban san Jewel ba Ya Sadeeq me zai sa in zaɓe ta? Anty Sunaiha zan ɗauka"

Kallon Sultana yayi ya ce "ke fa?"

"Ya Tiger kai kaɗai ka san wannan Jewel ɗin fa, nima as she said, Anty Sunaiha nake so"

Shiru yayi kafin ya sauke numfashi,  ya ce "good night"

Kallonshi suka yi,  Salma ta kalli Sultana, sannan ta sake kallonshi ta ce "Ya Sadeeq ba wai ba ma son Jewel ba ne fa, kawai dai wacce muka sani ita muka zaɓa,  amma yaushe za ka nuna mana Jewel ɗin sai mu sake tantancewa?"

Ɗan murmushi yayi saboda ya gane dalilin da yasa ta ce haka,  ya ce "idan Grandpa ya ji sauƙi, zan nuna muku ita"

Sultana ta ce "Allah ya ba shi lafiya to,  can't wait to see this Princess Jewel da ta ɗauke zuciyar Oga Tiger,  ta ƙi bari Antyn mu ta ji daɗi"

Yana kallonta kawai ta buɗe motar da sauri ta fita,  Salma tayi dariya sannan ita ma ta fita bayan ta mishi sai da safe, sai da ya kusan minti biyar sannan ya wuce

Ko bayan da ya je gida, bai damu ya duba ta ba, wanka yayi, yayi shirin kwanciya shi ma bayan ya sha coffee

Washe gari ma yana gama shiri tsaf, ya fita ba tare da ya jira ta ba,  ita ma yau da gangan ta ƙi fitowa har sai da ya wuce sannan ta fito ta gyara gidan tayi wanka ta haɗa wa kanta breakfast, kafin ta zauna

Kiran Najeeb ne ya shigo wayarta, ɗagawa tayi suka gaisa kafin ta ce "Najeeb kwana biyu"

Mamaki yayi sosai, kenan ta damu da kiran da yake mata shiyasa har taje tambayarsa?, ya ce "aiki ne, kwana biyu nayi tafiya jiya na dawo,  amma kiyi haƙuri"

Murmushi tayi ta ce "Allah ya taimaka"

"Ameen Cutie,  ya Prince"

Shiru tayi kafin ta ce "yana lafiya"

"Ki gaishe shi,  although ya ƙwace mun ke"

"Yau ka yarda ya ƙwace ni ɗin kenan? Na ga kai ke cewa har yanzu kana ji a jikinka sai na dawo gare ka"

"Har kullum ma haka nake ji Cutie"

"Yanzu misali,  idan na rabu da Prince, za ka iya aure na? "

"That's what i've been waiting for, za ki rabu da shi kenan? "

"Stop decieving yourself,  misali na ce ai, kai kana tunanin zan iya rabuwa da Prince ɗina ne?"

Murmushi yayi ya ce "shikenan to, i'll keep waitimg saboda na san zuciya ta ba za ta mun ƙarya akan ki ba"

"Fine then, sai anjima"

"Tnx" ya faɗa sannan suka kashe wayar

Haka kawai ta tsinci kanta da zubar da hawaye, sharewa tayi ta sauke numfashi ta ce "despite all i've done to him, he still have hope, amma Prince har yau ya kasa gane irin son da nake mishi... Ya Allah ka zaɓa mun wanda ya fi alkhairi tsakanin Sadeeq da Najeeb"

Ɗaukar waya tayi ta kira Najma, "Hi Sisto" cewar Najma

"Hi dear,  ya gida"

"Lafiya ƙalau,  jiya na kira wayanki ba kiyi picking ba"

"Nayi bacci ne, sai yanzu ma na tuna"

Murmushi Najma tayi ta ce "iye, kin mamta na kira ki ma kenan, ko dai kun shirya da Prince ne shiyasa kika fara mantawa da ni kuma? "

"Hmm, wane irin shi kuma Anty Najma? Ni fa na fara haƙura da Prince,  na haƙura ma dai zan ce"

"Kamar ya? "

Kwashe maganganun Sadeeq tayi nabjiya ta gaya wa Najma, ta ƙara da cewa "hakan ya sa tun jiya na yanke wa kaina hukuncin rabuwa da Sadeeq ba wai dan na daina son shi ba, amma rabuwa da shi ya zama dole dan in kare mutuncin kai na tunda kowavgaya wa yake yi ba ya so na,  mutane su na mun kallon wacce ba ta san darajar kanta ba... Anty Najma saboda ni ce har yau bai auri Jewel ɗin shi ba wanda hakan ya sa ya kasa rayuwar farinciki, kullum cikin damuwa yake, kin ga idan muka rabu da shi zai samu ya aure ta su yi rayuwarsu yanda yake buƙata, shikenan ya huta"

Shiru Najma tayi tana mamakin wace irin zuciya Sunaiha take da shi ne? Wai kuwa ba asiri aka mata da wannan Prince ɗin ba?, sai kuma ta ce "wai Sunaiha yanzu kina nufin za ki rabu da Sadeeq ne ba wai dan kin daina sonshi ba, sai dai kawai dan yayi farinciki ya samu ya auri wacce yake so?"

Tana ƙoƙarin danne kukanta ta ce "eh Anty Najma, ba na tunanin akwai ranar da zan iya daina son Prince, amma zan bar shi saboda farincikinsa nake buƙata, i don't really care what people might say about me,  aure na bai yi good six month ba, na fito, i don't care... Kuma in sha Allah Najeeb ɗin da kika ce kin yarda shi ke so na, shi zan aura"

"Ya Salam! Sunaiha Allah ya ba ki ikon cinye wannan jarabawar,  haƙiƙa kin jarabtu da soyayya.... To yanzu when are you planning to leave him?"

"Idan aka sallami Grandpa daga asibiti"

"Shikenan,  Allah ya ba shi lafiya... Yanzu kina asibitin ne ke ma ko kina gida? "

"Ina gida,  yau ba zan tafi ba"

"May be da kin tafi za ki haɗu da Daddy,  saboda ɗazu na ji yana gaya Mummy zai je duba Alhaji Saraki,  sai bayan da na shigo ɗaki ne ma na tuna waye Saraki"

"Ayya... Anty Najma bye,  ina so zan kwanta"

"Za ki kwanta ko za ki ci gaba da sana'arki ta kuka dai"

Ɗan murmushi tayi, ta ce "zan kwanta dai"

"Ok then,  bye" suka kashe wayar

A office ɗin Sadeeq kuwa,  shi ne tare da Anty Sadiya, yana gaya mata zai bayyana Jewel idan aka sallami Grandpa

Anty Sadiya ta ce "do you really think this is a good idea? "

"Of course yes, idan na jinkirta zuwa wani lokacin ban san kuma me zai faru ba,  kin ga dai na gaya miki yanda muka yi da su Salma jiya"

"Amma sai nake ganin bai kamata.... "

Katse ta yayi da "please Anty Sadiya don't say no,  ba zan iya bari zuwa wani lokacin ba, ke kin san i tried alot, i obey you, kin saka ni nayi abubuwa da yawa waɗanda kwata-kwata ban so ba kuma na cutu sosai akan su, kuma har yanzu ina kan cutuwa, i can't withstand this anymore, bayyana Jewel yanzu shi ne kwanciyar hankali na"

"Na sani Sadeeq, amma ni ina ji a jikina bayyana Jewel yanzu zai iya jawo maka wasu

matsaloli, akwai abubuwan da nake ganin ya kamata ka daidaita su"

"me zan daidaia kuma? Na yi iya haƙurin da zanyi fa... Wai ma meyasa na ga kamar ba kya supporting ɗin bayyana Jewel ne? "

"Kai ma ka san i always support you and your Jewel, amma if you try to.... "

Sake katse ta yayi a karo na biyu "no ifs and buts please Anty Sadiya, just say yes, and always think positively, ba abunda zai faru in sha Allah"

Ganin yanda ya takura, ya sa ta sauke numfashi ta ce "shikenan Sadeeq, yaushe kenan za ka bayyana ta ɗin? "

"Nan da kwana huɗu in sha Allah, kin ga Kawu ƙarami ya ce sai Grandpa yayi sati ɗaya sannan za'a sallame shi, to yau saura kwana huɗu"

"To Allah ya kai mu lafiya.... Amma na ga jikinshi da sauƙi sosai"

"Eh haka ne, amma idan aka sallame shi yanzu, ba lallai zai mayar da hankali ya sha maganinshi yanda ya dace ba, kuma tsab zai ci gaba da shan drinks, shiyasa sai ya kammala shan magani"

"Alright.. Sai kuma abu na biyu, na taɓa tambayarka me ya haɗa ka da Momi, ba ka ce komai ba"

"Anty Sadiya ina zargin Momi ne, she's planning something against me and this family, sai dai har yanzu na kasa tantance ko me take nufi"

Wani kallo ta mishi, ta ce "are you out of your senses Sadeeq? Momi kake zargi? "

"Na sani ai, ba za ki yarda ba, shiyasa ban so gaya miki ba sai na haɗa hujja"

"Sadeeq, kana da ɗaukan magana fa, dan Allah ka bari mu zauna lafiya"

"Zaman lafiyarmu shi ne in gane me Momi ke ƙullawa"

"Sadeeq dan Allah ka daina maganar nan, ni fa ban yarda ba, Momi fa ba baƙuwa ba ce a wurinmu, ba kuma bare ba ce, ta ya kake tunanin tana planning ɗin wani abu? "

Dama ya san ba yarda za tayi ba, ya ce "shikenan, a bar zancen kawai"

"Ya fi kam... Bari in je wurinsu Hajiya ka samu kayi aikinka"

"Ok"

Ta tashi ta fita, maimakon aikin da ya kamata yayi sai ya jingina jikin kujerarshi yana ta tunani.......

KUYI TA HAKURI DA SHORT PAGES DAN ALLAH, BAN DA LAFIYA WALLAHI,  COMMENTS DINKU NE KE BANI KARFIN GWIWAR TYPING DUK IRIN YANDA NAKE JI SAI NA YI, MUSAMMAN ƳAN GROUP DIN ƳAR SENATOR FANS, I REALLY APPRECIATE YOU GUYS DA DUK SAURAN MASOYAN ƳAR SENATOR, LOVE YOU ALL, MAY ALLAH BLESS YOU🥰💫🔐

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/KPe9OCufd1R9ZHf4PSEx7r

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_

🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Life is like a piano, White keys are happy moments and Black keys are sad moments. But remember both keys are played together to give Sweet music in life..._

*PAGE 57-58*

Sai da yamma sannan su Hajiya suka yi shirin barin asibitin, bayan sun fito me Momi ta ce su wuce kawai za ta zo daga baya

Umma ta ce "lafiya dai? Ina za ki tafi kuma?"

"Lafiya ƙalau, ina so zan je wurin Yaya ne, ta kira ni ɗazu ban san meyasa ba, shi ne nake so zan tafi"

"To Allah ya sa lafiya" cewar Hajiya

Gaba ɗaya suka amsa da ameen, kafin suka shiga motar da su Sauban suka zo da ita, sai ya kai su, ita kuma ta shiga motar da suka zo da ita, ta wuce

Kai tsaye gidansu Sarah ta nufa, tana shiga parlour ta tarar da Yayarta a zaune tana kallo, zama tayi suka gaisa, mahaifiyar Saraha ta ce "ba dai daga asibitin kika zo nan ba"

"Daga can nake" ta faɗa tana ajiye mayafinta gefe

"Kin ga ina ta so ma in je duba Alhaji Saraki"

"Ba ma sai kin je ba dan Allah, nima ai dole ke sa ina zuwa ba wai dan ina ra'ayi ba"

"Kai Basira, mahaifin mijinki ne fa, ya kamata noma in tafi ai"

"Yo Yaya mahaifina ne? Ai ni yanzu tun da na rasa iyayena, uban kowa ma ya mutu, ina ruwa
~~~~~~~~~~~~~~~~

na?!"

Ƴar dariya tayi ta ce "Basira kenan, Allah ya shirye ki"

"Ummm.... Ni fa Yaya ba ma wannan ya kawo ni b, kwana biyu ban ga Sarah ba, ta gaya miki wani abu akan Sadeeq kuwa? Akwai alamar nasara?"

"Eh akwai, dan a yanda take gaya mun, yanzu tana samun lokacinsa sosai"

"Yawwa, haka nake so, ta ko ina ana samun nasara, ita kanta mahaifiyarsa yanzu tana yawan magana akan Sarah, gaskiya aikinta yana kyau... Amma ana nuna mata gabas da, tana bijirewa"

Dariya tayi ta ce "ai yanzu ma tausayinsa take ji sosai,  dan jiya tana gaya mun firar da suka yo da shi akan wannan yarinyar da yake so, kin ga kenan har yanzu bai manta da ita ba"

Ɗan taɓe baki Momi tayi ta ce "dalla manta da shi, ni na tabbata in dai komai ya tafi yanda nake so, to komai zai yi dai-dai"

"Amma kin san ni har na fara tunanin ko mu koma kan Sameer ko Sauban tun da su ba suyi aure ba, na ga dai duk gida ɗaya ne"

Wani kallo ta mata kafin ta ce "har yanzu Yaya ba kya hango abunda ni jake hangowa, Sameer da Sauban ɗin duka nawa suke? Yanzu ne fa suke final year, Sadeeq kuwa asibiti biyu ke ƙarƙashinsa, kawai dai Abban su Salma yana zuwa ɗayan ne idan aiki yayi yawa, bayan chemists ɗin da yake da su, ko a iya kuɗinsa kuka tsaya mun taki sa'a, kuma kin ga Mahaifinsu Sadeeq shi ke da kampanoni... Kawai dai da Sadeeq ɗin za mu fi cin nasara"

Numfashi ta sauke ta ce "to shikenan, Allah ya ba mu sa'a..... Amma kin san nayu mamakin yanda har yanzu Sadeeq bai zargi komai ba duk yanda yake ɗin nan!?"

"Nima nayi mamaki kam, amma kuma kin san ban bada ko wace irin hanya da zai sa a yi zargin ina da wata manufar ba"

Tayi dariya ta ce "Basira manya, wanda bai san halinki ba yana tattare da wahala"

Ita ma dariyar tayi ta ce "wanda ma ya sani ba tsira yayi ba" haka dai suka yi ta firarsu har kusan magrib kafin ta wuce gida

A ɓangaren su Mummy kuwa, ita da Hajiyar london da Najma sai Sharif, suna zaune a parlour, Hajiyar london ta ce "wallahi yanzu gidan nan ba wani daɗi"

Kallon mamaki suka bi ta da shi, Mummy ta ce "me ya faru kuma?"

"Baby ba ta nan mana... Amma dai idan na tuna tana gidan mijinta kuma sai in ji daɗi, musamman idan na tuna irin mijin da ta samu, yaro mai hankali da sanin darajar manya"

Murmushi Mummy tayi ta ce "ai Sadeeq kam sai san barka, ni kai na yaron yana burge ni, yana da hankali sosai, kowane sati fa sai ya zo ya gaishe ni, sannan yana yawan kirana bayan kwana biyu muna gaisawa"

Hajiyar london ta ce "ai Sunaiha kam tayi dacen miji alhamdulillah, ga shi ita ma na ga ta natsu sosai kuma na tabbata shi ne sila"

Mummy ta ce "kai Hajiya, na ga fa yaron nan ya tafi dake to, a bar zancensa haka nan dan ina ɗan jin hot" ta ƙarasa tana murmushi

Hajiyar london ya ce "meyasa? "

"Ga ƴata a zaune ta ƙi kawo miji bare nima idan kin fara yabon mijin ƴarki nima in yabi nawa, amma dole sai dai in taya ki" ta ƙarasa tana kallon Najma dake chatting ɗinta

Hajiyar london ta ce "ai to ku kuka so, shegen ruwan idon tsiya, ban san wane irin miji take jira ba ai"

Sharif ya ce "balarabe take jira" ya faɗa yana dariya

Harararsa kawai Najma tayi, Hajiyar london ta ce "wane balaraben kuma? Wataƙila ita ma mijin na ta a mafarki yake, irin Sadeeq"

Sai a lokacin ta ɗaga ido ta ce "Allah ya kiyaye in so namiji har ya samu damar raina mun hankali, ai ni sai dai namiji ya haukace a kaina ba dai ni inyi hauka akansa ba"

Sharif ya ce "sannu Queen Of Beauty, ai na ga Sunaiha ita ma namiji ne yayi hauka akanta"

Kallonshi tayi ta ce "a ina ka ga yayi hauka akanta? Kullum fa ita ce ke damun mitane da zancen Prince dai Prince dau, but at last ga.... " sai kuma tayi shiru

Hajiyar london ta ce "at last ga shi ta aure shi ko, kuma yana sonta"

"Hmm Hajiya kenan" ta faɗa, sannan ta mayar da hankalinta kan chatting ɗinta

Sharif ya ce "Hajiya sai ma kinyi zancen so? Yana masifar sonta ma, ai daga gani ma kin sani"

Girgiza kai kawai Najma tayi tana ci gaba da abunda ke gabanta, Mummy ta ce "ni dai ya isa

haka, kuna ta damunta,  ai gaskiya ta faɗa, ta fi ƙarfin tayi ta mafarkin namiji sai dai yayi akanta, dan ƴar ta wa akwai class"

Hajiyar london ta ce "ku dai kuka sani, duk abun ku dai na san ba za'a samu irin na mu ba"

Sharif ya ce "ai irin namu na musamman ne, ƙyale su kawai"

Najma ta ce "nima ba na fatan samun irinshi" tana faɗin haka ta miƙe ta haura sama, bin ta suka yi da ido

Hajiyar london ta ce "yau dai halin ya motsa"

Sharif yayu dariya ya ce "kwana biyu ba'a yi ba ne"

Mummy ta ce "kun sa mun ƴa a gaba dai kawai, bari in je"

Dariya suka yi baki ɗaya,  Mummy kuma ta wuce ɗakin Najma. A kwance ta same ta tana shirin kunna laptop, miƙewa tayi ta zauna, ta ce "Mummy"

"Na'am Najma, zauna ina so za muyi magana ne"

Zama Najma tayi babu musu tana kallon Mummy,  ta ce "Allah ya sa lafiya"

"Lafiya ƙalau, kawai ina so ne ki gaya mun meyasa ba kya son miji irin Sadeeq?"

Murmushi tayi ta ce "au,  Mummy ba komai, wasa nake yi ai dan kawai sun dame ni ne shiyasa na faɗi hakan, amma wasa nake yi"

"Najma kenan, dan bamu zauna tare ba, ba shi ke nufin ban karanci halayenki ba, kamar yanda kika san duk lokacin da Sunaiha take magana ina karantar zuciyarta, haka ne ke ma, idan kuna magana ba saurarenki nake fara yi ba, karantarku nake yi first... Dan haka ko ki gaya mun, ko ki ɓoye mun, ni na san Sunaiha ba ta taɓa jin daɗin zaman gidan Sadeeq ba"

Zancenta ya daki kunnen Najma,  da sauri ta ɗaga kai ta kalle ta, ta ce "kin sani fa kika ce Mummy, ta ya? Meyasa kuma kika yi shiru kika bari ta ci gaba da zama a gidan? "

Murmushi Mummy tayi ta ce "Naima ni uwa ce fa, ta ya kike tsammanin ba zan iya fahimtar abunda Sunaiha take ɓoye mun ba? Tun bayan aurenta, ranar da ta fara zuwa gidan nan, tayi ƙoƙarin ɓoye damuwarta ga mahaifiyar da ta haife ta, ni kuma na ƙyale ta ne saboda na fahimci ba so take in sani ba"

"But Mummy why? Meyasa za ki biue ta ki ƙyale ta bayan kin san ba ta jin daɗi, a maimakon kiyi ƙoƙarin ganin kin raba ta da shi? "

Girgiza kai Mummy tayi,  ta ce "meyasa zan yi hakan? Idan na raba ta da mijinta, wace irin uwa ce ni kenan? Najma, kaza tana taka ƴaƴanta ne ba wai dan ba ta son su ba sai dan ta ba su kariya, nima hakan ne, ban ƙyale Sunaiha ba saboda ba na son ta ba ko kuma dan ban damu da damuwarta ba, na ƙyale ta ne ta ci gaba da zama tare da Sadeeq saboda na fahimci shi ne zai koya mata darasin da na daɗe ina fahimtar da ita amma ta ƙi ganewa"

Mamaki Najma ke yi sosai "amma Mummy.... "

Dakatar da ita tayi ta hanyar ɗaga mata hannu "ya isa Najma, ba wani bayani da zan miki ki fahimce ni sai nan gaba idan kin gane wa idonki, yanzu son da kike yi wa Sunaiha ya rufe miki ido, ba yanda za'a yi ki ga hasken Sadeeq, amma idan da zan miki wata addu'a ki ce ameen, to da zan ce Allah ya ba ki miji irin Sadeeq" daga haka kawai ta bar ɗakin, Najma kuwa ta kasa gane me Mummy ke nufi, ta ba ta mamaki sosai

Bayan sallar isha'i Sadeeq ya shigo gida, Sunaiha na parlour a zaune ba abunda ta ce mishi, har ya shiga yayi wanka ya fito sannan ya dawo ya zauna, sai a lokacin ta ce mishi "sannu da zuwa"

Kamar ba zai amsa ba, sai kuma ya ce "yanzu kika ganni?"

Ɗan rufe ido tayi, sannan ta miƙe ta ce "Allah ya baka haƙuri idan gaisuwar ma ta zama laifi"

Kitchen ta nufa ta ɗauko abinci ta kawo mishi, tana ajiyewa, ya kalli kulolin da kyau ya kalle ta, ya ce "yau kim ga daman yin girkin kenan"

"Kullum ina yi ai"

"Yau kika ga daman kawo mun kenan"

"Yau dai ka ga daman zama in kawo maka"

"Ok, ni kike gaya wa magana san ranki?"

"Allah ya baka haƙuri"

"Ki riƙe haƙurinki ba na so, fuska kika gani kuma na ƙyale ki shiyasa har kika samu damar gaya mun magana, amma very soon all this will come to an end, kowa ma ya huta"

"In sha Allah, ni kaina zan so komai ya zo ƙarshe dan ka huta"

"In huta? Kin gane na gaji ashe"

Murmushin takaici tayi ta ce "ai duk wanda ya sanka Ya Sadeeq ya san burinka bai wuce ka mallaki Jewel ba, ni kana zama da ni ne kawai dan dole, amma idan ana so ka huta shi ne ka samu Jewel, kuma in sha Allah within some few days komai zai zo ƙarshe"

Bai damu ya fahimci abunda take nufi ba dan a tunaninshi abunda ya faɗa ne ta maimaita, murmushi yayi ya ce "ba kiyi ƙarya ba, ashe dai kina gane abunda nake so"

"Hmm, Ya Sadeeq kenan.... Sai da safe" ta faɗa tana wucewa ɗaki

Sai da ta shige ɗaki sannan ya ɗauki wayarsa yana neman wata number yana murmushi ya ce "My Princess Jewel, burinmu ya kusa cika"

Sunaiha kuwa tana shiga ɗaki tayi wanka ta zo ta kwanta, tana cikin tunani hawaye ya cika idonta, ta miƙe ta zauna da sauri tana share hawaye, ta ce "it's over, i won't cry anymore, he don't deserve my tears, kullum sai nayi kuka akan wanda bai san daraja ta ba!? Duk abunda zan gaya mishi ba ya taɓa tsayawa ya fahimci damuwa ta, abunda ke ranshi kawai ya sa a gaba, ya gama tabbatar mun da baya so na, to kuka kuma na me? I won't cry again, i don't need u in my life Prince, although i still love you truly, but i deserve some respect and care, i'm done with you Prince, Allah ya ba Grandpa lafiya kowa ya huta, Allah ya ba ni ikon iya zama da Najeeb" magana take hawaye na bin fuskarta, ita kuma sai ƙoƙarin haɗiye kukan take yi tana share hawaye

Sai da ta ban natsu kafin ta miƙe ta je ɗauko ruwa, tana fita ta ga Sadeeq yana parlourn har yanzu yana waya, ba ma sai an faɗa ba, daga ji ta fahimci da mace yake wayar, yi tayi kamar ba ta ma san da shi ba, ta shiga kitchen ta tsiyaya ruwa a cup ta sha, sannan ta dawo ɗaki ta hau gado, ta kunna karatun ƙur'ani, ta saka earpiece sannan ta kwanta, kwata-kwata ba ta kai mintuna goma ba bacci yayi awon gaba da ita

♦💫♦💫♦
*Ƴ́AR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦

*YAR SENATOR*

♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*

_BY_

🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*

We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Luck is like sand in hands. It will sneak out through fingers, no matter gripped firmly or held loosely. Only hands in the praying posture can save it._

*PAGE 59-60*

**RECAP FROM LAST PAGE**

Sunaiha kuwa tana shiga ɗaki tayi wanka ta zo ta kwanta, tana cikin tunani hawaye ya cika idonta, ta miƙe ta zauna da sauri tana share hawaye, ta ce "it's over, i won't cry anymore, he don't deserve my tears, kullum sai nayi kuka akan wanda bai san daraja ta ba!? Duk abunda zan gaya mishi ba ya taɓa tsayawa ya fahimci damuwa ta, abunda ke ranshi kawai ya sa a gaba, ya gama tabbatar mun da baya so na, to kuka kuma na me? I won't cry again, i don't need u in my life Prince, although i still love you truly, but i deserve some respect and care, i'm done with you Prince, Allah ya ba Grandpa lafiya kowa ya huta, Allah ya ba ni ikon iya zama da Najeeb" magana take hawaye na bin fuskarta, ita kuma sai ƙoƙarin haɗiye kukan take yi tana share hawaye

Sai da ta ban natsu kafin ta miƙe ta je ɗauko ruwa, tana fita ta ga Sadeeq yana parlourn har yanzu yana waya, ba ma sai an faɗa ba, daga ji ta fahimci da mace yake wayar, yi tayi kamar
~~~~~~~~~~~~~~~~

ba ta ma san da shi ba, ta shiga kitchen ta tsiyaya ruwa a cup ta sha, sannan ta dawo ɗaki ta hau gado, ta kunna karatun ƙur'ani, ta saka earpiece sannan ta kwanta, kwata-kwata ba ta kai mintuna goma ba bacci yayi awon gaba da ita.......

_BAYAN KWANA UKU_

Sadeeq ne a parlour, da dukkan alamu fita zai yi, dan ya gama shirinsa tsab, wayarsa tayo ƙara, yana dubawa ya ga sunan Kawu Karami, ɗagawa yayi cike da girmamawa suka gaisa kafin Kawu Ƙarami ya ce "Sadeeq ina cikin asibiti, na ga ba ka ƙaraso ba har yanzu"

"Wallahi kuwa Kawu, amma gani nan zuwa yanzu"

"To shikenan.... Dama jikin Baba na duba, kuma na ga alhamdulillahi, kamar yanda muka yi tsammani, ya ji sauƙi, dan har BP ɗin shi na duba, it's now normal"

Cike da murna Sadeeq ya ce "Masha Allah, nima jiya da na duba shi da daddare normal ne.... Yanzu sai maganar sallama kenan"

"Eh, ka san dama one week muka yi, amma dai kar ka sallame shi ka bari dai gobe, saboda maganinshi na dare"

Murmushi yayi ya ce "Kawu kar ka damu, dan maganin dare kawai zan je har gida in ba shi, wallahi Grandma ta gaji da yawon asibitin nan, kuma taƙi yarda ta zauna a gida" ya ƙarasa yana murmushi, hakan yayi dai-dai fa fitowar Sunaiha, ya tsaya tana kallonshi

"To shikenan duk yanda kayi, ni zan wuce ne ma yanzu, idan ka shigo sai ka ƙarasa duba sauran patients ɗin, gobe ka zo mu je mu duba sauran chemists ɗin mu ga abunda ake buƙata"

"To, amma gobe akwai abunda zan yi mai muhimmanci, may be dai zan kira su sai su rubuto mun duk abunda ake so ɗin"

"What's so special Sadeeq? A sanin da na maka ba ka wasa da aikinka, to me za kayi gobe? "

Murmushi ya sake yi, ya ce "wani abu ne dai"

Sgi ma Kawu Ƙarami murmushin yayi, ya ce "to Allah ya taimaka... Sai ka zo"

"Ameen nagode" daga haka suka kashe wayar

Sai a lokacin ya kalli Sunaiha ya ce "sai da kika gama ɓata mun lokaci sannan za ki fito?"

Kallonshi kawai tayi ba ta ce komai ba, shi ma hai sake magana ba ya fita, ta ni bayanshi.

Suna hanya, ta ɗan kalle shi, ta ce "ɗazu na jo kaman kana cewa za'a sallami Grandpa yau ko? "

"Umm" ya amsa mata

Numfashi ta sauke, sai ta ce "ina so za muyi magana zuwa anjima idan mun dawo"

"Allah ya kaimu, nima ina so zan yi magana da ke ai" ya sake amsa mata hankalinsa na kan titi. Ita ma daga haka ba ta sake cewa komai ba har suka isa

Kai tsaye ɗakin da Grandpa yake ta wuce, Sadeeq kuwa sai da ya fara biyawa office. Tana shiga ta tarar da su Sultana da Salma, da gidu suka zo suka rungume ta, sannan suka koma suka zauna, ganin tayi Grandpa na bacci shiyasa ha ta gaida shi ba, ta kalli su Sultana ta ce "ina su Sauban da Sameer? Ko ku kuka kwana anan ɗin yau? "

Salma ta ce "kaiii, a'a, ai Abba ba zai bari ba, su Sauban suka kwana, kasancewar yau za su fara rubuta final exams ɗinsu, shiyasa muka zo da wuri sai suka wuce, su Umma sai anjima kaɗan"

"Allah Sarki, Allah ya ba su nasara"

Suka amsa da "ameen" Sannan Sultana ta ce "wallahi Anty Sunaiha munyi kewarki sosak, tun fa ranar da kika bar asibitin nan ba ki dawo ba sai yau, idan muka yi wa Oga Tiger zancenki sai ya ƙyale mu"

Murmushi tayi, ta ce "nima haka nayi kewarku, amma ai yanzu ga ni"

Salma ta ce "kin san me Anty Sunaiha, sai yanzu nake jin haushin meyasa Alhaji bai ce su Ya Sadeeq da Ya Safwan suyi part ɗinsu a cikin gidanmu ba tunda akwai wuri sosai, za suyi part ɗinsu girman yanda suke so har a samu ragowa sosai ma"

Sultana ta ce "ni kaina nayi wannan tunanin, saboda yanzu nake jin kewar Anty Sunaiha yan damu na"

Murmushi kawai Sunaiha ke yi tana bin su da ido, Sultana ta ce "amma yanzu ma ba matsala, tunda yau za'a sallami Grandpa, daga gobe za kiyi ta ganinmu har sai kin gaji"

Sunaiha ta ce "me zai sa in gaji da ku? Kullum buri na in zauna tare da ku ai"

Salma ta ce "Anty Sunaiha kiyi haƙuri yanda muka yi miki a baya, kawai yanda kika yi mana ne ya ɓata mana rai, amma kiyi haƙuri"

"Don't worry Salma, nima ban kyauta ba ai, kuyi haƙuri "

Sunaiha ta ce "ni dai bana jin dađi in ji Antyna tana ba ni hakuri" ta fađa tana ɓata rai

Sunaiha murmushi tayi ta ce "to na daina my dear"

Shiru suka đan yi, Sunaiha a ranta ta ce "Allah sarki, lokacin da nake shirin barin gidanku, sai a lokacin muka fara shakuwa da ku, ina jin sonku a raina kuma sosai... Amma hakan ba zai sauya mun ra'ayi na ba, dole zan tafi sabida samar wa kaina daraja, za mu ci gaba da zumuncinmu ko bayan tafiya ta, sannan ina fatan kamar yanda nake sonku a yanzu, Allah ya sa ita ma Jewel đin Prince za ta so ku haka, kuma ku so ta" duk yanda hawaye ya so fitowa a idonta, sai da tayi kokarin kayar da shi

Muryar Sultana ta dawo da ita, "Anty!!!! "

"Umm" ta amsa tana kirkirar murmushi

"Where were u lost haka? Muna ta magana shiru"

"Oh, i'm sorry, wani tunani nake yi ne"

Murmushi Salma tayi ta ce "can i guess!? "

"Guess what" cewar Sunaiha

"Abunda kike tunani mana"

Sultana ta ce "ai ba wani ɓoye-ɓoye, mijinta take tunani" ta fađa tana murmushi

"See this girl, wane miji kuma? Yanzu fa muka rabu"

Salma ta ce "and so!? Mu dai mun san shi kike tunani"

Kafin tayi wata magana, Grandpa ya ce "dan Allah ku kyale ni haka nan in yi bacci, yara sai kace Parrot? "

Kallonshi suka yi da mamaki, idanunshi a rufe, amma yake maganar, Salma ta ce "dama ba bacci kake yi ba Grandpa? "

Buđe ido yayi ya kalle ta ya ce "ta ya zanyi bacci kuna đakin nan? "

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "kayi hakuri Grandpa, na đauka kana bacci ne ai"

"Kar ki damu Sunaiha, ai yanzu na tashi, shi ne na ji surutunsu"

"To ya jikin? "

"Alhamdulillah, ni wannan yarin ma nake so ya zo ya sallame mu haka nan mu tafi gida kowa ya huta"

"Allah ya ƙara lafiya"

"Ameen"

Haka suka ci gaba da firarsu, har Sadeeq ya shigo ya duba shi ya fita, sannan su Hajiya suka ƙaraso suka ci gaba da zaman su tare

Sai bayan magrib kafin Sadeeq ya cika musu takardar sallama, sannan syka wuce gida. Gaba ɗaya gidansu Grandpa suka nufa har su Umma, Sannan Sadeeq ya wuce da Sunaiha gida, ko gate bai shiga ba, ya ce "ki je, ni zan koma dan akwai maganin da nake so sai na tabbatar ya sha, sanna zan dawo"

"Allah ya kiyaye" ta faɗa sannan ta fita, shi ma ya wuce

Tana shiga ta yi sallah, sannan ta dafa spaghetti, ta zuba a plate ta wuce parlour ta zauna, ta fara ci kenan kiran Ikram ya shigo wayarta, cike da murna ta ɗaga

"Mutanen Abuja" abunda ta fara faɗa kenan

Ikram ma cikin fara'a ta ce "Hajiya ta, ai na baro Abuja, ina cikin garin Gombe"

Da mamaki ta ce "Gombe kuma? "

"Kwarai kuwa, a Gombe ma, a cikin gidanmu"

"Saukan yaushe kenan? What a surprise!"

"ai ba ma haka ma so inyi surprising ɗinki ba, na so samun flight ɗin safe yanda kawai gani na za kiyi a gidanki, sai na samu na dare kuma, yanzun nan na dawo, wanka kawai nayi, nayi sallah, shi ne na kira ki"

"Hmm, to sannu da dawowa.... I thought ma kin manta dani, shagalin biki ya rufe miki ido"

"Haba Sunaiha, ai ba abunda zai sa in manta da ke, yanzu ki shirya, gobe tun safe za ki ganni a gidanki, kuma sai dare zan wuce"

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "ba gobe ba dai kam, ki bari zan gaya miki ranar da za ki zo"

"Ban gane ba, ok, ke ce ma ba kiyi missing ɗina ba"

"A'a wallahi, i so much missed you My Iky, gobe akwai wani abu da zanyi, it's very important"

"Important? Me kenan?"

"Yeah, idan na gama, i'll let you know"

Shiru Ikram tayi, kafin kuma ta ce "alright then, Allah ya sa in ji alkhairi"

"Ameen... Ki gaida Umma"

"Za tajl ji, sai da safe" suka kashe wayar a tare

Numfashi Sunaiha ta sauke, ta ce "i wish zan iya gaya miki me nake shirin yi, but i can't, saboda hana ni za kiyi"

Ɗaukar wayar tayi, ta kira Anty Najma, bugu biyu ba ta ɗaga ba, sai kawai ta ajiye wayar ta ci gaba da cin abincinta. Tana haka har Sadeeq ya dawo, ya shiga yayi wanka sannan ya dawo parlourn, abinci ta kawo mishi sannan ta zauna gefe

Tunani take ta yanda za ta fara magana, sai ta ji muryar sa yana cewa "ina jinki, ɗazu kin ce kina da magana" ya faɗa yana kallonta

Tayi mamakin jin hakan daga bakinshi, saboda a tunaninta ya manta, sai ta ce "a'a ka fara faɗa, ai kai ma ka ce kana da magana"

"Malama ba jayayya nake so muyi ba, umarni nake ba ki kiyi magana, ba shawara na tambaye ki ba"

Sai da ta tattaro courage, sannan ta ce "Ya Sadeeq"

"Umm" ya amsa yana ƙoƙarin kai abinci baki

"I need a divorce"

Maganar ta daki kunnenshi, bai san lokacin da ya saki cokalin hannunshi ba, kallon mintuna biyu ya mata, kafin ya ce "Divorce? Saki fa kenan kike nufi! "

"Eh Ya Sadeeq, ba ka so na, ba ka son zama da ni, muma zaune ne tare akan dole, Jewel kake so ba ni ba, Ya Sadeeq ba zan iya ci gaba da zama da kai kana kwasar zunubi ba, saboda ba ka taɓa sauke ko wane nauyi ma dake kanka ba, hakan kuwa babban matsala ne a wurinka

ran Allah zai tambaye ka, abu mafi sauƙi shi ne rabuwarmu Ya Sadeeq, dan haka dan Allah na roƙe ka, ka sauwaƙe mun"

Numfashi ya sauke, kafin ya ce "wa ya ba ki wannan shawarar? Dan wannan ba dabararki ba ce"

"What so ever Ya Sadeeq, ba abunda ya dame ka bane, ni dai dan Allah ka sake ni, dan Allah "

"Shikenan na ji, amma yanzu dare yayi, ki bari sai da safe" ya faɗa yana ƙoƙarin tashi

A hankali ta rufe ido, hawaye suka biyo fuskarta sannan ta buɗe, tana ganin ya miƙe, tayi saurin cewa "abincin fa? "

"Ki bar shi wurin"

Zai wuce, ta miƙe tsaye ta ce "Ya Sadeeq"

"Meye kuma? "

"Dan Allah kafin rabuwarmu, ina so zan roƙe ka wata alfarma guda ɗaya"

Kallonta yayi da kyau, ya ce "wace irin alfarma? Ki gaya mun zan miki, ba ki taɓa roƙo na wani abu nayi miki ba, amma yau saboda yamda kika faranta mun, dole zan miki ko menene"

A tunaninta ya ji haushin rabuwar da za suyi, kenan daɗi ya ji? Ta tambayi kanta kafin ta ce "Ya Sadeeq dan Allah, just once, ka nuna mun Jewel, please"

"Jewel? Why? "

"Kawai ina so ne zan ga wace ce ita, da me ta fi ni da har ka tsane ni saboda ita, ka nuna mun hotonta dan Allah "

Wani murmushi yayi sannan ya ce "Jewel dai kike so ki gani?! Well, za ki ganta, manta ma da zancen hoto, ita ɗin za ki gani a zahiri"

"A'a, bana buƙatar ganinta a zahiri, a hoto kawai"

"Ba hotonta ko ɗaya a tare da ni yanzu, infact, ita ma tana so za ta ganki, Dan haka ki shirya gobe by 12pm, zan kai ki"

"Hmm, daga nan sai in wuce gida? "

"As you wish, i don't care" daga haka ya wuce ɗaki

Zama tayi tana share hawaye, al'amarin Sadeeq ya wuce tsammaninta, ɗaukar waya tayi za ta sake kiran Najma dan ta gaya mata tayi abunda tayi planning, sai kuma ta fasa saboda ta san tsab Najma za ta hana ta zuwa ganin Jewel, ita kuma a halin yanzu babban burinta shi ne ta ga wannan Jewel ɗin, sai kawai ta mayar da wayar ta ajiye, ta ce "Ya Allah, ina roƙonka, ka sa wannan abunda zan yi shi ne mafi alkhairi a wurinmu ni da Prince" ta kai tsawon mintuna goma, kafin ta iya miƙewa zuwa ɗaki ta kwanta tana ta saƙa abubuwa daban-daban, musamman tunanin yanda haɗuwartada Jewel zai kasance

Washe gari da safe kusan ƙarfe goma, Najma ta kira ta, lokacin tana ɗakinta, tunani take ta faman yi, sai da ta kusa tsinkewa kafin ta ɗauka, suka gaisa, sannan Najma ta ce "sai yanzu nake ganin missed call ɗinki, kin san ni idan ga laptop a gabana mantawa nake da zance wata waya"

"Nayi tunanin haka ai"

"Yawwa, lafiya dai? Hope ba ki yi maganar nan da Sadeeq ba? "

"Nayi mana Anty Najma, i don't have any other choice"

"Gosh! Na so in gaya miki wata magana kafin hakan ta faru wallahi, gaba ɗaya hankali ya ɗauku"

"Don't worry dear, anjima idan na dawo sai muyi maganar"

"Yanzu take da amfani ai Sunaiha, akan Mummy ne, ta.... "

Katse ta Sunaiha tayi da "Anty Najma kar ki damu da su Mummy, i know how to explain everything, sai na zo kawai" ba ta jira jin komai ba ta kashe wayar, dan ita yanzu tunaninta ya fi karkata gefen Jewel

Najma kuwa kallon wayar take da mamaki, ta ce " how could she just hang up? Na so gaya mata abubda Mummy ta faɗa... Oh God"

Ƙarfe sha biyu da mintuna takwas, Sunaiha ta fito daga ɗaki, Sadeeq na nan a parlour yana jiranta, ya gama shirinsa cikin wando jeans blue da riga light blue mai buttons, dai madubi kalar wando, yayi kyau masha Allah

Kallon Sunaiha yake daga sama har ƙasa, ganin shigar da tayi, tayi kyau sosai, dan tun bayan aurenta, ba ta sake irin wannan shigar ta fita ba, jallabiya ce a jikinta kalar peach, kwalliyar jallabiyar kuwa brown ne, sai ƙaton madubinta, square shape da ya mamaye rabin fuskarta, kalar brown, flat sheos ɗinta brown, sai tayi rolling kanta da mayafin jallabiyar, tayi

kyau sosai ba kaɗan ba, dan yau ta fito a ƳAR SENATOR ɗinta

Ta ce "Malam mu tafi "

Sai a lokacin ya dawo daga tunanin da yake, ya ce "wannan wace irin shiga ce? Ke fa matar aure ce" ya faɗa yana ɓata rai

Kallon jikinta tayi, ta ce "meye aibun haka? Besides ma, me ya dame ka da shiga ta? Ina ce auren sauran few hours ya mutu"

Jinjina kai yayi, ya ce "good" sai kawai miƙe ya fita, ta bi bayan shi

A hanya gabanta sai faɗuwa yake, hawaye na taruwa a idonta amma tana mayar da su, waɗanda suka yi taurin kai suka gangaro, kafin su kai ƙasa take dabarar gogewa, dama dalilin saka tangamemen glass ɗin kenan, zafin da take ji a zuciyarta, yasa take ji kamar ta ce ta fasa ganin Jewel ɗin, kawai su koma ta sake ta, amma ta riga da ta sa ma ranta son ganin Jewel, kuma in sha Allah yau ɗin nan sai ta ganta, nothing will stop her..............

KU BA TA SHAWARA, SHIN TA JE GANIN JEWEL ƊIN NAN? KO DAI TA KOMA GIDA? NI DAI NA CE KAR TA JE, AMMA BA TA SAURARE NI BA

♦💫♦💫♦

*ƳAR SENATOR*

♦💫♦💫♦

*LIKE*

*SHARE*

*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_

🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Life is like a coin. Pleasure and pain are the two sides, only one side is visible at a time.... But remember, the other side is also waiting for it's turn ….. !!_

*PAGE 61-62*

Gaban wani babban gida ya tsayar da motar, gida ne mai girma kuma mai kyaun gaske tun daga waje ma kawai, an tsara gidan sosai, sannan an zagaye shi da wasu flowers masu kyau, da dukkan alamu suna samun cikakkiyar kulawa dan ba abunda ya same su, kamar yau aka saka su a wurin

Horn yayi, wani matashin mai gadi ya zo ya buɗe, dai-dai mai gadin ya tsaya ya sauke glass, cike da girmamawa mutumin ya ce "sannu da zuwa yallaɓai"

"Yawwa sannu da aiki, suna ciki? "

"Eh suna nan"

Bai ce komai ba ya ɗaga glass ɗin ya ƙarasa ciki. Wurin da aka tanada dan ajiye motoci, ya ajiye na shi, akwai mota biyu a wurin, sannan da wata motar da aka lulluɓe. Ita ta fara fitowa kafin shi ma ya fito ya rufe motar, 'Masha Allah', Sunaiha ta faɗa a ranta, saboda tsarin gidan ya matuƙar burge ta, ga shi akwai flowers ta ko ina, abunda take sha'awa kenan sosai ta gani a cikin gida, akwai gefen shaƙatawa, daga can gefe akwai garden da aka zagaye da net, za ta iya hango ɗawisu guda biyu suna ta kai-kawo a ciki, tana masifar son ganinsu, haka ma akwai swimming pool

Juyawa yayi ya kalle ta, ganin tana tsaye har yanzu, ya ce "lafiya? "

Ba tare da ta ce komai ba ta ɗaga ƙafa ta fara tafiya, shi ma ya wuce. Suna kaiwa ƙofar parlour kawai ta ga ya kai hannunshi wurin thumbprint ɗin jikin ƙofar ya buɗe, a ranta ta sake cewa "wato shi ma ya iya buɗe ƙofar mutane ba neman izini!? "
~~~~~~~~~~~~~~~~

Yana shiga ta bi shi, gabanta sai dukan uku-uku yake yi, dan ba ta san wa za ta gani ba. Parlour ne mai girman gaske, tun daga kan cushions ɗin, labule, carpet, wallpaper da komai da ke cikin ɗakin, pink da milk colour ne,  ga shi ya sha decorations, ɗakin bai da makusa ta ko ina. Kallon ta yayi ya ce "ina zuwa"

Ya buɗe wani ɗaki dake wurin ya shiga, ta ce "mutumin nan kan shi ɗaya kuwa? Sai shiga gidan mutane yake yi son ranshi, so yake ya nuna mun ya saba zuwa ne ko me?" daga nan kawai ta ci gaba da kallon ɗakin, ta rasa dalilin da yasa duk abunda ke cikin gidan nan, daga tsari da fasalin gidan har kala da komai irin wanda take masifar so ne

Ya kai tsawon mintuna goma kafin ya fito, duk tana tsaye, ya ce "zo mu je, tana sama"

Wani kallo ta mishi, ta ce "sama kuma? Ita ta sauko mana"

"Ba za ta sauko ba tunda har kika bari ta kai sama, ke kika ɓata mana lokaci ai da kin ganta a wannan ɗakin"

Shiru tayi, a hankali ta ce "lallai wannan ta fi ni izza, ni shanya mutum nake yi kafin in fito, ita kuma sai da ya same ta, tab! " ta sauke numfashi

Ya ce "mu je mana"

Tunani tayi na ɗan lokaci, kafin ta jinjina kai ta ce "mu tafi"

Haura stairs ɗin suka yi, a bakin ƙofar wani ɗaki ya tsaya sannan ya tura, nan ma mamaki take yanda ya tura ƙofar ba tare da tunanin a yanda zai ganta ba tunda ba matarshi ba ce, ganin ya shiga yasa ta shiga ita ma, sai dai ido a rufe, bugun zuciyarta ya ƙaru

Madubin dake idonta ne ya hana shi fahimtar idonta a rufe yake, ya ce "kin shirya ma ganinta ko daga bakin ƙofa za ki tsaya?"

Kaɗan-kaɗan take buɗe idanunta dan tayi tsammanin ya lura da ta rufe ido ne, sai dai abunda ya ba ta mamaki, ba kowa a ɗakin, babba ne sosai, sai furnitures masu tsada dake ciki, nan ma komai pink da milk ɗin ne har wallpaper, abunda ta fahimta, duk kayan gidan pink da milk ne. Ta ce "tana ina?  Ko toilet zan bi ta kuma? "

Ɗan murmushi yayi, sai kuma ya taka a hankali zuwa wani ɓangare na ɗakin, labule ne daga farkon bangon zuwa ƙarshe, daga ƙarshen ya tsaya, ya dinga jan wata igiya, a hankali labulen ya fara buɗewa daga tsakiya har ya kai ƙarshe

A take gabanta yayi mummunan faɗuwa, baki a buɗe take kallon abunda ya ɗaure mata kai, hotuna ne aƙalla za su kai guda saba'in zuwa tamanin cike tab a bangon, daga tsakiyar

hotunan, wani hoto guda ɗaya ne babba cikin circle shape, selfie ne, ta sha glass ɗinta irin no respect baƙi, hoton yayi kyau matuƙa, daga ƙasa aka yi rubutu mai ƙayatarwa 'PRINCESS JEWEL'. A hankali take cire madubin fuskarta tana kallon hotunan ɗaya bayan ɗaya.

Takowa yayi zuwa gefenta ya tsaya, ta naɗe hannu a ƙirji yana murmushi, ya ce "here she is, My Princess Jewel, I so much love her, i can't do without her in my life, she means alot to me.... SUNAIHA ABUBAKAR NURADDEEN"

Nan ma gabanta ya sake faɗuwa bayan ya ambaci sunanta, sai ka ce yau ta fara jin sunan, wataƙila kuma saboda yau ne ta fara jin sunan daga bakinshi, oho!? Ta kai minti goma tana kallon hotunan ko motsi ba tayi ba, sai kace an shuka ta

Ƙyasta yatsunsa yayi dai-dai fuskarta ya ce "why are you silent? Na cika miki burinki na son ganin Jewel ai, ya kika ganta? She's so cute and innocent"

Wani kallo Sunaiha ke mishi mai kama da harara, da ƙyar ta iya ɗaga hannunta ta nuna hoton, ta ce "kana nufin wannan ita ce Jewel ɗin da kake magana akanta? "

Murmushi yayi ya ce "kima magana kamar kin ga wata, ke ɗin ce, you're my Jew.... "

Kafin ta kai ƙarshe, ta ƙatse shi da ƙarfi "don't say so!! Kar ka ƙara gaya mun wannan maganar banzan... Me ka ɗauke ni? Shashasha? Ko kuma wawuya? A tunaninka ban san wannan plan ba ne ko me?"

Da mamaki ya ce "plan kuma? "

"Eh plan... Babban burinka shi ne ka ƙuntata mun tunda baka samu auren Jewel ba saboda ni, kafin ka ga ka kai matakin da kake so a wulaƙanta ni, Allah ya bani ikon samar wa kaina ƴanci, shi ne kake jin haushi burinka hai cika, dai ka ɓullo ta nan, wai nice Jewel ɗin ka, what a stupidity"

"Wallahi ba plan bane, you're my Jewel i'm telling you the truth"

A tsawace ta sake ce wa "na gaya maka ka daina gaya mun wannan maganar! Kar ka ɗauke ni wacce ba ta san abunda take yi, so kake in yarda, in bi ka ku ci gaba da zama, daga bisani ka ɗora daga wurin da ka tsaya? To bari ka ji, zama tsakanin ni da kai ya ƙare, ko a mafarki kar ka taɓa tsammanin zan zauna da kai... Saboda na ce ina son ganinta shi ne ka shirya wannan plan ɗin ko!? To na fasa ganinta ɗin, ba na buƙata, zan je in haɗa kaya na, in wuce gidanmu"

Ta juya za ta wuce, ya riƙe mata hannu dasl sauri, "ina za ki je? Kina da wani gida da ya wuce wannan ne? Duk abunda kika gani wallahi ba plan bane kamar yanda kika yi tunani, tun daga ginin gidan nan da abubuwan da ke ciki, da tsarinsa, da waɗannan hotunan gaba ɗaya, wallahi ba plan ɗin yanzu bane, komai a nan ya kai tsawon shekaru uku zuwa huɗu suna jiranki, they're

all meant for you"

A yatsine take kallon ɗakin tana wani murmushi ta ce "hmm, meant for me!? Ni? Rainun hankalinka ƙara yin gaba yake yi, ka je ka nemi wata Sunaihar ka gaya mata, not me"

Ba ta tsaya jin komai ba ta fita rai a ɓace, da sauri ya biyo bayanta yana kiran sunanta, amma ko juyowa ba tayi ba. A parlour ta tsaya cak bayan ta sauko, sabida ganin Anty Sadiya a zaune, Muhsin kuma yana fitowa daga ɗakin da Sadeeq ɗin ya shiga ɗazu

Miƙewa Anty Sadiya tayi tana kallonsu dai-dai lokacin da Sadeeq ya ƙaraso parlourn, murmushi tayi ta ce "ai na ɗauka ba za ku fito yanzu ba, Finally dai, kin gane ke ce Jewel"

Kallon mamaki Sunaiha ta mata,  ta ce "Anty Sadiya har da ke a wannan plan ɗin? "

"Plan kuma Sunaiha? "

Sadeeq ya ce "Anty Sadiya a tunaninta wannan duk shiri ne, dan Allah help me explain everything to her, i love her wallahi, kuma kin sani"

"I don't need explanation from anyone! Kar ku raina mun hankali mana, ta ya kuke tsammanin zan yarda da wannan ƙaryar? Ta ya kuke tsammanin zan yarda Ya Sadeeq yana so na? Ya wulaƙanta ni, ya ci mu mutunci, ba ya ganin daraja ta bare kuma girma na, ya faɗa kun baya so na,  ya faɗa wa mutane baya so na, and you all expect me to trust you?! Beside, a bar wannan maganar ma, a gaba na yayi waya da Jewel ba ɗaya ba, ba biyu ba, shi ma duk da ni yake wayar kenan tun da kun ce ni ce Jewel, rubbish!? " ta ƙarasa rai a ɓace

Yareema Muhsin ya ce "calm down Sunaiha, ki natsu mu yi miki bayani, za ki fahimce mu idan kika saurare shi"

# Sadeeq da jikinshi ya gama yin sanyi, ya zo gabanta ya tsaya ya ce "ban yi zaton hakan daga gare ki ba, amma yanzu na fahimci kuma hakan za ta iya faruwa, ki saurari abunda zan gaya miki, za ki yarda da ni.... Sunaiha, shekaru uku zuwa huɗu da suka wuce na sanki, na kuma fara sonki a raina, ranar da na fara ganinki a unguwarku ne mun zo wurin wani abokin Muhsin, ni da shi, ke kuma kin dawo tare da wannan ƙawar ta ki, Ikram, kallo ɗaya na miki kika tafi da ni, sonki ya shiga raina lokaci ɗaya, ban taɓa jin son wata a raina ba sai ke, kuma yanda nake jin ki yasa bana tunanin zan iya son wata bayan ke. A lokacin nayi yunƙurin zuwa in same ki, amma na ga kin nuna halinki akan wata tsohuwa da ta tsaya wurinki neman taimako, kin zage ta kin ci mata mutunci kin wulaƙanta ta, daga ƙarshe ma marinta kika yi, duk irin haƙurin da Ikram ta ba ki akma ba ki ji ba, hakan ya dakatar da ni daga zuwa wurinki, nayi shawarar sai nayi bincike akan halayenki, shin haka kike? Ko kuwa yau ne aka samu wannan akasin? Da taimakon Muhsin muka yi bincike, aka tabbatar mana da halayenki, na ji ba daɗi sosai, ba wai tunanin ko za ki karɓi soyayya ta nake yi ba, a'a, tunani na ɗaya, yanda zan kai ki gidanmu a matsayin wacce nake so zaj aura dan na san raba mu za'a yi, saboda gaba ɗaya gidanmu Allah ya ɗora

musu tsanar duk wani mai girman kai ko wulaƙanta ɗan adam, musamman Grandpa da Alhaji, waɗanda su ne ke da ikon sa wa ko kuma hanawa a gidan, tsoron hakan ne ya hanani tunkararki, na tsaya jiran ta yanda za'a yi in sauya ki. Kamar yanda kika sani, bana ɓoye wa Anty Sadiya komai, na sanar da ita komai akanki, ta vani shawarar bibiyar rayuwarki dan in ga yanda kike tafiyar da al'amuranki, ta hakan zan san ta inda zan fara tunkararki, nayi amfani da shawararta, na bibiyi rayuwarki tamkar inuwarki, duk wuraren da kike zuwa sai na sau numbern wani a wurin saboda a gaya mun idan kina can, idan kuma ina wani aikin Muhsin ne yake zuwa. Masu gadin gidanku ma, kusan fiye da rabinsu na ƙulla alaƙa da su, a wurin ɗaya daga cikinsu na samu labarin kina shirin zuwa london karatu, ba shiri na shirya tafiyar ƙarya, na ba Alhaji uzurin zan raka Muhsin london, abunda baki sani ba, jirgi ɗaya muka shiga dake. Ba mu fi sati a ƙasar ba, na lura duk in da za kije kina tare da Sharif, hakan ya sa na same shi, Allah ya taimake ni Sharif yana da sauƙin kai da saurin fahimta, a take yayi supporting ɗina har muka zama tamkar good friends da shi, yana ba ni information sosai a kanki, na daɗe da sanin Sharif, shi ma haka. Sai dai wani abu da ya sare mun gwiwa a lokacin da nake shirin zuwa gare ki, shi ne gaya mun da Sharif yayi kina da wanda kike so, kin ƙi kula kowa saboda shi, yanda y mun bayanin ƙarfin soyayyar da kike masa ya karya mun zuciya, amma ƙarfin nawa soyayyar ya hana ni rabuwa dake, har zuwa lokacin da kika kammala karatunki kao, kika dawo. Daga nan kuma aka fara kawo miki samari kina korarsu, har Allah ya sa mai martaba ya tura Muhsin wurinki, Muhsin ba mutum ba ne mai haƙuri, hakan yasa ake mamakin yanda abotanmu ta ɗore tuna halinmu ɗaya ba mai haƙuri, na tabbata da Muhsin bai san ina sonki ba, ba yanda za'a yi ki mishi yanda kika yi ba tare da ya ɗauke ki da mari ba, amma a maimakon haka, sai ya miki nasiha dan kawai ki natsu amma a banza. Ranar da Abbanmu ya zo mun da maganar auren wata, rasa gane kaina nayi saboda na san ba yanda za'a yi wata mace ta samu gurbi a zuciya ta idan ba ke ba, na tafi wurin Anty Sadiya ta gaya mun wai in je in sanarwa yarinyar ina da wacce nake so, na amsa mata da to kawai na bar wurinta, sam ban da niyar tafiya ko ina dan ba zan so kallon wata da sunan soyayya ba ma, da daddare bayan na dawo gida na kunna wayata, dai na ga Abba ya turo mun da address ɗin gidanku, na ji daɗi fiye da tunaninki, ba tare da wani tunani ba Washe gari muka shirya ni da Safwan zuwa gidanku, ban san me ya sake haɗa ki da shi ba lokacin da na koma ɗauko waya, amma ya fito rai a ɓace ya ja ni muka wuce, raina ya ɓaci amma na bi shi da niyar dawowa washe gari again, sai kawai da safe na samu kyakkyawan labari cewa ke da kanki kin ga hoto na, kin ce ni ne mai wanda kika tsaya jira, hakan yasa ja fahimci tabbas we're made for each other, shiyasa ke a mafarki Allah ya fara nuna miki ni, i'm really happy.... Hmm! Saura kwana ɗaya a ɗaura aure, na samu Anty Sadiya muka yi magana kan cewar ina tsoron ki bayyana halinki bayan aure, duk tsanarki za suyi saboda har su Sultana da Salma sun tsane ki kafin auren, ta gaya mun mafita ɗaya ne, tun da har kina so na sosai, idan ja nuna ba na sonki ba za ki ji daɗi ba, ita kuma za tayi amfani da haan wurin gaya miki halayenki ne ba na so, idan kika sauya za mu zauna lafiya, na fahimtar da ita ko da ace na nuna miki irin son da nake miki, tsab za ki sauya idan na buƙaci hakan, sai dai ta ce a fahimtar da tayi, na fi sonki fiye da son da kike mun, idab na nuna miki haka zai yi wuya kiyi yanda nake so, saboda za ki ga irin yanda nake sonki za ki iya yin abunda kike so ha zan iya rabuwa da ke ba. Duk abunda kika ga ya faru ko nayi miki bayan aurenmu, babu ra'ayi na a ciki, tsarin Anty Sadiya ne, waya da kika ga ina yi, wani lokacin ba waya nake yi ba wani lokacin kuma da Muhsin ne muke hakan, a duk lokacin da na ga hawayenki, ji nake zuciya ta tamkar

ana hura wuta a ciki, sai in ji kamar in gaya miki gaskiya, da kike ganin ina hanaki shiga ɗakinki sai lokacin da na tashi, ina yin hakan ne saboda idan kika zauna a gaban TV zai iya ɗauke miki yankai daga tunanin da kike yi, dan na lura idan kika shiga ɗaki tunani kike yi sai kiyi ta kuka. Sau da yawa na gaya wa Anty Sadiya kin sauya,  zan gaya miki gaskiya, sai ta ce in ƙara haƙuri, abunda Anty Saudat ta miki ne ya tunzura ni har na ji wannan karon ba zan ji maganar Anty Sadiya ba, zan yi abunda ya dace ne. Wannan gidan kuwa, na san kin fahimci komai na gidan nan yanda kike da buri ne ko? A wurin Sharif na samu information ɗin yanda kike so gidanki ya kasance, infact ma tare da shi muka nemi architect ɗin da ya zana gidan, na gina gidan nan da sunan Sunaiha ba Ƴar Senator ba, shiyasa na ce mu zauna a wancan har xuwa lokacin da za ki zama Sunaiha. Hotunan ki da kika gani, wasu ni na ɗauke ki su da kaina, wasu a wurin Sharif na samu, wasu kuma a accounts ɗinki na social media na samu, na samu numbernki a wurin Sharif duk da ban san yaushe zan fara kiranki ba, amma na karɓa kuma nayi saving da Jewel ..... Dan Allah Sunaiha ki yarda da ni, wannan ba plan ɗin yau ba ne, na tsawon shekaru ne, Sharif ɗan uwanki ne, ki tambaye shi, he knows everything, ko daina zancen rabuwarmu please, idan babu ke a rayuwa ta wallahi ba zan taɓa moruwa ba, please" ya ƙarasa maganar yana durƙusawa gabanta, ba ƙaramin tausayinsa Anty Sadiya sIda Muhsin suka ji ba

Nannauyan ajiyar zuciya Sunaiha ta sauke, a hankali ta share hawayen idonta, ta mayar da madubinta a fuskarta, ta ce "are you done? I'm leaving" ta juya za ta wuce

Da sauri ya ce "Sunie"

Cak ta tsaya, saboda tana masifar jin daɗin sunan nan, shi kaɗai ne wanda ta taɓa jin ta kira ta da hakan, shi ɗin ma a mafarki, yau ne ta fara jin hakan a zahiri sai kuma ta ji ya fi na mafarki daɗi. Zuwa yayi gabanta ya tsaya, ya ce "ina za ki je? I'm so sorry Sunie, na san na ƙuntata miki da yawa, dan Allah kiyi haƙuri, nayi dan mu samu farinciki mai ɗorewa ni da ke"

Wani numfashin ta sake saukewa,  ta ce "farinciki? Mai ɗorewa?... Kayi abunda kake tunanin shi ne dai dai, right? Nima zan yi abunda shi ne nake ganin zai fi samar mana farinciki na har abada.... Sadeeq, kamar ba ka fahimce ni ba, tun jiya na gaya maka it's over between us"

"Kamar ya, Sunie?"

"Ba wata alaƙa tsakani na da kai Sadeeq, ba na sonka, na tsane ka, na kuma gaji da zama da kai, duk wannan tatsuniyar ba abunda na ji bare kayi tunanin na ɗauka ko na yarda, daga nan gidanmu zan tafi dan na ma fasa ɗaukar komai a gidanka, ba na buƙatar komai naka Sadeeq, ka aiko mun da takarda ta, ka je ka auri Jewel, nima in auri wana yake so na, Allah ya ba mu ladan zaman da muka yi, Ya sa hakan shi ne alkhairi"

Anty Sadiya ta ce "me kike cewa ne haka Sunaiha?"

Muhsin ya ce "dan Allah Sunaiha ki tsaya ki ji, wallahi ba ƙarya a maganarsa, yana sonki, kuma

ke ma haka"

"No, ba na son shi, kuma shi ma Jewel yake so ba ni ba, i repeat myself, ba ni ba Sadeeq" ba ta tsaya jiran komai ba, ta juya a fusace ta bar gidan

Sadeeq kusan mutuwar tsaye yayi, yama kallo har ta fita bai iya cewa komai ba, kalma ɗaya ke mishi yawo a kunne, 'na tsane shi'. Kallonshi suke yi, ganin bai motsa ba, ya sa Anty Sadiya ta taɓa shi, hawayen da suka taru a idanunshi suka zubo, abunda yayi matuƙar ba su mamaki kenan, hawaye a idin Sadeeq?

Muhsin ya ce "Sadeeq!? Be a man mana, ya haka? "

Rufe idonshi yayi da ƙarfi, sannan ya buɗe a hankali ya sauke numfashi, kaɗan-kaɗan yake taku baya-baya har ya zauna kan cushion, ya ce "that's what i'm afraid of, kin gani ko Anty Sadiya! Amma ba ki saurare ni ba, kin ji me ta ce? She hates me... She hates me, ta tsane ni fa kenan Anty Sadiya, ba ta so na, ta tsane ni!!!! " ya ƙarasa maganar da iya ƙarfinsa, ya miƙe tsaye yana watsi da wasu glasses da aka yi decorating kan center table da su, suka watse a ƙasa, idanunshi sun yi ja sosai, jijiyoyin kansa sun bayyana, ko dan yana farar fata ne, oho?

Da sauri Muhsin ya riƙe shi yana faɗin "calm down Sadeeq"

Anty Sadiya ma da jikinta ya mutu, ta ce "i'm sorry Sadeeq, abunda na so fahimtar da kai kenan a asibiti ba ka saurare ni ba, kayi haƙuri dan Allah " tayi maganar kamar wacce za tayi kuka........

IDAN KUN YI COMMENT DA YAWA, ZAN YI DA WURI, AKASIN HAKA KUMA, SAI DAI KU JIRA SAI TIGER YA SAMU KANSA 😂 HONESTLY SPEAKING KUN RAGE COMMENTS, AMMA KULLUM DAGA MASU COMPLAIN PAGE ƊIN YAYI KAƊAN, SAI MASU COMPLAIN AYI POSTING KULLUM... TO NIMA YAU NA ZO DA NAWA COMPLAIN ƊIN, COMMENTS SUN RAGE YAWA, EHE😎

♦💫♦💫♦

*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Some Time Prayer Doesn’t Change The Situation..But it Changes our attitude Towards The Situation, And Give Us Hope Which Changes Our Entire Life. “A Busy Life makes Prayers Harder, ut Prayers Make a Hard and Busy Life Easier.”_

*PAGE 63-64*

Najma na fitowa daga kitchen hannunta riƙe da bowl ɗin fruits salad da ta sa aka haɗa mata, sai kawai ta ci karo da Sunaiha da ke shigowa parlourn da sauri, ko kallonta ba tayi ba ta zauna bayan tayi jifa da glass ɗinta, kuka take yi sosai

Da mamaki Najma ke kallonta har ta zo kusa da ita, ta ajiye bowl ɗin kan center table, ta ce "Sunaiha!? Mene ne?"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Sunaiha ba ta da niyar ɗagawa ma bare ta amsa mata, sai kukanta take tayi. Najma ta ce "Sunaiha talk to me please, lafiya?"

Nan ma ba ta amsa ta ba, Najma ta fita daga parlourn zuwa harabar gidan, ɗaya daga cikin masu aikin tayi wa alama da hannu ya zo, da gudu ya ƙaraso. Ta ce "umm ya sunanka ma...na manta, umm ka ga lokacin da Sunaiha ta shigo?"

Ya ce "eh Hajiya naga lokacin da ta shigo, ina waje ma"

"Yawwa, ita da wa ta zo?"

"Ita kaɗai ce ranki ya daɗe, cikin adaidaita ma ta zo"

"Adaidaita?" Ta tambaye shi

"Eh, tabbas cikin adaidaita sahu na ganta"

Shiru ta ɗan yi kafin ta koma ciki da sauri. Har yanzu tana nan wurin da ta bar ta, tana ta kuka, gefenta ta zauna, ta ɗago fuskarta, ta ce "kalle ni nan Sunaiha, ki gaya mun meye matsalarki? Me ya faru?"

Ganin ba ta da niyar amsa mata ya sa ta ce "shikenan, kar kiyi magana, bari in kira su Mummy su dawo, may be su za kiyi musu bayani"

Tana ɗaukar wayarta, Sunaiha tayi saurin karɓa, ta ce "No Anty Najma.... please" sai ta sake sakin wani kukan

Najma da ranta ya fara ɓaci, a hasale ta ce "then talk to me! Kin sa ni a gaba kina kuka kuma kin ce kar in kira Mummy, then what's wrong?"

Tana ƙoƙarin daidaita kukanta, ta ce "mun rabu da Sadeeq"

"Kun rabu? Ya sake ki ɗin ne?"

"A'a, bai sake ni ba, amma ba zan koma gidansa ba"

"Amma me ya sa kike kuka? Kuma me ya hana shi ya sake ki? Na ga abunda yake so kenan ai"

Share hawayenta tayi, sannan ta zauna da kyau tana kallon Najma, ta ba ta labarin abunda ya faru tun daga daren jiya da ta gaya mishi tana so su rabu, har zuwa abunda ya faru yau da kuma kuma labarin da Sadeeq ɗin ya bata, tana kai wa ƙarshe ta ƙara da "ban san meyasa yayi

tsammanin plan ɗin shi zai yi aiki a kaina ba, ba zan koma gidansa ba har abada bare ya cika burinsa" ta ƙarasa tana share hawaye a karo na ba adadi

Shiru Najma tayi ta kasa cewa komai, Sunaiha ta kalle ta ce "why are you quite?"

Numfashi ta sauke ta ce "wasu abubuwa nake tunani da suka ɗaure mun kai, amma bari Sharif ya shigo, shi zai warware mana komai"

"Ban fahimta ba"

"Sunaiha akwai ƙamshin gaskiya a maganarsa, saboda idan ƙarya ne, ba zai sako Sharif a ciki ba"

Kallonta take yi da idanunta da suka kumbura saboda kuka, ta ce "kina so ki ce kin yarda da wannan ƙirƙirarren labarin?"

"Sunaiha ba ƙirƙirarre ba ne, he's telling the truth"

"That's impossible! Yaushe kika fara goyon bayanshi? Ina ce da shawarar ki nayi amfani saboda ke ma kin ga irin wulaƙancin da yake mun yayi yawa, then how could you change your mind all of the sudden?"

"Ba zan taɓa goyon bayan wani in ƙyale ki ba, amma ina so kiyi tunani a kai .. and after all, jiya na so zan gaya miki maganar da muka yi da Mummy, kin san cewar duk irin zaman da kuke yi da Sadeeq tana sane?"

"How?" Ta tambaye ta da mamaki

Nan ta gaya mata tattaunawarsu da Mummy, sannan ta ce "kin ga tun da har Mummy ta iya ƙyale ki bayan ta san da haka, tabbas akwai dalili, kar kiyi saurin barin mijinki Sunaiha, da ni kaina ina so ku rabu, amma bayan wannan maganar ta Mummy sai na ji ina son zamanku tare, dan jiki na yana ba ni akwai abunda Mummy ta hango miki"

Girgiza kai Sunaiha tayi, ta ce "i don't care Anty Najma, duk abunda Mummy ta hango bai dame ni ba, i've already made my final decision, ba zan kara zama da Sadeeq" ta faɗa rai a ɓace, ta miƙe za ta bar wurin, Najma ta ce "but you love him!"

"I hate him, i only love Najeeb" ta faɗa da ƙarfi ba tare da ta juyo ba, sannan ta wuce

Wani nannauyan numfashi Najma ta sauke, ta ce "oh God, i think it's all my fault, dan ni na fara tunzura ta akan abunda Sadeeq yake mata, yanzu kuma ban so su rabu ɗin amma ta ɗauki zafi sosai...well, ta in da aka hau, ta nan ake sauka, zan shawo kanta kafin su Mummy su dawo" daga haka ta miƙe ta bi bayanta

Sadeeq kuwa sun ɗauki tsawon mintuna ashirin ba wanda ya ce komai, numfashi Sadeeq ya sauke kafin ya miƙe tsaye zai wuce, Muhsin yayi saurin tsayar da shi, "ina za ka tafi?"

Kallonshi kawai yayi da jajayen idanunsa bai ce komai ba, Muhsin ya sake maimaita tambayar, sannan ya ce "i'm leaving, wurin su Hajiya zan tafi"

"But you're not suppose to leave like this, ka bari ka samu natsuwa first, saboda idan ka tafi gida a haka za ka sha tambayoyi ne kawai"

"Natsuwa? Muhsin kana tunanin zan samu natsuwa bayan abunda ya fito daga bakin Sunaiha? She's My Jewel Muhsin, but she hates me, then ta ya kake tunanin zan samu natsuwa?"

Anty Sadiya ta ce "ba ta tsane ka ba Sadeeq, she loves you"

"Idan na ji hakan a bakinta zan yarda, amma ba a wurinki ba"

Muhsin ya ce "Sadeeq, Anty Sadiya ce fa"

Hararar shi yayi, kafin ya fita daga ɗakin ya bar su, kai tsaye wurin motarsa ya nufa, ya bar gidan gaba ɗaya

Anty Sadiya ta ce "Muhsin what have i done?" Ta faɗa cikin damuwa

"You did the right thing Anty Sadiya, don't blame yourself"

"Amma kamar Sadeeq is blaming me for everything"

"He's not blaming you, kawai dai ranshi ne a ɓace and kin san halinsa, komai zai iya fitowa daga bakinsa yanzu, idan ya sauko zai ba ki haƙuri"

Jinjina kai tayi, kafin ta ce "to yanzu ya kake tunanin za mu ɓullowa al'amarin nan?"

"Yanzu ba wani abu da zan iya cewa, babu idea ɗin da zai yi aiki yanzu saboda Sunaiha ranta ya ɓaci yanzu, Sadeeq kuwa ya kasa tsayar da zuciyarsa ya natsu, so ki bari mu ba su kwana biyu, sai mu san abun yi"

"Haka ne kuma, shikenan to... Nagode sosai"

"Don't mention, yanzu mu je in ajiye ki gida, ko wurinsu Hajiya za ki tafi ke ma?"

"A'a, ba zan tafi ba yau, ka kai ni gida"

Daga haka suka fito daga parlourn, suna jan ƙofar ta rufe kanta, sannan suka bar gidan mai gadi ya ci gaba da kula da shi kamar yanda ya saba

Har kusan ƙarfe uku na rana, Sunaiha tana ɗaki, ta ƙi fitowa ma bare Najma ta samu tayi mata magana. Tana parlour a zaune sai ga su Hajiyar London da Mummy sun shigo, Sharif na bayansu.

Zama suka yi ta musu sannu da zuwa, Mummy ta ce "mun bar ki ke kaɗai ko"

Hajiyar London ta ce "ai ita ta zaɓi hakan, ba ta son shiga mutane"

Sharif ya ce "kuma wallahi Sis in gaya miki kin yi missing, har gidansu Tiger sai da muka tafi, sun iya ƙarɓar mutane sosai, mun tafi wurin su Grandpa ma, i'm so glad to meet them all"

Najma ta ce "waye Tiger?"

"Oh, sorry...Prince ɗin Sunaiha"

Hajiyar London ta ce "dan Allah ni tashi ka bani wuri sharhabilu kawai, mutum sai surutun tsiya!?"

Dariya yayi ya miƙe daga kujerar, gyara zaman da za tayi ta ga wayar Sunaiha, ta ce "a'a, wannan wayar kamar ta Baby ko? Ta zo nan ne?"

Najma ta ji gabanta ya faɗi, ta ce "eh ta zo"

"To ya aka yi ta manta wayarta, bayan a sanin da na mata 24 hours waya na hannunta"

Mummy ta ce "ai da kenan, yanzu ta rage"

Najma ta ce "tana nan ma, ba ta wuce ba"

Kafin wani yayi magana sai ga Sunaiha tana saukowa, har ta zo kusa da su ta zauna wurin Hajiyar London, murya can ƙasa ta gaishe su

Hajiyar London ta ce "kina da lafiya kuwa Baby?" Ta tambaye ta tana taɓa jikinta

Girgiza kai tayi a shagwaɓe, Mummy kuwa kwaɓe baki tayi tana kallon ikon Allah, Hajiyar London ta ce "gaya mun Baby, menene?"

"Rabuwa muka yi da Sadeeq"

Anty Najma ji tayi kamar ta buge bakinta, dan sam ba ta so su Mummy su ji ba. Zuba mata ido Mummy tayi tana kallo, Sharif ya ce "me!? Rabuwa kuma?

Hajiyar London a razane ta ce "wane irin rabuwa kuma Sunaiha? Me kike nufi?"

"Rabuwa dai irin na ma'aurata, mun rabu na har abada, na dawo gidanmu"

A fusace Hajiya ta ce "wannan ma zancen banza ne Sunaiha, dan Allah jokes aside, ni ba sa'arki ba ce"

Najma ta ce "tun ɗazu na so lallaɓa ta dan ta wuce amma sai yanzu ma ta fito daga ɗakin"

Kallonta Hajiya ke yi sosai, ta ce "lallai Sunaiha ba kya da hankali...Hajiya Binta kina jinta fa, day something"

Wani kallo Mummy ke musu, ta ce "ba wani abu da zance ai Hajiya, wannan zancen iskan ta san ba za tayi shi da ni ba"

Sharif kuwa da mamaki ya cika shi, ya ce "wai Partner gaya mun, shi Sadeeq ɗin ne ya ce ki dawo gida ko me?"

Ba abunda ta iya ce mishi sai numfashi da ta sauke

Sadeeq kuwa yana zuwa gidansu, kai tsaye parlourn Umma ya nufa, tana zaune ganin yanayin shi ya sa ta miƙe, ta ce "Sadeeq lafiya?"

Bai iya cewa komai ba ya zauna ƙasa, ita ma ta zauna kan kujera, ta sake cewa "Menene Sadeeq? Hawaye nake gani a idonka...kayi magana mana dan Allah ka tsorata ni" ta ƙarasa cikin damuwa

Hawayen da ke kwance a idanunsa ne suka zubo, abunda ya sake tsorata Umma kenan, jira take ta ji wa ya mutu, ya ce "Maa, ba ta so na, ta tsane ni, zuciya ta zafi take mun idan na tuna kalmar nan, Maa zan iya mutuwa wallahi" ya ƙarasa wasu hawayen na zuba

"Sadeeq wace ce? Yi mun bayani dan Allah, ka daina kiran mutuwar nan"

"My Jewel, she hates me"

"Jewel?" Ta faɗa da mamaki tana mishi wani kallo kafin ta ce "kana nufin har yanzu kana son

wannan yarinyar? Na yi tsammanin kun rabu tun bayan aurenka"

Da ƙyar ya ce "Maa ta ya zan daina son Jewel? Har da ke da kika fi kowa fahimtar waye ni kina so ki ce ba ki gane irin son da nake wa Jewel ba? Maa ina sonta, i can't do without her"

Umma ta ce "Sadeeq?! Anya kuwa Abbakar ɗina ne kai? Na manta when last da na ga hawaye a idonka, yanzu saboda wata mace ka zubar da ƙwalla dan kawai ta ce ba ta sonka? Autar mata ce ita ko me? Ka manta da ita, ga matarka nan, she loves you, ga Sarah kuma, to meye abun damuwa?"

"Hmm, Maa ba za ki gane ba ne, ba wacce za ta iya replacing ɗin Jewel a wurina har abada, infact matar ta wa ita ce Jewel ɗina, kuma ta tafi gidansu, ta ce ba ta so na Maa, she hates me"

"Wace matar? Ba dai Sunaiha kake so ka ce mun ita ce Jewel ɗin ba!?"

"Ita ce" ya faɗa a hankali

"To meyasa ba ka taɓa gaya mana ba?"

Shiru yayi kafin ya ce "wani dalili ne"

"Wane irin dalili?"

Ba tare da ya ce komai ba, ya miƙe ya hau kujera kawai ya kawanta yana kallon fankan ɗakin, Sai dai bugun zuciyarsa yake saurare ba wai juyin da fankan ke yi ba......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

FREE BOOK!!!!!!!

_Sometimes the people who are thousands of miles away from you can make you feel better than the people who are right beside you._

*PAGE 65-66*

Kusan mintuna goma Sadeeq yana kwance, kafin Umma ta takura mishi ya bata labarin abunda ke faruwa, ba abunda ya ɓoye mata daga kan farkon ganin Sunaiha da yayi, har zuwa irin zaman da suka yi bi sa shawarar Anty Sadiya, har zuwa abunda ya faru yau

Salati Umma tayi bayan ta sauke dogon numfashi, ta ce "yanzu Sadeeq duk wannanina matsayin mahaifiyarka amma ka ɓoye mun? To yanzu meye amfani haka? Na san tsakaninka da Sadiya sai Allah ba kwa ɓoye wa juna komai, amma akwai abubuwan da ya kamata ni ma in sansu a matsayina na wacce ta haife ka"

Cikin damuwa sosai, ya ce "i'm sorry Maa, amma dan Allah ki gaya mun me zan yi"

"Me za kayi kuwa? Ai aikin gama ya gama kuma"

"Kamar ya? Na rasa Jewel kenan? "

"Eh mana, ba tana gidansu ba? To me zan maka yanzu, the best thing kawai yanzu ka tura mata da takardar saki, saboda duk wacce za ta furta maka kalmar tsana, to ba za ta taɓa sonka ba"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Sake rikice wa yayi da jin zancen Umma, ya ce "Maa wallahi tana so na, na sani kawai ɓacin rai ne, ba zan iya sakinta ba sai dai idan mutuwa kike so in yi, infact Maa, nima fa nayi ta gaya mata ba na sonta kuma ba da gaske bane, ita ma haka ɗin ne, dan girman Allah Maa help your only son, tell me what to do, i can't do without her, i so much love her, i love her more than anything in this world, dan Allah Maa ki taimaka mun, bring My Jewel back to me, please" ya ƙarasa maganar zafafan hawaye na bin kyakkyawar fuskarsa

Ba ƙaramin tausayinshi Umma ta ji ba, amma ta basar, ta ce "yanzu ka san ina nan? Yanzu ka san zan iya taimaka maka bayan ka gama wulaƙanta ƴar mutane ka ci zarafinta sannan yanzu za ka ce in dawo maka da ita, haba Sadeeq, muyi wa junanmu adalci, idan da Saudat ce ko Sultana kai ka san ba zan bari ta koma wurin mijin da ya mata irin abunda kayi wa ƴar wata ba saboda ƴa ba ta fi ƴa ba... Just recently, shekara biyu da suka wuce, na san ba ka manta da abunda ya samu Saudat ba, da kuma irin hukuncin da ka ɗauka, to sai a kan ƴar mutane kuma zan nuna son kai? Ka san ba halina bane"

Tana maganar ji yake kamar ya fe tayi shiru, sabida ƙara mishi wani zafin take yi, kasancewar ta mahaifiyarsa, sai ya daure ya ce "Maa na san ban kyauta ba, kuma zan gyara kuskure na i promise, after all, duk abunda nayi saboda ina sonta ne nayi, kuma wallahi na fi ta cutuwa da hakan"

Harararsa tayi, ta ce "hmm, ka san me!?  Tashi ka fita, ni za ka kalla ka ce kana sonta? Nima irin tunaninta nake yi fa, you plan everything, wa ya gaya muku ana gyara mutum ta haka? Kai da Sadiya wannan karon ba ku kyauta ba, dan haka ni ba wani abu da zan yi"

Durƙusawa yayi gabanta, ya riƙe hannunta, ya ce "Maa dan Allah, ke kaɗai za ki fahimce ni shiyasa wurinki kawai na zo, na ji ban kyauta ba, zan gyara, ina matuƙar ƙaunarta"

A hankali ta cire hannunta cikin na shi ta ce "duk yanda kake sonta, sai ka kyale ta kuma dole ne, da kake cewa you can't do without her, wannan zance ne kawai, dan ko ni na mutu tsab za ka rayu sai idan kwananka ya ƙare, haka ma ita.... Kuma bari in gaya maka, wallahi idan iyayenka suka samu wannan labarin... Kai ka san sauran, musamman Alhaji ko Abbanku, gwara Kawu Ƙarami zai iya supporting ɗinka.... Ni ka ga tafiya ta"

Ta miƙe xa ta wuce, ya sake riƙe ta, idanunsa cike da hawaye, "Maa dan Allah " ya kasa ƙarasa maganar

Kallonshi tayi ta ɗan rufe ido, ta ce "tashi ka tafi nace, zan kira ka" ba ta jira jin komai ba ta wuce ɗaki, saboda idan ta ƙara wasu daƙiƙu a wurin za ta iya zubar mishi da hawaye dan ba ƙaramin tausayinsa ta ji ba. Tana matuƙar son ɗanta, kuma ba ta taɓa ganinshi cikin wannan yanayin ba sai yau shiyasa duk jikinta yayi sanyi, ta daure ta mishi haka ne dan ya gane yayi kuskure abunda ya aikata.

Tunda ta wuce ya kasa gane abunda ke mishi daɗi, ga zuciyarsa sai raɗaɗi take masa, har jiri yake gani, da ƙyar ya iya barin part ɗin zuwa tsohon ɗakinsa ya kwanta, yayi sa'a kuwa duk yaran gidan ba wanda ya ganshi, Sameer da Sauban kuwa ba sa gida.

Umma kuwa tana jin fitarsa, ta dawo parlour ta zauna, ta kira wayar Anty Sadiya, bugu ɗaya ta ɗauka,  suka fara gaisawa, sannan Umma ta ce

"Sadiya na ji duk abunda ya faru, kun kyauta kenan? "

Da mamaki Anty Sadiya ta ce "Umma wa ya gaya miki? "

"Wa zai gaya mun banda Sadeeq? "

Ajiyar zuciya ta sauke, dama tsoron ta kar daga gidan su Sunaiha ne aka gaya musu, ta ce "Umma kiyi haƙuri, duk shiri na ne kuma wallahi duk abunda yayi ba da sin ranshi bane, yanzu kuma komai ya kwaɓe, na rasa abunda zan yi"

"Ai ba za ki san me za kiyi ba, yanzu meye amfanin ɓoye mana da kuka yi? Na san sanin halin Family ɗin nan ya sa kuka yi haka, amma at least ku gaya mun ko ku gaya wa Hajiya mana"

"Umma, na karɓi laifin gaba ɗaya, kiyi haƙuri dan Allah ki yafe mana... Yanzu ina Sadeeq, nayi ta kiransa bai ɗaga ba"

Umma ma numfashi ta sauke, ta ce "shikenan na ji... yanzu ya bar wurina, ban sani ba ko yana cikin gidan nan ba ko ya fita"

"To Umma ya za'a yi yanzu? Ni tsoro na ɗaya kar Abba ya san yarinyar nan har ta koma gidansu, kar ya ji abunda ya faru, tunda Alhaji ba ya nan, yanzu Abba nake ji"

"Ke ma kin san dole za su ji, amma ina so zuwa lokacin da za su sani, ta dawo gidan"

"Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un, to Umma meye abun yi? "

"Ina so bayan magrib ki je gidansu, dan ki dawo da ita, kafin nan ni kuma anjima zan kira mahaifiyarta muyi magana"

"To Umma, in sha Allah... Nagode "

"Sai anjima, ki gaida su Armaan" daga haka suka kashe wayar

Daga ɓangaren Sunaiha kuwa, ita ma ta gama zayyana musu komai kamar yanda Hajiyar london ta umarce ta, ta ƙara da "dan haka ni ba zan koma ba, na haƙura da shi "

Hajiyar london ta ce "yanzu irin wannan zaman kuka yi shi ne ba ki taɓa gaya mana ba?"

"Nayi tsammanin zai gyara ne, ashe ba haka bane,  dan haka ni na samar wa kaina kwanciyar hankali yanzu, zan zauna gidanmu ya je ya auri Jewel ɗin, nima Allah ya kawo mun wanda ya fi shi"

Sharif ya ce "ba da kar in faɗi ba dai-dai ba,  da sai in ce har abada ba za ki taɓa samun anda ya kai Sadeeq sonki ba, bare kuma ya fi shi"

Hajiyar london ta ce "kamar ya? Kana nufin duk irin abunda ya mata sonta yake yi? Wannan ai zancen banza ne, ina mishi kallon mai hankali ashe ba haka bane"

Sharif ya ce "duk abunda kika ji ta faɗa ba ƙarya a ciki, yana sonta sosai, ita ce ta rikita mishi lissafi, amma ya gaya mun yana so zai haɗa mata wani surprise party idan zai gaya mata yana sonta kuma ita ce Jewel, na tabbata sakin da ta ambata ne bai ba shi damar haɗa party ba"

"Wannan ba dalili ba ne Sharif, me zai sa ya mata abunda yayi yanzu dan kawai wani dalili na shi na banza"

Mummy ta ce "ba dalilin banza bane, Hajiya ya kamata ki yarda yaron nan yana sonta, ko da kuwa ban ji wannan labarin ba, ni na yarda yana sonta da gaske, saboda wannan shi ake kira soyayya ba irin wanda mahaifinta ke mata ba, ki gaya mun, Alhaji ya taɓa damuwa da Sunaiha ta gyara lahirarta? Ko ya taɓa damuwa da yanda take gudanar da al'amuran addininta? Alhaji ya taɓa gyara mata gobenta? Ko ya taɓa damuwa da yanda take mu'amala da mutane ko kuma ta kyautata wa iyayenta?... Hajiya ba ko ɗaya, shi kuwa Sadeeq duk waɗannan abubuwan ya gyara mata su wanda ba ita ba har mu mun ji daɗin wannan sauyin na ta, ke kanki kin faɗa tayi hankali, waye sila? Sadeeq... Sunaiha duk wanda zai ba da gudummawa a rayuwarka wajen ganin ka gyara tsakaninka da Ubangijinka, to shi ne babban masoyinki a duniyar nan"

Sunaiha ta ce "Mummy kina nufin Sadeeq ya fi mahaifina so na kenan? "

"Ba haka nake nufi ba, ba wanda zai kai iyayenki sonki, amma akwai wanda zai iya fin iyayenki kula da ke, kamar dai yanzu yanda kika gani, mahaifinki yana sonki amma ba ya iya kulawa da ke, shi dai kullum burinsa me kike so kawai ya ba ki and that's all, ni kuma ba kya saurare na ma bare in miki abunda ya fi dace wa, wataƙila addu'ar shiriyar da nake miki ne Allah ya karɓa har ya haɗa ki da Sadeeq saboda ya zama silar shiriyar ki ɗin, kuma ina ƙara gode wa Allah a kan haka"

Numfashi Sunaiha ta sauke ta ce "Mummy ni fa na gaya miki, ba zan koma ba, na ji ya taimaka mun wurin gyara ɗabi'u na kuma na gode, amma ni da gidan Sadeeq har abada"

Najma ta ce "wai ke meye matsalarki ne? Ana nuna miki gaskiya kina bijire wa"

Mummy ta ce "manta da ita Najma, ni na haife ta ai ba ita ta haife ni ba, wallahi ko kina so ko ba kya so sai kin koma gidan Sadeeq kuma a yau ɗin nan, idan har kika ga kin kwana a nan gidan, to shi Sadeeq ɗin ne da kansa ya buƙaci hakan, amma ko yau ko Alhaji bai isa ya bar ki a gidan nan ba" ta ƙarasa rai a ɓace

Sharif ya ce "Tiger ma ba zai yarda ta kwana a nan ba"

Hajiyar london ta ce "Binta, zan so ki bi komai a hankali... "

"Hajiya, this is my final say, i'm sorry " ta miƙe ta bar musu ɗakin, Sharif ma fita yayi yana ƙoƙarin kiran Tiger

Hajiya kuwa sai rarrashin Sunaiha da ke ta faman kuka take yi, "Hajiya bana son shi, har yanzu Mummy ba ta fahimci irin azabar da na sha a gidan ba"

"Ta fahimta Baby, ita mahaifiyarki ce, ki yarda kawai yana sonki"

"Ba ya so na Hajiya, ni na san wacce yake so wallahi, ki yarda da ni, it's all plan "

Najma ta ce "wa yake so? "

Tana share hawaye ta ce "Sarah"

Hajiyar london ta ce "wacece Sarah? "

Ba abunda ta ce mata, ta sake kwanta wa kan jikinta tana kuka

Sarah ce tare da ƙawarta Jamima, sun fito daga lectures, Sarah sai kallon wani hoton Tiger take tana murmushi, Jamima ta ce "wallahi Sarah kin kusa cin kai, tun lokacin da kika ƙwallafa rai a kan mutumin nan kika daina samun natsuwa, kullum sai kin sa shi gaba kina kallo"

Ƙayataccen murmushi Sarah tayi, ta ce "bari kawai Jamima, wallahi ina son gayen nan to the core, i love him"

"Amma ban ga alam ba ai"

"A haka? Duk yanda nake jin shi a raina amma ba ki gani ba? "

"Ban gani ba ni dai, saboda har yanzu ba kiyi abunda za ki mallake shi ba, wai ke kina jira sai ranar da ya gane Jewel ɗin shi tayi aure"

"Eh mana, to me kike so in yi apart from this? "

"Sarah da sauranki, yanzu idan ya gane Jewel ɗin tayi aure, kar ki manta fa yana da mata, kuma ta fi ki kusanci da shi yanzu duk da ba sonta yake yi ba, amma baza ta ƙyale shi haka ba, tarairayarsa za ta dinga yi fiye da tunaninki, kyautatawar da za ta mishi shi zai sa ya manta da Jewel ɗin har ya fara sonta, ke kin tashi a tutar babu kenan"

Sarah ta ji gabanta ya faɗi, ta ce "to ya zan yi ni yanzu? Soyayyar sa ta dawo mun sabuwa kuma yanzu, i don't want to loose him"

"Abu ɗaya za kiyi, ki nemi kusanci da shi sosai fiye da wanda kuke da shi yanzu, ki shiga jikinshi sosai yanda idan yayi kwana ɗaya bai ji ki ba ko ba ganki ba, zai neme ki, hakan ne kawai zai sa ki same shi bayan babu Jewel"

Shiru tayi tana jinjina kai alamar ta gamsu, sannaj ta ce "nagode sosai Jamima, sam wannan dabarar ba ta zo mun ba"

"Ba komai, ai ni dake abu ɗaya ne"

"Kin ga yanzu ma bari in tafi gidansu"

"Akwai wani lectures ɗin fa"

"Manta kawai, mu haɗu gobe" ta miƙe cikin rawar jiki ta wuce

Murmushi Jamima tayi, ta ɗauki waya ta kira, sai da suka gaisa kafin ta ce "Hajiya nayi abunda kika ce, yanzu ma tana hanyar zuwa gidanku"

Murmushi Momi tayi ta ce "Good job Jamima, ki turo mun account number ɗin na ki in tura miki"

"To Hajiya, nagode sosai"

Suka kashe wayar a tare, Momi cikin murna ta ce "mu je zuwa dai, za ku sha mamaki"

Najeeb na tare da abokinsa cikin office ɗinshi, suna tattaunawa kan kasuwancinsu, sai da suka kammala kafin Najeeb ya ce "Nasir ka san me ya bani mamaki yau? "

"Me ya faru? "

"Ɗazu kamar a mafarki, na ga saƙon Sunaiha"

"Wace Sunaihar?"

"My cutie pie"

"Replying message ɗinka tayi ko kuwa? "

"Dan kanta ta turo mun wallahi, let me show you"

Ya ɗauki wayarsa ya miƙa mishi saƙon, kamar haka:
'There's no Special reason for this msg, I just want to steal a single moment out of your busy life and hope I can make u smile, Take care '

"Chirr, Najeeb kana ba ni tsoro fa, duk girman kan mace in dai ka nace mata, sai ta dawo nemanka" cewar Nasir

Murmushi Najeeb yayi ya ce "this is just the beginning ai Nasir, sai ta kawo kanta da kanta"

Dariya yayi, ya ce "to Allah ya tsare matanmu daga mutum irinka"

Shi ma Najeeb dariyar yayi, ya ce "idan kuka riƙe su da kyau, nothing will happen"

Daga haka suka ci gaba da firarsu........

HELLO FANS🙋 NA ZO DA MAGANA..... LITTAFIN ƳAR SENATOR FREE NE, BA NA KUƊI BA NE, KAR WACCE TA SAKE BA DA KUƊINTA A SAYAR MATA DA SHI, BA RUWANA, NI DAI FREE NAYI ABU NA, IDAN KIKA SAKE BA DA KUƊINKI MA WANI, RUWANKI NE, KAR WACCE TA SAKE MUN MAGANAR TA BADA KUƊINTA BA'A TURO MATA COMPLETE NOVEL ƊIN BA, YANZU NAKE KAN TYPING ƊIN SHI, BAN KAMMALA BA MA BARE IN SAYAR.... NA MAIMAITA FREE NE, FREE BOOK, FREE BOOK, NA DAI GAYA MUKU, EHE. MASU SAYARWA KUMA, BAN SANKU BA, AMMA ALLAH YANA GANINKU, KO DAI KU DAINA KO KUMA IN MUKU ALLAH YA ISA. I'VE WARNED YOU

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*

*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Keep ur HEAD up, so that people know you are afraid of no one, But... Keep ur EYES down, so that you are known to be a respectable person!!!_

*PAGE 67-68*

"That's impossible!!!" Cewar Senator cikin ɓacin rai bayan ya gama jin abunda ke faruwa daga bakin Hajiyar London, ya ce "wannan ai zancen banza ne, da wannan abu da yaron nan yayi kuke tunanin zan bari Baby ta koma gidansa!? Sam...wallahi Alhaji Usman ya bani mamaki, ban taɓa zaton zai bari ayi wa ƴa ta irin wannan riƙon ba, amanar kenan!?" Ya ƙarasa cikin tsananin ɓacin rai

Mummy dake zaune daga gefensa kasancewar su uku ne a parlourn dama, ta ce "ka ga Alhaji, gwara ma kar ka sako sunan Alhaji Usman a maganar nan saboda bai san komai ba, kuma shi kan shi yaron ban ga laifinsa"

"Ai ba za ki ga laifinsa ba tunda dama can baki taɓa ɗaukar damuwar Baby a matsayin damuwarki ba..."
~~~~~~~~~~~~~~~~

A fusace ta katse shi "nuna damuwar tawa kenan saboda ni na haife ta ba kai ka haifar mun ita ba...Alhaji na gaji da zuba maka ido kana lalata mun rayuwar yarinya, lokaci ne da zan yi magana kuma dole ka ji, Sunaiha ba za ta zauna a gidan nan ba wallahi, sai ta koma gidan mijinta kuma a yau ɗin nan"

"Binta!? Yau ni kike gaya wa magana haka? Ni kike tsammanin zan lalata rayuwar Baby? Duk ƙoƙari na in sama mata farinciki, shi ne kika kiran haka da lalacewa?"

"To akwai abunda ya fi hakan lalacewa ne? So kake fa ta dawo gida ta zauna, ka mayar mun da ƴa ƙaramar bazawara ko? To wallahi ba ka isa ba"

Hajiyar London ta ce "haba mana dan Allah, meye haka kuke yi sai kace ƙananan yara? Wannan fa ba abun tashin hankali bane, ku zauna a natse mu sasanta komai, meye na tayar da jijiyoyin wuya fisabilillahi ku fa ba yara bane"

Mummy ta ce "kiyi haƙuri Hajiya, amma yau sai nayi magana, Sunaiha sai ta bar gidan nan, domin ba ta da gidan da ya kai mata gidan mijinta bare ya fi shi"

"Zancen banza, kina nufin mijinta ya fi mahaifinta kenan" cewar Daddy

"Tabbas haka nake nufi,matsayinka daban na shi daban, amma ba wanda ya fi mijinta iko da ita a yanzu, kuma zaman ta a gidansa shi ne kwanciyar hankalinta kuma wurin samun lada, zama a gidan nan ba abunda zai tsinana mata face baƙin ciki da nadama, kuma ba zan bari hakan ta faru ba"

"Binta...!!"

"Enough Daddy.... please!" Cewar Sunaiha dake ƙoƙarin saukowa daga stairs ita da Najma, wanda hakan ya dakatar da Daddy daga maganar da yake shirin yi

Sai da ta zo tsakiyar ɗakin sannan ta zauna ta share hawayen idanunta, a hankali ta ce "Daddy, Mummy, dan Allah kuyi haƙuri, sam ba zan taɓa jin daɗi ba idan na ga hakan na faruwa tsakaninku saboda ni, dan Allah kuyi haƙuri"

Numfashi Daddy ya sauke, ya ce "Baby, meyasa duk abubuwan nan da suka faru ba ki taɓa gaya mun ba?"

Shiru tayi ba ta ce komai ba, ganin ba ta da niyar yin magana ne ya sa shi cewa "it's okay, ai yanzu komai ya zo ƙarshe, ba ke ba komawa gidansa, ai ba cewa nayi na gaji da ke ba, shi kuma Alhaji Usman zan same shi"

A hankali ta ce "Daddy, nima kaina ban gaji da ku ba ko kuma gidan nan, kuma na san yanda

ranka yake ɓaci a duk lokacin da nake cikin damuwa, you're the best Daddy...but i'm sorry to say, zan koma gidan Sadeeq"

Ba Daddy kaɗai ba, gaba ɗayansu sun yi mamakin yanda ta furta hakan kai tsaye, Daddy ya ce "what!?"

Jinjina kai tayi, ta ce "yes Dad, zan koma gidan Sadeeq...Daddy tun da na taso kake nuna mun soyayya wanda hakan ya rufe mun ido ba na jin zancen kowa sai naka, Mummy tana iya ƙoƙarin ta a matsayin ta na mahaifiya ta wajen ganin ta ɗora ni akan hanya mai kyau amma ina bijirewa, ba na ganin kan kowa da gashi, ba na mutunta kowa, mahaifiya ta ma kanta ba lallai in bi maganarta ba sai na ga dama, na tabbata sanadiyyar haka ne Allah ya jarabce ni, Daddy kayi haƙuri amma ba zan sake tsallake maganar Mummy ba, duk abunda ta ce shi zan yi"

"What are you saying Sunaiha? Za ki koma fa kika ce, kin manta irin abunda ya miki? To ni ba zan lamunta ba"

"Ban manta ba Daddy, amma zan koma saboda Mummy, ba dan ina so ba, amma zan faranta wa Mummy na. Daddy ka san tarbiyyarka na dinga ɗauka shiyasa Allah ya saka wa waɗanda na wulaƙanta ta hanyar haɗa ni da Prince, saboda Allah bai wulaƙanta bawansa ba, ba wanda ya isa ya wulaƙanta su ya ci bulus, sannan kuma Daddy kar ka manta na amfana sosai a auren Sadeeq, saboda shi ne na haɗu da Anty Sadiya har ta koyar da ni addini na, ta sa na gyara tsakani na da Ubangiji na, abunda ba ka taɓa damuwa da shi ba kenan Daddy, in da ka damu da gyara mun hakan, ba yanda za'a yi alhakin mutane ya bi ni....dan Allah kayi haƙuri idan ranka ya ɓaci, amma zan koma yau ɗin nan bayan magrib kamar yanda Mummy ta buƙata, i'm sorry" tana gama faɗar hakan ta miƙe tana kuka ta bar parlourn, Najma ta bi bayanta

Murmushi Mummy tayi ta ce "alhamdulillah,Allah na gode maka da ka nuna mun wannan ranar da Sunaiha ta fara gane gaskiya, alhamdulillah..wannan kuma duk aikin Sadeeq ne, Allah ya mishi albarka"

Ran Daddy in ya kai dubu ya ɓaci, wani kallo yake wa Mummy kafin ya ce "ba dai kin hure wa yarinyar nan kunne ba!? Shikenan ta koma ɗin, sai kun yi nadama"

"Ba zancen nadama Alhaji, ai na taɓa gaya maka, watarana sai Sunaiha tayi kuka da kai, kuma ga shi Allah ya nuna maka"

Hajiyar London ta ce "dan Allah ku sasanta kanku mana, to meye amfanin ku gyara auren ƴarku, ku kuma ku zo kuna irin wannan abun?"

Ba abunda suka ce, Mummy ta haura sama zuwa ɗakin Sunaiha, Daddy kuwa ya fita yana baza riga rai a ɓace, ya nufi masallaci

Anty Sadiya tun kafin sallar magrib take kiran Sadeeq bai ɗaga ba, daga baya ma kashe wayar yayi, haka ta haƙura ta nufi gidan su Sunaiha.

Mummy da Hajiyar London na zaune sun sa Sunaiha gaba suna mata nasiha, sai Sharif da ya shigo yanzu kusan tare da Anty Sadiya. Zama tayi ki a ƙasa ta gaida su saboda nauyinsu take ji, cikin fara'a suka amsa mata, sannan ta gaisa da Najma, Sunaiha kuwa ko kallonta ba tayi ba

Anty Sadiya ta kalli Mummy ta ce "Mummy dan Allah...."

Ɗaga mata hannu Mummy tayi ta ce "kar ki ce komai Sadiya, wallahi ni ba laifin da kuka mun sai dai in gode miki, yanzun nan muka gama waya da Umma ku take ta bani haƙuri har sai da na ji wani iri"

Murmushi Anty Sadiya tayi ta ce "ba mu kyauta bane ai Mummy"

"Sadiya na ce a bar zancen nan ya wuce ... Ga ta nan dama yanzu nake so Sharif da Najma su rakata, amma tunda ga ki, sai ku tafi tare"

Ba ƙaramin daɗi Anty Sadiya ta ji ba, ta ce "yanzu kuwa zan wuce da ƙanwa ta, mun gode sosai Mummy"

Najma ta ce "ni fa Mummy na so in tafi in ga wannan sabon gidan wallahi, Sharif sai yaba irin kyaun gidan yake yi, shi ne nake so in gane wa ido na"

Hajiyar London ta ce "ikon Allah, to ai sai ki bari gobe ki tafi ko"

"To ban san gidan bane ai" ta faɗa tana ɓata fuska

Sharif ya ce "haba, kina da ni, kuma za kiyi complain akan ba ki san gidan ba? Ai ni na sani"

Mummy ta ce "ai kuwa, ga na hannun daman Sadeeq nan"

Dariya suka yi baki ɗaya, kafin Sunaiha ta miƙe dan su wuce, sai da ta gama sallama da su gaba ɗaya, sannan ta ɗaga ido tana kallon stairs hawaye na bin fuskarta, tsab Mummy ta gane manufar hakan, ta tako zuwa gabanta ta rungume ta tana rarrashinta

Cikin kuka ta ce "Mummy for the first time Daddy yana fushi da ni, ko kallona ya ƙi yayi tun da ya dawo daga masallaci, nayi ta knocking ƙofar ɗakinsa dan ya buɗe muyi magana amma ya ƙyale ni...anya Mummy ba zan yi kuskure ba idan na tafi yana fushi da ni?" Ta ƙarasa hawaye na zuba

Hannu Mummy ta sata share mata, kafin ta ce "stop crying dear, ki je kawai ba abunda zai faru in sha Allah saboda ba wurin aikata zunubi za ki tafi ba, gidan aurenki za ki je..kuma kin san mahaifinki yana sonki sosai, ba zai iya fushi da ke ba, na tabbata wannan na wucin gadi ne, zai neme ki da kansa, ki tafi kawai"

Jinjina kai tayi tana ƙara share hawaye, sannan ta rungume Hajiyar London da Najma, ta miƙa wa Sharif hannu suka yi shaking hands irin na ƴan gayu kamar yanda suka saba, sannan ya kalle ta ya ce "pls smile a little bit My Partner, if not..."

Kafin ya ƙarasa ta ƙirƙiro murmushin da ya haska fuskarta, sannan suka fita, har wurin mota Sharif da Najma suka raka su kafin suka wuce

Tun da suka fara tafiya ba wanda ya ce komai har suka kai gidan. A tsakiya parlourn suka tsaya, Anty Sadiya ta ce "Sunaiha...."

Sunaiha tayi saurin ce wa "Anty Sadiya dan Allah ba ai na ji komai ba, Please leave me alone"

Kallonta take yi sosai, ganin yanda ta wani haɗe rai ya sa Anty Sadiya ta ce "shikenan, gud nyt" daga haka ta fita, Sunaiha kuwa ta samu wurin ta zauna

Cikin mota Anty Sadiya ta zauna ta rubuta wa Sadeeq saƙo sannan ta wuce, kamar haka:

'Idan ka gama fushi da ni, ka dawo gida ga matarka nan na kawo maka, GN"

Sadeeq yana ɗakinsa a kwance kasancewar ya samu yayi bacci bai ma san anyi sallah ba, tashinsa kenan ya ji saƙo ya shigo, kamar ba zai duba ba musamman da yake numbern Anty Sadiya ne, amma ya daure ya duba. Farinciki ne ya ziyarce shi lokaci ɗaya bayan ya gama karantawa, bai yi tsammanin za ta dawo yau ba, da sauri ya fito dag ɗakin zuwa parlourn su

Sauban da Sameer ne kawai a wurin sai karatusuke ta faman yi saboda jarabawa, da mamaki suke kallonsa saboda ba su san cewa yana ciki ba, Sauban ya ce "Ya Sadeeq yaushe ka shigo?"

Maimakon ya amsa mishi, sai ya tambaye shi "Abba ya dawo?"

"A'a, amma Ya Safwan ya shigo, har tambayar ka yayi, kuma ya kira wayarka ba ka ɗaga ba" cewar Sauban

Kallon tsaf Sameer ya mishi, ya ce "wai Ya Tiger lafiya kake ma kuwa?"

Numfashi ya sauke ya ce "i'm okay, Allah ya ba ku nasara"

Tare suka amsa da ameen kafin ya fita, bai kai mintuna uku da fita ba Sultana ta shigo, sai da ta zauna kafin ta ce "a gaida ƴan boko"

Sauban ya ce "kin zo ki hana mu karatu ko?"

"A'a, ai ba zan hana ku ba dan kar ku rama idan lokacin namu ya zo"

Dariya Sauban yayi, ya ce "to what's wrong? Ina Salma?"

Ɗan yamutsa fuska tayi ta ce "tana can ɗakinmu yau mun yi faɗa ai da tare za ka ganmu"

"Meyasa?"

"Wai na ce ta mun VTU ina so zan kira, saboda ni yau bankinmu na da matsalar network, amma ta ƙi"

Cikin ɓacin rai Sameer ya ce "dan Allah ka tashi ka bi ta ku fita, kun dame ni wallahi"

Sauban ya ce "kai dai za ka bi ta ku fita, saboda kai za ka mata VTU ɗin"

Hararарsa Sameer yayi, Sultana kuwa ta ce "meyasa shi zai mun?"

"Kin manta the same bank muke amfani da shi? Sai dai shi ya miki"

Sameer ya ce "ba zan yi ba"

Sultana ta harare shi ta ce "ai dama ban ce kayi ba, dan ba na so...zan je wurin Hajiya ai" ta miƙe ta fita

Sauban ya ce "wai me ya haɗa ka da Sultana ne kuma? Yau kwana huɗu kenan ina kallonku kullum sai kun yi faɗa"

"Ka rage sa ido, kayi karatu"

Murmushi Sauban yayi ya ce "ko dai saboda ka ganta da wannan saurayin ne?"

Ɗaga ido yayi ya kalle shi ya ce "ina ruwa na da saurayinta? Sauban ban son gulma wallahi"

Dariya yayi ya ce "shikenan na ji, idan tayi tsami ai gaya wa sauran za kayi, ni dai na san komai"

Ganin Sameer ya ɗauki gorar ruwan da ke wurin ya da shi tashi da sauri ya nufi ɗakinsa yana dariya

Sadeeq kuwa yana fita, a parlourn ƙasa suka haɗu da Sarah, cikin murna ta gaida shi, ya amsa ba tare da ya tsaya ba, da sauri ta shiga gabansa ta tsaya, ta ce "haba Sadeeq, ka tsaya mu gaisa mana, tun da yamma na tafi gidanka ba ka nan, shi ne na zo nan saboda ina tunanin zuwanka, amma sai yanzu da nake shirin wuce wa sannan ka zo"

"Lafiya kike ta nema na haka? Ai ina nan tun ɗazu"

"Lafiya ƙalau...ai kuwa Umma ma ba ta san kana nan ba, wurinta na zauna muka yi ta fira"

"Ayya...tunda kin ce lafiya ƙalau, bari in wuce"

Har zai wuce ta dakatar da shi, "to in zo ka ajiye ni?"

"Sorry Sarah, sauri nake yi, amma su Sameer na nan, kiyi musu magana za su kai ki pls" bai jira jin me za ta ce ba ya fice

Ranta ya ɗan ɓaci, amma kuma tayi murmushi ta ce "ba komai dai, duk da hakan na fahimci yanzu yana girmama ni, ji yanda ya mun magana cikin sanyin murya kamar ba Tiger ba" ta sake sakin wani murmushin ta fita, dama can da mota ta zo

A masallacin layinsu ya tsaya yayi magrib, ya jira aka yi isha'i sannan ya ƙarasa gida. Tana nan zaune cikin parlour, da dukkan alamu ko sallar isha'i ba tayi ba

Kusa da ita ya zauna yana ta fara'a, ya ce "i knew it Sunie, na san za ki dawo dan Jewel ba za ta taɓa barin Prince ɗin ta ba"

Wani wawan kallo ta mishi ta ce "um, na dawo..but don't deceive yourself, ba saboda kai na dawo ba, dan in faranta wa Mummy rai shiyasa na dawo, ba dan ina sonka ba, kuma zaman wucin gadi ne, dan dai ka sake ni nan ba da jima wa ba"

Gaba ɗaya ya nemi farincikin ya rasa, ya shiga yanayin da yake a ɗazu, ya ce "pls Jewel, stop saying all this, zuciya ta zafi take mun"

"Ina ruwa na ko wuta ke kamawa a ciki, it's none of my business, and for the last time, ka daina kira na da wannan sunan naka na ƙarya, i'm Sunaiha not Jewel, okay!?" Daga haka ta haura sama ta bar shi wurin da sanyayyen jiki

Ɗakin da suka shiga ɗazu ta tsaya tana kallo kusan mintuna biyu, kafin ta girgiza kai ta kalli

ɗayan ɗakin da ke kallon wancan ɗin sannan ta buɗe shi ta shiga

Sak irin wancan ɗakin yake, kalarsa, da tsarinsa da komai, banda furnitures, wancan Royal Furnitures ne, wannan kuma Italian, amma komai iri ɗaya, kallon ɗakin take yi sosai tana zagaya shi, har ta kai wurin gefen wani bango, kamar dai yanda a wancan ɗakin, wannan gefen yake cike tab da hotunanta, haka ma wannan gefen yake, cike yake tab da hotunan Sadeeq, daga tsakiyar su hoton da ta fara ganin sa ne, wanda yake a dpn Abbansa, ya fi sauran girma, daga ƙasansa anyi wani ƙayataccen rubutu, an rubuta 'MY PRINCE'

Kallon hotunan take ɗaya bayan ɗaya, ta ji muryarsa yana cewa "i'm sorry Sunie, na dan har yanzu kina jin haushi na, but it's matter of time, zan ƙyale ki zuwa gobe, before then, ga hotunan Prince ɗinki nan su taya ki fira kamar yanda nima na Jewel ɗina za su taya ni"

A fusace ta juyo ta kalle shi, ta ce "Prince? Ai bana da wani Prince for now, Prince ɗina ya daɗe da mutuwa ya bar ni, but very soon idan ka sake ni, na san my second prince yana jira na....amma wannan, never!!!" Ta ƙarasa tana kallon hotunan

Ta taka zuwa wurin, ta ja igiyar labulen, gaba ɗaya wurin ya rufe kamar ba komai, ta ce "i don't need this, ba na son kallon wannan fuskar a kusa da ni, kai ma dan Allah ka fita"

Da jajayen idanunsa yake kallonta, ya ce "Sun...."

Ta katse shi a tsawa, "i said leave!!!...i don't want to see your face, i don't love you, leave me alone for God sake"

Rufe idonsa yayi da ƙarfi, bugun zuciyarsa na ƙaruwa, ya juya da sauri ya bar mata ɗakin bai ko tsaya rufe ƙofar ba. Yana fita ta bi bayansa ta rufe ƙofar, sannan ta zame a wurin ta saki kukan da take ta riƙewa.......

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*

*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Never shortchange yourself for someone else, or else, you will lose your own identity._

*PAGE 69-70*

A wannan daren gaba ɗayan su ba wanda ya samu yayi bacci sosai, da tunanin da ke ransu. Washe gari da safe Tiger ya fara fitowa, sam bai so barin gidan ba, amma kiran da Kawu Ƙarami ya mishi ne ya sa dole ya fita ba tare da ya ganta ba

Ita kuwa tana kwance sai dai ba bacci take yi ba, sai kusan ƙarfe tara kafin ta samu ta tashi, wanka ta shiga tayi ta fito, sai a lokacin ta tuna da ba ta da kaya a nan gidan, gaba ɗaya suna can, tsaki tayi tana juye-juye

Kai tsaye ta nufi wurin ƙaton wardrobe ɗin da ke wurin, sliding ɗin shi tayi, baki a buɗe take kallon jerin kayan da ke ciki, set by set haka aka jera su, gefen atampopi daban, na less da materials daban, jallabiya da Pakistan dress daban, sannan english wears daban, ba ƙaramin ƙayata ta wannan tsarin yayi ba saboda duk wannan na cikin dreams ɗinta
~~~~~~~~~~~~~~~~

Sai da ta gama washe baki kafin ta kai hannu gefen atamfa za ta ɗauka, sai kuma ta dakata, ta koma gefen english wears ta ɗauko wasu kaya, baƙin wando ne mai kyaun gaske da haɗaɗɗiyar riga maroon, za ta kai mata rabin cinya, sai hair band shi ma maroon.

Sai da ta gama shafe jikinta da lotions da turare sannan ta saka kayan, tayi masifar kyau, wataƙila saboda ta daɗe ba tayi irin wannan shigar ba ne?

Fitowa tayi ta shiga kitchen ta haɗa wa kanta indomie sannan ta dawo parlour ta fara ci. Kiran Najeeb ne ya shigo wayarta,  sai a na biyu sannan ta ɗaga

Najeeb ya ce "hi dear,  ki yi haƙuri na ga saƙonki jiya amma aiki ya hana ni kiranki, sorry kin ji"

"Ba komai, ya aikin?"

"Da godiya amma ba daɗi"

"To Allah ya taimaka...ina cin abinci yanzu, bye"

"Abinci kuma? Sai yanzu kike yin breakfast?"

"Eh" ta amsa mishi

"Ni na san wannan Prince ɗin ba zai taba kulawa da ke yanda ya kamata ba, idan ni ne da kin yi breakfast tun 7am, amma ba matsaka, very soon ai za ki zama ta wa"

Ɗan bata rai tayi, ta ce "Najeeb!!..bye" Ba ta jira jin mai zai ce ba ta kashe wayar. Numfashi ta sauke ta ce "to meyasa ma rai na zai baci? Ai gaskiya ya faɗa, Sadeeq ba zai iya kulawa da ni ba, kuma very soon zan bar shi ɗin ai"

"Stop decieving yourself with this rubbish" cewar Ikram da shigowarta kenan

Kallon mamaki Sunaiha ke mata har ta zauna, ta ce "Ikram? Wa ya kawo ki nan?"

Ajiye mayafinta tayi kafin ta ce "tun da har ban kai matsayin da za ki gaya mun abunda ke faruwa ba, to Anty Najma ta gaya mun, kuma Sharif ne ya kawo ni"

"To ina Anty Najma da Sharif ɗin?"

"Anty Najma tana gida, Sharif kuma ya wuce.... Duk ba wannan ba, me na ji kina faɗa? Wa za ki bari?"

"Sadeeq mana, ba zan iya ci gaba da zama da shi ba, Najeeb nake so"

Wani kallo ta mata, ta ce "ƙarya kike yi, ba kya son Najeeb wallahi, Sadeeq kike so"

"Meyasa za ki faɗi hakan? Ni ke da zuciyata fa, na fi ki sanin abunda take so"

"Wataƙila haka ɗin ne, amma dai ƙarya kike yi ki ce ba kya son Sadeeq, to me kike yi a gidansa"

"Saboda Mummy na dawo ai"

Tsaki Ikram tayi, ta ce "Malama, na ji komai a wurin su Anty Najma da Sharif, wallahi bari in gaya miki, kar kiyi kuskuren rabuwa da Sadeeq, dan ina tabbatar miki da cewar ba za ki sake samun mutum kamarsa ba har abada, i'm telling you"

Kallonta kawai Sunaiha ke yi ba tare da ta ce komai ba

Sadeeq na office ɗin shi a zaune, gaba ɗaya ya kasa yin komai, sai ga Sharif ya shigo, kusan sallama uku yayi kafin Sadeeq ya iya dawo wa daga tunanin da yake yi, murmushin ƙarfin hali yayi sannan ya ce ya zauna

Gaisawa suka fara yi, Sharif ya ce "ya ai Oga Tiger? Tunanin me kake yi ne haka?"

"Sunaiha" ya faɗa a gajarce

"Ka daina damun kanka dan Allah, in dai Sunaiha ce na gaya maka she loves you, kawai ɓacin rai ne"

"Haba Sharif, ta faɗa ta sake maimaitawa, duk cikin ɓacin rai ne?"

"Of course yes, amma za ka gani da kanka"

Kafin Sadeeq yayi magana sai ga Muhsin da Safwan, zama suka yi kafin Safwan ya ce "so Sadeeq dama Sunaiha ita ce Jewel ɗin? Yanzu Muhsin ya ke gaya mun"

Jinjina kai kawai yayi, Safwan ya ce "ashe kuwa bari in shirya gaya wa jama'ar gida"

Da sauri Sadeeq ya ce "no Safwan, kar ka gaya musu yanzu"

"Why? Ni wallahi ba ka ji daɗin da naji ba da aka ce ita ce Jewel, ni ka san yanzu akwai mutunci da girmamawa a tsakanin mu, so i'm happy"

"But she's not happy" cewar Sadeeq

"Meyasa? Ba tana sonka ba?" Ya tambaya da mamaki

Muhsin ya ƙarasa mishi bayanin abunda ke faruwa, Safwan yayi shiru kafin ya ce "amma dai nake ganin kamar gaya wa mutane zai daidaita komai"

Sadeeq ya ce "i don't think so, Maa da Anty Sadiya kawai suka san da wannan zancen a gidan nan sai kuma kai yanzu, ina so sai ta daina wannan fushin da ni, idan mun dawo normal sannan sai in gaya wa kowa, but for now dan Allah kar su sani, more especially Anty Saudat"

Numfashi Safwan ya sauke ya ce "shikenan, Allah ya mana zaɓi mafi alkhairi"

"Ameen" suka amsa. Sharif ne ya fara musu sallama ya wuce kafin Safwan shi ma ya tafi dan akwai aiki a gabansa, ya rage Muhsin da Tiger suna tattaunawa

"Hajiya gani, what next? Me kike so inyi kuma? " cewar Jamima da ke tare da su Momi da mahaifiyar Sarah a wani wurin shan iska

Murmushi Momi tayi, ta buɗe jakarta ta ɗauko wani magani cikin leda ta miƙa mata, sannan ta ce "wannan, ina so ki tabbata kin ki zuba wa Sadeeq da Sarah a ruwa ko wani abu dan su sha, kuma ina so ya kasance suna tare"

Haɗe gira Jamima tayi wuri ɗaya, ta ce "kamar ya Momi? Ban fahimta ba, taya zan haɗa du wuri ɗaya kuma in ba su drink su sha? "

Momi ta ce "kiyi amfani da basirarki, amma dai ki sani, Sadeeq bai damu da sha drinks ba dan kar ma ki wahalar da kanki wurin zuba wa a drink ɗin, ki san yanda za kiyi, zan miki bayanin sauran ta waya... Yanzu zan tura miki da 50k ki sha ruwa"

Murmushin jin daɗi Jamima tayi ta ce "Momi abun bai yi yawa ba? Har yanzu fa ina da sauran waɗancan kuɗin"

"Kar ki damu kanki, ai kogi ma bai ƙi daɗi ba ko!? " ta faɗa tana murmushi

"To nagode sosai... Momi bari in tafi, ina ƙara makara"

"To sai na kira ki"

Miƙewa Jamima tayi ta wuce, Momi ta kalli Mahaifiyar Sarah da tayi jugum tana tunani, "Yaya lafiya kuwa? "

Dogon numfashi ta sauke ta ce "Basira ina tsoron kar al'amarin nan ya ƙi yiwuwa yanda muke so fa! "

"Ya salam Yaya! Matsala ta dakw you always think negatively, ni kin gan ni nan, idan na sa abu a raina ba na taɓa ganin rashin yiwuwarsa, kullum haske nake gani, ke ma ki sa hakan a ranki, just trust me"

Numfashin ta sake sauke wa bayan tayi nazari "shikenan, Allah ya mana jagora"

"Ameen, haka nake son ji....tashi muje in ajiye ki gida" tare duka miƙe suka bar wurin

Jamima kuwa tana isa makaranta, kai tsaye wani hall ta nufa in da ta tabbatar Sarah na wurin, ai kuwa tana nan, sai da ta zauna kusa da ita ta ce "Hi Babe"

Ɗaga ido tayi daga kallon wayarta da take yi, ta ce "wai yau ina kika tsaya ne? Na kira wayarki ba ki ɗaga ba, ga shi kin yi missing first lecture ɗin"

"Ya ɗauki attendance yau ma?"

"Eh mana, kuma ya ce it's part of our assessment"

"Oh gosh!" Jamima ta faɗa tana dafa kai, "anyway, na san yanda zan yi da shi, manta kawai"

"Hmm, Allah ya shirye ki"

"Ameen" ta faɗa tana dariya kafin ta ce "wai ya mutuminki? Ku haɗa jiya ɗin?"

Ɗan ƙaramin tsaki tayi ta ce "yeah, amma bamu zauna ba coz he's in hurry"

"To yaushe za ku sake haɗuwa?"

"Don't know"

"To zama za kiyi ki ce mun ba ki sani ba?"

"It's like akwai abunda yake damunsa ne shiyasa"

"Sarah, wataƙila ya gane Jewel ɗin shi tayi aure ne fa shiyasa yake cikin damuwa, kin ga yanzu lokaci ne da za ki nuna mishi kulawa"

Kallonta Sarah tayi ta ce "really?"

"I think so"

"Ai kuwa idan haka ne dole zan gan shi gobe dan in ji meye matsalar"

"Hakan ya kamata kafin a riga ki"

Ɓata fuska Sarah tayi lokaci ɗaya ta ce "amma kin san ina jin haushi sosai idan na je gidan nan na ga wannan tsinanniyar matar ta sa"

Tsaki Jamima tayi ta ce "to ina ruwanki da ita?! Ke, ba ma dole sai a gida za ki gan shi ba, ki shirya kawai gobe tunda ba mu da lectures, zan raka ki asibitinsu, sai ki gan shi"

Jinjina kai Sarah tayi ta ce "yeah, good idea, Allah ya kai mu"

"Ameen" Jamima ta amsa tana mata wani irin kallo, a ranta ta ce 'in dai har mahaifiyar ki ba ta jin haushi illata rayuwarki ba, to nima ba abunda ya dame idan na taya su wargaza ki, ai ko ba komai na samu what i deserves, 100k a cikin kwana biyu, uban wa ya isa ya bani su, kuma na san wasu na kan hanya in dai nayi yanda suke so....Allah ya kai mu goben lafiya' ta ƙarasa tana murmushin gefen baki tare da lumshe ido

Tun bayan tafiyar Ikram, Sunaiha ta kasa sukuni, sai tunanin maganganun ta take yi. Miƙewa tayi ta nufi wurin da hotunansa suke, ta yaye labulen ta zuba ma hotunan idanu tana kallo, kafin ta tsayar da idonta kan wani guda ɗaya da ya masifar burge ta, take hawaye duka ciko idonta

"I love you My Prince, i truly loves you...duk abunda na aikata maka cikin ɓacin rai ne, ba zan iya rabuwa da kai ba, ɓacin ran da ka sani ya sa nake tsammanin Najeeb is better than you saboda yanda yake nuna mun so a fili, amma yanzu na gane Najeeb is nothing compare to you, you're the best darling, I'm sorry"

Share hawayen tayi, sannan ta ci gaba "na sa ma Najeeb hope ɗin samu na, i have to clarify everything to him, zan ba shi haƙuri kawai ya manta da ni ya nemi wata, zan dawo mu fara sabuwar rayuwa me cike da so, kulawa da farinciki a cikinta, ina ƙaunarka Mijin Jewel" ta ƙarasa tana wani murmushi da ke fitowa daga ƙasan zuciyarta

Kusan mintuna goma tayi a wurin sannan ta shiga toilet tayi alwala ta dawo tayi sallar isha'i, sannan ta koma parlour cike da tunanin meyasa bai dawo ba tun safe? Bayan ta san yakan dawo ƙarfe biyu zuwa uku kafin ya sake fita. Ba ta gama tunanin ba kuwa sai ga shi ya shigo, ta ji wani sanyi a ranta amma a fuska kamar ba ta san ya shigo ba

Zama yayi kusa da ita yana kallonta, ya ce "Jewel i've been asking for your forgiveness

amma kina share ni, ko ba komai to, at least ki ɗan nuna kin damu da ni mana dan Allah, kin ga ban dawo ba meyasa ba za ki kira ni ki lafiya ta ba? Idan da mutuwa nayi kuma fa....?"

Wawan kallon da mishi mai kama da harara ya sa shi yin shiru, numfashi ta sauke a hankali tana rufe ido, kafin ta miƙe za ta bar wurin, ya ce "ba za ki ce komai ba?"

"Malam ban aike ka ba, so i don't care, okay!?" Ta faɗa a tsawace "abincinka na kan dinning idan ka ji za ka iya ci, kuma ba dan na damu da kai ya sa na girka maka ba, sai dan ina tsoro kar alhakin ka ya kama ni...and gobe zan fita da safe kar ka fe ban gaya maka ba"

Magana take ba ƙaƙƙautawa sai da ta kai ƙarshe, shi kuma zuba mata ido kawai yayi yana kallo, sai bayan ta bar wurin kafin yayi murmushi ya ce "i love you My Baby" sannan ya miƙe ya haura sama shi ma zuwa ɗakinsa dan yayi wanka

Sunaiha kuwa tana shiga ɗakin ta kwanta, ta shiga kiran Najeeb, bugu ɗaya ya ɗaga "Hello Cutie"

"Hi" ta faɗa fuskar nan ba annuri, "ina so za mu haɗu gobe"

"Why?" Ya tambaye ta da mamaki

"Idan muka haɗu za ka ji, ka turo mun da address ɗin wurin aikinka"

"To shikenan, yanzu kuwa" ya faɗa yana murna, ita kuma ta kashe wayar

Knocking ta ji, ta san Sadeeq ne kuma idan ya shigo ba sake mishi fuska za tayi ba, sannan ta tsani yanda take mishi ɗin, sai kawai tayi sauri ta ajiye wayarta kan bedside drawer ta rufe ido kamar mai bacci, hakan yayi daidai da tura ƙofar da yayi ya shigo

Zama yayi kan bedside drawer ɗin yana kallon cute face ɗin ta, ya ce "so cute and innocent, I love you My Jewel" ya faɗa yana murmushi

Hannunsa ya kalla da ke ɗauke da makullin mota, "wannan na zo kawo miki dan ki tafi wurin da za ki je, amma har kin yi bacci... kuma na san gobe ba lallai ki saurare ni ba, but i know what to do"

Wayarsa ya ɗauka ya shiga rubuta mata text kamar haka : Hi Wifey! Ina fatan rahamar Ubangiji ya kasance da ke a koda yaushe...duk wurin da za ki tafi you're free to go dear, na miki izini, sannan ga makullin ɗayan mota na kiyi amfani da shi, ina ƙaunarki.

Miƙewa yayi ya ajiye makullin kusa da wayarta, duk abunda yake yi tana jin shi, har zai tafi kuma ya dawo, ya ce "bari in gani ko tayi saving contact ɗina ma"

Take gabanta ya faɗi, ɗaukar wayar yayi, ya ga two mssgs sun yi appearing, ɗayan My Prince, ɗayan Najeeb dear. Mamaki ne ya cika shi, ko dai bai gani da kyau ba? Kasancewar wayar ba ta da security ya sa ya shiga message box ɗinta kai tsaye, duk wasu messages ɗin Najeeb kaɗan ne kawai bai karanta ba, zuciyarsa ba ta gama bugawa ba sai da ya karanta last message ɗin da ta mishi, sannan da address ɗin da ya turo yanzu

A ransa ya ke cewa "waye wannan Najeeb ɗin? Meye matsayinsa a wurinta? Me waɗannan saƙonnin suke nufi? What's going on here? What's all this rubbish?...Dama wurin shi za ta tafi kenan? Impossible!!!!" Gaba ɗaya ya gama fita hayyacinsa, jikinsa har rawa yake yi, ga bugun zuciyarsa na ƙarasa sauri, ji yake kamar ya tashe ta ya mata waɗannan tambayoyin, amma bai san meyasa ya kasa yin komai ba. Jifa yayi da wayar kan gadon ya fita

Tana jin fitarsa ta miƙe da sauri ta ɗauki wayar tana faɗin "what have i done? Meyasa na ajiye wayar a nan bayan na san ba ta a security? Allah ya sa bai gan komai ba, i'm sorry dear"

Jikinta ne yayi sanyi bayan ta shiga message ɗin, dan ko shakka babu ta san ya gani, kusan mintuna biyar, sannan ta ce "dole zan bar gidan nan da wuri, ba zan bari mu haɗu ba har sai na gama da matsalar Najeeb sannan zan dawo, i know how to explain myself, i will make him understand, zan gaya mishi komai kawai sannan in gaya mishi dalilin zuwa na wurin Najeeb"

Ta ƙarasa tana sauke numfashi da ƙyar........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_Never Try to Go Back And Repair The Past, That Is Impossible...But, Be Prepared To Construct The Future Which Is Predictable..._

*PAGE 71-72*

Washe gari da safe kusan ƙarfe bakwai Sunaiha ta bar gidan ba tare da Sadeeq ya sani ba. Ƙarfe 7:22am ya fito, kasancewar daren jiya ya daɗe bacci bai ɗauke shi ba, shiyasa bai tashi da wuri ba, ɗakinta ya wuce kai tsaye ba ta ciki, ya fito ya duba ko ina na gidan sama da ƙasa amma ba ta nan, wurin mai gadi ya nufa da sauri rai a ɓace

"Yaushe Sunaiha ta fita ne?"

"Tun ƙarfe bakwai ne yallaɓai" ya amsa a tsorace dan tun da yake mishi aiki bai taɓa ganin ranshi a ɓace haka ba

"Darn it" ya faɗa da ƙarfi yana dukan gate ɗin. Komawa yayi cikin gidan, ya samu wuri ya zauna yana ƙara tuna saɓon daya karanta

"Why Sunie? Why?....I can't bear all this" ya faɗa cikin wani irin yanayi. Ƙara harzuƙa yayi kuma, ya miƙe tsaye ya ce "Kaii!!! Impossible!! I've to kill that man in dai abunda zuciya ta ke gaya mun haka ne" Ɗakinsa ya nufa ya ɗauko ɗayan makullin sa ya bar gidan shi ma
~~~~~~~~~~~~~~~~

Sunaiha kuwa tana fita ta je ta samu wani wuri tayi parking motar, ta san ba zai yiwu ta je wurin yanzu ba, saboda zuciyarta na gaya mata Sadeeq zai iya zuwa tun da har ya ga address ɗin. Kiran Najeeb tayi ta gaya mishi wani wurin, ta ce su haɗu a can kawai, duk yanda ya so ya san meyasa ta sauya wuri, amma ta ce idan ya zo za ta gaya mishi

Sadeeq bai tsaya ko ina ba sai kampaninsu Najeeb, mafi yawan ma'aikatan sun fito kowa ya fara aikinsa, reception ya tafi ya samu wata budurwa tana duba computer, sallama ya mata kafin ya ce "office ɗin Najeeb nake nema"

Kallon tsab take mishi, ya masifar tafiya da imaninta, anya ta taɓa ganin kyakkyawan mutum irin shi a zahiri kuwa? Take tambayar kanta

Ganin irin kallon ya ƙara hasala shi, ya ɗan daki table ɗin gabanta, "magana nake, ina ne office ɗin Najeeb"

Sai a lokacin ta dawo hayyacinta, ta ce "oh sorry! Um...Yallaɓai Najeeb kake nufi?...Ba ya nan, amma waye kai?"

Ji yake kamar ya zabga mata mari haka kawai, ya ce "sanin ni waye bai da amfani..."

"Amma aiki na nake yi"

Shiru yayi kuma dan ya san ta fi shi gaskiya, aikinta take yi, wannan fushin ba zai yi maganin komai ba, numfashi yake saukewa a hankali, ya ce "i'm sorry"

Ganin ya bata haƙuri cikin sanyin murya ya sa ta ji wani irin daɗi, ta ce "ba komai....lafiya?"

"Najeeb nake son gani"

"Kayi haƙuri amma bai shigo ba"

"Yana kai ƙarfe nawa kafin ya zo?"

"Ko wane lokaci yana iya zuwa, amma ba ya zuwa da sassafe haka, sai kusan 9 to above"

Shiru yayi yana shafa fuska, sai kuma ta ce "kamar kana buƙatar ganinshi da gaggawa, amma meyasa ba za ka kira shi ba"

Kallonta yayi ya ce "ban fito da wayar ba, na manta" ya sharara mata ƙarya

"Well, bari in kira shi mu ji ko ƙarfe nawa zai zo yau"

"Da kin taimaka mun kuwa"

Kiran Najeeb tayi, yana ɗaga wa suka gaisa sannan ta ce "Yallaɓai kana da baƙo"

"Baƙo kuma?" Ya amsa

"Eh"

"Waye?"

"Nima dai ban taɓa ganinshi a nan ba"

"Alright then, ki gaya masa ba zan fito yau ba, ya dawo gobe"

"Amma Yallaɓai, like it's urgent"

"If it's urgent, he'll give me a call ko waye"

Jinjina kai tayi jin yanda ya amsa mata a tsawace, ta kashe wayar, ta kalli Sadeeq ta ce "Sorry, ya ce kayi haƙuri ka zo gobe, akwai uzurin da zai hana shi fitowa yau"

"Haka ya gaya miki?" Ya tambaye ta da mamaki

"Ƙwarai kuwa"

Ajiyar zuciya yayi ya ce "shikenan, thanks"

Bai jira jin ta bakinta ba ya fita da sauri, yana shiga mota ya jingina da jikin kujera, ya ce "ba zai zo ba? Sannan Sunaiha ta fito tun ɗazu, does that means sun canza wurin haɗuwa ne ko me?...Amma me zai sa ta zo wurin shi da safen nan haka? Me hakan ke nufi?...I need to know who's he and where he lives, i must do something"

Yana gama faɗar haka, wayarsa tayi ƙara, ɗaga wa yayi kasancewar Kawu Ƙarami ne, sai da suka gaisa sannan ya ce "Sadeeq, kai da muka yi da kai kan cewar za mu fito 6:30 mu ƙarasa aikin nan, amma kalli har 8:04am ban ganka ba, meye hakan? Meyasa ka rage ɗaukar patients ɗinka da muhimmanci ne?"

"Kayi haƙuri Kawu, i'm on my way"

Bai amsa mishi ba ya kashe wayar. Cike da ɓacin rai Sadeeq ya ce "duk lokacin da nake buƙatar time dan in yi something very important, lokacin Kawu Ƙarami ke kira na, Why? Sai kace ni kaɗai ne doctor a wurin!? Meye amfanin sauran to?"

Shiru ya ɗan yi kuma dan ya ga bai kyauta ba ya faɗi wannan maganar, ko ba komai ya san

Kawu Karami yana gaya mishi ya fi yarda da ƙwarewarsa akan na sauran, patients da yawa na gaya mishi sun fi so ya duba su, to meyasa zai yi fushi kuma da irin baiwar da Allah ya masa? Numfashi ya sauke sannan ya tada motar ya nufi gida, ya ɗauki abunda zai ɗauka sannan ya tafi asibitin

Sai wurin ƙarfe da rabi sannan Najeeb da Sunaiha suka haɗu a wurin da ta gaya mishi, ba wuri bane mai cikar mutane shiyasa ta zaɓi wurin, zuwa yayi ya zauna yana ta murna da ganinta

Ya ce "Hi Cutie...wallahi kar ki so jin irin farincikin da nake ciki yau ɗin nan, i'm so happy to see you, nayi kewarki da yawa"

Kallonshi kawai take yi har ya kai ƙarshe, sannan ta sauke numfashi ta ce "Najeeb, ka san dalilin kiran nan?"

"Abunda nake so in sani dai kenan" ya faɗa yana ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya

"Najeeb, na san ka so ni, kuma har yanzu kana so na, i really appreciate that, thank you...amma dan Allah ka taimake ni ka taimaki kanka kayi haƙuri ka ƙyale ni, dan Allah" ta faɗa cikin murya mai sanyi

Kallon rashin fahimta yake mata, kafin ya ce "repeat yourself, ban gane ba"

Ganin yanda fuskarsa ta sauya ya sa ta yin shiru, kafin ta ce "Najeeb, try to understand what i'm saying, ka ga ni matar aure ce, kuma ina son mijina, shi ma yana so na, and we can't do without each other...na san na gaya maka zan rabu da shi in dawo wurinka, duk cikin ɓacin rai ne na yanke wannan hukuncin, dan Allah Najeeb zunubin ya isa haka nan for God sake, saboda kalaman da kake gaya mun sam bai kamata ka gaya mun ba a matsayina na matar wani, it's haram, dan Allah na roƙe ka let's forget the past, delete me from your heart and memory, let's go our separate ways please Najeeb, i......"

A tsawace ya katse ta har sai da ta razana ta rufe idanunta, ya ce "keep your mouth shut my friend!!!! Har kin isa ki tsaya kina gaya mun waɗannan maganganun? A tunaninki zan ɗauka ne ko me? Kin san yanda nake jinki a raina kuwa da har za ki ce in rabu dake kina son mijinki?"

Gaba ɗaya ta gama razana da shi, magana take so tayi amma ta kasa, da ƙyar ta iya furta "na..na sani Najeeb...i know you love me....amm...."

Wata tsawar ya sake daka mata "i said quite!!! Amma me!?.... To ki saurare ni da kyau Sunaiha, ni Najeeb da kike gani, wallahi duk abunda nake so sai na same shi, kar kiyi kuskuren nisanta kanki da ni dan ba za ki ji da daɗi ba, i love you kuma sai na mallake ki ko kina so ko ba kya so, ko da hakan na nufin sai na ga bayan shi mijin naki ne" yana gama faɗar hakan ya bar wurin a fusace

"Najeeb!! Najeeb!!...Najeeb" kiran shi take yi amma ko juyowa bai yi ba. Ta daɗe wurin a zaune, gaba ɗaya a tsorace ta ke musamman idan ta tuna kalamrsa ta ƙarshe, dogon numfashi ta sauke, ta ce "i don't want to lose you Prince... dole zan gaya ma sa komai dan muyi wa tubkar hanci tare, ba zan bar wannan abun a raina ba ni kaɗai, i can't manage it"

Wayarta ta duba, ƙarfe 9:11am, ta ce "ba zan iya komawa gida yanzu ba...to ina zan tafi kenan?..yeah, gidansu Ikram" ta faɗa lokaci ɗaya tana miƙewa tsaye

Ba ta tsaya ko ina ba sai gidan su Ikram, har cikin gidan tayi parking motar kafin ta ƙarasa ciki. Ikram na parlourn tare da mahaifiyarta, cikin girmamawa ta gaishe ta sannan ta zauna kusa da Ikram

Kallonta Ikram tayi ta ce "to ke me ya kawo ki yanzu da safen nan? Jiya fa muka rabu, har kin yi missing ɗina haka?" Ta ƙarasa tana dariya

Harararta Sunaiha tayi ta ce "ban son rainin hankali fa, ni ba ma wurinki na zo ba, wurin Umma na zo" ta faɗa tana kallon Umman Ikram da ke kallonsu tana murmushi

Sunaiha ta ce "Umma? Lafiya kuwa? Me ke damunki?"

Numfashi Ikram ta sauke ta ce "na ji daɗin zuwanki ma, ki taya ni roƙon Umma dan Allah ta bari mu tafi asibiti, wallahi ba ta da lafiya kusan kwana biyu kenan, ta ƙi yarda mu je asibiti, sai fama take da ciwo a tsaye"

Cikin tausayi Sunaiha ta ce "Ayya...amma Umma meyasa ba za ki tafi asibitin ba? Kar ciwon yayi yawa fa"

Umma ta ce "Sunaiha ƙyale ta kawai, ai na gaya mata jikin da sauƙi, yi yake yana taso mun ne shiyasa ban damu da zuwa asibitin ba"

"To Umma sai abun ya fi ƙarfin mu za mu tafi asibiti?" Cewar Sunaiha cikin sanyin murya

Ikram ta ce "ah to, help me ask her...Umma sai ka ce ba a birni kike ba? Kamar ƴar karkara"

Sunaiha ta ce "ke fa ba ki da mutunci wallahi, ai asalin kowa ne, kar ki zagi ƴan karkara"

Dariya Ikram tayi, sannan ta ce "Umma dan Allah ki bari mu tafi asibitin nan, ban so in rasa ki, ke kaɗai nake da ita a faɗin duniyar nan"

Umma ta ce "ai kowa ba zai wuce lokacin sa ba..amma zan tafi since you insisted, sai dai akwai wani asibiti da wata ta gaya mun idan na je na ga wani Dr, in sha Allah zai gane matsalar"

Sunaiha ta ce " wane asibiti ne, sai mu tafi yanzu"

"Saraki Hospital"

"Saraki Hospital? Asibitinsu Sunaiha kenan, na family ɗin su Sadeeq" Ikram ta faɗa

Umma ta ce "ai kuwa haka ne, wallahi sam na manta kuwa, in Allah ya yarda ma Sadeeq ɗin ne matar ke nufi, dan ta ce Dr Sadeeq"

Ikram ta ce "abu har gida, tashi mu tafi kawai Umma" ta ƙarasa tana kallon Sunaiha tana dariya

Sunaiha dai ba abunda ta ce har ta shiga ta ɗauko mayafinta da na Umma, suka bar gidan Ikram na ta zolayar Sunaiha, ba ta tanka mata ba, sai Umma da ke magana a madadin Sunaihar

Sadeeq na office ya gama duba waɗanda zai duba, ya tura sauran wurin wasu doctors ɗin dan gaba ɗaya ya kasa samun sukuni, ya rasa abunda ke mishi daɗi, so yake ya koma gida ya ga Sunaiha suyi magana, amma har yanzu Kawu Ƙarami ya ƙi barin asibitin ma bare har ya samu damar fita, yayi tsaki ya fi kala talatin

Kan shi na kan table, ya ji an turo ƙofa an shigo, ko ɗaga kai bai yi ba dan ya san ko waye, ya ce "Dan Allah Tahir ku ƙyale ni, ba zan iya duba kowa ba yanzu, su Dr Abbas su na nan da Dr Suhail, Please i need to rest"

Tahir ya ce "Yallaɓai ba patients ba ne, wasu mata ne su biyu, wai su na buƙatar ganinka"

"Wasu mata kuma?" Ya faɗa yana ɗaga kai

"Eh"

"Wa suka ce maka"

"Ba su gaya mun sunayensu ba, amma dai sun faɗi sunanka"

Shiru ya ɗan yi kafin ya ce "shikenan"

Tahir bai jira ƙarin bayani ba ya juya ya fita dan ya gane me yake nufi, bai fi mintuna biyu ba, sai ga Sarah da Jamima sun shigo

Har suka zauna yana kallonsu dan yayi mamaki sosai, me ta zo yi nan kuma?

"Barka da safiya babban likita" cewar Sarah tana murmushi

Murmushin ya ƙirƙira ya ce "Kina lafiya?"

"Alhamdulillah, ya aikin?"

"Ga shi nan muna kai"

"Allah ya taimaka ya ba ku lada"

"Ameen" ya amsa sannan suka gaisa da Jamima da ke ƙoƙarin gaida shi

Mayar da kallonsa yayi kan Sarah, ya ce "lafiya na ganki yanzu?"

"Eh lafiya amma ba lau ba....tun ranar da muka rabu da kai a gidansu Umma hankali na bai kwanta ba, nake jin kamar akwai abunda yake damunka, shi ne na ga a matsayina na ƙawarka yanzu, ya kamata in ji me ke damunka"

Buɗe baki yayi zai yi magana, tayi saurin ɗaga masa hannu ta ce "Tiger Please, na san halinka yanzu za ka iya mun faɗa akan hakan, dan Allah ka fahimce ni, kawai na damu da kai ne a matsayin ka na aboki na shiyasa, and nothing else"

Ɗan girgiza kai yayi ya ce "ba faɗa zan yi ba, kin damu da ni ne ai shiyasa, kuma ba kya cikin mutanen da zan dinga nuna wa ɓacin rai na kai tsaye tun ranar da na fahimci kina da wani matsayi a wurin Maa, kin san duk wanda take so ina son shi, duk wanda ba ta so kuma ba na son shi, that's it"

"Yawwa to alhamdulillah....then, me ke damunka?"

"Kawai yanayin rayuwa ne, but i'm ok"

"Anya kuwa?"

"In sha Allah" ya amsa mata

Kafin wata magana ta fito tsakaninsu, Jamima ta ce "kuyi haƙuri fa idan nayi interrupting, wai nikam Dr ba wani abun sha ne a nan?"

"Oh sorry, ba drinks amma akwai ruwa da coffee, bari in kira a haɗa muku" cewar Sadeeq

Jamima ta ce "a'a meye kuma sai ka wahalar da mutane, ai ga ni, zan haɗa mana ma gaba

ɗaya"

"Thanks, but i'm not in the mood of drinking anything, ki haɗa muku dai"

"Ni dai na mutum uku zan haɗa" ta faɗa tana miƙewa ta nufi ɓangaren da kayan haɗa coffee ɗin yake

Tana gama haɗawa ta juya a fakaice ta kalle su, hankalinsu ba ya kanta, da sauri ta buɗe maganin da Momi ta ba ta, ta saka a cup ɗin su, ta kawo ta ajiye musu sannan ta koma ta ɗauko nata

Sha take yi a hankali tana kallonsu, fatan ta kawai su ma su sha, amma ta ga Sadeeq sai faman rubutu yake yi cikin wasu files duk da ba daɗin aikin yake ji ba, hankalinsa na wani wurin daban, Sarah kuwa sai kallon shi take yi

Ganin ba su da niyar sha, ta ce "zai yi sanyi fa, kuma kun san ba daɗi"

Sarah ce tayi murmushi ta ɗauki na ta ta fara sha, shi Sadeeq bai ma ji me take cewa ba. Jamima na ganin Sarah ta kusan shanye wa ta miƙe ta ce "excuse me, ina zuwa"

Sarah ta ce "to sarkin yawo, ina nan ni dai"

Dariya Jamima tayi ta ce "na ji dai" a ranta kuwa ta ce "shashasha, ai dama so nake yi ka zauna a nan ɗin" sannan ta fice

Tahir na can kan table ɗin shi a zaune yana nashi aikin, Jamima ta same shi ta ce "sannu da aiki"

"Yawwa Malama, har kun fito?"

Murmushi tayi ta ce "a'a har na fito dai..Dr Sadeeq ya ce kar wanda ya shigo office ɗin sa yanzu, har kai"

Haɗe gira yayi cikin mamaki ya ce "har ni? Meyasa to?"

"Ban sani ba kam, amma haka dai ya ce, ka ga ai nima na fito...zan ɗan zaga asibitin in gani dai kafin in damu komawa ciki" ba ta jira jin mai zai ce ba ta wuce, shi kuwa mamaki ya cika shi, sai kuma ya ɗan ɗaga kafaɗa ya ci gaba da aikinsa

Jamima ba ta fi mintuna goma da fita ba, Sarah ta fara ganin jiri, dafe kai tayi ta miƙe tsaye, kallonta Sadeeq yayi ya ce "lafiya dai?"

"Sadeeq i'm feeling some how"

"Kamar ya? Menene?"

Tsayawa tayi tana buɗe idonta a hankali ta kalle shi, wurin da yake zaune ta nufa, kallonta yake yana so ya fahimci wani abu har ta ƙaraso, zama tayi kan table ɗin da ke gabansa, ta cire mayafinta ta ajiye gefe, hannu ta kai za ta taɓa shi ya miƙe da sauri ya ba ta wuri

A tsawace ya ce "are you out of your senses? What the heck!!"

Cikin wata irin murya ta ce "i love you Sadeeq"

Kallonta yake sosai yana wani tunani, miƙewa tayi ta ƙaraso kusa da shi, jiri ya sake ɗibanta ta faɗi kan kujerar da ke wurin, tana so ta tashi amma ta kasa. Tsab ya gama gane matsalarta da kuma dalilin hakan, zagayawa yayi ya ɗauko mayafinta ya ɗora ma, sannan ya nufi wurin cup ɗin da ta ajiye

Ya gama duba abunda zai duba, ya miƙe ya zo kusa da ita. Murmushi tayi da ta buɗe ido ta ganshi, sake cire mayafinta tayi ta jefar, gaba ɗaya ya kasa gane kanta, abubuwa take kala-kala, yayi tunanin fita ya bar ta, amma ya ga hakan bai dace ba, gwara ya tsaya yayi maganin abun kafin ya ji da waccan

Sunaiha su na isa asibitin suka nufi wurin da ake ganin likita, layi ne sosai a wurin, Ikram na murmushi tayi wa Sunaiha magana a hankali, "Madam a san yanda za'a yi da mu mana ba sai mun bi layin nan ba"

Harararta Sunaiha tayi, Ikram ko a jikinta, ta ce "a taimaka Please ranki ya daɗe" ta faɗa tanaɗaga mata gira ɗaya, duka Sunaiha ta kai mata a baya tana wani haɗe rai

Dr Suhail ne ya fito daga ɗakin da sauri, ganin Sunaiha a tsaye ya sa ya dakata, ya ce "Ah ah, Madam...barka da safiya"

Murmushi tayi ta ce "barka, ya aikin?"

"Da godiya ga shi nan muna ta fama ba daɗi"

"Haka ne, Allah dai ya saka"

"Ameen...lafiya dai na ganki a nan?"

"Eh, Ummata na kawo, ga ta nan a zaune"

Kallon Umma yayi suka gaisa, ya mata ya jiki, sannan ya mayar da kallonsa kan Sunaiha ya ce "to amma Madam meyasa kika tsaya nan? Dr Sadeeq yana office ɗinsa, da alama dai bai ma san kuna nan ba ko?"

"Eh bai sani ba, yanzu muka zo"

"To kin san me, ki je kawai ki mishi magana ya zo ya duba ta dan ba abunda yake yi, mu nan kin ga patients sun mana yawa"

"Shikenan Nagode"

"Ba komai" ya faɗa sannan ya wuce

Ko kallon Ikram ba tayi ba dan ta lura da irin kallon da take yi mata tana murmushi, Umma tayi wa magana kan ta jira tana zuwa, ta wuce ta nufi office ɗin sa

Wurin Tahir ta fara tsayawa suka gaisa cikin girmama juna, ta ce "Malam Tahir dan Allah Dr yana ciki kuwa?"

"Eh Hajiya yana nan, sai dai ya ce kar wanda ya shiga"

"Kar wanda ya shiga kuma? Meyasa?"

"To nima dai Hajiya ban sani ba, haka aka gaya mun, ba ya buƙatar kowa ya shiga"

Shiru tayi tana nazari, a ranta ta ce "ko dai saƙon da ya gani ne har yanzu abun ke damunsa ya kasa natsuwa?....Hmm, I'm sorry dear, zan maka bayani anjima, so sorry" tana gama faɗar hakan ta juya, sai kuma ta tsaya cak, ta ce "anya kuwa idan na tafi na kyauta? Ya kasa yin aikinsa fa saboda ni, i can't just leave him alone, zan shiga in lallaɓa kaya na"

Juyawa tayi ta kalli Tahir ta ce "Malam Tahir bari in shiga in gani"

"To Hajiya, amma dan Allah hakan ba zai shafe ni ko aiki na ba?"

"Kar ka damu, in sha Allah ba abunda zai shafe ka"

"To Hajiya, nagode"

Murmushi ta mishi sannan ta nufi hanyar ƙofar da sauri...........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_Nothing gives one person so much advantage over another as to remain always cool and unruffled under all circumstances._

**Page 73&74**

Tana shiga office ɗin, abunda ta gani ne ya sa ta kasa motsi, take idanunta suka ciko da hawaye. Tun ɗazu Sadeeq yake so ya ma Sarah wata allura, amma ta ƙi natsuwa, hakan yasa ya tashi da nufin zuwa ya kira wata Nurse dan ta riƙe ta, yana miƙewa ta tashi ita ma tana ƙoƙarin riƙe shi, haushin da ta ba shi ne yasa shi ture ta da ƙarfi, kaɗan ya rage ta bugi table, hakan ya sa ya jawo ta da ƙarfi, ai kuwa suka yi baya suka faɗi ƙasa a tare, ta faɗo kansa, wanda hakan yayi daidai da shigowar Sunaiha
~~~~~~~~~~~~~~~~

Ture ta yayi gefe ya miƙe tsaye da sauri ya nufi wurin Sunaiha da har ta juya, riƙe mata hannu yayi, ya ce "Sunie please don't misunderstand me, it's not what....."

Ɗaga mishi hannu tayi, ta share hawayenta, sannan ta ce "i'm sorry,ban san me ya kawo ni ba nima, sai da aka gaya mun ka ce kar wanda ya shigo, amma na ƙi ji, i'm really sorry"

"Sunie, dan Allah ki tsaya ki ji, let me explain, please....."

"I don't need any explanation, ka ƙyale ni" ta faɗa a tsawace hawaye na bin fuskarta, fizge hannunta tayi da ƙarfi ta bar office ɗin

Kallon Sarah yayi wacce har yanzu ba ta tashi ba, ba ta ma san me suke yi ba, juyawa yayi ya fita da sauri. Tahir na zaune ya ga fitowar Sunaiha da sauri tana share hawaye, sannan kuma yanzu ya ga Sadeeq shi ma ya fito da sauri, abun ya ba shi mamaki sosai, sam ya ma manta da Sarah tana ciki, sai da Sadeeq ya ɗan tsaya ya mishi magana kafin ya wuce

Jamima na gefe, tana kallon lokacin da Sadeeq ya wuce amma bata lura da Sunaiha ba, yana wucewa ta shiga office ɗin, Tahir na kallonta har ta shige, sannan ya taso a hankali ya jawo ƙofar ya rufe ta da makulli, Jamima hankalin ta ba ya wurin, gaba ɗaya ba ta ji ba

Har yanzu Sarah na ƙasa sai dai ta tashi ta zauna, tana dafe da kai, kallonta sosai Jamima tayi lokaci ɗaya fuskarta ta sauya dan ba ta ga alamar abunda take so ta gani ba. Wucewa tayi kan table ta duba cup ɗin da ta ajiye wa Sadeeq ta ga ko ɗaga shi bai yi ba

Ta ce "innalillahi, i think i've failed this plan.....yanzu ya zan yi kenan" ta faɗa tana kallon Sarah da ke ta juyi a ƙasa

Ɗan ƙaramin tsaki tayi kuma, ta ce "i've to leave, idan ba haka ba ina cikin matsala....da Sarah zan ji ko da Momi? Ko kuma Sadeeq? Dan i'm very sure ya fahimci wani abu"

Tana gama maganar ta ɗauki jakarta da sauri ta nufi ƙofar, janta take iya ƙarfinta amma ya ƙi buɗe wa, bubbuga ƙofar take yi tana kiran sunan Tahir, yana jinta amma ya share ta, dan ba ƙofar office ɗin Sadeeq kawai ya rufe ba, har main door ɗin shigowa office ɗin na su gaba ɗaya sai da ya rufe dan ma kar wani ya gan shi a bude ayi tunanin ko suna nan a shigo a ji ta, jin ta dame shi da kira ya sa ya kunna kallo a laptop ya maƙala earpiece ya ɗora ƙafa kan table ya ƙyale ta

Ganin babu sarki sai Allah ya sa ta haƙura da dukan ƙofar dan ba ta ma ji alamar akwai mutum a wurin ba, "i'm stuck over here, asiri na ya tonu" ta faɗa a tsorace. Da gudu ta ƙarasa wurin windows ɗin da ke office ɗin ta duba, ba yanda ma za'a yi ta fita ta window, sai ta zame a wurin kawai tana kuka, Sarah kuma na can gefe ita ma tana fama da na ta ciwon

Ikram kuwa suna can a zaune, sai ga Dr Suhail ya sake dawowa, kallon Ikram yayi ya ce "ba

ke ce kuka zo tare da matar Sadeeq ba?"

Ta ce "eh ni ce"

"To ina Madam ɗin?"

"Tun da ta je kiransa nima har yanzu ban ganta ba"

Murmushi Dr Suhail yayi ya ce "Mata da miji kenan, wataƙila ma sun manta da ku a nan" ya ƙarasa yana dariya kafin ya kuma cewa "ku shigo in duba ta kawai"

Duk da dai ba haka Umma ta so ba, Sadeeq ɗin ta so a ce ya duba ta, amma dole ta shiga haka nan, Ikram kuwa sai kiran Sunaiha take yi amma ba ta ɗaga ba, tsaki kawai tayi ta zauna jiran Umma

Sunaiha tana barin office ɗin, kai tsaye mota ta nufa ta bar asibitin tana kuka, Sadeeq ya lura da lokacin da ta fita daga gate ɗin, bai tsaya ɓata lokaci ba shi ka ya shiga motarsa ya bi bayanta

Gudu take har ta kai gida, tana shiga shi ma Sadeeq ya shigo, kafin ya gama parking motar ya fito har ta shige cikin gidan. Ɗakinta ta nufa ta mayar da ƙofar ta rufe da makulli, ta faɗa kan gado tana kuka iya ƙarfinta

Buga ƙofar Sadeeq ke yi yana cewa "Sunie dan Allah ki buɗe ƙofar nan, ki saurare ni in miki bayani, wallahi ba abunda kike tunani ba ne, it's not my habit, dan Allah ki buɗe"

Ko motsawa daga wurin da ke ba tayi ba, ya ci gaba da bugun ƙofar, ya ce "Please Jewel... please...ki buɗe, abunda kika gani ba haka bane wallahi, i can explain myself" ya faɗa cikin murya mai rauni

Da ƙarfi cikin kuka ta ce "to hell with your explanation!! Me za ka gaya mun bayan abunda na gani? Na daɗe da sanin kana son Sarah, amma ban taɓa tsammanin abun na ku har ya kai haka ba... Sadeeq na tsane ka, ba na son ganinka, ba ka son jin muryarka...dan Allah ka tafi ka bar ni dan Allah, Idan kuma ba za ka wuce ba, wallahi zan iya aikata komai cikin ɗakin nan, na rantse maka da Allah anything can happen" ta ƙarasa in a serious tune

Jin abunda ta faɗa ya sa shi ja baya daga ƙofar, ya ce "shikenan, don't harm yourself dan Allah, zan tafi, amma ki sa a ranki ke ce wacce Sadeeq ya fara so a rayuwa, kuma ke kaɗai ce har yanzu, kuma ke ɗin ce har abada" yana gama faɗar hakan ya juya jiki ba ƙwari ya bar gidan

Bai tsaya ko ina ba sai asibiti, ta ƙofar baya ya bi dan kar wanda ya gan shi, spare key ya sa ya buɗe main door na office ɗin, Tahir na ganin shi ya miƙe tsaye da sauri ya buɗe mishi waccan ƙofar, ya ce "tana ciki"

Da ƙarfi ya tura ƙofar, Jamima na ganin shi ta firgita ta miƙe tsaye, Sarah kuwa na gefe, ta rage jin abun da take ji amma jikinta ba ƙwari, ƙarasawa yayi kusa da Jamima, ya ce "wa ya aiko ki?"

Murya na rawa ta ce "ka..ka..kamar ya wa ya...waya aiko ni? Me nayi?"

Ƙyawawan maruka biyu ya ɗauke ta da su sai da ta kai ƙasa, jinta da ganinta ɗauke wa suka yi na wucin gadi, kusan mintuna biyu, sannan ta dawo hayyacinta, ta fashe da kuka, a tsawace ya ce "miƙe tsaye"

Ba musu ta tashi da sauri, ya sake cewa "wa ya aiko ki?"

Ko tantama ba ta tsaya yi ba ta ce "Momi ce" dan ta maru ba ƙarya

Ya ce "wa ce Momi?"

"Mominku, Auntyn Sarah"

Yayi matuƙar mamaki da jin hakan, amma bai musanta mata ba dan ya san za ta iya yiwuwa, kallon Sarah yayi a har yanzu idanunta a rufe suke sai dai ya san tana jin su

Ya ce ma Jamima "je ki ɗaga ta mu tafi"

So take ta tambaye shi wurin da za su tafi, amma ta san ko giyar wake ta sha ba za ta iya cewa komai ba, dan har yanzu tana jin zafin marin da ya mata har cikin kanta. Zuwa tayi ta ɗaga Sarah kamar yanda ya umarce ta, ya sa ta gaba suka fita

Ta hanyar da ya biyo ya shigo, ta nan ya nuna mata suka bi, sai cikin mota, ya zagaya ya shiga ya fizgi motar suka wuce, gabanta sai dukan uku- uku yake yi

Suna hanya ya ɗauki wayarsa ya kira Sameer, bugu ɗaya ya ɗauka, kafin Sameer ya ce komai, Sadeeq ya ce "kana ina?"

"Ga mu nan yanzu za mu shiga exams, lafiya dai Oga Tiger?"

"Umm" ya amsa masa sannan ya kashe wayar

Numbern Salma ya nema, ya kira ta, tana ɗaga wa ya ce "Kuna gida ne?"

"Eh Ya Tiger" cewar Salma

Ɗan lumshe ido yayi ya buɗe ya ce "ina so ki tashi yanzu ku tafi wurin su Grandpa ku duba

shi"

"Amma Ya Tiger jiya fa a can muka wuni"

Cikin ɓacin rai ya ce "umarni nake ba ki, i'm not asking you! Mintuna biyar na ba ku, kar ki kuskura in zo in same ku, gaba ɗayanku"

"To" ta amsa ba dan ranta yaso ba, ta kashe wayar, ya ba ta mamaki, meyasa zai tura su wurin Grandpa haka kawai. Sanin halinsa ya sa ta tashi da sauri ta gaya musu, ba ɓata lokaci suka shirya suka bar gidan, Hajiya sai mamaki take yi ita ma, lafiyar Sadeeq ƙalau kuwa?

Tafiyarsu ke da wuya, sai ga shi cikin gidan, ya tasa Jamima a gaba tana riƙe da Sarah har suka shiga main parlourn, Hajiya na zaune da Umma tana gaya mata hukunci irin na Sadeeq, haka kawai ya tura yara su bar gida

Ganin yanayinsa ya sa Hajiya da Umma suka fahimci ran shi a ɓace yake, miƙewa suka yi tsaye, Umma ta nufi Sarah tana taɓa ta, Hajiya kuwa ta kalli Sadeeq ta ce "Sadeeq lafiya?"

Bai amsa ta ba, sai ma tambayarta yake "Hajiya ina Momi?"

"Menene? Lafiya kake nemanta?"

"Lafiya, tana ina?"

Cikin ɓacin rai Umma ta ce "ban son rainin hankali Sadeeq, tambayarka fa ake yi kana tambayarta ita ma"

"Maa i'm sorry, yanzu ina so ne in sani Momi tana nan ko kuwa a'a!?"

Momi da fitowar ta kenan daga sashenta, ta ce " Malam Sadeeq ga ni nan, lafi......" Jamima da Sarh da ta gani ne ya hana ta ƙarasa maganar, gabanta ya yanke ya faɗi musamman da ta ga Jamima da hawaye shaɓe-shaɓe a fuska...........

MANAGE IT PLS, NA SAN YAYI KADAN BA SAI KUN YI MAGANA BA😂😻 I'M SORRY🙇‍♀️❤️

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_We love ourselves even after making so many mistakes...Then how can we hate others for their small mistakes?...Strange but true! So make habit of FORGIVING._

**Page 75&76**

Gaba ɗaya Momi ta kasa motsawa, kafin Sadeeq ya ce komai sai ga Safwan ya shigo gidan, kallonsu yake da kyau ya fahimci akwai wani abu

Ya ce "Umma lafiya?"

"Hmm, mu ma abunda muke son sani kenan, Sadeeq ne ya shigo gidan nan da Sarah da wannan yarinyar, da alamar akwai wani abu"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Safwan ya kalli Sarah da Jamima, sannan ya ce wa Sadeeq "menene Sadeeq?"

Kallonshi kawai Sadeeq yayi, kafin ya kalli Momi ya ce "Ƙaraso mana Momi!" Ya faɗa yana ƙare mata kallo, ko motsawa daga wurin da take ba tayi ba. Wani irin murmushi yayi ya ce "calm yourself down Momi, ki ƙaraso"

Kallonsu Hajiya ke yi da kyau, ta ce "wai menene?"

Sadeeq ya ce "za ki sani Hajiya, kawai so nake ta ƙaraso dan ta gaya muku komai da bakinta"

Hajiya ta kalli Momi ta ce "what's going on? Ki gaya mana"

A hankali Momi ke taku ɗaya bayan ɗaya har ta ƙarasa cikin parlourn, Sadeeq ya ƙara haɗe fuska ya ce "then, tell them what you did"

Umma ganin yanda Sadeeq ke wa Momi magana yau ba wani girmamawa ya ɓata ranta, ta ce "Sadeeq ka san da wa kake magana kuwa?"

Cikin ɓacin rai yake kallon Umma, ya ce "ni kuwa na san da wa nake magana ai shiyasa nake yi" mayar da kallonsa yayi kan Momi ya ce "what are you afraid of? Ai ban yi tsammanin za ki ji tsoron faɗar abunda kika yi ba a gaban kowa, tun da har ba ki iya jin tsoron mahaliccin ki ba lokacin da kika aikata...just feel free and say it out, sai da na tabbatar da ƴaƴanki ba sa kusa ai kafin na zo nan, dan ba zan iya gaya miki magana a gabansu ba...we respect each other... come on say it out!!!" Ya ƙarasa maganar a tsawace wanda ya sa kap ɗin su sai da suka razana

Turo ƙofar parlourn aka yi, Abba ne da Alhaji, cike da murna Alhaji ya ce "surprise!!" Sannan suka ƙarasa ciki

Hajiya ta ce "Alhaji!? Saukar yaushe?"

"Yanzun nan, dama na ce zan yi surprising ɗinku ne, shi ma Aliyu na kira shi, ba ya nesa da gida"

Alhaji bai ga wata walwala a tattare da su ba, hakan ya ba shi mamaki, ya ce "you look so worried, Allah ya sa lafiya"

Safwan ya ce "Alhaji sannu da zuwa"

Sadeeq ma yayi ƙarfin halin daidaita kan shi, ya ce "Sannu da zuwa"

A tare ya amsa musu da "yawwa" kafin ya ce "some one should please tell me what's going on here"

Sadeeq ya ce "Alhaji, mu zauna, zan gaya muku komai"

Sai a wannan lokacin Kawu Ƙarami ya shigo, sai da suka gaisa da Alhaji, sannan suka zauna baki ɗaya

Kan Sadeeq na ƙasa ya kasa cewa komai kuma, Abba ya ce "ban son shashanci fa, ya za ka tara mu a nan kuma kayi shiru?"

"Kayi haƙuri Abba, maganar ce nake jin nauyin yin ta a gaban Kawu"

Kawu Ƙarami ya ce "wace magana ce haka kake jin nauyin yin ta a gaba na kuma Sadeeq? Feel free kawai ka faɗa ko menene"

Da ƙyar Sadeeq ya iya magana, ya ce "kayi haƙuri Kawu, magana ce akan Momi, ta aikata abunda na san zai yi wuya ku yarda da hakan....Momi ta daɗe tana so ta haɗa ni da Sarah, amma kasancewar ina da wacce nake so ya sa na ba wa Sarah haƙuri, kuma ta haƙura saboda ita mace ce da ta san darajar kanta, bayan aure na da Sunaiha, Momi tayi tsammanin bana son Sunaiha saboda ina cewa akwai Jewel ɗin da nake so, sam ba ta san Sunaiha ita ce Jewel ɗin ba, dalilin haka ne ta fito da wani plan dan mu sake samun kusanci da Sarah ta hanyar kyautatawa Umma,ita kuma Sarah ba ta san hakan plan bane. Tabbas abunda take so, ya faru, saboda na ɗauki Sarah tamkar ƴar uwata kuma ƙawata, ba dan komai ba saboda Umma na sonta....wannan ƙawar Sarah ce, Jamima, yau Momi ta haɗa baki da ita tayi spiking coffee ɗin da za mu sha ni da Sarah wanda hakan zai sa na kusance ta, dalilin ta kuwa shi ne in har na kusance ta, to dole ne sai na aure ta, sai dai ta manta wani abu ɗaya, idan na haɗu da mutum a karon farko, bana sha ko cin abunda ya bani musamman ma idan ban yi insisting ba, kuma ya nace akan sai na karɓa, abunda Jamima tayi kenan, tun da ta bani coffee ɗin nan hankali bai kwanta da shi ba, musamman da tayi ta magana akan mu sha, ban yi tsammanin har na Sarah tayi spiking ba saboda na ga ƙawarta ce. Sarah ta shiga wani irin yanayi bayan shan coffee ɗin, hakan kuma ya jawo mana matsala ni da Sunaiha, saboda a lokacin da nake ƙoƙarin taimakon Sarah ta hanyar yi mata wata allura da za ta samu relief kuma za ta iya yin bacci, a lokacin Sunaiha ta shigo, ta kuma yi tsammanin wani abu ne tsakanin mu, yanzu haka tana gida, na yi ƙoƙarin yi mata bayani, amma ta gaya mun ba ta son gani na ko jin murya ta, har iƙirarin illata kanta tayi idan ban bar gidan ba...." Shiru ya ɗan yi bai sake magana ba kuma har yanzu bai ɗaga kansa ba

Dogon numfashi Alhaji ya sauke ya ce "Sadeeq ka tabbatar da abunda kake faɗa kuwa?"

"Alhaji wallahi ba ƙarya na mata ba, ga Jamima ɗin nan....sannan bayan haka ma...." Ya sake yin shiru

Alhaji ya ce "ci gaba, sannan me?"

"Momi ta daɗe tana shirye-shiryen yanda duk wasu properties ɗin Saraki Family za su koma da sunanta, na san haka ne ranar da na taɓa shiga ɓangaren ta zan ɗauko wa Kawu Ƙarami wasu files, a lokacin na ji tana waya akan tsare-tsaren da take yi, kuma na ji ta kira har da sunan lawyer ɗinta , ban ɓata lokaci ba na tafi wurinsa, da farko bai so gaya mun komai ba, sai da na mishi barazana akan aikinsa sannan ya gaya mun komai, ni kuma da taimakon wani lawyer na sauya komai...Alhaji idan ba ka manta ba, akwai ranar da na gaya maka na sauya komai na Family ɗin nan daga yanda kowa ya san shi, kuma na buƙaci kar ka gay wa kowa, to wannan shi ne dalili, ita kanta Momi bayan ta gano an sauya komai, ranta ya ɓaci, jira take ta ji wani yayi magana akai dan tasan idan tayi saurin tambaya za'a yi tunanin wani abu, tunda sai ayi shekara ma ba wanda ya damu da properties ɗin dan kowa na da na shi"

Shiru ɗakin yayi na ɗan lokaci, kowa ya rasa abun faɗa saboda tsananin mamakin abunda Momi tayi, ita kuwa sai kuka take kanta a ƙasa

Miƙewa Kawu Ƙarami yayi yana shafa fuska, gaba ɗaya ya kasa gane kansa, Momi na ganin ya miƙe, ta nufo shi da sauri tana kuka, ta ce "Abban Sameer dan Allah....."

Bai bari ta ƙarasa ba ya ɗauke ta da lafiyayyen mari, Alhaji ya miƙe ya riƙe shi, ya ce "meye haka Aliyu? Meyasa...?"

Cikin ɓacin rai Kawu Ƙarami ya ce "meyasa kake tambaya? Kai ba ka ji abunda ta aikata ba? Wallahi wannan matar nayi dana sanin saninta a rayuwa"

Alhaji ya ce "Aliyu, kayi shiru" juyawa yayi ya kalli Jamima dake sunkuye da kai, ya ce "ke, tashi ki tafi"

Ɗaga kai tayi ta kalle shi sannan ta kalli Sadeeq ta ga yana mata wani irin kallo, ba ta sake yarda sun haɗa ido ba ta tattara kayanta ta fita

Alhaji ya zaunar da Kawu Ƙarami, sannan ya ce "Aliyu ina so ka natsu mu bi komai a hankali, muyi bincike, ta yiwu akwai dalilin da yasa ta aikata...."

Katse shi Kawu Ƙarami ya sake yi ya ce "me za mu bincika? Wallahi duk abunda Sadeeq ya faɗa bana tantama akan sa, wane dalili kake tunanin zai sa ta aikata wannan abun idan ba son duniya irin na ta ba? Me ta rasa a gidan nan? Menene ba na mata? Wane irin kyautatawa ne ba nayi wa danginta? Wane dalili ne take da shi wanda zai sa tayi burin ganin ta tarwatsa family ɗin nan? An taɓa nuna mata wani banbanci ne? Ko an taɓa nuna banbanci tsakanin ƴaƴanta? Yaya wannan matar da kake ganin ba abokiyar zama ba ce, nayi nadamar zaɓenta a matsayin uwar ƴaƴan wallahi, kuma dole ne yau sai ta....."

Da sauri Alhaji ya rufe bakinsa, ya ce "kar ka ƙarasa dan Allah, Aliyu bana son idan ranka ya ɓaci ka yanke hukunci, na sha gaya maka yanke hukunci cikin fushi yana haifar da dana sani daga baya"

"Wallahi ba zan taɓa dana sani ba dan na yanke hukunci akan wannan matar"

Numfashi Alhaji ya sauke ya kalli Abba da yayi shiru bai ce komai ba, sannan ya ce "Aliyu da kai da Usman ku tashi mu tafi parlour na, za muyi magana" yana gama faɗar hakan ya miƙe ya wuce suka bi bayansa

Safwan da Sadeeq ma suka nufi na su ɓangaren. Hajiya ta sauke numfashi ta ce "dama an ce makashinka yana tare da kai, wallahi Basira kin ji kunya, kuma kin bani matuƙar mamaki, ban taɓa sanin haka kike ba, yanzu kika iya aikata hakan akan ƴar ƴar uwarki, to ai kowa ma za ki iya cutarwa, yanzu in da abunda kike so ya faru tsakanin su, kuma aka zo ba'a yi auren ba, shikenan fa kin zubar mata da mutuncinta da ƙimarta a idon duniya, dan iskanci a wurin namiji ado ne, ba zai yi affecting rayuwarsa sosai ba, amma ita mace kuwa matsala ne a wurin har tsufanta, ke har lokacin da za ta mutu...hmm, you better change your habit" ta ƙarasa tana mata wani irin kallon tsana

Sannan ta juya kan Sarah da ta wani dunƙule wuri ɗaya tana kuka, ɗaga ta tayi, ta ce "tashi mu je ɓangaren Ummanku kiyi wanka kin ji, tun da su Alhaji na ɓangaren mu" da taimakon Hajiya suka bar parlourn

Umma ta miƙe za ta wuce, Momi tayi saurin riƙe ta tana kuka, ta ce "Umman Sadeeq dan girman Allah ki yafe mun, nayi nadama ba zan sake ba...."

"Hmm, Allah ya yafe mana baki ɗaya, kiyi shiru haka nan, ya isa" daga haka ta bar mata parlourn ita ma

Alhaji kuwa suna shiga parlourn sa, ya ce "Aliyu, na san hukuncin da kake ƙoƙarin yanke wa akan abunda ya faru, tabbas na yarda da abu da Sadeeq ya faɗa, kuma tayi kuskure, amma ba na son ka yanke hukuncin rabuwa da ita, dan Allah"

Sai yanzu Abba ya samu ce wa "Yaya me kake nufi? So kake ya ci gaba da zama da ita despite what she did?"

"Usman! Shiyasa ku ka ga bana so in bari ku biyu kuyi shawara a duk lokacin da ranku yake a ɓace, saboda Usman ne baya wurin ɓacin rai ko Aliyu?"

Abba ya ce "Yaya, kai kan ka fa ka ce tayi kuskure"

"Eh na faɗa hakan, amma ko Allah muka yi wa laifi yana bamu dama dan mu gyara kuskuren mu, to me yasa mu ba za muyi wa junanmu uzuri ba? Mu gode wa Allah ma duk abunda tayi ɗin ba wanda ta ci nasara akai, sannan mu ba ta dama ta gyara....ba ma wannan ba, kar ka manta da Sameer, Salma, Safna da Sajid, duk ƴaƴanta ne, ya kake tunanin za su ji idan suka dawo gidan nan aka gaya musu ka saki mahaifiyarsu? Ya kake tunanin za su ji? Ka bar ganin Hajiya

da Umman su Sultana za su riƙe su, na san za su yi iya ƙoƙarin su, amma wallahi duk yadda uwa take, ba wanda zai iya maye gurbin ta komai lalacewarta, dan haka na roƙe ka bari ta ci albarkacin su, kar ka sake ta"

Shiru suka yi, sannan Kawu Ƙarami ya ce "shikenan na ji, za ta ji albarkacin ka da na ƴaƴanta, amma for now ba zan iya zama da ita ba wallahi, dole sai ta bar gidan nan na ƴan kwanaki"

Alhaji ya buɗe baki zai yi magana, Abba yayi saurin cewa "Yaya kar ma kayi ƙoƙarin hana shi wannan kam, ka bari ta tafi ta bar gidan nan na ɗan lokaci, ku bar ni dasu Sameer zan yi magana da su"

"Usman!!" Cewar Alhaji

Kawu Ƙarami ya ce "Yaya gaskiya ya faɗa maka ai, ko da ka roƙe ni akan in bar ta, wallahi ba zan iya ba, sakin ne dai na ji ba zan yi, amma sai ta tafi daga gidan nan zuwa lokacin da zan neme ta"

"Shikenan Allah ya sa mu dace"

Sarah na fitowa daga wanka, ta haɗa ta da wasu kayan Salma, kasancewar yanayin jikinsu ɗaya, ta kawo mata abinci. Hajiya ta ce "bari in je a kai ma su Alhaji abincin su"

Umma ta ce "ai na sa an musu"

Hajiya ta ce "yawwa....Sarah ki ci abincin mana" ta faɗa tana kallon Sarah da har yanzu ko rabin abincin ba ta ci ba

Ture plate ɗin Sarah tayi, ta dawo gabansu ta durƙusa, ta ce "Hajiya, Umma, dan Allah kuyi haƙuri ku yafe mun, wallahi ban taɓa yin wani abu a gidan nan da wata manufa ba, wallahi da zuciya ɗaya nake yi, ban san abun da Anty Basira ke shiryawa ba, gaba ɗaya kunyarku nake ji, ina jin haushin kai na"

Umma ce ta share mata hawaye ta ce "meyasa kike wannan maganar? Ba wanda kika yi wa laifi Sarah, ki daina kuka"

Hajiya ta ce "Sarah, kiraina jin haushin kanki, ki gode wa Allah ma da mutunci bai zube ba, kin ji ko!"

Jinjina kanta tayi tana ƙara share hawaye, ta ce "yanzu da wane irin ido zan kalli Sadeeq in nemi afuwarsa?"

Hajiya ta ce "me zai sa ki nemi afuwarsa? Ba fa abunda kika masa, kuma in dai Sadeeq ne, na tabbata bai riƙe ki a rai ba dan ya san ba kya da laifi"

Umma ta ce "ki ajiye wannan damuwar kin ji ko Sarah, yanzu abu ɗaya nake so da ke, ki natsu ki ci wannan abincin, ki huta sannan ki tafi gida"

Hajiya ta miƙe mata plate ɗin, ta ɗauka amma ta ƙi sakin jiki ta ci yanda ya kamata. Nan dai Umma ta fara ba Hajiya labarin irin zaman da su Sadeeq suka yi d Sunaiha kafin ya gaya mata gaskiya

Safwan ya kalli Sadeeq da ya rufe ido yana nazari, ya ce "Sadeeq dama wannan dalilin ne yasa ka daina gaida Momi? Amma meyasa kaƙi gaya mun? Meyasa ka nemi wani lawyer ya taimaka maka bayan ga ni?"

Buɗe ido Sadeeq yayi ya gyara zama, sannan ya sauke numfashi ya ce "sanin halinka ne ya sa ban gaya maka ba, har Anty Sadiya ta buƙaci in gaya mata amma ban yi ba, yanzu dai ai ga shi nan ka ji"

"Na ji kam, amma sam ban ji daɗi ba, wallahi ko da wasa ban taɓa tunanin hakan zai faru ba, yanzu ya su Sameer za su ji idan suka samu wannan labarin? Fatana ma kar Kawu ya kore ta"

"Nima bana so ya sake ta ko saboda su, Allah ya sa Alhaji ya mishi magana.....Safwan ni fa ba ma wannan ke damu na ba yanzu, Sunaiha ce kawai a raina"

"Kar ka damu kan ka da Sunaiha, za ta fahimta idan ka mata bayani yanda ya kamata, ni ma zan iya mata bayani tun da kai na san zai yi wuya ta saurare ka"

"Haka ne, amma akwai wata matsalar kuma"

"Wane matsala kuma?

Labarin saƙonin Najeeb ya ba shi da duk wani abu da ya sani, Safwan yayi mamaki sosai, ya ce "amma kar kayi saurin yanke hukunci ba tare da ka san gaskiyar abunda ke tsakanin su ba"

"Ba zan iya zarginta ba Safwan, dan na san ina da laifi a cikin kula shi ɗin da take yi, da ace ta samu lokaci na yanda ya kamata, ba za ta saurare shi ba... Ni yanzu shi tsinannen Najeeb ɗin nake son gani"

"Me za kayi mishi"

Wani irin kallo yayi wa Safwan, ya ce "me zan mishi????" Sai kawai yayi tsaki ya tashi ya bar gidan........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_Success is never permanent, Failure is never final. So always, do not stop effort until your victory makes a history....._

**Page 77&78**

Lokacin da Sadeeq ya sauko main parlour ya tarar da Kawu Ƙarami ya jawo wa Momi jakarta,
~~~~~~~~~~~~~~~~

ya jefa mata mayafinta cike da ɓacin rai, Umma da Abba, sai Alhaji suna gefe suna kallonsu

Kawu Ƙarami ya ce "tashi ki tafi, bana buƙatar ganinki, ki tashi ki tafi kafin in sauya miki kamanni"

Umma ce ta ɗan ƙarasa kusa da shi ta ce "dan Allah Abban Sameer kayi haƙuri, kar ka kore ta, kayi haƙuri"

"Umman Sultana ba za ki gane irin raɗaɗin da nake ji ba idan na kalli wannan matar, wallahi yau sai ta bar gidan nan, kiyi shiru kawai ..... Ki tashi na ce ki bar gidan nan" ya ƙarasa a tsawace yana kallon Momi da ke ta kuka

Miƙewa tayi ta nufi wurinsu Abba da Alhaji tana ba su haƙuri, sai magiya take musu akan su taya ta roƙonsa kar ya sake ta. Abba juyawa yayi ya bar parlourn zuwa ɓangaren su, Alhaji ne ya ce "kin ga Hajiya Basira, ba abunda zan iya cewa, nayi duk abunda zan iya yi, ke ma kin san ba ki kyauta wa kanki ba...Aliyu mijinki ne, shi yake da haƙƙin yanke duk wani hukunci da ya gama a kanki, fatana ɗaya, Allah ya sa hakan ya zame miki izina" yana gama faɗar hakan shi ma ya bar parlourn

Dama can Kawu Ƙarami ya wuce tun da ya ga Alhaji na magana, Umma ta kalli Sadeeq, shi ma ya kalle ta, ba abunda ya faɗa ya bar gidan

Umma ta zo ta ɗaga ta, ta ce "kiyi haƙuri, ki tafi kar ya sauko ya same ki a nan,ba ki san me zai iya miki ba dan ranshi ya ɓaci"

Cikin kuka Momi ta ce "yanzu idan na bar gidan nan ina zan tafi? Kin san ba na da kowa a duniyar nan sai Yaya"

"Ki je wurinta mana"

"Ƴaƴana kuma fa?"

"Kar ki damu da su, ai muna tare, ga ni ga Hajiya"

"Sai dai ke, amma Hajiya ta tsane ni yanzu, kin ga ko saukowa ba tayi ba"

"Ɓacin rai ne kawai, amma ba ta tsane ki ba"

Share hawaye Momi tayi, da ƙyar Umma ta lallaɓa ta har ta tafi sannan ta haura wurinsu Hajiya da Sarah, ta tarar da Sarah na shirin tafiya

"Ta wuce?" Hajiya ta tambayi Umma

"Eh, abun tausayi wallahi" ta faɗa cike da tausayi, harararta kawai Hajiya tayi, saboda tana mamakin irin zuciyar ƙanwarta, ɗan ta ne fa matar nan ta so tozarta wa, amma wai tausayin ta take ji

"Sarah har za ki tafi?" Cewar Umma

"Eh Umma, zan tafi"

"To Sarah, dan Allah kar abunda ya faru ya sa ki sauya wa mahaifiyarki daga yanda kike mata biyayya, ki ci gaba da bin ta yanda na san kina yi, kuma kar kiyi tunanin wannan abun tayi miki shi ne dan cin zarafi, tayi ne saboda tana sonki, tana so kiyi aure ne a wurin da za ki huta, shiyasa ta biyo ta wannan hanyar, sai dai ta manta Allah shi ne mai yi ba ɗan adam ba, amma kar ki ga laifinta Sarah, uwa tana iya yin komai saboda ta ga ɗanta ya samu ingantacciyar rayuwa, besides, no one is beyond mistake, ki manta da komai ki yafe mata, sai Allah ya miki zaɓin da ya fi alkhairi a rayuwarki, Antynki ma gidanku ta nufa, dan Allah ki yafe musu, kin ji"

Shiru Sarah tayi tana kallon Umma, tabbas Umma tana da kyakkyawar zuciya, ta dan a maganganunta akwai gaskiya, sai dai akwai waɗanda ta faɗe su ne kawai dan tana so ta ci gaba da ganin mahaifiyarta da girmanta a matsayin ta na uwa, amma idan ba haka ba, wace uwa ce za ta yarda ta zubar da mutuncin ƴar ta dan kawai neman abun duniya

Dogon numfashi ta sauke, ta ce "in sha Allah Umma zan bi duk abunda kika faɗa, na gode, Allah ya saka miki da alkhairi"

"Kar ki damu" ta faɗa tana murmushi

Sallama tayi da Hajiya, ita ma ta sa mata albarka sannan ta wuce

Sadeeq kuwa yana isa gida, ya tarar da Najma da Sunaiha a ɗaki, Sunaiha na ganinshi ta miƙe ta nufi ɗakinta, zama yayi suka gaisa da Najma

"Sadeeq na yarda da kai tun lokacin da muka yi zancenka da Sharif, amma ya aka yi hakan ta faru? Ina gida kawai ta kira ni wai in zo, shi ne Sharif ya kawo ni ya wuce"

Ajiyar zuciya ya sauke, ya ce "na gode wa Allah da har kika yarda ba zan aikata abunda ta gaya miki ba, amma zan fi farinciki idan da ace Jewel ce ta mun wannan yardar"

"Ita ma ta yarda da kai ai Sadeeq, kawai kishi ne irin na mu na mata, amma za ta sauko, na dai yi nasarar hana ta komawa gida kamar yanda ta so, saboda ba na so su Mummy su ji wannan maganar"

"Na gode sosai" jingina yayi jikin kujera

Kallonshi Najma tayi ta ce "kar ka damu kanka Sadeeq, i'm very sure everything will be ok, stop worrying yourself"

Jinjina kai yayi sannan ya zauna da kyau, ya ce "Najma may i ask you?"

"Yes of course"

"Dan Allah waye Najeeb?"

Ita kanta sai da ji gabanta ya faɗi, ta ce "Najeeb kuma? Ka san shi?"

"Idan na san shi me zai sa in tambaye ki kuma? Na san kin san komai a kansa, dan Allah kar ki ɓoye mun, ki gaya mun gaskiya Please Najma"

Ganin yanda yake maganar cikin damuwa ya sa ta kwashe komai ta gaya masa, ba abunda ta bari daga labarinsa da Sunaiha ta gaya mata

Ya ce "kina nufin shi ke bibiyarta, ita ba ta taɓa son shi ba?"

"Abunda na gaya maka, haka ta gaya mun, ba ta taɓa son shi ba, saboda nacin da yayi ne yasa ta ɗuke shi a matsayin aboki kafin kuyi aure, bayan auren kuma tayi duk yanda za tayi dan ya ƙyale ta amma ya ƙi"

Shiru ya ɗan yi kafin ya ce "to amma meyasa na ga ta ce su haɗu? Kua akwai wani saƙo da ta tura mishi"

"Wannan sai dai ka tambaye ta, ban san meyasa tayi hakan ba"

"Ki taimaka ki tambaye ta, kin ga ko saurare na ba tayi, na fi so in gama da matsalar Najeeb ɗin kafin in dawo rarrashinta"

Dariya Najma tayi, ta ce "haba Tiger, tsoronta kake yi kuma?"

Murmushi yayi ya ce "a'a, tsoron ɓata mata rai dai nake ji"

"Ka tambayi duk abunda kake so idan kana ra'ayi" cewar Sunaiha tana saukowa daga kan stairs, fuskarta ba fara'a ko kaɗan har ta zo ta zauna ta ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya, kai ba sai an gaya maka ba, daga ganin fuskarta za ka tabbatar da ta sha kukanta ta ƙoshi

Bai bari yanayin fuskarta ya karya masa zuciya ba, kai tsaye ya ce "meyasa kika je haɗuwa da Najeeb?"

Sai da ta mishi wani kallo kafin ta ce "zan gaya maka dalilin zuwa na wurin, ba wai dan wani abu ba, sai dan in hana ka zargi na, saboda ka san wanda yake aikata abu haka yake ganin kamar kowa yana yi.....na je wurin Najeeb ne dan in gaya miki ya rabu da ni, amma Najeeb na so na sosai, ya gaya mun ba zai taɓa rabuwa da ni...and for your own benefit, ya ce ba zai taɓa rabuwa da ni ba ko da hakan na nufin sai ya ga bayanka ne, left to you, ko ka ɗauki mataki ko ka ƙyale shi"

Sadeeq tsaya wa kawai yayi yana kallonta, Najma ta ce "kin san me kika faɗa kuwa? Gaba ɗaya fa hankalinki a kwance kika faɗar wai zai ga bayan mijinki"

"To ni ina ruwa na?" Ta faɗa tana yatsina fuska

Sadeeq ya ce "Najma ni ba wannan ne ya bani mamaki ba, kamar da ya ce yana sonta kuma ba zai iya rabuwa da ita ba, can you imagine!? She's my wife and someone is saying all this?!" Ya ƙarasa maganar a hasale

Najma ta ce "calm down Sadeeq, wannan bai kai wancan furucin matsala ba"

"I should calm down? How? Matata ce fa! Wallahi is better ma ya kashe ni ɗin idan zai iya akan in sake jin wannan kalmar wai yana sonta...na rantse ko ni ko shi, it's not that easy to defeat Sadeeq"

Ya juya zai fita, Najma ta ce "where are you heading to?.... Sunaiha talk to him mana"

Sadeeq ya ce "wurin shi zan tafi" bai jira komai ba ya fita, yana jin lokacin da Sunaiha ta ce "Allah ya raka taki gona"

Sai bayan da ta tabbatar da ya bar gidan, sannan hawayen da take ta riƙewa suka zubo, ta ce "i'm really sorry Prince, Allah ya tsare mun kai"

Najma ta kalle ta da kyau ta ce "meye hakan kuma? What's going on in your mind?"

"Bayan na shiga ɗaki ne, mahaifiyarsa ta kira ni ta mun bayanin komai da ke faruwa, kuma na gamsu da hakan, dama can zuciya ta taƙi yarda da abunda idanuwa na suka gani, i love him so much Anty Najma"

"Amma in da gaske kike, meyasa kika mishi haka yanzu?"

"Nayi ne saboda ya ji haushi sosai, dan ya mana maganin Najeeb once and for all, dan tun da yace zai iya kashe mun Sadeeq ya gama fita a raina gaba ɗaya, kuma a yanda na san Prince ɗina, Najeeb ba zai iya masa komai ba, kin ga idan yayi settling komai, sai mu dawo daidai"

"But i don't think this is a good idea"

"But to me it is, zan tayi mishi addu'ar tsari a ko da yaushe, ke ma ki taya mu"

"Zan taya ku, amma idan zan baki shawara ki ɗauka, zai fi kyau ki gay masa gaskiyar komai ya wuce a wurinki, hakan zai sa hankalinsa ya kwanta kuma ya karkata shi wuri ɗaya, ya damu da ke sosai wallahi, ba fa'ida a hakan da kika yi"

Shiru tayi, sai kuma ta ce "shikenan, na gode"

"Yawwa ko ke fa, Mata a gidan Prince"

Dariya Sunaiha tayi tana rufe fuska.........

BA YAWA, AYI MUN UZURI NEXT PAGE ZAI YI YAWA IN SHA ALLAH

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_Being in love does not mean that someone is perfect, it simply means you accept them just the way they are with all their failures and stupidities, Cause we are not perfect either!_

**Page 79&80**

Sarah na zuwa gida ta tarar da mahaifiyarta da Momi a parlour, sun yi jugum ba mai magana sai Momi da ke share hawaye

Ba tare da ta kalli gefen su ba ta zo wuce wa, mahaifiyarta ta kira ta, kamar ba za ta tsaya ba, amma tuna nasihar Umma ya sa ta dawo ta zauna

Mahaifiyarta ta ce "Sarah, na...."

Katse ta Sarah tayi "hold on Mom, me za ki gaya mun? Kina da wasu kalamai da suka rage a bakinki da za ki iya gaya mun ne? Wallahi i'm so surprised and also disappointed with this attitude of yours, ban san yaushe kika zama haka ba, an ya kuwa ke uwa ce?"

Shiru mahaifiyarta tayi, sai Momi ce ta samu damar magana, ita ma murya a sanyaye, ta ce "Sarah, please let bygones be bygones, mahaifiyarki ce, ki daina wadannan maganganun, duk...."

A tsawace ta katse ta, "enough Malama, i'm not talking to you, da mahaifiyata nake magana, wacce ita ma tantama nake yi, anya kuwa ita ta haife ni? Dan duk uwar kirki ba za ta aikata abunda tayi ba, so stay out of this kafin in nuna miki the worst side of me, zan manta ke ƙanwar mahaifiyata ce wallahi"

Gaba ɗaya bakin Momi ya gama mutuwa, sam ba ta taɓa tsammanin irin waɗannan maganganun daga bakin Sarah ba, saboda yarinya ce mai hankali da girmama na gaba da ita, amma yau magana take yi ba tare da ta ji wani abu a ranta ba

Mahaifiyarta ta ce "Sarah dan Allah kiyi haƙuri,na san da amincewa ta aka tsara komai, amma wallahi nayi ne saboda mu amfana baki ɗayanmu, kiyi aure a gidan da za ki ji daɗi nima in ji, after all, na ga kina son shi shiyasa na amince"
~~~~~~~~~~~~~~~~

Murmushin takaici tayi ta ce "hmm, jin daɗi ko!? A tunaninki dukiya ne jin daɗi? To ba haka bane, wallahi wallahi wallahi, ban taɓa son Sadeeq saboda kuɗinsa ba, ban taɓa son Sadeeq saboda kyaunsa ba, ban taɓa son Sadeeq saboda background ɗin family ɗin su ba, son Sadeeq Allah ne ya sa mun shi a raina, daga ranar da ya gaya mun yana son wata na roƙi Allah ya cire mun sonsa, har na fara mantawa da soyayyarsa, amma wannan matar da mun ƙarya ta kuma tsara ni, a tunani na zan iya taimaka masa da soyayyar da nake masa kar ya shiga wani hali idan ya gane gaskiyar wacce yake so tayi aure, ashe duk ƙarya ne, dan kawai wata mummunan manufarta ta nemi ta lalata mun rayuwa, ke kuma a matsayin ki na mahaifiyata kika biye ta..."

"Ba mu yi hakan dan mu lalata rayuwarki ba Sarah, dan jin daɗinki ne...." Cewar mahaifiyarta

"Ni na gaya miki ba na jin daɗin rayuwa ta yanzu? Tabbas na sani mahaifina ya rasu, amma Abban su Sameer ya zame mun tamkar uba, duk wani abu da mahaifina ne ya kamata ya mun, Alhaji Aliyu yana mun tun kafin in tambaye shi, ke kanki ya zame miki wani jigo na rayuwa, amma duk hakan bai miki ba? Har sai kin nemi wani jin daɗin kuma? Kina tunanin za ki iya ba kanki abunda Allah bai ba ki bane? Mom irinku ne matan da suka sa maza da yawa ba sa ganin mu da daraja, maza da yawa suna ganin mata mayun kuɗi ne, za su iya yin komai saboda kuɗi, sai ki ga saurayi ma tsoron bayyana kansa yake yi wurin mace a yanda yake sai ya haɗa da ƙaryar kuɗi, kuma duk saboda mata irin ku ne masu shegen son kuɗin tsiya, wallahi Mom mutunci na ya fiye mun duk wani ƙyalƙyalin duniya, kuma ina sake gode ma Allah da burinku bai cika ba....Mom i'm sorry to say, amma wallahi ki bar ganin Anty Basira ƴar uwarki ce, na rantse miki ba ta sonki...."

Momi ta ce "Sarah dan Allah kiyi haƙuri, wallahi ina son ƴar uwa ta...."

"Dalla Malama ki mun shiru, idan kina sonta meyasa za kiyi planning wannan muguntar akan ƴar ta? Ina ce kina da ƴaƴa mata, akwai Salma akwai Safna, meyasa ba kiyi musu abunda kika mun ba? Na ga ai akwai aure tsakaninsu da Sadeeq da Safwan da Sauban ma, meyasa sai ni?...Mom, ta san ɗayan biyu zai faru, ko dai Sadeeq ya kusance ni a tursasa mishi aure na, ko kuma ya kusance ni, amma auren yaƙi yiwuwa, shiyasa ba ta aikata akan nata ba, idan har anyi auren, ta san kin yarda da ita kuma komai ta ce shi za kiyi, za tayi amfani da hakan ta juya mu son ranta.....Mom, ke mahaifiya ta ce, ba zan daina miki biyayya ba, amma kiyi wa kanki nasiha, ki gyara, wannan ba hali ba ne mai kyau"

Ta share hawayenta sannan ta juya kan Momi ta ce "ke ma kiyi wa kanki faɗa idan za ki iya, dan dai a hakan ma Allah ya nuna miki shi ne mai yi, ba abu ɗaya da kika tsara wanda ya faru, at last ma an kore ki daga gidan, abunda kike da shi ma ba ki tsira da shi ba bare kuma abunda kike hari" tana gama faɗar haka ta miƙe zuwa ɗakinta, su kuwa shiru suka yi aka rasa mai cewa komai sai nazarin maganarta suke yi

Sadeeq kuwa yana barin gidansa, kai tsaye office ɗin su Najeeb ya nufa, wani mutum ne

yanzu a reception ɗin, gaisawa suka yi kafin ya ce "Najeeb yana nan?"

"A'a, yau bai fito ba"

Shiru yayi, sai kuma ya ce "dan Allah za ka iya gaya mun address ɗin gidansa?"

Kalonshi mutumin yayi, ya ce "wane ne kai? Meyasa zan gaya maka address ɗin gidansa?"

Rufe idonsa yayi ya buɗe, ya ce "meye amfanin ka san ko ni waye tunda shi ya san ni?"

"Gaskiya kayi haƙuri Malam, amma haka kawai ba zan iya ɗaukar address ɗin sa in ba ka ba, ba tare da na san waye kai ba, i'm sorry, amma na san aiki na"

Ran Sadeeq ƙara ɓaci yayi, yana tunanin abunda zai ce wa mutumin nan, sai ji yayi an kira sunansa daga baya, "Dr Sadeeq"

Juyowa yayi ya ga mai kiransa, sam bai gane shi ba, amma ya ga sai fara'a yake yi har ya ƙaraso kusa da shi, "Dr Sadeeq barka da rana"

"Yawwa barka" ya amsa yana ƙoƙarin gano inda ya san shi

"Dr ba ka gane ni ba ko?"

"Eh, ban gane ba"

"Ai ba za ka gane ba saboda mutanen da yawa, kwana huɗu da suka wuce, iyali na ta haihu a asibitinka, operation aka mata, kuma ba ka da kuɗin biya, amma kayi mata shi kyauta, ka ba ta magani kyauta sannan ka siya wa jaririyar kaya, a lokacin ba na asibitin, da na dawo kuma ka wuce, kwana biyu ina zuwa muna samun saɓani, ina so zan maka godiya"

"Ba komai yi wa kai ne, Allah ya bamu lada baki ɗaya"

"Ameen ameen Dr....amma lafiya na ganka a nan? Dama ka san Yallaɓai Najeeb ne? Ban taɓa ganinka a nan ba"

Kallonshi Sadeeq ke yi, a ransa ya ce "wannan akwai surutu, amma zai mun amfani" a zahiri kuwa ya ce "wurinsa na zo amma ba ya nan, kuma address ɗin gidansa ya kwanta mun, shi kuma wancan abokin aikin na ka ya ƙi gaya mun, ba komai dai, ya san aikinsa ne"

Juyawa yayi ya kalli wanda ke reception ɗin, kafin ya ja Sadeeq zuwa waje ya ce "zan gaya maka address ɗin dan na san ba za ka cutar da shi ba, shi Najeeb ɗin ne da kansa ya taɓa bada umurnin duk wanda ya zo neman address ɗin sa kar wanda ya bada, idan mai muhimmanci ne ko waye ya kira shi, amma kai zan gaya maka, kar ka bari ko ya sani"

Sadeeq ya ji daɗi sosai, ya ce "kar ka damu, just tell me"

Nan ya kwatanta mishi gidansu Najeeb sai da ya tabbatar da ya gane sannan suka rabu bayan ya ba shi kuɗi

Sadeeq kuwa bai wahala ba, har ƙofar gidan ya kai kansa, parking motarsa yayi gefen gidan sannan ya je ya fara knocking ƙofar, mai gadi ya buɗe, gaisawa suka yi sannan Sadeeq ya ce "Najeeb yana nan?"

"Eh yana nan, ya san da zuwanka?"

"Eh ya sani, dama ya gaya mun zan iya in same shi a gida, kuma zan iya tarar da ba ya nan"

"Ai kuwa yanzu ya dawo, bismillah" ya buɗe masa ƙofar ya shiga

Main door ɗin da ya gani ya nufa, bai tsaya komai ba ya tura ƙofar, Najeeb na tsaye yana waya, ganin Sadeeq ya sa shi cewa "i'll call you back" sannan ya kalli Sadeeq da ke kallonsa shi ma, ya ce "waye kai? Lafiya?"

Sai da Sadeeq ya ƙare masa kallo, kafin ya ce "Najeeb nake nema"

Murmushin rainin hankali Najeeb yayi, ya ce "Najeeb kake nema? Ni ɗin? Wa ya turo ka neman wanda ba ka san....."

Kafin ya ƙarasa Sadeeq ya ɗauke shi da wawan mari sai da ya kusa faɗuwa, a fusace ya ɗago yana kallon Sadeeq da fuskarsa ta koma ta ainihin Tiger ɗin da ake kiransa

Najeeb ya ce "how dare you slap me!?"

Yana gama rufe bakinsa, Sadeeq ya sake marinsa, ɗagowa ya sake yi da ƙarfi, ya ɗaga hannu zai mari Sadeeq, amma ya riƙe hannun tare da murɗa shi, ya ce "i will keep on slapping you har sai na sauya maka kamanni fuska, zan nuna maka wane ne ainihin ɗan iskan a tsakaninmu" ya ƙarasa maganar yana tura shi da ƙarfi sannan ya kai mishi naushi a fuska, nan dambe ya kicime a tsakanin su kamar ba za su bar juna da rai ba

Yayan Najeeb ne ya ƙaraso parlourn da sauri yana cewa "wai hayaniyar me nake ji ne Najee..." Abunda ya gani ne ya riƙe mishi baki, zuwa yayi ya shiga tsakanin su, da ƙyar ya samu ya raba su bayan shi ma ya samu rabonsa a fuska

Fuskantar Sadeeq yayi ya ce "lafiya Malam? Ta ya za ka shigo mana gida sannan ka dinga dukansa haka?"

Sadeeq na huci ya ce "dukansa ma yanzu na fara wallahi, sai na gani tsakanin ni da shi wane ne cikakken ɗan iskan, zan ga wa zai iya bada ransa akan Sunaiha, sai na nuna mishi Sadeeq ba ya cikin irin mazajen da ake bibiyar matansu....kai ƙaramin kwarto ne wallahi, na rantse a shirye nake da in ɗauki ranka a kan Sunaiha, kuma ka jira dawowa ta, dan ban gama ba, ko ni ko kai, idiot!!" Yana gama faɗar hakan ya juya ya tafi

Sai a lokacin Najeeb ya san mako shi waye, Yayan shi ya kalle shi da kyau, duk ya kumbura masa fuska, ya ce "Najeeb meyasa ba ka jin magana? Na sha fahimtar da kai abunda kake yi bai dace ba amma ba ka saurare ni ba, yanzu wa gari ya waya? Kalli yanda ya sauya maka kamanni, ka fita harkar yarinyar nan, tana da mijinta, kuma wallahi wannan mutumin ya fi ƙarfin ka, ka ga dai tun kana taɓo waɗanda ka fi ƙarfin su yanzu har ka taɓi wanda zai yi maganinka, Najeeb ka natsu ka haƙura da ita, ka ji da wannan raunin ma da ya bar ka da su"

A hasale Najeeb ya ce "keep quiet!! Enough dan Allah!!! What are you saying? Wanda zai yi magani na fa ka ce, kuma in yi haƙuri? Impossible wallahi... ba'a taɓa yi mun irin wannan cin mutuncin ba, kuma ba za'a fara akan sa ba, ba dai ya ce sai ya ga wanda zai rayu a tsakanin mu ba? Then he shall see, na rantse sai ka ɗauki ransa ko da kuwa ba zan samu Sunaiha ba, amma sai na ɗauki fansar wannan abun da yayi, ni ne zan zama ajalinsa"

Da mamaki Yayansa ya ce "Najeeb?! Kisa kuma? Bayan duk waɗannan halaye naka, kisan kai kuma za ka fara? Najeeb wai kai wane irin mutum ne? Sai yaushe zan gaya maka magana ka ɗauka? Ba za ka taɓa shiryuwa ba ne?"

"Yaya, ko zan shiryu, to sai bayan na kashe Sadeeq, that's it" bai tsaya sauraren komai ba ya nufi ɗakinsa

Zama Yayansa yayi ya ce "innalillahi wa'inna ilaihi ra'jiun, wannan wane irin taurin kai ne haka?"

Ɓangaren Sadeeq kuwa har ya iso gida huci yake, yana shiga parlour ya ji an rungume shi ta baya, cike da murna ta ce "you're welcome dear!"

Ji yayi kusan kaso hamsin na ɓacin ransa ya gushe, kyawawan murmushi ya sauka kan kyakkyawar fuskarsa. Juyowan da Sunaiha za tayi zuwa gabansa, ta lura da jinin da ke hannunsa

Ta ce "meye haka? Meyasa same ka?....zo nan" ta ja shi ta zaunar da shi kan kujera, ta ce "lafiya"

Shu kuwa kallonta yake yi sosai yana wani ƙayataccen murmushi, ganin ba ya da niyar yin magana ya sa ta miƙe, da sauri ya riƙe ta ya ce "ina za ki je?"

"Zan ɗauko abunda zan goge maka jinin nan ne"

Jawo ta yayi sai da ta zauna ya ce "meyasa za ki goge mun shi? Ɗazu fa ke kika ce ko mutuwa nayi ba ruwanki, amma meyasa yanzu ɗan wannan ciwon ya sa kika firgice haka?"

"Are you out of your mind? You're my husband, amma kake tunanin ban damu da kai ba? I don't mean what i said"

Murmushi ya sake yi ya ce "ooh, haka ne ashe i'm your husband"

Ganin yanda ma ya mayar da ita abun dariya ya sa tayi tsaki tare da ƙwace hannunta, ta miƙe tana faɗin "ni ka ƙyale in goge maka wannan jinin dan ba zan iya kallon ciwo a jikinka ba"

Sake zaunar da ita yayi sai ka ce wata baby, da hannu ɗaya yake jawo ta sai ta kai zaune, in a serious tune ya ce "kika ce ba za ki iya kallon ciwo a jiki na ba?"

"Yes of course"

"To meye amfanin ki mun maganin wannan ɗan ƙaramin ciwon, amma kuma ki bar ni da ciwon da zai iya kashe ni ma gaba ɗaya?"

"Stop saying that please, ka daina cewa za ka mutu ka bar ni, wannan wane irin ciwo ne? Ka gaya mun, na maka alƙawari zan maka maganin shi, idan ma ba zan iya ba, zan iya kai ka ko ina ne dan a maka maganin shi"

"A cikin zuciya ta yake, sannan duk faɗin duniyar nan, ba wanda zai iya warkar mun da wannan ciwon idan ba ke ba, you're the only doctor"

"Me ya samu zuciyar ta ka? Wane irin ciwo ne? Ban yi tunanin kana da wani ciwo ba"

"Ina sonki sosai, sonki ya mun yawa, ina matuƙar kishinki, zan iya yin komai saboda ke, amma kin bari Najeeb ya shiga rayuwarki da yawa, kina fushi da ni, and also, kin tsane ni, sannan kuma kina zargi na..... Jewel a tunaninki waɗannan ba ciwo ba ne? Hakan zai iya illata rayuwa ta, anything can happe...."

Rufe mishi baki tayi da sauri, ta ce "stop saying all this dan Allah, wa ya gaya maka ina fushi da kai ko ina zarginka? Idan har zan iya tsanarka, to ba abunda zai hana in tsani kai na, duk abunda ka ji na faɗa a kanka, sonka ne ya jawo hakan ba wai ƙiyayya ba, i love you so much, ban taɓa zarginka ba saboda na yarda da imaninka, kishinka ne ya sa bana fahimtar komai a lokacin, amma all thanks to Umma, dan ta mun bayanin komai... nothing can happen to you matuƙar muna tare sai abunda Allah ya ƙaddara faruwarsa"

Ya ji daɗin maganganun ta har zuciyarsa, farinciki ya ziyarce shi mara misaltuwa, ya ce "da gaske kike?"

"Hundred percent"

"I love you My Jewel"

"Love you too My Pri..." Sai kuma tayi shiru

Ya ce "ƙarasa mana"

Girgiza kai tayi ta ce "a'a, ka hana ni faɗar sunan ai"

"Oh no, just say it out, ni kai na na yi missing jin wannan sunan daga bakinki, say it please"

Murmushi tayi ta ce "I love you My....Boss"

Haɗe gira yayi ya ce "wane irin Boss kuma? Prince fa za ki ce"

"Noooo..ai tun da ka ce kayi missing jin sunan, to ba za ka ji shi so easily ba" ta ƙarasa tana dariya tare da mishi gwalo

Ya kai hannu zai riƙe ta, ta miƙe da sauri tana dariya, ta ce "ɗazu ma da ka riƙe ni ɗin tausayi ka ba ni, amma yanzu ba za ka iya ba"

"Really?"

"Yeah, ɗazu kaman ka ce it's not easy to defeat you right!?, To zan nuna maka i can defeat you, catch me if you can, ni kuma zan faɗi sunan da kake so ka ji, idan kuma ba ka iya kama ni ba, to tabbas ka yarda kawai Sunaiha za ta iya defeating ɗinka"

"Zan kama ki ne fa"

"Then let's see"

Kusan mintuna uku suna zagayar parlourn cike da farin ciki, sai ga Sunaiha a hannun Sadeeq, ɗaukarta yayi cak, ya tsaya yana kallon fuskarta, sannan ya ce "kin gani, na gaya miki zan kama ki"

Ɓata fuska tayi ta ce "ai na ce ka kama ni ba ka ɗauke ni ba, so let go of me"

"It doesn't matter, ko in kama ki ko in ɗauke ki, it's all the same, so ki faɗa kawai"

"Ba zan faɗa ba to sai ka sauke ni" ta faɗa a shagwaɓe

"Idan kika ga na sauke ki, to kin faɗa ne sai in sauke ki dan ki haɗa mun ruwa inyi wanka...kin ga ma kin fama mun hannu na, sai ciwo yake yi"

Gaba ɗaya ta ma manta da ciwon hannunshi, ta ce "oops, i'm sorry My Prince, ka sauke ni in ga hannun"

Murmushi yayi sannan ya sauke ta ya nuna mata hannun, ya ce "kin gani ba wani fama ni da kika yi, kawai wayo na miki kuma kin faɗi sunan, so Malama je ki haɗa mun ruwan wanka" ya faɗa yana murmushi

Ɓata rai tayi, ta wani tura shi gefe ta ce "ji kan shi" sannan ta haura sama, shi kuwa ƙara faɗaɗa murmushinsa yayi ya ce "alhamdulillah"

Sai da ta haɗa mishi ruwan sannan ta fitar mishi da wasu kaya jeans da t-shirt of her choice, sannan ta bar ɗakin zuwa kitchen, ta fito da abinci ta shirya musu shi akan dinning. Yana gama shiryawa ya fito suka ci abinci, ciyar da juna suka cike da so da ƙauna, da kuma kulawa har suka gama

Gaya mata yayi zai fita, sai kuwa ta ɓata rai, bata so ya fita, da ƙyar ya rarrashe ta tare da mata alƙawarin ba jimawa zai yi ba, sannan ta yarda ya fita bayan ta mishi addu'a

Kai tsaye office ɗin Senator ya nufa, bai wani wahala da secretary ɗin ba, ya bari ya shiga, cike da girmamawa ya gaida shi, ya amsa

"Takwara kwana biyu ka daina kawo mun ziyara ko?" Cewar Senator yana ƙoƙarin ture computer da ke gabansa ya mayar da hankali wurin Sadeeq

Murmushi Sadeeq yayi ya ce "ba haka bane Daddy, aiki ne ya mun yawa shiyasa"

"Aiki kuma Sadeeq?"

"Eh... Daddy yanzu ma zuwa nayi in baka haƙuri akan abubuwan da suka faru tsakani na da Sunaiha, Sharif ya gaya mun ranka ya ɓaci sosai akan hakan, har ma ka ce ba za ta dawo gidana ba, Daddy ban yi dan in ɓata ranka ba, dan Allah kayi haƙuri"

Murmushi Daddy yayi ya ce "Sadeeq kenan, meye kuma na zuwa ka bani haƙuri? Ai nayi zaton ba wannan a tsakanin ɗa da mahaifi ko! Sadeeq son da nake wa Sunaiha ne ya kawo ɓacin ran ba wai dan kayi laifi ba, nima daga baya mahaifiyarta ta fahimtar da ni abubuwa da dama waɗanda ya kamata a ce a irin shekaru na na fahimta, Sadeeq a matsayina na uba, ni nayi jagaba wurin ɓata tarbiyar ƴa ta, amma a matsayinka na masoyin gaskiya sai ka gyara mun ita, godiya ya kamata in maka ba wai kai ka bani haƙuri ba, na gode sosai Sadeeq, ba Sunaiha

kawai ka gyara wa ɗabi'unta ba, har da ni"

"Daddy, kamar yanda ka ce babu bada haƙuri tsakanin ɗa da mahaifi, to haka ma ba godiya, kawai ka sa mun albarka ita na fi buƙata"

Murmushi ya sake yi, ya ce "albarka kam kullum a cikinta kake Sadeeq, sai dai an ce kogi ma bai ƙi daɗi ba, Allah ya maka albarka Ya kuma tsare ka daga dukkan sharri"

"Ameen Daddy na gode sosai, Allah ya biya"

"Ameen takwara na"

Murmushi yayi ya ce "zan tafi Daddy" ya faɗa yana miƙe wa

"To Allah ya kiyaye, ka gaida Sunaiha"

"Za ta ji" daga haka ya wuce, Daddy kuma ya ci gaba da aikinsa

Bai tsaya ko ina ba dai gidan Anty Saudat, lokacin da ya tafi mijinta na shirin fita, gaisawa suka yi, sannan mijinta ya ce "Sadeeq na ji daɗin ganinka ma, ga ta nan na ta son shan magani ko kaɗan, ba ta kula da kanta ma bare kuma Babyn cikinta"

"Anty Saudat ai haka take, amma kar ka damu za ta sha"

"To Shikenan, bari in fita, ka gaida mun su Hajiya"

"To an gama yallaɓai" ya faɗa yana dariya, shi ma dariyar yayi kafin ya fita

Kusa da Anty Saudat ya dawo ya zauna, ya ce "Maman Baby how far"

"Ban sani ba, yanzu ka ganni?"

"Oh, sorry! Kin ga ai ina gaisawa ne da Babban Yaya"

"Uhm, yau ya ci sa'ar gaisuwar kenan....wai ma yau you look so happy, lafiya"

Murmushi ya ƙara yi wanda ke ma fuskarsa kyau sosai, ya ce "ai dole zan yi farin ciki, duk da na san na ɗan lokaci ne"

"Kamar ya ban fahimta ba"

"Zan gaya miki, amma sai kin fara shan maganin nan"

Sanin yayi Anty Saudat akwai son labari shiyasa ya gaya mata haka, ba musu kuwa ta ɓalla maganin ta shanye sannan ta ce "to yanzu gaya mun"

Ɗan ɓata rai yayi, ya ce "yau ɗin nan Jewel ɗina ta ƙara tabbatar mun da irin son da take mun, kuma ta kusan shigowa rayuwa ta, amma na san very soon zamu rabu"

Da sauri ta ce "meyasa to?"

"Saboda ba kya sonta mana Anty Saudat, kuma kin san zan iya rabuwa da ita saboda farin cikinki, amma ni kuma zan iya mutuwa"

"Stop it mana, ko da ba za ka mutu ba, ka san ba zan ƙi abunda kake so ba Bro, wace ce"

"Are you really sure, ko wace ce za ki so ta?"

"Of course in dai kana sonta"

"Are you sure?"

"Hundred percent sure mana Sadeeq, ba ka yarda da ni ba ne yau?"

"Na yarda da ke Sisto, kawai ji nake kamar ba za ki yarda ki so ta ba"

Riƙe hannunsa tayi ta ce "Sadeeq ka yarda da ni, na rantse maka ko wace ce in dai kana sonta, zan so ta ko da kuwa ba na sonta a baya, kai ka sani Sadeeq, ina son duk abunda kake so, abunda ba ka so kuma ba na so, that's your Sister"

Murmushi yayi ya ce "My Jewel is no one rather than Sunaiha"

Buɗe ido tayi ta ce "Sunaiha? Your wife?"

"Of course yes"

"Sadeeq let's be serious, Sunaiha ita r Jewel ɗinka, then why the hatred? A sani na ba ka sonta, wanda hakan ya sa nima ba na sonta, why did you change your mind all of the sudden"

"I haven't change my mind or my love, ita ɗin ce dai tun farko, kuma ita ce har yanzu, kuma ita ce har abada"

"But i'm confused"

"And i will clear up the confusion"

Labari ya fara bata tun daga farkon haɗuwarsa da Sunaiha har sonta da yayi ta yi, har plan ɗin da suka yi da Anty Sadiya kafin auren, har dai zuwa ƙarshe, zuwa yau ɗin nan da suka shirya

Shiru Anty Saudat tayi ba ta ce komai ba, ya ce "why are you silent? Kin ce fa za ki so ta, ko ba za ki iya ba nima in haƙura da ita?"

"A'a Sadeeq, ina tunanin abunda na mata ne haɗuwarmu ta ƙarshe, ta ya zan sake fuskantar ta har in ba ta haƙuri, kai ma na san you feel bad for that"

"Come on Sister, ni ba abunda na ji, saboda na san son da kike wa ƙaninki ne yasa kika taya shi ƙin abunda ba ya so"

"But you love her Sadeeq"

"Amma ai ba ki san da hakan ba, yanzu kuma da kika sani sai ki taya ni sonta, ita ma Sunaiha i'm very sure ta yafe miki"

"How are you sure about that"

"Na an ba za ta so ni sannan ta ƙi Yaya ta ba"

"Sai na ji hakan daga bakinta, bari in nemi permission, yanzu mu tafi ka kai ni in bata haƙuri, bayan magrib sai ya je ya ɗauko ni"

"A'a ba za'a yi haka ba, ki bari sai gobe, da kaina ma zan nema miki permission ɗin"

"Meyasa, haka nace dai, goben ya fi kamata ki ba ta haƙuri"

"To shikenan as you wish"

"Aha, i'm going" suka yi sallama sannan ya wuce

Yana shiga mota ya kira layin Muhsin, bugu biyu ya ɗauka, suka gaisa sannan ya ba shi labarin sun shirya da Jewel

"Congrats Dude, finally dai everything is back to normal"

"In sha Allah, yanzu ka san me, ina son ganinka, so that we can plan for tomorrow"

"Plan?!....oh yeah, na tuna, no delay kenan" ya faɗa yana dariya

"Eh mana, kai ma ka san na daɗe ina jiran wannan ranar"

"Haka ne, amma ka nemi Sharif da su Saif, saboda ina tunanin gobe zan tafi America kuma in wuce Singapore, dama ina so in kira ka in gaya maka"

"No excuse Buddy, ba ruwa na, i just need you"

"Ka gane mana, yanzu ma booking flight zan yi fa"

"I don't care, i just need you kawai na ga maka"

Numfashi Muhsin ya sauke ya ce "shikenan, da kai da mai martaba idan kuka so abu dole sai mutum yayi, ina dai bayan magrib ne komai, to zan nemi flight ɗin ko da na 11pm ne ko 12pm idan zan samu, dan dai gobe zan bar ƙasar nan, abu ne da ya shafi aiki na"

"Whatever dai, tunda har za ka tsaya, thank you, zan zo yanzu in same ka" ya faɗa yana dariya

"Sai ka zo, da wani kanka a wurin"

"Na dai ji" ya kashe wayar yana dariya...........

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_A smile of a lover is joy and happiness, A smile of a strong person is confidence, A smile of a child is contentment, A smile of a man is love and strength, A smile of a women is fondness and appreciation, A smile of a mother is acceptance and gratification A smile of a father is safety, A smile of a rich person is optimism, A smile of a weak person is praise and thanksgiving, A smile of a poor person is satisfaction....So let's keep smiling, NO CONDITION IS PERMANENT_

**Page 81&82**

Bayan magrib, Sameer da Sauban suna parlourn su, su na fira, Sauban ya ce "yawwa Sameer, wai sai yaushe za ka gaya wa Sultana abunda ke ranka ne? Ka ce sai mun gama exams, to yau mun gama ai"

Sameer ya numfasa ya ce "nima ban sani ba Sauban, ina sonta sosai ka sani, amma wallahi haka nake gani kamar ba za ta so ni ba, ka san yanda muke da ita a gidan nan kullum cikin faɗa"

"Haba mana, ai kowa ya san wannan ba faɗan gaskiya kuke yi ba, kawai kuna tsokanar juna ne, dan Allah kar ka bada maza mana, kawai ka gaya mata, idan ba haka ba kana zaune a gidan nan za ka ga mutane sun zo neman aurenta"

"Ban son mugun baki fa, shikenan zan gaya mata"

"Wace ce za ka gaya wa? Kuma me za ka gaya mata?" Abunda Sultana ta faɗa kenan kafin ta samu wuri ta zauna
~~~~~~~~~~~~~~~~

Kallonta suka yi a tare dan a tunaninsu ta ji me suke cewa, Sauban ya ce "yaushe kika fara shiga ɗaki ba sallama kuma Sultana?"

Shagwaɓe wa tayi ta ce "sorry, zan yi sallamar ne na ji ana cewa za'a gaya mata, wace ce?"

Sameer ya ce "ai dama gulma ba zai bari ki samu yin sallama ba, ana ganin Sajida na da gulma, kin ma fi ta ai"

Sultana ta ce "eh ɗin anyi, ai kai ma gulmar wata kake yi yanzu" ta ƙarasa tana murguɗa mishi baki

"Zan cire miki baki idan kika sake murguɗa shi"

"Ka shirya zaman kotu kuwa, saboda ina da Ya Safwan"

"Ba dai kin iya jan magana ba, sai ki wani ce kina da Ya Safwan ko!?"

"Eh, ni na san wata rana Ya Safwan sai ya tsaya mun a matsayin Lawyer na, kuma zai yi nasara, ehe"

Sameer ya jinjina kai ya ce "ai dama wata rana kam hakan za ta faru, saboda rashin jin nan naki sai ya ja an kai ki ƙara"

"Zan kai ka ƙara dai, saboda takura mun da kake yi da shanye mun ice-cream idan na ajiye"

"An shanye ɗin, ki ɗauki mataki"

"Zan ɗauka ai very soon"

Sauban ya girgiza kai ya ce "kai dan Allah, enough! Wai ku ba kwa da aiki ne sai na faɗa, kullum"

Sultana ta ce "ai shi ke fara ja na, kuma ni ba ma wurin shi na zo ba"

"Ai dama me zai kawo ki wuri na?" Cewar Sameer

Sauban ya ce "ƙyale shi, gaya mun, menene?"

"Ya Sauban system ɗinka za ka ara mun"

Sameer ya ce "aikin kenan ai, daga ara mun system, ara mun wayarka, ka mun VTU, ka mun transfer, shikenan fa aikinki, kai kuma dan ba kada wayo sai ka yi mata abunda duk tace, ban ga amfanin kuɗin da ake sa musu each and every month ba"

Sauban ya ce "ba ruwanka dai, kana da sa ido"

Sultana ta ce "ƙyale shi dai, idan kuma wani yayi ya ce zai yi magana"

Muryar Abba suka ji yana cewa "ku da ba kwa da sa idon, ku tashi ku bamu wuri zan yi magana da Sameer"

Dariya suka yi a tare, Sameer ya ce "Abba, ai da kira na ma kawai kayi sai in zo"

Abba ya ce "sau biyu fa na kira wayarka ba ka ɗaga ba"

Dubawa yayi, ya ce "oh, yi haƙuri Abba, silent na saka wayar na manta, kuma wannan talkative ɗin ta dame mu bare in ji vibration ɗinta"

Sultana ta wani ƙara haɗe tana kallonshi, Abba ya ce "kafin ki samu abun faɗa, fita ku bamu wuri, Sauban ja wannan shirmammiyar ku wuce"

Murmushi Sauban yayi sannan ya sa ta gaba suka wuce. Zama yayi kafin ya nuna wa Sameer kusa da shi ya ce ya zauna, ba musu ya zauna, ya ce "Abba lafiya?"

"Kwantar da hankalinka Sameer, lafiya ƙalau.....wato Sameer, zuwa yanzu na san kayi girman da za ka iya fahimtar abunda malam bahaushe ke cewa zo mu zauna, zo mu saɓa, ko?"

"Eh Abba na sani"

"To me ka fahimta da hakan?"

"Abba kowa ne zama ana samun matsala, duk yanda zama yayi daɗi kuwa, duk yanda ake son juna wata rana sai an ɓata ran juna, hakan na faruwa tsakanin ƴan uwa, abokanai, masoya, tsakanin ɗa da iyayensa, har tsakanin mata da miji ma"

Jinjina kai Abba yayi ya ce "alhamdulillah, na ji daɗin bayanin nan naka...um, Sameer"

"Na'am Abba"

"Ɗazu mahaifinku da mahaifiyarku sun samu saɓani kaɗan, wanda hakan ya jawo har shi mahaifin naku ya ce wa Mominku ta tafi gida"

"Subhanallah, dama Momi ba fita tayi ba? I thought ta fita ne ai shiyasa ban wani damu ba, amma Abba me yayi zafi har haka?"

"Sameer, ba abunda za ka ɗaga hankalinka ba ne, saboda ba sakinta yayi ba, ya ce ne ta tafi

gida sai ya neme ta...na gaya maka haka ne saboda kai ne babba a cikin ku huɗu, kuma ba na so ka ji maganar wani wuri dan ban san a yanda za ka ji shi ba"

"To amma Abba me ya haɗa su har haka?"

"Idan lokacin da ya kamata ka sani yayi, da kai na zan gaya maka idan har da yiwuwar sai ka sani, ba na so Safna da Sajid su ji wannan maganar, a bar shi a tunaninsu kawai ta fita, Salma kuma za ka iya gaya mata ta sigar da za ta fahimta"

Shiru Sameer yayi kafin ya ce "shikenan Abba, Allah ya kyauta ya ba su haƙuri, kuma ya daidaita su"

"Ameen ya Allah" daga haka ya fita

Kusan mintuna biyar yana zaune shiru bayan fitar Abba, sannan ya ɗauki waya ya kira Salma, bugu ɗaya ta ɗauka

"Salma ki zo part ɗin mu yanzu"

"Haba Ya Sameer, sai yanzu da ka san ina kallo shi ne za ka kira ni, an fara series ɗin nan wallahi" magana take kamar za tayi kuka

"Magana ce mai muhimmanci da amfani, ki bar kallon nan, ai ana maimaitawa"

Tana turo baki ta ce "gani nan" ta kashe wayar, sai da ta gama kallon wannan scene ɗin kafin ta tashi ta fita da gudu

Zama tayi kusa da shi tana kallon yanayinsa, ta ce "lafiya dai? You look somehow"

Numfashi ya ja kafin ya mata bayanin komai kamar yanda Abba ya gaya mishi, a tsanake. Ta ce "dama Momi ba fita tayi ba? Da na tambayi Umma fa ce mun tayi ta fita"

"Nima haka nayi tunani, amma ba na so ki sa abun a ranki sosai, komai zai wuce very soon, although ba daɗi zama gida ba tare da mahaifiya ba, amma kar ki wani damu kanki, tun da nake hakan bai taɓa faruwa tsakaninsu ba, so ko ma menene na tabbata Momi ta ɓata mishi rai ne sosai, amma zai sauko"

Cikin ɓacin rai Salma ta ce "you're talking as if abun bai dame ka ba, ko ma me tayi ai bai kamata ya kore ta ba a irin wannan matsayin da suka kai, at this age of hers a ce mijinta ya kore ta? Bai ko duba ƴaƴanta ba? For the first time mahaifi na ya mun abunda ban ji daɗin sa ba ko kaɗan, kuma sai na ji dalili"

Sameer ya ce "ba kya da hankali ne ko me? Iyayenki ne fa na ce sun samu saɓani ba

ƙannenki ba, da har za ki ce sai kin ji dalili, kan ki ɗaya kuwa? To ko ni da na girme ki ban damu sai na ji ba, wataƙila hakan ne alkhairi shiyasa ban damu sai na ji ba"

"Dama kuwa ta ya za ka damu tun da ba ka san daɗin mahaifiya cikin gida ba saboda ba zama kake yi ba, ni kuwa da kullum ina gida sai idan makaranta muka tafi, duk da ba wani yawan xama nake yi da ita ba, mun fi zama da Hajiya da Umma, amma i can't live in this house without her, dan haka zan je in same shi"

Gaba ɗaya ta gama ba shi mamaki, shiru kawai yayi yana bin ta da ido har ta fita, ya ce "lallai Salma"

Tama fita kuwa ɓangaren su Kawu Ƙarami ta nufa, da sallama ta shiga, yana zaune a parlour, shi kaɗai ya san tunanin da yake yi, ganinta ya sa shi gyara zama ya mayar da hankali kan ta

"Ya aka yi ne Salma?"

Shiru tayi tana tunanin ta in da za ta fara, sannan ta ce "Ina so ne in san dan Allah me ya sa ka kori Momi? Me tayi har da ka kasa yin haƙuri sai da ka kore ta?"

Kallonta yake yi bai ce komai ba, hakan ya sa ta ɗaga ido suka yi ido biyu kafin ta sauke na ta, ya ce "Salma, zuwa kika yi ki tuhume ni ko kuwa aiko ki aka yi?"

"Ba aiko ni aka yi ba, zuwan kai na ne, meyas...."

A tsawace ya katse ta, ya ce "keep your mouth shut!!! Ke har kin yi girman da zan aikata abu ki zo ki tsare ni kina tambaya ta meyasa nayi? Ke ƴa ta ce, ni na haife ki ba ke kika haife ni ba... wallahi Salma idan kika sake zuwa mun nan da zancen mahaifinki, sai nayi mummunan saɓa miki, ashe ba ki da kunya ban sani ba?"

Kanta na ƙi, ta ce "kayi haƙu...."

Sake katse ta yayi a karo na biyu "get out i said, mutumiyar banza kawai...to idan ba za ki iya zama a gidan ba, ki kwashe kayanki ki bi ta"

Da gudu ta nufi ƙofa tana kuka, tana fita ta ci karo da Sultana, zagaya ta tayi za ta wuce, Sultana ta dawo da ita, sannan ta rungume ta tana rarrashinta

Sai da ta tabbatar tayi shiru sannan ta ja ta zuwa part ɗin su suka zauna ta ce "Salma na ji duk abunda ya faru tsakanin ki da Kawu Ƙarami, abu na farko da zan ce miki shi ne kiyi haƙuri, na biyu kuma, kin aikata ba daidai ba, sam wannan ba tarbiyyarki ba ce, ya aka yi kika bari mahaifinki yana faɗa kina faɗa? Me ma ya kai ki?'

"Sultana ba ki san meke faruwa bane shiyasa kika ga laifi na"

"Na sani Salma, i know what's going on, daga maganar da kuka yi da Kawu Ƙarami na fahimci komai...Salma na san uwa, uwa ce, amma idan da za kiyi wa Kawu Ƙarami adalci, ki natsar da hankalinki wuri ɗaya, tabbas da zuciyarki ta fahimtar da ke bai yi laifi da ya kore ta"

"Kenan kin san me Momi tayi?"

"Ban sani ba Salma, dalilin da yasa nayi saurin ba wa Momi rashin gaskiya, ba wai dan ba ita ta haife ni bane, sanin kanki ne Momi na ɗauke ta matsayin mahaifiya ta ne, amma tun da muka tashi a gidan nan, kin taɓa jin wata hayaniya ko faɗa ya shiga tsakanin Momi da Kawu Ƙarami? Amsar ita ce a'a, ba wai kuma dan ba sa yi bane, saboda ko wane irin zama sai ɓata wa juna, amma ba ki taɓa jinsu ba duk tsawon shekarun da suka yi tare, sai ga shi rana ɗaya, kwatsam sun yi faɗan da har ya ce ta tafi gida, anya kuwa ba kya tunanin wannan karon tayi laifi ne sosai? Ba kuma na ce ita kaɗai tayi laifi ba, shi ma Kawu Ƙarami idan aka bibiya ya mata laifi...amma a matsayinki na ƴa, bai kamata ki je kai tsaye ki ba wa ɗaya daga cikinsu laifi ba ko da kuwa a gabanki aka yi faɗan, kin san mai gaskiya, bare kuma ba ki sani ba, sai dai ki zuba musu ido ki kuma roƙi Allah ya daidaita tsakanin su, idan ma sai kin yi magana, to bai wuci ki ba su haƙuri ba, saboda duk iyayenki ne, ba wanda za ki watsar a ciki"

Shiru Salma tayi, kafin ta ce "amma Sultana ko me tayi ya kamata yayi haƙuri"

"Ina so ki fahimci akwai laifin da idan mutum yayi, hankali gushewa yake yi har sai an ɗauki mataki, daga baya kuma sai ki ga komai ya wuce"

"To wane irin laifi ne wannan? Ina so in sani"

"Shikenan, kin ga yanzu dare yayi, amma gobe da safe, muyi wa Umma magana, sai mu tafi wurin Momi, wataƙila za ta iya gaya miki....sannan kuma zan raka ki dan ki ba wa Kawu Ƙarami haƙuri, saboda kar yayi ta fushi da ke"

"Yanzu?"

"A'a, da safe dai, idan ya sauko"

"Ok" ta faɗa tana sauke numfashi, gaba ɗaya ta ƙi sakin ranta

Sultana tayi murmushi, ta ce "chill up dear, kin san i hate to see you like this, ko kyau ba kya yi"

Murmushi Salma tayi, sannan suka rungume juna

Sadeeq kuwa sai kusan ƙarfe tara sannan ya dawo gida, Sunaiha na sama, sai kawai ya zauna parlour sannan ya kira Anty Sadiya, gaisawa suka fara yi, kafin ta ce "Oga Tiger ka gama fushin? Yanzu ka tuna da ni?"

Murmushi yayi ya ce "oh no Sweet Sis, ba zan taɓa manta wa da ke ba"

"Really!? Yanzu da ka gama fushin sannan ka san da haka? Ai tunda yanzu ka sauko, ni kuma zan hau"

"Ya Salam, i'm sorry, the day won't be good for me without you"

"Um hm, ai na ɗauka da ne kawai, ashe har yanzu"

"Har abada ma, i'm sorry, ke kin san halin Sadeeq ɗin naki ai"

Dariya tayi ta ce "Sanin haka ɗin ne ya sa na haƙura....yanzu Safwan ya kira ni yake gaya mun you've told him about the plan, sai dai saurin me kake yi? Ya ce gobe ka ce, ka bari nan da kwana biyu mana, sai mu ƙara shirya komai yanda ya kamata"

"Ba wani shiri Anty Sadiya, abunda nayi shekaru ina shiri a kansa, duk abunda bai shiryu a shekaru uku ba, ai kwana biyu sun yi kaɗan...yanzu aikinki ɗaya a nan, ki tabbata kin yi wa sauran bayanin komai, that's all, sauran kuma ni, Muhsin, Safwan, Saif  da Aryaan duk za mu ji da su"

"To an gama Mijin Jewel, dama can nayi packaging komai kamar yanda ka sani, and it's all safe"

"Yawwa, a gida za mu haɗu gaba ɗaya kafin time ɗin"

"No vex, bye"

"Thanks"

Ya kashe wayar yana murmushi, ɗaga kan da zai yi ya ga Sunaiha ta wani haɗe rai tana kallonshi, ƙara faɗaɗa murmushinsa yayi ya ce "Ya dai My Jewel, what's wrong?"

"Oh, ba ka ma san me kayi ba? Ka ce fa ba daɗewa za kayi ba za ka dawo, amma shi ne sai yanzu, kenan idan daɗe wa za kayi, a can zaka kwana ko"

Dariya ta ba shi yanda ta haɗe rai tana faɗa, ya ce "kiyi haƙuri, nayi yawo ne sosai wallahi, i'm so so tired" ya faɗa yana rufe ido

"To shikenan, yawo dai kayi ko? And you're tired...well, good night" ta juya za ta wuce

Buɗe ido yayi ya ga da gaske ta juya za ta wuce, ya miƙe da sauri ya shiga gabanta, ya ce "ina za ki je kuma?"

"Zan je in kwanta mana, in bari ka huta tun da dai yawo kayi, kuma ka gaji, so you don't need me here, kar in takura maka"

"Ayya, ba fa abunda nake nufi ba kenan Jewel...yanzu ma idan kika kwanta, wa zai bani ruwan wanka, da abinci kuma?"

"Kai ta shafa, ina ruwa na!"

"Kiyi haƙuri dan Allah, ba zan sake maimaita irin hakan ba to in sha Allah"

"Ka maimaita ma kawai, ai na san ba ni da muhimmanci a wurin ka"

"Ya Salam, subhanallah... stop saying all this dan Allah, ke kin san kina da matuƙar muhimmanci a rayuwa ta"

Magana yake amma ko kallonsa ba tayi, a hankali ya ce "na shiga uku" ya ɗan ja ƙafar wandonsa zai yi kneel down, tana ganin hakan, sai tayi sauri ta riga shi kai wa ƙasa, sai da ya kai ƙasa shi ma, sannan ya tsaya kallonta, ya ce "meye haka?"

Ta ce "ai kai zan tambaya meye haka, me kake shirin yi?"

"Haƙuri zan ba ki mana, na ga a tsayen kin ga kamar na raina ki ne ai"

"Stop Please, kar ka sake faɗar wannan maganar, so kake Allah yayi fushi da ni ne? Ko so kake in shiga cikin irin matan da ba sa yi wa mazajensu uzuri?...Na san waye kai Prince, ko a lokacin da kake punishing ɗina, ba ka taɓa kai wa wannan lokacin ba, ba tare da ka dawo gida ba, so yau dan kayi ai dole zan maka uzuri, i'm very sure akwai abunda ya tsayar da kai mai muhimmanci, right!?"

Murmushi yake sosai yana ƙara gode wa Allah a ranshi, sannan ya ce "of course dear, na gode da kika fahimta, Allah ya miki albarka"

"Ameen" ta faɗa tana murmushi, sannan ta rungume shi

Sai da yayi wanka kafin suka ci abinci, sannan suka nufi ɗakinshi dan su kwanta, kafin su yi bacci ya ba ta labarin wuraren da ya tafi, kuma duk suna gaida ita, sai dai bai gaya mata ya je wurin Muhsin ba, bare ya bata labarin abunda suka tattauna

Washe gari da safe, ya gama duk wani shirinsa, sun yi breakfast, zai fita ya ce "ki shirya nan da one hour zan dawo in kai ki gida"

Da mamaki ta ce "wane gidan?"

"Gidanmu"

"Lafiya kuwa?"

"Lafiya ƙalau, kawai dai ki shirya idan muka je za ki gani"

"Allah ya sa ba laifi nayi ba"

"Ai ba kya laifi Matar Prince, ki shirya ke dai, kowa da kowa ma zai tafi can ɗin, har Nasreen...yawwa kuma ki gaya wa ƙawarki Ikram ita ma zuwa anjima ta tafi can ɗin"

Shiru tayi, ta ce "to shikenan dai, Allah ya sa mu ga alkhairi...sai ka dawo"

Murmushi yayi dan ya fahimci hankalinta bai kwanta, amma ya fita. Ta daɗe a zaune kafin ta kira Ikram ta gaya mata, ita kanta tayi mamaki amma ta amsa da "Allah ya kaimu anjiman lafiya"

Ɓangaren su Mummy kuwa, sun gama break fast, suna parlour a zaune bayan Daddy ya fita. Mummy ta ce "sarkin yawo yau ba za ka fita bane? Na ga jiya sai kusan ƙarfe goma ka dawo"

Murmushi Sharif yayi ya ce "kamar kin san kuwa abunda zan faɗa kenan Mummy"

"Fita za kayi ko!?"

"Eh, amma har da Sis"

Ɗaga ido Najma tayi ta kalle shi ta ce "wace Sis ɗin?"

"Ina da wacce ta fi ki ne Anty masifa?" Ya faɗa yana wani juya mata baki sai ka ce mace

Dariya Hajiyar London tayi, ta ce "wallahi Sharif ɗan rainin hankali ne kai, Anty masifa ko!? Ina gefe za ta mazge ka"

Mummy ta ce "ai ni zan fara mazgarsa, mara kunya"

Sharif ya ce "to Mummy yi haƙuri....dan Allah Sis ki shirya mu tafi"

Harararsa tayi ta ce "ban inda za ni"

"Haba Sisi, kiyi haƙuri mana..wai ma kin san wurin da za mu tafi?"

"I don't care" ta faɗa hankalinta na kan system ɗinta

Ya ce "gidan su Tiger za mu je"

"Meyasa?"

"Nima ban sani ba, amma shi yayi requesting"

"To ba zan tafi ba"

"Kiyi haƙuri mana ranki ya daɗe, ko saboda Partner, ita ma za ta tafi"

"Ba laifi ai, ita gidan surukanta ne, ni kuma a wa?"

Hajiyar London ta ce "ke kuma kina da matsala wani lokacin, kin ga dama ba ki taɓa zuwa ba, kuma ba ki san meyasa ya buƙaci zuwanki ba, ki shirya ku tafi mana"

Za tayi magana, Mummy ta ce "don't say a word dear, tashi ki shirya ku tafi"

Ba dan ranta ya so ba ta tashi ta haura sama, Sharif kuwa murmushi yayi ya ce "yes"

Mummy ta ce "amma dai ƙarya kake yi, ka san meyasa ya kira ta"

"Eh mana, it's a surprise and secret for now, amma idan ta je za ta ji"

"To mu ka gaya mana" cewar Hajiyar London

"Oh no, idan na gaya muku ai ya tashi daga secret kuma, wannan tsakanin mu ke ni da Tiger da Ya Safwan, sai abokansa gida uku" yana gama faɗar hakan ya bar ɗakin, dan ya san idan ya ci gaba da zama, kafin Najma ta fito za su tilasta masa sai ya faɗa musu

Salma da Sultana kuwa, suna gama shiri suka nufi wurin Umma, sai da suka gama gaya mata wurin Momi za su tafi, da kuma dalilin hakan, sannan ta ce "Salma, Sultana, ban ƙi zuwan na ku ba, amma ina jiye muku kar mahaifinku ya sani, yayi faɗa, da kanki dai kike gaya mun yanda kuka yi jiya"

Salma ta ce "Umma ba zai sani ba ma in sha Allah, dan Allah ki yarda mu tafi kawai, ba ma son barin gidan nan ne ba tare da izinin kowa daga cikinku ba, shiyasa muka zo wurinki"

"Haka ne, shikenan to, amma Salma sai nake ganin rashin sanin abunda tayi shi ne alkhairi a wurinku, watakila ma shiyasa Abbanku bai gaya wa Sameer ba, kar ki je ki tono abunda zai dame ki kuma fiye da haka"

"Umma ba zan tono ba, idan ma ba ta gaya mun ba zan takura mata ba, at least dai na ganta"

"To sai kun dawo, ku gaishe ta, amma kar ku daɗe, yanzu ma su Sameera suka kira ni, wai suna nan zuwa baki ɗayansu"

Sultana ta ce "yau kuma sun yi kewarmu ne? Ni dai Anty Sunaiha nake son gani"

Salma ta ce "wallahi nima, kwana biyu ba mu haɗu ba"

Umma ta ce "idan kuka yi haƙuri ita ma Sadeeq ya ce zai kawo ta, har da ƴa ta Nasreen da ba kuyi missing ba"

Dariya suka yi, Sultana ta ce "Allah ya ba ki haƙuri Hajiya Umma, ita ma we missed her so badly"

Salma ta ce "of course Umma"

Ta ce "dalla ku tafi ku bani wuri, na saba da jin wannan daɗin bakin naku"

Fita suka yi suna dariya, Umma ta ce "Allah ya shirya mun ku My tom and jerry"

Sultana ke driving har gidan su Sarah, suna shiga parlour suka ga Momi a zaune ita kaɗai, da gudu suka faɗa jikinta suna gaishe ta, ita ma cike da murna take amsa musu

Sultana ta ce "Momi, Sarah fa?"

Momi ta ce "tayi tafiya, ta tafi garin ƴan uwan mahaifinta"

"Tafiya kuma? Yaushe? Tafiya haka ba sanarwa?"

Momi ta ce "yau da safen nan ta wuce shiyasa"

Salma ta ce "to Umman Sarah kuma fa?"

"Ita ma ta fita, kin san tana zuwa aiki"

"Ok....umm, Momi"

"Na'am"

"Momi dan Allah me kika yi wa Kawu Ƙarami har ya kore ki, what happen? Na tambaye shi amma ya mun faɗa ya kore ni, Umma ma ba ta gaya mana ba"

Shiru Momi tayi, kafin ta ce "Salma meyasa kike so ki sani?"

"Momi i want you back home, shiyasa nake so in dan abunda ya haɗa ku, may be i can help"

"Hmm, Salma... Kamar yanda kika ga ba wanda ya gaya muku what happened, kawai mu bar shi a hakan dan Allah, abunda kawai zan iya gaya miki, mahaifinki bai da laifi, ni ce nayi mishi babban laifi, in sha Allah na san zai haƙura saboda yana da yafiya"

"But when Momi? Sai yaushe zai yafe miki har ki dawo gida?"

"Ban sani ba, but it might take time"

Sultana ta ce "but we need you Momi"

"Ummanku da Hajiya za suyi muku duk wani abu da kuke buƙata a wurin, besides ma kun fi saba wa da su"

"Haka ne, amma Momi kowa da matsayinsa, kowa da amfaninsa" cewar Sultana

"Haka ne, ni kai na ina son zama da ku, yanzu nake jin haushin yanda ba na zama da ku, sai yanzu nake jin ina kewarku da yawa"

Sultana ta ce "don't worry Momi, in sha Allah za ki dawo gida very soon, anjima zan yi wa Kawu Ƙarami magana, ina fatan zai saurare ni"

Momi ta girgiza kai ta ce "ba zai saurare ki ba Sultana, kar ma ki tafi ku damu matsala....mutum ɗaya nake da tabbacin zai mishi magana ya ji"

Salma ta ce "waye?"

"Sadeeq, na tabbata zai saurare shi, amma kuma Sadeeq ba zai mishi magana ba"

Salma ta ce "meyasa to ba zai mishi magana ba?"

"Saboda shi ma Sadeeq ɗin fushi yake da ni, na mishi laifi"

"Wane irin laifi kuma kika masa? Momi ke kowa kin yi wa laifi ne wai?" Cewar Salma

Sultana ta ce "it's okay Salma, bar zancen haka nan, in sha Allah zan yi magana da Ya Sadeeq, zai ba Kawu Karami haƙuri"

Momi ta ce "kin san waye Sadeeq, ba zai saurare ki ba"

"Na sani Momi, na san Ya Sadeeq yana da fushi, amma wani lokacin yana da sauƙin kai, so i'll give it a try"

Shiru suka yi, kafin Momi ta ce "to, Allah ya bada sa'a"

"Ameen" suka amsa kafin suka yi mata sallama suka wuce saboda tuna abunda Umma ta faɗa musu

Suna zuwa gida kuwa suka ga ya cika maƙil, Anty Sadiya, Anty Sameera, Anty Saudat, Sunaiha, Anty Najma, Nasreen, Ikram, duk sun hallara, sannan ga sauran ƴan gidan, gaba ɗaya an haɗu wuri ɗaya sai surutu suke kamar za su tayar da gidan, nan suka zauna suka sa baki, saboda suna matuƙar jin daɗin irin haka, abun gwanin burgewa

Sadeeq ya shigo, Safwan na bayanshi, sai faɗa yake yi, "wai me za ka ɗauka ne dan Allah, kana so kayi delaying ɗin mu wallahi, idan wani ne kuma faɗa za kayi, duk abunda bai yi daidai ba kar ka ga laifin kowa"

Tsayawa Sadeeq yayi, ya ce "abunda zan ɗauka kuma idan babu shi ma faɗa za kayi, na ce ina zuwa mana" sai kawai ya wuce tsohon ɓangaren su

Hajiya ta ce "wallahi Safwan wani lokacin kana da faɗa"

Umma ta ce "ke kuma wani lokacin ba kya son gaskiya, yanzu meye laifin Safwan?"

"Ai ba za ki ga laifinsa ba"

"Kamar yanda ba za ki ga laifin Sadeeq ba" cewar Umma

Anty Sameera ta ce "ni ba ma wannan ba, wai duk wannan tara mu ɗin da aka yi nan na menene?"

Umma ta ce "ki jira Sadeeq ɗin ki tambaye shi"

"Ah, Umma so kike ya cinye ni ɗanye" dariya suka yi gaba ɗaya

Anty Sadiya ta ce "you people should calm down, alhakin gaya muku komai yana kai na, i'll explain everything idan suka fita"

Sultana ta miƙe da sauri ta ce "bari ina zuwa"

Anty Najma ta ce "ina za ki je kuma?"

Sajida ta ce "gulma mana, idan tana da rabon shan faɗa ai sai ta je"

Ba ta saurare su ba, ta wuce, ɗakin shi ta nufa kai tsaye, sai dai ba ta shiga ba sai da ya ba ta izini, yana tsaye bakin wardrobe, ya kalle ta ya ce "lafiya?"

Girgiza kai tayi, saboda jira kawai take yi ya kore ta, ta ce "a'a"

Ajiye kayan hannunsa yayi ya tako zuwa gabanta, ya taɓa wuyanta da goshinta, ya ce "what's wrong with you?"

Murmushi tayi, ta ce "hold on babban likita, ba ciwo nake yi ba fa, i want to talk to you dan Allah"

Wani kallo ya mata, ya ce "i'm in hurry, ki bari sai gobe"

Riƙe mishi hannu tayi ta ce "na sani Ya Sadeeq, amma won't you give two minutes to your sister, please... it's very important"

Ganin yanda tayi ya sa shi murmushi, kaɗan daga aiki Sultana kenan, shiyasa yake jinta a ranshi, wataƙila saboda ita kaɗai ce ƙanwarsa da suka fito ciki ɗaya

Janta yayi suka zauna kan gado, ya ce "to ina jinki"

"Ya Sadeeq, duk duniya na san ba wanda kake so sama da Umma, haka ne? Just answer me and not ask me please"

"Eh haka ne, sosai"

"To amma meyasa hakan?"

"Meyasa? Saboda ita uwa ce, Sultana duk mai hankali ba zai iya gaya miki dalilin da yasa yake son mahaifiyarsa ba, because the love is totally different from the others, it has reason, da shi ake haifar mutum, a cikin jikin mutum yake gaba ɗaya, a mother is the best, Sultana kar ki ɓata lokacinmu akan wannan, go straight to the point"

"Hmm, to amma Ya Sadeeq za ka iya juriyar tayi nisa da kai? Kamar kayi kwana biyu ba ka ganta ba?"

"A'a ko kaɗan, yanzu ma da nayi aure, kina ganin yanda kullum sai na zo gidan nan at least sau biyu ko uku, kuma saboda ita ne"

Jinjina kai tayi ta ce "to Ya Sadeeq kai da kake babba kuma namiji, kana jin ba za ka iya juriyar rashin Umma a kusa da kai ba na kwana biyu, to kayi tunanin yanda Salma za ta ji idan aka nisanta ta da Momi, ya Safna za ta ji ita da Sajid, da Ya Sameer?..Ya Sadeeq ban san me Momi tayi ba, kuma ba ka buƙatar sani, amma dan Allah ka taimaka, kayi ƙoƙari ka ga ta dawo gidan nan, dan Allah Ya Sadeeq ka manta da komai ya wuce, duk ɗan adam ajizi ne, ba zai taɓa yin komai daidai ba, ka yafe mata, kuma ka roƙi Kawu Ƙarami ya yafe mata ta dawo, wallahi ina jin haushi idan na ga Salma cikin damuwa, kai ma ka sani, dan Allah do this for their sake, kai kaɗai za kayi magana ya ɗauka, Please"

Saurarenta yake har ta kai ƙarshe, ya sauke numfashi ya ce "naji duk abunda kika faɗa, kuma na yarda, of course Momi tayi laifi, amma ni kai na ban ji daɗi da Kawu Ƙarami ya kore ta ba, ba dan komai ba sai saboda su Sameer....in sha Allah zan yi mishi magana"

"Sure?" Ta tambaye shi cike da murna

"Hundred percent, ba za ki roƙe ni ba in ce a'a ai"

Rungume shi tayi ta ce "i love you Oga Tiger"

"Love you much more dear"

Kallonshi tayi ta ce "da gaske?"

"Sosai ma kuwa"

"Amma shi ne ba ka nuna mun, kullum sai dai faɗa, sai dai idan ka ga i'm serious za ka saurare ni, Ya Safwan ya fi nuna yana so na, kai kuma ka fi son Salma" maganar take yi a shagwaɓe

Murmushi yayi ya ce "Anty Saudat tana so na ko ba ta so na?"

"Tana sonka mana sosai"

"To shikenan dan Anty Sadiya ta fi nuna mun so hakan na nufin ta fi Anty Saudat so na?"

Girgiza kai tayi, ya sake cewa "dan kin fi nuna son Hajiya a fili, hakan na nufin kin fi sonta fiye da Umma?"

Ta sake girgiza kai, ya ce "to nima haka ɗin ne, dan Safwan ya fi nuna sonki ba shi ke nufin ya fi ni sonki ba, i love you alot Sister, so chill dear" ya ƙarasa maganar yana ja mata kumatu,

sannan ya ɗauki abunda zai ɗauka ya fita, murmushi tayi ta ce "the best brother ever" sannan ita ma ta fita...............

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~
_Without respect there is no love, without mercy there is no pity, without forgiveness there is no future.... Let's forgive and forget, then move on!_
~~~~~~~~~~~~~~~~

**Page 83&84**

Da yamma da misalin ƙarfe shida, kusan sallar magrib, Anty Sadiya ta gama waya da Sadeeq a tsohon ɗakinta, Sunaiha na kallonta, ta ce "Anty Sadiya tun ɗazu ba ki gaya mana komai ba fa, ni dai har na gaji da haƙuri"

Dariya Anty Sadiya tayi ta ce "ke ce dai ba ki san komai ba, amma ai na gaya wa sauran, lokacin da Hajiya ta kira ki ɗazu, sai nayi amfani da wannan opportunity ɗin na gaya musu"

Ɓata fuska tayi ta ce "to ni me nayi da ba za ki gaya mun ba?"

"Umarnin mijinki na bi ai, shi ne ya ce kar in gaya miki"

Ƙara haɗe rai tayi tana mata wani kallo, ita Anty Sadiya dariya ma take ba ta, sai da ta gama dariyar, sannan ta ce "yi haƙuri, kina so ki sani"

Ɗaga mata kai tayi kafin ta ce "eh"

"To ina zuwa, za ki san komai, amma ban son yawan tambaya, just do as i say and smile"

Murmushi Sunaiha tayi, sannan Anty Sadiya ta nufi wardrobe ta ɗauko wani madaidaicin akwati, ta ajiye kan gado ta buɗe, wata fitted gown ta fitar, pink colour, anyi mata kwalliya daga gaba da milk colour sannan aka zuba mata wasu stones ma su matuƙar ƙyalli

"Wow!!" Sunaiha ta faɗa tana rufe baki

Anty Sadiya ta ce "ta yi kyau?"

"Over ma, wallahi tayi kyau sosai Anty Sadiya, musamman wannan colours ɗin da aka yi combining, sai suka ƙara mata kyau"

"Gaya mun gaskiya dai, ko dan colours ɗin na favorite colours ɗinki ne ya sa kika ga tayi kyau"

"Eh to, they're my favorite colours, amma ko ba dan colours ɗin ba, tayi kyau sosai Anty Sadiya"

"To shikenan, yanzu ki tashi ki je kiyi alwala, sai ki zo ki saka, kafin nan zan je in gani idan masu make up ɗin sun zo, sai ɗaya ta zo ta miki, sai kiyi sallah"

Da mamaki Sunaiha ke kallonta ta ce "in saka? Masu make up kuma?"

"Eh mana, na gaya miki ban son tambaya, kawai kiyi yanda na gaya miki" cewar Anty Sadiya,

tana gama wa ta fita

Kallon rigar Sunaiha ke yi cike da mamaki da kuma shauƙin son rigar, kusan mintuna uku sannan ta tashi ta shiga toilet, alwala tayi kamar yanda aka umarce ta, sannan ta fito ta sa rigar

Tsab tayi mata, kamar an auna ta, ta sauka mata har ƙasa, bayan rigar har bin ta yake daga baya, yanayin style ɗin kenan, gaban madubi ta nufa, tana ta murmushi, ita kanta ta yaba irin kyaun da rigar tayi mata, sai juyawa take yi tana ƙare wa kanta kallo, ba ta san Anty Sadiya ta shigo ba, sai jin muryarta tayi tana faɗin

"Malama kar ki cinye kyaun na ki kafin Oga ya gani"

Dariya suka yi tare har da me make up ɗin da suka shigo tare, Sunaiha ta ce "Anty Sadiya i'm really surprise ne yanda rigar nan ta mun"

"Ki daina mamaki da duk abunda mijinki zai miki, saboda ya san abunda zai miki da wanda ba zai miki ba"

Sunaiha ta ce "wai dama shi ne ya mun wannan?"

"Kina mamaki ne? To ba ki ga komai ba, yanzu dai ki zauna a miki make up"

Ta juya wurin me kwalliyar, ta ce "Simple make up za kiyi mata kamar yanda aka yi wa sauran, amma ki tabbatar na ta ya fi kyau, shiyasa na kira ki dan na ga ke ce shugabarsu"

Murmushi me make up ɗin tayi, ta ce "ai za tayi kyau ita ma sosai kamar dai sauran, saboda kuna da natural beauty, kin ga kuwa dole simple make up zai muku kyau"

"To mun gode sosai, yanzu dai kiyi mata kwalliyar sai tayi sallah, sannan sai ki ɗaura mata head ɗin"

"To shikenan"

Zama Sunaiha tayi aka fara kwalliya, Anty Sadiya ta sake buɗe wannan akwatin, ta ɗauko head milk colour ta ajiye musu, sannan ta fita dan ita ma ta shirya

Bayan kusan mintuna ashirin, sannan Anty Sadiya ta dawo ɗakin, "Masha Allahu la ƙuwata illa billa, Tabarakallahu ahsanul khaliƙin" abunda Anty Sadiya ta fara faɗa kenan tana kallon Sunaiha

Sannan ta ƙara cewa "Sunaiha you look so so so so gorgeous, masha Allah...anya kuwa Tiger ba zai rikice ba?"

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "Anty Sadiya kina fasa mun kai na"

"Ki bari kawai in fasa shi Sunaiha, ai yabon gwani ya zama dole, wallahi kin yi masifar kyau"

"Nagode sosai Anty Babba"

Murmushi tayi kafin ta juya wurin me kwalliyar, ta ce "ki je za ki ga saƙo, dan aikinki yayi kyau"

"To Hajiya, Nagode, sai anjima" daga haka ta fita

Anty Sadiya na aikin kallon Sunaiha, wayarta tayi ƙara, Anty Sameera ce, "Samy ya aka yi?" Cewar Anty Sadiya

"Su Saif ne suka ƙaraso"

"Mota nawa ne? Ai zai ishe ku ko?"

"Ina ganin mota huɗu ne, na Saif, Aryaan, Sameer da Sauban"

"Yawwa dama ya gaya mun su huɗu za su zo, to ki gaya wa sauran su tashi ku tafi"

"To an gama, amma ke da Sunaiha fa?

"Za mu zo daga baya, ni zan kawo ta"

"Amma dai Anty babba kin san kin mana rowar ganin Sunaiha ko? Ko kwalliyar ta ba ki bari mun gani ba, bare dressing ɗinta"

"To me kuke ci na baka na zuba ne Hajiya Samy? Za ku ganta ku tafi kawai, ai ita ma ba ta ga dressing ɗinku ba"

"Shikenan" cewar Anty Sameera sannan ta kashe wayar

Hotuna Anty Sadiya ta dinga yi wa Sunaihai, sai da ta tabbatar da sun kai mintuna goma da barin gidan, sannan ta ɗauko mayafi milk colour ta ɗora mata, ta ba ta takalmi flat shoes pink da ratsin milk ta saka, sannan suka fito, sai da suka tsaya wurin su Hajiya da Umma kafin suka bar gidan

Tun da suka shiga mota ba wanda ke magana, Sunaiha na so tayi tambaya, amma ta kama bakinta ta saka mishi padlock, sai kallon ikon Allah take yi. Abunda ya bata mamaki, ganin Anty Sadiya ba ta tsaya ko ina ba sai gidansu ita da Sadeeq

A lokacin ne ta kasa haƙuri, ta ce "Anty Sadiya me muka dawo yi gida kuma?"

"Duk suna nan ai, just keep quiet"

Horn tayi mai gadi ya zo ya buɗe suka ƙarasa ciki, daga cikin motar, Sunaiha ke ƙare wa gidan kallo cike da mamaki, gaba ɗaya harabar gidan ya sha decorations sosai kamar ba gobe, ga wasu ƙananan glubs masu fitar da multi-colour lights aka saka ta ko ina, kayan decorations ɗin gaba ɗaya pink da milk ne har balloons

Daga ta can gefe wurin wani stairs, aka yi decorating ɗin wata ƴar rumfa, aka ɗora kujeru guda biyu, ɗaya aka rubuta His Jewel, ɗayan Her Prince, sai table a gabansu ɗan madaidaici, da ƙaton cake a kai, three steps pink da milk, sai drinks da champagne, su kan su kujerun da table ɗin sun ƙayatu da decorations, sai wasu kujeru da ke wurin, ko ina kujera uku da table ɗaya, su ma an ƙayata su sosai, ko wane table yana ɗauke da cupcakes da drinks

Wuri dai masha Allahu, sai wanda ya gani komai so perfect, har yanzu Sunaiha ta kasa buɗe ƙofar motar bare ma ta fito, mamakin yanda aka tsara wurin take ta yi, sai kace wani shahararren event hall, ba wai gidansu ba

Ƙofar motar aka buɗe, ba ta damu ta ga wanda ya buɗe ba tana can tana kallon wuri, a tunaninta Anty Sadiya ce, saboda ba ta ga kowa a wurin ba, sai ganin hannun mutum tayi alamar ta miƙo hannu, ko ba'a gaya mata ba, ta san hannun Prince ne

A hankali ta ɗaga ido ta kalle shi, idanunsu suka sarƙafe, kusan mintuna uku su na kallon juna, kafin yayi ƙarfin halin ɗauke na shi, dan tayi mishi kyau sosai, kamar kar ta fito

Ya ce "can you come out your highness, ko sai na ɗauko ki?"

Wani murmushi tayi tana sauke kai, sannan ta miƙa mishi hannu, a hankali ta fito, janta yake a hankali har suka kusa kai wurin da za su zauna, sai kawai ta ga anyi blowing flowers, sannan ta ji suna ta tafi suna ihu, ɗaya bayan ɗaya suka dinga fitowa, mata na fitowa daga gefenta, maza daga gefen Sadeeq

Sai a lokacin ta ƙarewa shigarsu kallo da kyau, matan gaba ɗaya, tun daga kan Anty Sadiya, Anty Sameera, Anty Saudat, Anty Najma, Nasreen, Ikram, Salma, Sultana, Sajida da Safna, tummy skirt suka saka milk colour, sai t-shirt ɗinsu na polo pink colour, jikin rigar anyi wani rubutu mai ƙyalli mai kyau da milk colour, gaban rigar an rubuta JEWEL'S TEAM, baya kuma BEST COUPLE S², sai suka saka hula milk colour, suka ɗora facing cap pink da rubutu a jiki da milk colour shi ma mai ƙyalli, an rubuta SADAIHA, sunan Sadeeq kenan da Sunaiha, Sad daga sunan Sadeeq, Aiha daga sunan Sunaiha, sai dai duk wacce take da aure a cikinsu, sai da ta yafa mayafi milk colour kamar dai yanda Sunaiha tayi

Juyawa tayi gefen mazan tana kallo, su ma daga kan Muhsin, Safwan, Saif, Aryaan, Sharif,

Sameer, Sauban da Sajeed, wandonsu Milk colour da t-shirt pink komai irin na matan, sai dai rubutun gaban rigar ne kawai ya banbanta, na su PRINCE TEAM aka rubuta, amma bayan iri ɗaya ne, sai facing cap shi ma komai irin na matan ne har rubutun da ke kai

Kallon Sadeeq tayi da sai yanzu take ƙoƙarin tantance shigar da yayi, shi ma sak irin shigar mazan yayi, wando milk colour da riga pink, sai dai rubutun su ya banbanta, gaban rigar aka rubuta HER PRINCE, baya kuma SADAIHA, na shi salon rubutun ma daban ne, sannan bai saka facing cap ba, sai dai gashin kansa ya sha gyara sosai sai ƙyalli yake, ya saka baƙin madubi. Gaba ɗayansu sun yi matuƙar kyau, ba wanda aka bari a baya

A hankali ta buɗe baki ta ce "all this is...."

Bai bari ta ƙarasa ba ta ya rufe mata baki, ya ce "ki adana zancenki, not now" sannan ya ja ta har wurin zamansu suka zauna kafin sauran ma suka zauna

Anty Sameera ta fara buɗe taron da addu'a, kafin Sajeed yayi karatun al'ƙur'ani, sannan Anty Sadiya ta ɗora da jawabin abunda ya tara su

"Assalamu alaikum warahmatullah wa barakatuhu, na tabbata gaba ɗayanku kun san me ya tara mu anan, wannan shiri ne na musamman wanda Oga Tiger ya daɗe yana yi dan nuna wa Sunaiha irin son da yake mata, for almost two years kenan da ya shirya komai, saboda ya san ta da shekara ɗaya, sannan ya fara wannan tanadin, muna fatar hakan zai faranta ran su...amma Sadeeq ina da tambaya" cewar Anty Sadiya tana kallon shi

Sai a lokacin ya ɗauke idanunsa daga kan Sunaiha ya mayar wurinta, ya ce "ina jinki Anty Babba"

"Meyasa wannan bikin ba ka bari mun tara mutane ba? Iya mu kawai ka tsara"

"Ina kishinta ne, sai yanzu ma nake jin har ku da ban gayyato ku ba" ya ƙarasa yana murmushi

Muhsin ya ce "jar uba, see this guy, to ni dai i'm leaving"

Safwan ma ya ce "we're leaving dai"

Dariya matan suka yi da sauran mazan, Sadeeq kuwa yana dariya ya ce "i'm sorry, ba haka nake nufi ba fa"

Anty Sadiya ta ce "Muhsin ku ƙyale shi, ai gobe ma rana ce, zan ga waɗanda zai nema ai"

Zama suka yi suna mishi wani irin harara, shi kuwa dariya yake yi (wai dama Sadeeq na dariya haka?)

Anty Sadiya ta ci gaba "saboda mu ƙayatar da wannan party ɗin, mun shirya competitions tsakanin Jewel's team da Prince team, sannan duk team ɗin da suka yi winnning, akwai gifts ɗin da Tiger ya tanadar musu, i hope you're all ready, kuma Jewel's team kar ku ba ni kunya"

Muhsin ya ce "haba Anty Sadiya, ya za ki nuna ba kya tare da mu?"

Sharif ya ce "this is not fair"

Anty Sadiya ta ce "see me see trouble, nima fa i'm part of Jewel's team, ka ga kuwa ai dole su zan yi supporting, right?"

Salma ta ce "manta da su Anty Sadiya, we will win"

Aryaan ya ce "how sure are you about that?"

Anty Najma ta ce "we have the confidence ne ai, we trust ourselves, right!?"

Gaba ɗaya suka amsa da "hundred percent kuwa"

Safwan ya ce "ku tsaya ma, ban ga judges ba"

Sajeed ya ce "kuma Ya Safwan ba ma so Anty Sadiya tayi judging, za tayi mana mugunta"

Dariya suka yi, Anty Saudat ta ce "ni inyi?"

"Halinku ɗaya, gwara ma Anty Nasreen"

Sauban ya ce "ba kayi komai ba ai"

Sameer ya ce "ai ni matan nan ba wacce na yarda za tayi mana adalci yanzu"

Ikram ta ce "to ku tsaya ku ji, kawai couples ɗin su yi judging"

Anty Sameera ta ce "yawwa shikenan ma, good idea"

Sultana ta ce "amma fa ayi tsakani da Allah, Ya Sadeeq kar ka mana cuce"

Sadeeq ya ce "ok, ni ne ma ba ki yarda da ni ba, Ki ja wa Sunie kunne ita ma"

Sunaiha ta ce "ai ta san mata muna da adalci ne"

"Mu ba ma da shi?" Ya tambaye ta

"Da sauƙi dai" ta faɗa tana dariya

Jinjina kai yayi yana wani murmushi, ya ce "okay...ok... shikenan a fara"

Ba ɓata lokaci suka fara gudanar da competitions ɗin cike da farinciki, sai dariya suke gwanin burgewa har suka gama, daga ƙarshe aka haɗa sakamakon gasar, cike da murna Anty Sadiya tayi announcing Jewel's team ne suka yi winnning, nan kuwa suka sa ihu sai tsalle ƴan matan ke yi

Sharif ya ce "laifinka ne Oga Tiger, meyasa ka bari suka yi winnning?"

Dariya Sadeeq yayi ya ce "a gabanka fa aka ce ba ma da adalci"

Safwan ya ce "oh, shiyasa ka ba su mark da yawa?"

Muhsin ya ce "yana tsoro su yi losing ne Madam ta rikice masa, wai shi Romeo" ya faɗa yana harararsa

Sajeed ya ce "ka gani ko Ya Tiger, ka ja mana, sai dariya suke wa mutane"

"Oh no, sorry dear, ka san me, ka ƙyale su, ai yanzu za muyi competition ni da Sunaiha, kuma ni zan yi winnning, ka ga shikenan na rama mana"

"Ka tabbata za ka yi winnning?" Cewar Sajeed

"Yes Bro"

Aryaan ya ce "Allah ya sa za ka yarda kayi winnning ɗin"

"Just wait and watch"

Su dai in banda dariya ba abunda suke musu, Safna ta ce "Anty Sunaiha kar ki bari yayi winnning, yanzu ma team ɗin mu muke so yayi winnning"

"An gama My dear" Sunaiha ta faɗa tana murmushi

Wani ɗan bowl Anty Sadiya ta ɗauko ta ajiye a kan table, cike yake da ƙananan takardu da aka rubuta tambayoyi a ciki, tambayoyin abunda suka shafi Sadeeq da Sunaiha ne, a tsarin gasar, mutum ɗaya daga team ɗin Prince zai ɗauko tambaya ɗaya sai yayi wa Sunaiha akan abunda ya shafi favorites ɗin Sadeeq, idan ta amsa sai mutum ɗaya daga team ɗin Jewel ta ɗauko wata tambayar ta yi wa Prince shi ma akan abunda ya shafi favorites ɗin Sunaiha, haka za su tayi har tanbayoyin su ƙare, Anty Saudat da Saif ne judges ɗin yanzu

Haka kuwa aka yi, daga ƙarshe Sadeeq ya tashi da total mark ɗin 19 out of 20, Sunaiha kuma 11 out of 20. Nan mazan su ma suka sa ihu suna musu gwalo, gaba ɗaya suka wani haɗe rai har Sunaiha

Sameer ya ce "shikenan kun rasa gift, mu za'a ba wa"

Sultana ta ce "wa ya gaya maka? Mu ke da gift ai, saboda a gasarmu, mu ne muka yi winnning, wannan ma ai mugunta ku ka yi, saboda Ya Sadeeq sai da ya tabbatar ya gama bincike sosai akanta sannan yayi wannan gasar"

Sharif ya ce "sai yanzu za ki wani tsaya kame-kame, Malama kawai mu ne da gift"

Sajida ta ce "mu dai ba za mu yarda ba, ai ba'a ba ta time ɗin da ta san komai akansa ba"

Sadeeq murmushi yake yana saurarensu, kallon fuskar gimbiyar yayi, har yanzu ta ƙi yin murmushi, sai ya ce "to shikenan ku tsaya, zan yi wa Sunie tambaya ɗaya, idan har ta amsa ta daidai a kalma ɗaya, shikenan zan bar mata, ita tayi winnning, sai in ba ta gift ɗinta"

Aryaan ya ce "Tiger ba ka so a zauna lafiya"

Muhsin ya ce "ai na gaya maka dama"

Murmushi kawai yayi ya ce "tambayar tana da sauƙi, are you ready for it?"

Ta ɗaga mishi kai, ya ce "who do i love most?"

"Oh no Ya Sadeeq, ai ta san wannan, ita ce mana" cewar Sauban

Girgiza kai Sunaiha tayi ta ce "ba ni ba ce, Umma ce, you loves her alot"

"You get it right" ya faɗa

Wani sabon ihu suka saka, su kuwa mazan sai haushi suke ji, kallonsu yayi ya ce "i'm sorry, next time za mu yi winnning, after all ai mu maza ne, we can accept defeat saboda suyi farinciki, we can do anything for them, amma su ma sun san we're ahead of them, kuma gift na kowa da kowa ne a nan"

Jin abunda ya faɗa ne yasa suka saki fuska suka fara jin daɗi. Muhsin ne ya je mota ya ɗauko wani ƙaton kwali ya ajiye akan table, sannan ya ce "here's the gift, amma wannan ba wai na winners ba ne ko losers, kyauta ce da ta fito daga ƴan uwa, zuwa ƴan uwansu, Safwan da Sadeeq suka haɗa kuɗinsu, suka siya muku"

Sai kallon juna suke yi suna so su ga menene? Ba ɓata lokaci Muhsin ya fitar da su, latest phone of the year ne(2018), a ƙalla kuɗin ko wace guda ɗaya ya kai naira dubu ɗari da sha biyar, duk wanda ke wurin sai da aka ba shi banda Sadeeq ɗin da Safwan sai kuma Sajeed, daɗi suka ji sosai daga fuskokinsu kawai za ka gane, addu'a suke musu sosai

Sajeed ya wani ɓata rai ya ce "Ya Sadeeq, Ya Safwan, ni ne kawai ban samu gift ba, meyasa kuka ba da gift ɗin waya tun da kun san Alhaji ya ce sai mun kai SS2 sannan za'a fara ba mu waya, ni kuma ina primary 5" magana yake kamar zai yi kuka

Sadeeq ya ce "wa ya gaya maka ba ka da gift, ai ba mu manta da kai ba auta"

Safwan ya miƙa mishi laptop sabuwa dal ƴar madaidaiciya, ya ce "here's yours"

Buɗe ido yayi ya ce "system!!!?"

"Of course, ka ga ka huta da zuwa aro dan kayi kallo da buga game, ana maka yanga" cewar Sadeeq

"Thank you so much Ya Sadeeq da Ya Safwan, i love you...kuma ba wanda zan ara ma wa, more especially ma Anty Sultana, ta fi kowa iya aron abun mutane"

Dariya suka yi baki ɗaya ta ce "sai na ara ɗin"

Sadeeq komawa yayi kusa da Sunaiha ya tsaya, ya ɗauki wani ɗan ƙaramin box dake kan table ya miƙa mata, ya ce "and this is your next gift"

Kallon box ɗin tayi da kyau, sannan ta karɓa ta hau buɗewa, gaba ɗaya idonsu na kai, jira suke yi su ga ko menene, makullin mota ne, ta ce "it's a car key, this is too much Prince"

"You deserve more My Baby, je ki duba motar" ya faɗa yana nuna mata motar da ke lulluɓe a parking space, wacce tun farkon zuwanta gidan ta lura da ita, sai dai ko tayar motar ba ta taɓa gani ba saboda a lulluɓe take

Zuwa tayi ta tsaya gaban motar, Sameer da Sharif suka zo suna cire lulluɓin motar, hannu biyu ta sa tana rufe baki tare da buɗe ido, cike da tsananin farin ciki da murna ta ce "My dream car!!!"

Mota ce ƙirar Acura MDX, royal blue colour, sai ɗaukar ido motar ke yi, ba Sunaiha kaɗai ba, gaba ɗayansu shauƙin son motar ne ya taso musu, banda Sharif da Muhsin sai Anty Sadiya kasancewar sun san da ita. Sabuwar mota ce, ba ko ina ake saurin samunta ba sai wurin manyan dilolin motoci, ta daɗe tana son motar, ba ta ma yi tsammanin ta iso Nigeria ba

Daɗi take ji sosai, gaba ɗaya ta ma manta da mutanen da ke wurin, ta juya ta rungume shi

sosai, ta ce "thank you so so much My Prince, i love you, you're the best husband and lover ever, i love you"

"Don't be so excited just because of this, there are much more ones to come, i can do anything for you Jewel, i love you and i will always love you till eternity"

Wani irin ihu suka yi suna musu tafi, sai a lokacin ta dawo duniyar da suke, cike da kunya ta sake shi sannan ta nufi ƙofar parlour da gudu, Anty Saudat kuwa ta bi ta ɗaki dan ta ba ta haƙuri kan abunda ya faru a baya

Sadeeq ya ƙarasa kusa da Nasreen ya ce " Hajiya ba mu san favorite car ɗinki ba, amma mun yi magana da su kan cewar gobe za ku je ki zaɓa, idan ma babu, za mu yi wa Alhaji magana a kawo"

Murmushi tayi ta ce "ni kuma Oga Tiger, ai ban iya mota ba"

"Haba har kin isa? Kina da Safwan ɗin ne za ki ce ba ki iya mota ba? Ai dole zai ajiye komai ya koya miki, idan ba haka ba kuwa za mu shiga kotun da ba alƙali a cikinta, kin ga shari'a sai yanda muka ga dama"

Dariya tayi ta ce "haka ne kam, to godiya nake Tiger"

"A'a ba ruwana, ki gode wa Mijinki, shi yayi ba ni ba"

"Ai godiyar sa ta musamman ce"

Dariya yayi ya ce "oh!!"

Muhsin ya ce "ni dai idan ka gama zo muyi magana kasan zan wuce ne"

Gefe suka koma, Muhsin ya ce "Tiger na riga da na shirya wa barin ƙasar nan yau, kuma sati ɗaya zan yi ko kwana biyar, zan bar maka amana kafin in dawo"

"Wane irin amana kuma Yareema?"

"I think i'm in love"

Baki buɗe Sadeeq ya ce "what!!? Are you serious Muhsin? With who?"

Ɗaga kai yayi, ya ce "ga ta can"

Kallonta Sadeeq yayi ya ce "Najma?"

"Yeah, i love her, and i don't want to lose her, please ka san yanda za kayi kafin in dawo"

"Like serious, i just can't believe it Dude! You're finally in love! I'm so happy, zan so in fara gaya wa mai martaba"

"Malam ka jira tukunna sai na yi confessing love ɗin kuma na samu karɓuwa"

"In sha Allah ma ka karɓo Yareema, Allah ya kaimu ranar biki"

Ɗan tsaki Muhsin yayi ya ce "it's like yau kana farinciki da yawa, anya kuwa na taɓa ganinka haka?"

"Muhsin kenan, ai idan ba ka ga ina farinciki haka yau ba, akwai matsala, kai ka san yanda na daɗe ina jiran wannan ranar, sannan kuma yanzu ka zo mun da zancen nan, dole yau zan zama Abubakar Sadeeq, ba Tiger ba"

Dariya suka yi baki ɗaya, kafin Muhsin ya je yayi sallama da su, suka mishi addu'a sannan Sadeeq ya raka shi airport, a hanya suka gama magana kan zai yi wa Sunaiha zancen sai ta sanar da Najma, sai da jirginsu ya tashi kafin ya dawo gida

Lokacin da ya dawo gaba ɗaya sun wuce dan kusan ƙarfe 11:14pm, Sunaiha idonta biyu, sai da yayi wanka kafin suka ci abinci dan tayi wankanta tun ɗazu, sannan suka je suka kwanta, sun daɗe suna fira kafin suka yi bacci

Washe gari da safe, yana gama breakfast misalin ƙarfe takwas ya fita, asibitin da ya tabbatar Kawu Ƙarami na can ya nufa, sai da suka gaisa kafin Kawu Ƙarami ya ce "Sadeeq lafiya dai na ganka yanzu?"

"Lafiya ƙalau Kawu, wata alfarma na zo nema dan Allah"

"Na me kenan Sadeeq?"

Cike da girmamawa ya ce "Kawu na san Momi ta ɓata maka rai sosai, na san bata kyauta ba kuma, sai dai Kawu ban gaya maka abunda tayi ba dan ka kore ta, na san ɓacin rai ne kai ma ka san bai dace ka kore ta ba, Kawu dan Allah kayi haƙuri ta dawo ko dan su Sajeed, dan Allah Kawu"

Numfashi ya sauke ya ce "Sadeeq kenan, ai ko sakinta nayi ban yi laifi ba, ita ta ja wa kanta, sannan kuma ai ta san da ƴaƴan nata amma tayi abunda tayi"

"Kawu dan Allah kar ka duba hakan, kayi haƙuri ta dawo"

"To Sadeeq idan ni nayi haƙuri, kai kuma fa da sauran ƴan gidan da su Baba?"

"Kawu wallahi ni na yafe mata, sauran kuma na san ma za su yafe mata idan suka ji hakan, amma dan Allah ba sai an gaya musu ba, har su Grandpa"

"Sadeeq ba ka gama sanin Basira ba ne"

"Kayi haƙuri dai Kawu dan Allah, ba zan iya jure ganin su Salma cikin ɓacin ran rashin uwa a kusa da su ba, tana da muhimmanci sosai a rayuwarsu"

Shiru ya ɗan yi kafin ya ce "shikenan na ji za ta dawo, amma gaskiya ni ba zan iya kiranta ba ma"

"Da izininka ma sai in je in dawo da ita"

"Duk yanda kayi Sadeeq daidai ne"

"To Kawu Nagode sosai" yayi mishi sallama sannan ya fito

Kai tsaye gidansu Sarah ya nufa, har cikin parlour aka mishi iso ya shiga, sai da suka gaisa kafin Mahaifiyar Sarah ta ce "Sadeeq dama ina so zan ganka in baka haƙuri....."

Ya katse ta "ba komai, ya wuce, Allah ya tsare gaba"

"Ameen Sadeeq" ta amsa ita ma kai a ƙasa kafin ta miƙe ta bar shi da Momi

"Sadeeq, wallahi nayi nadama, ban san da wane ido zan kalle ka ba in baka haƙuri, dan girman Allah ka yafe ni"

"Momi you're like a mother to me, kuma ɗan adam ajizi ne, dole zai aikata ba daidai ba, amma a dinga kula, a san me za'a aikata"

"Wallahi zan dinga kulawa Sadeeq, ka yafe mun"

"Ni na daɗe da yafe miki Momi, Allah ya yafe mana baki ɗaya, bisa umarnin Kawu na zo in mayar da ke gida"

"Ka mayar da ni gida Sadeeq!!?"

Ta tambaye shi da mamaki, dan ba ta taɓa tsammanin komawarta nan kusa ba, ya ce "eh, kiyi sauri saboda zan je wurin aiki" yana gama faɗa ya fita

Shiga tayi ciki cike da murna ta haɗo kayanta suka yi sallama da Mahaifiyar Sarah sannan suka wuce. Ko bayan isarsu gida, kowa yayi farin ciki da dawowarta ban da Hajiya da gaisawa

kawai suka yi ta nufi ɓangaren ta, Sultana da Salma sai dadɗ suke ji, sauran yaran kuwa da ba su sani ba, Umma ce musu tayi ai tafiyar kwana biyu tayi, haka suka yi ta murna, Momi ta so ta nemi gafarar Umma, amma ta nuna mata bata son ta tayar da maganar, komai ya wuce

Sadeeq kuwa wurinsu Grandpa ya fara zuwa, kafin ya wuce asibiti ya ci gaba da aikinsa cikin kwanciyar hankali, dan ji yake ba wanda ya kai shi jin dadɗ yanzu. Kusan ƙarfe uku na rana, Sameer ya shigo office ɗin shi

Ya ce "Sameer? Lafiya na ganka nan?"

"Lafiya ƙalau Ya Tiger, wani aboki na ne aka kawo mahaifinsa asibitin nan jiya, shi ne na zo duba shi sai na biyo ta nan"

"Oh, Allah ya ba shi lafiya, amma da sauƙi?"

"Eh da sauƙi, Ameen"

Ajiye wayar hannunsa yayi, ya kalli Sameer ya ce "kamar ka san kuwa nemanka nake yi kai kaɗai"

"Allah ya sa ba laifi nayi ba"

"Laifi kayi mana, tunda har za ka iya ƙuntatawa zuciyarka"

Murmushi Sameer yayi ya ce "me nayi to Ya Tiger?"

"Dariya ma na baka kenan, wallahi Sameer na yi experiencing yanda mutum yake ji idan yayi ta ɓoye soyayya a zuciyarsa ba tare da ya bayyana ba, it really hurts... ba ka tsoron ayi maka overtaking? Kana zaune kawai ka ji an bayar da ita?"

Da mamaki sosai Sameer ke kallonsa, kar dai ya fahimci abunda ke ransa da daɗewa?, Ya ce"Ya Sadeeq what do you mean?"

"Ka sani, ka san me nake nufi, kawai kana mamakin yanda na sani ne ko? Sameer na daɗe da fahimtar kana son Sultana, amma na rasa dalilin da yasa ba za ka iya gaya mata ba"

Shiru yayi kafin ya ce "Ya Sadeeq ban san yanda za ta ɗauki kalmar bane, ka san yanda muke da ita, always teasing each other, kar in gaya mata ta ƙi amincewa"

Murmushi Sadeeq yayi ya ce "amma sai nake ganin kamar za ta amince...but ina da wani idea, wanda duk yanda ta so ta ja maka class ta wahalar da kai, idan kayi using wannan method ɗin baza ta iya ba"

Dariya Sameer yayi, ya ce "wane irin method ne kenan?"

"Method ɗin da na so in bi dan gaya wa Sunaiha ina sonta amma ta rikita ni, dole na faɗa ban shirya ba, da ace ba ta rikita mun lissafi ba, a partyn da aka yi jiya na so gaya mata ina sonta,kuma da tuntuni anyi shi ba wai jiya ba"

"Ka gaya mun to Ya Sadeeq"

Tashi yayi daga kan kujerarsa ta aiki, ya dawo ya zauna kan wacce ke facing ɗin Sameer da kyau, sannan ya ce "Sameer akwai wani abu da na fahimta a mata, idan ka fito straight forward ka gaya mata kana sonta, to sai ta ja maka aji kafin ta gaya maka abunda ke ranta, amma idan ka fara nuna mata irin muhimmancin da take da shi, and you make her feel so special, ta ji ta kamar duk duniya ka fi kowa sonta, ka bata kyautar abunda ta fi so sannan ka gaya mata kana sonta, to ba sai ta amsa maka ba, daga reactions ɗinta kawai za ka ba wa kanka amsa...and hakan ba wai ina nufin mata sai da kuɗi ba, no, tabbas akwai matan da sai da kuɗi, waɗannan ba za ka sa su a jerin masoya ba saboda kuɗinka suke so ba kai ba, ina magana ne akan matan da kuɗinka ko wani abu na ka ba ya gabansu, kai ɗin kawai suke so, matuƙar kayi musu haka zai yi wuya kayi failing, although dama zuciya tana son me kyautata mata ne, sannan matan arziki ba mayun kuɗi ba, sun fi buƙatar kulawarka da lokacinka fiye da komai, just think about it"

Jinjina kai Sameer yayi ya ce "wannan gaskiya ne Ya Sadeeq, na yarda da hakan sosai...to amma Ya Sadeeq ta ina zan fara?"

"Zan taimaka maka for sure, a sani na, Sultana na matuƙar son agogo da zobe, wannan kowa ya sani kap family...to ina so kafin gobe, ka siyo mata zobe da agogo, kuma ka tabbatar da ka zaɓo masu masifar kyau yanda kallo ɗaya zai tafi da ita, na san ka iya zaɓe"

Murmushi Sameer yayi ya ce "in sha Allah kuwa za siyo"

"Yawwa, zuwa gobe sai muyi magana"

"Thank you so much Oga Tiger"

Murmushi yayi, sun kai mintuna ashirin suna ashirin suna fira kafin Sameer ya wuce

Da daddare Sadeeq su na parlour tare da Sunaiha yake gaya mata Muhsin na son Najma, tayi matuƙar farinciki da jin haka, ta ce "i can't wait to tell her, wallahi na ji daɗi, kuma ka san ba ta taɓa kula kowa ba, Allah sarki ashe babban rabo ke jiranta, wa ya ga Anty Najma a gidan sarauta"

Dariya yayi ya ce "gimbiya Najma, kafin ta zama sarauniya Najma"

"Amma ka san ba ta son harkar sarauta kuwa!? Ko kallon films ɗin da ya danganci sarauta ba tayi, wai yanda suke jin kansu haushi yake ba ta"

"Anko suka yi kenan, haka Muhsin yake, Allah ne yayi shi a gidan sarauta amma sam ba ya son abubuwan mulkin nan, idan fa ba wanda ya san Muhsin ba, ba wanda zai gan shi ya ce yana da alaƙa da masarauta"

"Wallahi kuwa, he's different, Allah ya tabbatar mana da alkhairi, in sha Allah gobe zan tafi in gaya mata"

Dariya ya fara yi kafin ya ce "mun zama ma su haɗa masoya ne ko me? Nima fa gobe akwai plan ɗin da zan yi akan Sameer da Sultana"

"Sameer da Sultana? Dama suna soyayya ne?"

Ba ta labarin komai yayi, sannan da plan ɗin shi da yake shirin yi gobe

Ta ce "ai kuwa za su bada perfect couples, to gaskiya ba za'a bar ni ba, duk da dai ka ce su biyu kawai za ka yi wa shirin dan su fahimci juna, ba komai, amma dai i'll help, zan kawo Sultana har wurin, saboda yanda suke ka san ba lallai yana kiranta za ta zo ba, amma idan ni ce kai tsaye zata biyo ni without hesitation"

"Eh haka ne kuma, da kin taimaka...Allah ya tabbatar masu da alkhairi su ma"

"Ameen"

Wannan ɓangaren kuwa, Najeeb ne a ɗakin wani abokinsa yana shan shisha, abokinsa ya kalle shi ya ce "Najeeb abun nan fa ya fara maka yawa, kusan kwana uku kenan da ka ɓata kanka da shan shi da yawa, kar ya taɓa lafiyarka fa"

Najeeb ya gama fita hayyacinsa, idanunsa sun yi ja sosai, magana yake kamar ba shi ba, ya ce "JB, idan ka ga na koma normal yanda ka sanni, to tabbas na ga bayan wancan mutumin, ba'a taɓa ko da mari na ba, amma ya iya duka na!? To wallahi sai na kashe shi hankali na zai kwanta, kuma gobe goben nan zan yi hakan...za ka ara mun bindigar ne ko kuwa?"

JB ya ce "ba ara maka bane ba zan yi ba, kar ka jefa mu a matsala ne kawai, ka ga ba wanda ya san ina da bindigar nan sai kai saboda ba na amfani da ita a cikin gari"

"Dalla can matsoraci kawai, ba wata matsala, idan ma har kama ni aka yi, zan ce nawa ne, ba zan ambaci sunanka ba, bare ma ba wanda zai iya kama ni, zan aika shi ne kawai in dawo"

JB ya ce "to shikenan, da daddare zan je in ɗauko, sai in kawo maka da safe"

Jinjina kai kawai yayi ya ci gaba da busar hayaƙinsa............

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*
_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~~
_The worst pain in lyf is when you see ur lyf being spoiled by the one you trust most & you can't do anything except standing quite & asking yourself, Is it the gift of Trusting??_

**Page 85&86**

Washe gari da misalin ƙarfe ɗaya na rana, Sadeeq ya kira Sameer ya gaya mishi park ɗin da
~~~~~~~~~~~~~~~~~

za su haɗu, kafin ya fita. Ita ma Sunaiha kiran Sultana tayi ta gaya mata ta shirya, za ta zo ta ɗauke ta, za ta raka ta

Cike da murna Sultana ta shigo cikin parlourn su, Salma na kan kujera a kwance tana kallo, wucewa tayi cikin ɗakinta, ba tafi mintuna goma ba ta fito cikin shirin abaya fara, aikin jikinta da stones maroon, tayi rolling mayafin, Masha Allah

Kallonta Salma tayi da kyau, ta ce "ina za ki je kuma?"

Sultana ta ce "Anty Sunaiha zan raka wani wuri, ke ma ki tashi ki shirya mu tafi"

"Ta zo ne?"

"A'a, kira na tayi dai"

Komawa tayi ta kwanta kafin ta ce "ki je kawai, kai na ke mun ciwo ba zan iya yawo ba"

"Amma kin san na fi jin daɗin yawo tare da ke"

"To ai na ga da Anty Sunaiha za ku tafi, then what's the big deal, wallahi kai na ciwo yake mun, i'm sorry"

Kallonta Sunaiha ke yi har ta gama magana, ta ce "shikenan, Allah ya ba ki lafiya"

"Ameen" Salma ta amsa, juyawan da za tayi ne ta lura da takalminta ne a ƙafar Sultana, ta ce "wai ke kayanki ba sa miki ko, ki dawo ki ajiye mun takalmi, ke ma fa kina da shi"

Dariya Sultana tayi ta ce "eh ina da shi ɗin, amma yau na ki nake so in saka"

Da sauri Salma ta miƙe ta nufe ta tana faɗin "ai kuwa yau sai kin ajiye mun takalmi" kafin ma ta samu kamo ta, har ta bar ɗakin da gudu tana dariya, rufe ta tayi daga waje tana ta dariya

Salma ta ce "ki buɗe kofar nan, kuma ki dawo mun da takalmi, na dai gaya miki" magana take tana jan ƙofar

Sultana na dariya ta ce "sai na fita da takalmin nan yau yarinya kiyi haƙuri kawai, idan na sauka main parlour zan turo miki da Safna ta buɗe ki, sai na dawo, i love you" tana gama faɗar haka ta wuce tana dariya, Salma kuwa rai a ɓace ta koma ta kwanta kan kujerar ta ci gaba da kallonta, ta ce "har ta ƙara mun ciwon kai, za ki sani"

Lokacin da ta sauka parlourn, ta tarar da Sunaiha a parlourn tare da su Umma da Momi suna ƴar fira, ganinta ke ya sa Umma ta ce "ke ba make up ba, amma duk wanda zai jira ki sai kin ɓata masa lokaci"

"Umma ai ban san ta zo ba" ta faɗa tana turo baki

Murmushi Sunaiha tayi ta ce "to mu tafi...Umma sai mun dawo, Momi sai anjima"

Umma ta ce "to Allah ya kiyaye"

Momi ma ta ce "A dawo lafiya"

Amsawa suka yi da ameen kafin suka fita, suna shiga mota, Sultana ta ce "ni ce first da shiga motar nan" ta ƙarasa tana jin daɗi

Sunaiha murmushi tayi ta ce "saboda nafi sonki ne" tana gama faɗar hakan ta tayar da motar ta bar gidan

Daga tsallaken gidan, wasu maza ne guda biyu, kallo ɗaya za ka musu ka fahimci ba sa da gaskiya, ɗayansu ne ya ɗauki waya ya kira, ana ɗagawa ya ce "Oga Najeeb, ta sake barin gidan yanzu amma ba tare da Sadeeq ɗin ba, da wata ce"

Daga ɗaya ɓangaren Najeeb ya ce "ku ci gaba da bibiyarta, na tabbata za ta sada mu da wurin da Sadeeq ɗin yake, idan ma ba ku gan shi ba, kawai ku ɗauko mun ita, shi da kanshi zai kawo kanshi, ka ga riba biyu kenan, zan kashe shi ita kuma in bar ƙasar nan da ita"

"An gama Oga Najeeb" ya kashe wayar sannan suka hau mashin suka ci gaba da bin motar Sunaiha

Babban park ɗin garin ta nufa kai tsaye, ta samu wuri tayi parking motar sannan suka fita. Ganin haka ya sa masu bibiyarsu kiran Najeeb, gaya mishi wurin da suka zo suka yi

Ya ce "ku jira ni, ina kusa da wurin, yanzu zan zo within few minutes"

"Ok" ya faɗa sannan suka zauna suna kallonsu a fakaice

Eatery ɗin cikin park ɗin su Sunaiha suka nufa, ta nuna ma Sultana wuri ta ce ta jira ta, ita kuma ta shiga VIP section

A nan ta tarar da Sameer da Sadeeq, wani gefe ta ga sun yi decorating ɗin shi so simple kuma yayi kyau sosai, sai rose flowers ɗin da suka watsa kan table, daga tsakiya kuma wani gift box ne a kai

Ta ce "wow! Awesome! Good job My Prince, da alama sai ka fara decorating ɗin wuri musamman wa masoya, za muyi kuɗi fa" ta faɗa tana dariya

Sameer ma dariyar yayi ya ce "ai Anty Sunaiha kallonsa kawai nake tayi, ban taɓa tsammanin Ya Tiger yana da lokacin irin wannan abun ba fa, ashe he's an expert"

"Wallahi kuwa" cewar Sunaiha

Murmushi Sadeeq yayi ya ce "to idan kun gama sai ki saurare ni, ina Sultana?"

"Tana daga waje, na zo in gani ne idan kun shirya sai ta shigo"

Sadeeq ya ce "everything is ready, Sameer all the best" daga haka ya ja Sunaiha suka fita

Sultana na ganin Sadeeq ta ce "Ya Sadeeq dama kana nan?"

"Yeah, ki shiga ciki, Sameer yana nan"

"Ya Sameer kuma? Menene?"

"Yana so za kuyi magana ne"

"Sabon salo kenan" ta faɗa tana dariya, kafin ta shiga

Zama suka yi kan kujera bayan ta shiga ciki, aka kawo musu coffee su na sha suna fira

Sultana kuwa tana shiga ta saki baki tana kallo, tana taku a hankali har ta kai kusa da shi ta tsaya, ta ce "Ya Sameer what's all this?"

Murmushi yayi ya ce "it's for you"

"For me?" Ta faɗa cike da mamaki

"Yes...yau ba faɗa, akwai abunda zan gaya miki me muhimmanci, let's sit first"

Ba musu kuwa ta zauna dan ba ta ga alamar wasa a fuskarsa ba, he's serious. Nuna mata gift box ɗin yayi, ya ce "open this, it's yours"

Sai da ta kalle shi sosai kafin ta fara buɗewa, farinciki ne ya bayyana a fuskarta bayan ta ga wani zobe me kyau sosai, sai sheƙi yake, ta sake kallonshi ta ce "it's mine?"

"Yes" ya faɗa yana murmushi saboda ya ji daɗin yanda zoben ya burge ta

Zoben hannunta ta cire ta saka wannan ɗin, sai juya hannunta take tana murmushi saboda yayi ma farin hannunta kyau, ta ce "lallai yau Ya Sameer ka so zaman lafiya, thanks"

Ta ci gaba da buɗewa, kyakkyawan agogo ta gani, na mata ne ɗan siriri me haɗe da bracelets guda biyu, ɗaya shape ɗin heart ɗayan kuma an rubuta LOVE, ƙara faɗaɗa murmushinta tayi ta hau cire na hannunta ta fara saka sabon

Tana gamawa ta buɗe wata ƙaramar takardar da ta gani, ta fara karantawa kamar haka:

'It is very hard to pretend that you love someone when you don't, and it is even harder to pretend that you don't love someone when you really do...'

Ɗaga ido tayi tana kallonshi dan neman ƙarin bayani, bai bari tayi magana ba, ya ce "I love you, I love you Sultana, I just wish that for one moment you could be me, and maybe, only then you'll realize how much I love you, I love you each and every second..I truly loves you"

Kallonshi take yi sosai tana ji gabanta na faɗuwa, sai kawai ta ɗan juyar da fuskarta tana kallon waje ta window tana murmushi. Shi ma kallonta yake yi yana so ya ji me za ta ce

Gaba ɗaya ta kasa cewa komai, sai kallon waje take yi tana ta murmushi, a lokacin ne ta hango wani mutum a tsaye da bindiga a bayan wata bishiya, sai saita ta yake yi, haɗe gira tayi da mamaki tana ƙara kallon shi

Miƙewa tayi ta ƙarasa kusa da windown ta leƙa da kyau dan ta ga waye wannan ke so ya harba, gabanta ne yayi mummunan faɗuwa ganin Sadeeq a tsaye yana waya bai ma san da mutumin ba

Da ƙarfi ta ce "Ya Sadeeq!!!" Sai kawai ta juya a guje ta fita, Sameer na ganin haka ya tashi ya bi ta shi ma da gudu dan ya ga ko lafiya? Sunaiha ma tana zaune ta ga Sultana ta fita da gudu, Sameer shi ma ya biyo ta, ba ta tsaya ɓata lokaci ba ita ma ta bi bayansu

Tana fita waje ta sake kallonshi, ta ga da gaske harba bindigar zai yi, ta ƙarasa kusa da Sadeeq da gudu ta ture shi gefe, hakan yayi daidai da harba bindigar, kusa da zuciyarta harsashin ya shiga, sai da ta ja dogon numfashi kafin ta sauke a hankali tana kiran sunan Sadeeq, wanda ya jefar da wayar hannunsa da sauri ya riƙe ta, ya ce "Sultana!!!"

Ɗaga idon da zai yi suka yi ido huɗu da Najeeb da ya hau mashin suka bar wurin da gudu, Sadeeq na ƙoƙarin sake mata hannu ta sake riƙe shi, dole ya durƙusa ya rungume ta, Sunaiha ma durƙusa wa tayi tana kuka, Sameer ma kasa motsi yayi, mutanen wurin dama can ba sa da yawa, sun zagaye su suna ta salati

Sadeeq da idanunsa suka cika tab da hawaye, a rikice yake kiran sunanta, yana cewa "Sultana!! Sultana open your eyes dan Allah"

Da ƙyar take buɗe ido, sai ƙara riƙe shi take yi tana numfashi da ƙyar, ta ce "Ya...Ya Sadeeq"

"Sultana what have you done? Meyasa?" Ya ƙarasa maganar hawaye na bin fuskarsa

Da ƙyar ta ce "stop crying My Tiger...ba zan..ba zan iya jure rashinka ba, i'll be haa happy idan ni ce na mutu, ba...ba kai ba"

"No Sultana, ba za ki mutu ba, nothing will happen to you"

Murmushi kawai tayi, Sadeeq ya ɗaga kai ya kalli Sameer ya ce "ɗauko mota mu tafi asibiti Sameer"

Sam bai ma san yana yi ba, kallonta kawai yake yi kamar wani hoto, wani mutum ne ya taɓa shi, sai a lokacin ya dawo hayyacinsa, wasu zafafan hawaye suka gangaro, a hankali ya ce "Sultana!"

Sadeeq ya ce "we don't have much time Sameer, ka ɗauko mota" bai ma gama rufe baki ba Sameer ya juya da gudu

"Ba abunda zai same ki Sultana" cewar Sadeeq yana kuka

A hankali ta ɗaga hannu ta shafa fuskarsa ta ce "ka daina kuka Yayana...ina..ina sonka sosai, ina son kowa na gidanmu, ka gaya musu.. sannan...sannan ka kula da Anty Sunaiha sosai, da Umma na, da.. da Salma, kuma ka gaya wa Ya Sameer...ina sonsa sosai, i love him!" ta ƙarasa tana rufe ido da ƙarfi tana ƙara jan numfashi

Gabansa ne ya faɗi, ya sake ɗaga ta yana dukan fuskarta a hankali, ya ce "wake up Sultana, wake up"

A lokacin ne Sameer ya tsayar da mota kusa da su, da sauri Sadeeq ya ɗauke ta ya sa ta bayan motar kafin ya shiga ya ɗora kanta kan ƙafarsa, Sunaiha ma ta shiga gidan gaba, Sameer ya fizgi motar da gudu yana share hawaye

Sultana dake ta rufe ido hawaye na bin gefen fuskarta, ta ce "Ya Sadeeq kar mu je asibiti...mu tafi gida in gan su for the last time...Ya Sadeeq ba zan rayu ba na sani...kar...kar ka ɓata lokacin ka a banza"

Ba abunda ya iya ce mata kallon ta kawai yake yi yana kuka yana girgiza kai, ta ci gaba da cewa "Ya Sameer ina sonka...na san..na san abunda kake so ka ji kenan, of course I love you, amma Allah bai ƙaddara za mu rayu tare ba...Ya Sameer...Allah ya ba ka wacce za ta...za ta so ka fiye da ni"

Sameer tuƙi yake yana share hawaye, mayar da kallonta tayi kan Sunaiha, ta ce "Anty Sunaiha... kina ji na?"

Sunaiha na ƙoƙarin controling hawayenta amma ta kasa, ɗaga mata kai kawai tayi, Sultana ta ce "duk wanda ya haihu a family ɗin mu daga yanzu, dan Allah kar...kar ki manta ki ba su labari na...and..and also tell them i love...i love them"

Ta mayar da kallonta kan Sadeeq da yanzu kam kuka yake sosai, ta ce "ka mun alfarma ɗaya Yayana, idan Anty Sunaiha ta.... ta haifi mace, ka saka mata Sultana, idan ma namiji ne, ka saka mishi Sultan, ka ji Yayana, kar wanda ya sa wannan sunan idan dai ba ƴaƴanku ba ne"

Rufe mata baki yayi sannan ya rungume ta yana ƙara kuka ita ma kukan take yi, ba ta sake cewa komai ba, sai kuka da take ta yi tana numfashi da ƙyar har suka isa asibitin, bai jira komai ba ya ɗauke ta zuwa ciki da gudu, su Sameer na bayansa

Doctors da nurses ɗin wurin suka nufe shi da sauri ganin duk farar rigar Sultana ta sauya kala zuwa ja, saboda jinin da ya zuba, ko ta kansu bai bi ba ya shiga theatre room ya ɗora ta kan gado, zai wuce dan ɗauko kayan aiki ta riƙe mishi hannu, kallon cikin idanunsa tayi ta ce "ina alfahari da kai Yayana, ka kula da kanka...da iyayenmu....da Saraki's family baki ɗaya" tana gama faɗar haka ta sake mishi hannu

Bai tsaya ba ya fara haɗa kayan aikin yana share hawaye, ɗayan likitan da ke wurin ne ya duba ta, Sadeeq na juyowa, ya ce "me kuke jira ne? Ba ku san aikinku ba ne?" Maganar yake a hasale yana share hawaye

Likitan ya ce "Sadeeq she's no more"

Wani wawan kallo ya masa da jajayen idanunsa da suka cika da hawayen da suka kasa tsayawa ya ce "don't... don't say that again, idan aikin ne ba za ku iya ba ku ƙyale ni, ni zan yi dan in ceto ran ƙanwata"

Cike da tausayi likitan ya sake cewa "i'm sorry Sadeeq, ta riga mu gidan gaskiya, ba wani abu da za mu iya"

A tsawace ya ce "Stop it!!! Stop dan Allah.....dan Allah ka daina, dan Allah ka daina cewa ta mutu, dan Allah" ya ƙarasa maganar hawaye na zuba

Kawu Ƙarami ne da Sameer da Sunaiha suka shigo ɗakin da sauri, kai tsaye wurin Sultana Kawu Ƙarami ya nufa, taɓa ta yayi ya duba ta da kyau, sannan ya ja baya yana ta maimaita "innalillahi wa'inna ilaihi ra'jiun, lahaula wala ƙuwata illa billa"

Sai da ya matso kusa da Sadeeq sannan ya dafa shi ya ce "Sadeeq, Sultana ta rasu, ka...."

Buge hannun shi yayi daga kan jikinsa ya ce "No! Meyasa kuke so dole sai ta mutu? My sister is still alive, suma tayi kuna cewa ta mutu, i can help her"

Wucewa ya zo yi wurinta, Kawu Ƙarami ya riƙe shi, ya ce "leave me alone, zan taimaka mata, she did this just to save me, dan haka nima ba zan ƙyale ta haka ba"

"An taɓa dawo da mamaci ne wai Sadeeq? Come back to your senses" cewar Kawu Ƙarami

"Ba matacciya ba ce na gaya muku, ku kyale ni!!" Sadeeq ya faɗa a tsawace yana kuka

Saukar mari kawai ya ji a fuskarsa sai da yayi shiru ya natsu bai sake motsawa ba, likitoci da nurses ɗin da ke ɗakin suka fita, Kawu Ƙarami cikin fushi da tausayin Sadeeq ɗin ya ce "me ke damun kanka ne? Na gaya maka ta mutu, ta mutu, me za ka iya yi ne kuma? Ina ilimin ka ya tafi? Sultana ta rasu Sadeeq, kayi haƙuri" ya gama faɗar hakan ya fita waje jiki a sanyaye yana kiran waya

Sameer a hankali yake tafiya har ya isa bakin gadon ya durƙusa yana kallonta yana kuka, kallonta yake sosai, ga hannunta ɗauke da agogonta da zobe

Sadeeq ya zube ƙasa ya kasa cewa komai, Sunaiha da idanunta suka sauya kala ita ma tana kuka ta zo kusa da shi ta durƙusa tana share mishi hawayen da ke zuba

Ta ce "Kayi haƙuri Prince...dan Allah, stop crying"

Kallonta yayi, a hankali ya ce "but you're also crying right? Kiyi shiru mana, don't cry"

Girgiza kai kawai take yi, kamar ya ce ta ƙara kukan ne ba ta daina ba, ya ce "kin gani, ke kanki ba za ki iya dainawa ba, to meyasa ni kike so in daina kuka? She's my sister, kuma saboda ni ta mutu, saboda kawai ta taimake ni ya sa ta tsaya ita ta mutu, and you expect me to stop crying, Sunaiha? I can't, i can't...." Ya ƙarasa wasu zafafan hawaye na sauka, ita ma Sunaiha kukan take yi sosai, ta rungume shi ba mai rarrashin wani

Kusan mintuna biyu sun a haka, sai kawai ya ɗaga ta daga jikinshi, ya miƙe da sauri yana faɗin "impossible!! Wallahi Najeeb kayi kaɗan" Bai tsaya komai ba ya fita da sauri kamar zai tashi sama bayan ya ɗauki makullin motar da Sameer ya yar a ƙasa

Kawu Ƙarami na waje ya gama waya da Safwan da Abba, ya ga wucewarsa, da mamaki ya bi shi da ido, sai ga Sunaiha ta fito, ganin Kawu Ƙarami ya sa ta tsayawa

"Ina zai je haka"

Da dasashiyar muryarta ta ce "ban sani ba Kawu, amma ina kyautata zaton wurin Najeeb za shi"

"Waye Najeeb"

"Shi...shi me wanda ya harbi Sultana"

"Ya san shi ne? Dama ina so in ji ya aka yi aka harbe ta"

"Eh Kawu ya san shi" ta faɗa tana share hawaye

"Yanzu ma ba wannan ba, yanda ya fita ɗin nan anything can happen, kin san wurin da Najeeb ɗin yake?"

"Na san gidansu dai"

"Safwan yana hanya, bari ya zo sai mu tafi tare da ƴan sanda" jinjina kai tayi ta koma gefe ta ci gaba da kuka

Sadeeq kuwa yana fita ya figi motar, bai tsaya ko ina ba sai ƙofar gidansu Najeeb, ƙofar a buɗe take kuma mai gadin ba ya nan, hakan ya ba shi damar shiga kai tsaye, ƙofar parlourn ma a buɗe, yana shiga ya ga mai gadin ya jawo akwatin Najeeb ɗin yana ƙoƙarin fita

Kafin ma ya tambayi mai gadin komai, Najeeb ya sauko, bai lura da shi ba sai da ya kawo tsakiyar parlourn, gabanshi ya yanke ya faɗi

Sadeeq ya nufe kamar wani zaki ya kai mishi naushi a fuska, take jini ya fara fita daga bakinsa, dukansa Sadeeq ke yi kamar an aiko shi, ko tsayawa ba ya yi ya ɗaga, haka ya dinga naushinsa, ya ja shi ya buga mishi a bango, wani vase flower da ke kan center table ya ɗauka ya rafka mishi a kai, faɗuwa ƙasa Najeeb yayi fuskarsa da kansa duk jini, jiri ma yake gani, Sadeeq kuwa idanunsa sun rufe bai ji bai gani, naushinsa yake yi yana kwallo da shi kamar ba mutum ba

Mai gadi na gefe ya maƙale, gaba ɗaya tsoron Sadeeq ya kama shi, sai ka ce mai sabon hauka. Su na a haka ne sai ga Sunaiha ta shigo tare da Safwan, Kawu Ƙarami da ƴan sanda na bayansu

Da sauri Safwan ya riƙe shi, amma ya ture shi gefe ya ci gaba da dukansa, da ƙyar Safwan ya iya riƙe shi da taimakon wasu ƴan sanda su biyu, sai huci yake yi, jikinsa har rawa yake ga shi yayi zafi, idanunsa jajir

Kawu Ƙarami ya ce "meye haka Abbakar? So kake yi ka kashe shi ko me?"

Inspector ɗin da suka zo tare da shi ya ce "me ya rage kuma Alhaji? Ai ya kashe shi, kalli jinin da ke fita a jikinshi"

A hasale Sadeeq ke magana muryarsa har rawa take, ya ce "kashe shi ɗin dai nake so in yi, wannan jinin duk bai wadatar da ni ba, ba mutuwa yayi ba, suma yayi, kuma ina tabbatar muku

sai na kashe wannan tsinannen, shi ya kashe mun ƙanwata, faɗanka da ni ne, meyasa za ka sa ta a ciki? Ba ruwanta, she's innocent...." ya kasa ƙarasawa saboda kukan da ya fi ƙarfinsa

Sakinshi ƴan sandan suka yi, Safwan ya ci gaba da rarrashinsa, shi kan shi idanunsa hawayen ne a ciki

Yayyafa wa Najeeb ruwa suka yi, a firgice ya buɗe ido, yana ganin Sadeeq ya dinga ja baya, ɗaga shi ƴan sandan suka yi, inspector ya ce "Alhaji ba za mu kama shi ba a wannan halin da yake, dole sai mun kai shi asibiti anyi treating ɗin shi kafin mu san abun yi, amma zan ajiye ƴan sanda biyu da za suyi gadinsa har ya warke dan idan muka tafi da shi station a haka zai iya mutuwa, ka ga kai ma kafin nan kun haɗa hujjojin ku"

Kawu Ƙarami ya ce "in sha Allah inspector, na gode"

"Ba komai" sannan suka fita shi da sauran ƴan sandan da Najeeb, su ma su Kawu Ƙarami suka bar gidan

Sai da suka fara ajiye Sunaiha gida, ba tare ma da sun shiga gate ɗin gidan ba, tana fita suka miƙe zuwa asibiti, a nan suka tarar da Abba da Sameer da har yanzu yake gabanta, da Alhaji da su Sauban

Sai da aka fara cire harsashin daga jikinta, sannan suka ɗauke ta, aka je aka mata wanka aka shirya ta, aka kai ta makwancinta

A gidan kuwa, Umma ce ta fara samun labari a wurin Sunaiha kasancewar ita kaɗai ce a parlourn, yanda ta ga Sunaiha ɗin ne ya ba ta tsoro, ta takura mata sai da ta gaya mata, kuka da salatin da Umma ke yi ne ya su Hajiya fitowa su na tambayarta, har ta gaya musu

Salma da shigarta parlourn kenan ta ji abunda suke faɗa, tayi mutuwar tsaye, tana so ta tabbatar, a hankali take matsowa kusa da Umma, ta ce "Umma me na ji kina faɗa? Sultana ta rasu? Kamar ya? As how?" Jero mata tambayoyin take yi kamar yanda hawayenta ke ta jerowa suna zuba

Ɗaga mata kai Umma tayi tana share hawaye, Salma ta ce "Umma dan Allah idan ma wasa kuke mun dan Allah ku daina, kar ku fara wannan wasan, saboda kawai yau na ce ba zan raka ta ba shi ne za ku mun irin haka, don't do that please" magana take tana ƙoƙarin mayar da hawayen, dan ba ma ta so wannan tunanin ya shiga kanta

Hajiya na nata kukan ta ce "Salma an taɓa wasa da mutuwa ne? Da gaske ne ta rasu"

Dole dai hawayen nan na Salma sai da suka fito, kuka take sosai ta ce "innalillahi wa'inna ilaihi ra'jiun, Sultana ta rasu fa kuka ce? Ta tafi ta bar ni?....oh no, na kasa yarda, ɗazu fa ba da daɗewa ba muna tare, ta ce in rakata, meyasa ma ban bi ta ba? Yau ce rana ta farko da Sultana

ta fita ba tare da ni ba, kuma ana nufin shi ne na ƙarshe? A'a, a'a dan Allah, ku sake bincikawa ku ji, ba ita ba ce ta mutu, Sultana ba za ta mun haka ba"

Hajiya ta riƙe ta ta ce "kiyi haƙuri Salma, ba wanda ya ke wuce lokacin sa...."

Ba ta ƙarasa ba, Salma ta ce "to Hajiya lokacin ta bai ƙare ba, Hajiya meyasa za ku ce ta mutu? Wallahi in dai saboda takalmi na ne da na ce sai ta kawo, na janye, Hajiya ku ce ta dawo wallahi na bar mata kaya na da komai ma nawa na bar mata, amma dan Allah ta dawo, dan Allah" magana take tana kuka sosai har muryarta na sarƙewa

Hakan yayi daidai da shigowar su Alhaji, Abba, Kawu Ƙarami, da su Sadeeq gaba ɗaya, sauran waɗanda suka je maƙabartar tare su na daga waje. Da gudu Salma ta ƙarasa wurin Sadeeq da yayi kamar wanda ƙwai ya fashe wa a ciki

Ta ce "Ya Sadeeq ka gaya mun gaskiya, na san Anty Sunaiha ba za ta ɓoye maka komai ba, dan Allah a ina ta ɓoye Sultana, dan Allah ta dawo, wallahi i miss her, ka san tare muke komai, tun ɗazu har yanzu ban ganta ba"

Ganin bai da niyar magana ne ya sa ta nufi wurin Safwan "Ya Safwan, ka san dai you're always by her side, kullum tana faɗar za ka tsaya mata a ko yaushe, then me kake jira yau kana ji fa suka ce ta mutu, ba za ka iya yin komai ba? Ka ƙaryata su dan Allah"

Shi ma ba abunda ya ce mata sai share hawaye yake yi, haka ta dinga binsu ɗaya bayan ɗaya kamar zautacciya, muryarta duk ta sauya, idanunta sun yi ja sun kumbura

Alhaji ne ya riƙe ta ya ce "control yourself Salma, ki natsu"

Girgiza kai take yi tana ta kuka, ta ce "Alhaji to ka gaya musu ba ta mutu ba, idan ta mutu da wa suke so in dinga fira? Da wa zan dinga fita? Da wa zan dinga shawara? Da wa zan dinga karatu? Alhaji kana gani fa kowa da ɗakinsa, amma ni da ita kullum a ɗaki ɗaya muke kwana, a gado ɗaya kuma, idan suka ce ta mutu da wa zan dinga kwana? Ba mai taɓa mun kaya sai ita, idan suka ce ta mutu Alhaji da wa zan dinga faɗa? Ina sonta Alhaji, kuma tana so na, dan Allah ka gaya musu su dawo mun da ita, dan Allah, nayi alƙawari daga yau ko a gadon asibiti nake idan ta ce in raka ta wallahi zan tafi, ni dai kawai ta dawo, dan Allah" ta ƙarasa tana sakin wani kuka mai ban tausayi

Duk mutanen ɗakin kuka suke yi banda Alhaji da ya dake, bubbuga mata bayanta yayi da alamar rarrashi, ya ce "it's ok Salma, ai dai ba ki yarda ta mutu ba ko?" Ta ɗaga, ya ci gaba "to za ta dawo, amma yanzu ina so ki fara zuwa ɗaki ki kwanta, za ta dawo kinji"

"Da gaske za ta dawo?" Ta faɗa tana kallonshi

"Eh, je ki kwanta"

Da ƙyar take tafiya jiri na ɗibarta, Sunaiha ce ta taimaka mata zuwa ɗakinta. Alhaji ya kalli Sadeeq da ke zaune, shi kan shi abun tausayi ne, sai kawai ya ce wa Kawu Ƙarami "Aliyu"

"Na'am" ya amsa da murya mai sanyi

"Ka samu kayi wa Salma allurar da za tayi bacci, wannan sambatun da take yi zai iya jawo mata matsala, gaba ɗaya a rikice take, ka mata allura" cike da tausayi Alhaji ke maganar

Kawu Ƙarami ya amsa da "to" sannan ya wuce

Alhaji ya ce "Safwan ka kira sauran ƴan uwanku, su Sadiya, kar ku gaya musu komai sai sun zo...Sauban kai da Sameer ku je ku gani idan an gama shimfiɗa tabarmar, ku zauna da mutane yanzu za mu fito da Abbanku"

Ko motsawa su Sauban ba su yi ba, sai kuka suke ta yi, ya sake cewa "kuyi haƙuri dan Allah, idan ku kuna wannan kukan, wa zai rarrashi su Sajida su kuma? Maza kuke fa, dan Allah be strong" sai da suka yi mintuna uku kafin suka tashi suka fita tare da Safwan sannan Abba ya bi bayansu

Momi ma tattara su Sajida tayi suka shiga ciki, Hajiya ta lallaɓa Umma da ƙyar suka wuce ciki su ma, ya rage daga Sadeeq sai Alhaji, kusa da Sadeeq ɗin ya zauna bai ce komai ba sai kallonsa yake yi yanda hawaye ke zuba idonsa, wani na kori wani

Ba abunda Sadeeq yake gani illa fuskar Sultana lokacin da take cikin azabar mutuwa, ta riƙe shi sosai, ba abunda kunnuwansa ke jiye masa illa sautin muryarta lokacin da take ta ba shi wasiya, hakan ke ƙara sa shi kuka

A hankali Alhaji ya ce "Sadeeq, na san it really hurts to lose someone, more especially to lose him forever, amma kar ka manta, Ubangijin da ya ɗauke ta Ya fi mu sonta, babban gatan da za muyi mata yanzu shi ne addu'a, ka daina mata kuka Sadeeq dan Allah"

Maganganun Alhaji ƙara narka mishi zuciya suka yi, yana kuka ya ce "Alhaji a gaban ido na ta mutu, ni ya kamata a harba amma ta shiga tsakani, ina kallonta but i can't do anything, kasancewa ta likitan da aka yarda da ƙwarewarsa, ban iya yin komai ba dan taimaka mata....i don't deserve to be call a brother....i don't..." Kuka ya sake fin ƙarfinsa

Alhaji ya ce "Sadeeq kar mutuwar Sultana ya taɓa maka imaninka, ka manta idan lokacin mutum yayi, duk duniyar nan ba wanda ya isa ya hana? Komai dabararka da wayonka? Ka natsu dan Allah, ban taɓa ganinka haka ba, ba ka taɓa kuka haka ba, tabbas wannan aikin sai mutuwa, amma haka za ka daure, idan kai kana haka, wa kake so ya rarrashi mahaifiyarka? Mahaifinka madauriya ce kawai yake yi tun ɗazu amma ya ji mutuwar nan, Sadeeq gidan nan kowa mutuwar ta girgiza shi, dan Allah ina so kayi haƙuri ka zo mu shiga mutane wataƙila za ka

rage wannan raɗaɗin"

Shiru yayi kafin ya share hawayen, ya ce "zan fito Alhaji ka je kawai, i need some minutes to rest" yana gama faɗar hakan ya nufi ɓangaren su, Alhaji cike da tausayinsa shi ma ya fita

Bayan magrib, gidan ya cika sosai ta ko ina, har su Mummy da Hajiyar London da Najma, da su Grandma da Grandpa, duk su na nan, Senator ma yana waje, Muhsin ma da ke ƙasar waje kusan 6:47pm ya iso, shiru kake jin gidan, daga masu kukan zuci, sai masu yin na fili, idan ka zauna wurin, dole duk fuskar da ka kalla sai ya ba ka tausayi

Salma kuwa tana ɗakinta ita kaɗai ta rufe ta hana kowa shiga, tun da ta farka take rungume da hoton Sunaiha ta kuka, sallah ma da ƙyar ta iya miƙewa tayi, sosai tayi wa Sultana addu'a tana kuka, bayan ta gama ne ta jingina da jikin gado tama kallon hoton, ta ce "why do you leave me Sultana? Why? I feel incomplete without you, ta ya zan ci gaba da kwana a ɗakin nan ba tare da ke ba? Ya kike so in yi da rayuwa ta? I have alot to tell you, we planned so many things, yanzu kin tafi kin bar ni....Allah ya miki rahama Sultana, Allah ya sa mutuwa hutu ce a gare ki, Allah ya haskaka makwancinki, i miss you my beloved sister...ko da yaushe kina ɗaukar matsala ta, matsalarki, damuwa ta ma ta ki ce, yanzu da wa zan yi sharing thoughts and feelings ɗin na!????....." Ta ƙarasa tana kuka sosai, ta rungume hoton ta ci gaba da kuka.............

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

_Full of Arrogance, Ego, Jealous And_ _Love_

*CREATED AND WRITTEN*

_BY_
🥰 *UMMEETA* 🥰

*🌙MOONLIGHT WRITER'S ASSOCIATION🌙*
We shine all over the world

https://www.facebook.com/profile.php?id=100094397072466

بِسم الله الرحمن الرحيم

~~~~~~~~~~~~~~~~

_The strongest among us are the ones who smile through silent pain, cry behind closed doors and fight battles nobody knows about..._

**FINAL PAGE**

**Kafin mu shiga cikin final page, ina so zan yi magana akan comments ɗin da nayi ta samu kan last page, na samu comments sosai fiye da tsammani, Ummeeta ba ki kyauta ba, meyasa kika kashe Sultana, ban ji daɗin mutuwarta ba, ki dawo da ita, bai kamata ta mutu ba, meyasa kika kawo musu mutuwa lokacin da suke jin dadi? This and that😂🥺 To farko dai ba ni na kashe Sultana ba, kuna gani fa Najeeb ne ya kashe ta ba ni ba, dan Allah ku daina zargi na😄. Honestly speaking, abunda ya sa na kawo zancen mutuwa kuma lokacin da suke jin dadi, saboda Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wasallam ya ce mu yawaita tuna abunda yake yanke jin daɗi, wato mutuwa, shi ne abunda ya faru, ba zai taɓa yiwuwa a ce ko da yaushe ɗan adam yana cikin farinciki ba, dole ne sai yau ka ji daɗi gobe kuma akasin hakan, komai yawan arzikinka kuwa, fatanmu kawai Allah ya mana kyakkyawan ƙarshe kuma Ya sa mu mutu muna masu imani, sannan Ya gafartawa magabatanmu🤲 Wadanda kuma suka yi kuka saboda hakan, i'm really apologising🙏 I'm sorry😅😂**

**Page 87&88**

Kwanaki uku da rasuwar Sultana, yawan mutane sun fara ragewa a gidan, sai dai Salma tana kwance har yau ba ta da lafiya, har ruwa an ƙara mata, Sadeeq kuwa ba za'a kira shi mai lafiya ba, sai dai bai kwanta ba, yana nan dai sai a hankali, Najeeb kuwa ya samu sauƙi, yana hannun ƴan sanda a tsare

Da misalin ƙarfe uku na rana, Salma na ɗakinta a zaune kan gado tana rungume da hoton Sultana, bayan Sadeeq ya gama cire drip ɗin hannunta, shi ma yana gefe ya miƙa mata tea ɗin da ya haɗa mata, karɓa tayi sannan ya ɗauko dankalin turawa ya ajiye mata
~~~~~~~~~~~~~~~~

Cikin sanyin murya ya ce "Salma ki ɗauka ki ci, kullum tea kawai kike sha idan dai ba ni na baki ba"

"Ya Sadeeq ba zan iya cin komai ba, tea ɗin kawai ya isa"

"Kiyi haƙuri ki ci wannan ko kaɗan ne, saboda lafiyarki"

A hankali ta ɗaga idanunta da suka cika tab da hawaye ta ce "Ya Sadeeq, a duk lokacin da na saka hannu na cikin kwanon abinci, to tabbas hannun Sultana yana kusa da nawa, amma yanzu ba ta nan, Ya Sadeeq ta ya zan iya ci?" Ta ƙarasa hawayen na sauka kan fuskarta

Duk da cewa hawaye ne kwance a idanunsa, amma hakan bai hana shi ƙirƙirar murmushi ba, ya ce "idan Sultana ba ta nan, ki sa wa ranki Yayanki yana nan, kuma zan tabbatar kin ƙoshi"

Ɗaukar plate ɗin yayi ya dinga ɗiba yana ba ta a baki, a hankali take ci kamar mai ciwon baki, tana share hawaye, shi ma sai ƙoƙarin mayar da na shi yake ta yi, suna a haka Safwan da Sauban suka shigo, kujerar mirror Safwan ya ja ya zauna, sannan ya ce

"Zan so in ga ka ci abinci kamar yanda kullum kake ƙoƙarin ciyar da Salma"

Kallonshi kawai yayi ya ci gaba da ba ta, Salma ta ce "Ya Sadeeq ba ka cin abinci?"

"Ina ci" ya amsa a gajarce

"Ya Sadeeq dan Allah ka ci abinci, kar wani abu ya same ka, na rasa Sultana, idan na kalle ka ita nake gani because you resemble her, ba na so in rasa ka dan Allah"

"Don't worry Salma, ki fara ƙoshi first, zan ci"

Safwan na kallonsu har ta gama cin abincin, sannan ya kalli Sadeeq ya ce "Sadeeq, dama na shigo ne saboda ka tashi mu tafi station, ina so mu ga DPO saboda a tura mu kotu kawai, Alhaji na waje yana jiran mu, da Kawu Karami"

Girgiza kai Sadeeq yayi ya ce "ba zan je ba, ku tafi kawai"

"Meyasa?"

Cikin ɓacin rai ya ce "Safwan idan har na ga mutumin nan, wallahi ba abunda zai hana in kashe shi yau ɗin nan, is better ku tafi kawai, Please"

Safwan ya ce "Sadeeq haƙuri za kayi ka danne zuciyarka, ka zo mu tafi"

"Ba inda za ni, na gaya maka, idan kuma so kake in kashe shi, fine, mu tafi"

Miƙewa yayi, Sauban ya ce "a'a Ya Sadeeq ka zauna a gida kawai, Ya Safwan mu tafi, dama firar da muka yi da Sultana last, ta faɗi cewa wata rana za ka tsaya mata, kuma za kayi nasara, kamar ta san abunda zai faru, ka tashi mu tafi kawai, idan Ya Sadeeq ya tafi matsala kawai za a samu" ya ƙarasa yana share hawayen da suka zubo masa

Ba musu Safwan ya miƙe suka fita ba tare da ya ce komai ba. Salma dai tana jinsu, kuka kawai take yi har suka fita, wayar Sadeeq tayi ƙara, Umma ce, ba tare da ya ɗaga ba kawai ya miƙe ya fita zuwa ɓangaren ta

Sameer na kwance a kujerar parlourn Umma shi kaɗai, haɗa ido suka yi da Sadeeq ba wanda ya ce komai, saboda Sameer kan shi ba ya son magana da kowa yanzu, cikin ɗakin Umma kawai Sadeeq ya shiga

Tana kan gado a zaune, da abinci kan bedside drawer, zuwa yayi ya ja wata kujera zuwa gabanta sannan ya zauna, ya ce "Maa, gani"

Har yau idanunta a kumbure suke, a hankali ta ce "Sauban ya gaya mun kai da Sameer ba kwa cin abinci, yanzu na sa Sameer ya ci, saura kai ka ɗauka ga shi nan"

Kallon abincin yayi, sannan ya ce "Maa na ƙoshi"

"Da ka ci me? Coffee ɗin da kake sha ne abinci? Sadeeq so kake kai ma in rasa ka? Ku uku nake da su, ɗaya ta tafi saura ku biyu, Sadeeq ba ka gaji da ganin hawaye na bane?" Ta faɗa hawaye na bin fuskarta

Hannu yasa ya share mata ya ce "stop it please Maa, ki daina kuka, nothing will happen to me in sha Allah, zan ci"

"To ka ci in gani"

"Zan ci"

Anty Saudat ce ta turo ƙofar ta shigo, duk ta sauya, dama can ga ciki ga kuma wannan rasuwar, zama tayi kusa da Umma, ta ɗauki abinci ta diɓa ta kai mishi baki, ba musu ya buɗe ba ki ya ci

Sannan ta ce "Umma da haka kika mishi tsab zai ci, kin manta haka Sultana take yi wa mutane idan ba sa da lafiya, idan mutum ya ƙi ci abinci, ba shi take yi a baki"

Murmushi Umma tayi ta ce "muna ƙaunarki Sultana, amma Allah ya fi mu ƙaunarki, kuma shi kaɗai ya san dalilin da yasa ya karɓe ki a lokacin da kike ƙaramarki, Allah ya sa aljanna ce

makomarki ƴata, ku kuma Allah ya ƙara raya mun ku, Allah ya sa in ga jininku kafin mutuwa ta" magana take tana kuka, hakan ya sa su Anty Saudat da Sadeeq zubar da hawaye, Anty Saudat ta rungume ta, Sadeeq kuwa yana share mata hawaye

A station kuwa, su Alhaji sun gama magana da DPO, ya tabbatar masu da gobe zai aika da case ɗin na su kotu, sun ji daɗin hakan sosai, suka mishi godiya sannan suka bar wurin

A hanya, Sauban na driving, Safwan na gidan gaba, su Alhaji su na baya, Alhaji ya ce "Safwan da ka matsanta sai mun je kotu, kana da hujjojin da za ka tabbatar da cewa shi ya kashe ta?"

"Eh Alhaji, tun ranar da abun ya faru ban zauna ba, na je har park ɗin na samu shaidun gani da ido, sannan mai gadin gidan Najeeb ɗin ma ya taimaka mun sosai, saboda ya bani information akan wani abokin Najeeb ɗin da ya ji su na waya ranar da yakan ta faru, ya gaya mun ya ji ya kira sunan mutumin sannan ya gaya mishi wurin da za su haɗu dan ya ba shi bindigarsa, shi ne ma ya raka mu har gidan abokin na sa dan ya san shi, yanzu haka shi ma yana hannun ƴan sanda, kuma ya amsa cewa shi ya ara mishi bindigar, kuma ya gaya mishi me zai yi da ita"

Kawu Ƙarami ya ce "amma ban ganshi a cell ɗin ba lokacin da na je duba Najeeb"

"Ai ba wannan station ɗin yake ba, wani station daban na kira saboda ba na so su haɗu da Najeeb ɗin, kuma sanadiyar abokin na sa ma mun gama ɗayan yaronsa da aka yi a gabansa, ɗayan ya gudu....Kawu ku kwantar da hankalinku, na shirya wa case ɗin nan sosai, ba yanda za'a yi Najeeb ya kuɓuce"

Alhaji ya ce "to amma abunda ke bani mamaki shi ne, shi Najeeb ɗin ba ya da ƴan uwa ne ko iyaye?"

"Iyayensa sun rasu aka ce, ɗan uwansa ɗaya, kuma na samu numbern sa na kira shi kwana biyu da suka wuce, amma y gaya mun tun da har Najeeb zai iya ɗaukar ran ɗan adam, ya yafe shi, ba abunda zai iya yi mishi dan ya san hukuncin kisa za'a yanke mishi, shiyasa ma ba zai zauna a ƙasar ba"

Alhaji ya ce "kuma ɗan uwansa ne?"

Kawu Ƙarami ya ce "da wuya kam, idan ma har ɗan uwansa ne to ba ciki ɗaya suka fito, dan da ba abunda zai hana shi tsaya wa Najeeb ko da kuwa ya san ba za suyi nasara ba"

Safwan ya ce "yanzu ma dai ko menene, can tsakaninsu, ni buri na kawai in ga wannan mutumin ya bar duniya"

"To Allah ya bada sa'a" cewar Alhaji

Suka amsa da amin

Kwana ɗaya da hakan, aka shiga kotu domin sauraren ƙarar, an ba Najeeb damar kiran lawyernsa kafin aka fara shari'ar, duk wasu gamsassun hujjoji sai da Barrister Safwan ya gabatar da su a gaban kotu, kusan mintuna talatin ana abu ɗaya, duk iyalan Saraki's family suna kotun idan ka cire Hajiya, Umma, Momi da Grandma, sai Salma, amma har Grandpa yana wurin, Sadeeq ma da ƙyar Abba ya lallaɓa shi ya zo

Daga ƙarshe dai Barrister Safwan yayi nasara, domin kuwa alƙalin yayankewa Najeeb hukuncin kisa, abokinsa ma da yaransa an yanke musu hukunci daidai da laifinsu, Saraki's family sun ji daɗin hukuncin sosai, suka gode wa Allah tare da roƙarwa Sultana rahamar Ubangiji

Ranar da Sultana ta cika kwana bakwai da rasuwa, aka yi sadaka sannan aka yi addu'a sosai a gare ta da sauran waɗanda suka riga mu gidan gaskiya

Zuwa wannan lokacin, Salma ta samu sauƙi sosai, sai dai har yau ta kasa sakewa, amma tana cin abinci sai dai tare da su Hajiya, su Anty Sadiya, Anty Sameera da Anty Saudat ma duk Alhaji ya ba su umarnin koma wa gidajensu, duk da ba su so hakan ba amma dole suka koma. Sadeeq ma ya fara zama mutum, dan ya daina zama shi kaɗai, tun ranar dasuka baro kotu bayan an yanke wa Najeeb hukunci, ya ke jin an rage mishi wani nauyi da ke kansa

Da daddare Sadeeq suna ɗakin Sunaiha, zaune yake kan gado ya jingina, ita kuma ta kwanta gefensa kan jikinshi, ta wani ƙanƙame shi kamar zai gudu, numfashi ta ja, a hankali ta ce "Prince"

"Umm" ya amsa

"Prince ni na jawo Najeeb into our lives, ban taɓa tunanin he's capable of doing all this ba, i always feel guilty, i think i'm responsible for everything Prince, could you please forgive...." Rufe mata baki yayi, hawaye na zuba kan fuskarta, ya share mata kafin ya ce

"Stop blaming yourself, ban taɓa ganin laifinki ba ko da da rana ɗaya ne akan wannan, komai muƙaddari ne daga Allah, ko da ke, ko babu ke, die Najeeb sai ya kashe ta saboda shi ne ajalinta, dan haka kar in sake jin wannan maganar dan Allah"

Kallonshi tayi sannan ta sake rungume shi ta ce "i love you, Allah ya mata rahama"

"Ameen, i love you too" ya ɗora hannunsa kan gashin kanta yana shafawa, ya rufe ido, Sultana kawai yake tunani da duk memories ɗin da suka yi sharing as usual, lokutan da yake mata faɗa da lokutan da suke shiri, sannan da maganar da ta gaya mishi ta ƙarshe, 'Ka kula da kanka, da iyayenmu, da Saraki's family baki ɗaya' hawaye suka biyo fuskarsa, yayi sauri

gogewa saboda yana so ya daina zubar mata da hawaye, sai dai duk lokacin da ya tuna ta, ya mata addu'a

**BAYAN SHEKARA UKU**

Abubuwa da yawa sun faru cikin waɗannan shekaru ukun, ciki kuwa har da rasuwar Grandpa wanda ya rasu bayan wata biyu da rasuwar Sultana, Grandma ita ma ta bi shi bayan watanni huɗu da rasuwarsa, Wannan shekarar kam mutuwa ta waiwayi gidan Saraki, dam haka rayuwar take, wani lokacin idan mutuwar ta waiwaye ku, sai ka ji tamkar kai kaɗai mutuwar ke tunawa, sai ka ji tamkar ba ka taɓa farinciki ba a rayuwa, hakan wani darasi ne da ya kamata duk wani ɗan adam ya fahimta, rayuwar ba ta taɓa tafiya a ɓangare ɗaya, dole sai ka ɗanɗana ko wane ɓangare

Domin kuwa bayan sun gama jimamin rasuwar, a shekara ta gaba farin ciki ya fara ziyartarsu, domin Anty Saudat ta haifi santalelen ɗanta wanda ya ci sunan Grandpa, wato Al'ameen suna Kiransa da Ashraf. Bayan murnar haihuwar Anty Saudat, Nasreen ta haihu, ita ma kyakkyawan ɗa ta haifa, aka saka mishi sunan mahaifinta Al-Mustapha, ana kiransa da Mukarram. Sannan Anty Sameera ma ta sake haihuwar ƴa mace, aka saka mata suna Fatima, ana kiranta da Zarah, gida ya ƙara cika masha Allah, Baba Sajeed ya sake tara yara

A shekara ta gaba kuwa hidimar aure ce, Salma ta kammala karatunta, ta zama cikakkiyar nurse a asibitin su, bayan ta kammala ne aka ɗaura aurenta da saurayinta, ɗan abokin Alhaji ne, mahaifinsa mai kuɗin gaske ne, shi kan shi yaron sanannen ɗan kasuwa ne, sannan anyi auren Anty Najma da Yareema Muhsin, sai Ikram da Aryaan, Sarah kuma da Saif

An sha biki kam masha Allah, yanzu kuma auren Sauban da Sameer ake jira, duk da dai har yanzu Sameer ya kasa mayar da hankali ya samu wacce yake so, Sauban yana da budurwa, amma a cewarsa yana jiran sai ranar da Sameer ya tashi yin auren sai suyi tare shiyasa bai yi mata alƙawarin aure a nan kusa ba, Su ma sun far aiki, Sameer na aikin banki, Sauban kuma MD ne a ɗaya daga cikin kampanin Abba. Sai kuma sarkin ɗaukar rahoto, Sajeeda da kuma Safna, waɗanda yanzu suna jami'a, Sajeeda na mataki na biyu, Safna kuwa mataki na farko, duk da dai su ma ba shirya wa auren suka yi ba, amma iyayensu na jiransu, sai dai akwai soyayya mai ƙarfi tsakanin Sajeeda da Sharif

Sai Oga Tiger, Sadeeq ya sake gina wasu asibitin guda uku a wuraren daban-daban, sai dai guda biyu ya buɗe, ɗayan ya ce sai bayan haihuwar Sunaiha sannan za'a buɗe shi, tana nan da tsohon cikinta, haihuwa yau ko gobe, tana wurin Hajiya kamar yanda ta riƙe Nasreen a wurinta har ta haihu, haka take shirin yi a kan Sunaiha

Kamar yanda suke tsammani, a ranar da EDD ɗin ta ya cika, a ranar ta fara naƙuda, ba ɓata lokaci aka garzaya da ita asibitin da Sadeeq ke yawan zama, da taimakonsa da wasu nurses guda biyu, Sunauha ta haifi kyawawan twins ɗinta mace da namiji, murna a wurin Sadeeq faɗarsa ma ɓata lokaci ne

Cikin ƙanƙanin lokaci, labari ya isa kunnen duk wani da ya shafi Saraki's family, kafin yamma gida ya cika, kowa Allah-Allah ya ke a ba shi twins ya ɗauka, dan su ne ƴan biyu na farko da aka fara samu a familyn. Parlour ya cika maƙil, sai gardamar ake yi wanda twins suka ɗauko, wasu su ce Sadeeq suka biyo, wasu su ce Sunaiha ce, Sadeeq shi dai yana ɗakin Hajiya yana jinyar matarsa

Kafin ranar biki ya zagayo, twins sun cika da kyaututtuka daga wurin iyayensu da kakanninsu, kowa ji yake yi da su. Ranar suna kuwa an sha biki kamar ba gobe, gagarumin biki aka shirya na ji da faɗi, shagalin bikin kusan duk wanda ke Jahar Gombe ya samu labari, masu amfani da social media ma sun gani yanda shagalin ya gudana

Hassan ana kiransa da Sultan, Husaina kuma Sultana, a wannan ranar Sadeeq yayi farinciki sosai saboda yau ya cika wasiyar Sultana na ƙarshe da ya rage, kuma ya sake godewa Allah da ya ba shi ƴan biyun mace da namiji, wataƙila saboda ya cika wannan wasiyar ne

Bayan sati ɗaya da bikin, Sadeeq yayi bikin buɗe ɗayan asibitin, wanda sai a ranar ne kowa ya san sunan asibitin, dan ya banbanta da saura gudu huɗu ɗin da ake kira Saraki's Hospital, wannan asibitin sunansa SULTANA USMAN SARAKI HOSPITAL (SUS HOSPITAL) , tsarin wannan asibitin ma daban ne, har kayan da ya zuba a ciki na daban ne, yayi kyau kamar ba asibiti ba, sannan ya miƙawa Salma takardun mallaka mata asibitin, ba wai dan ta zama shugabar asibitin ba, hakan ba zai yiwu ba saboda Nurse ce ita, ya ba ta shi ne halak, ko da mutuwa yayi ba ya cikin kayan gadonsa, ba Salma kaɗai ba, kowa sai da yayi murna da hakan, tayi mishi godiya sosai har da hawayenta

Rayuwa ta ci gaba da tafiya cikin farinciki da kwanciyar hankali, duk lokacin da suka tuna da waɗanda suka rasu, su kan bi su ne da addu'a da fatan rahama da gafarar Ubangiji, komai na su sai san barka, fatanmu shi ne Allah ya raya yaran baki ɗaya, waɗanda suka rasu kuma Allah ya gafarta musu, ma'aurata kuma Allah ya ƙara musu zaman lafiya da haƙuri da juna, ma su soyayya kuma Allah ya nuna musu ranar aure, Allah ya ƙara mana lafiya baki ɗaya, ya mana kyakkyawan ƙarshe.......Nayi nan, rahoton familyn Saraki ya isa haka nan (Hhhhhh).......

ALHAMDULILLAH, A NAN NA KAWO KARSHEN WANNAN LITTAFIN NA WA NA YAR SENATOR, INA ROKON ALLAH DUK ABUNDA NA RUBUTA BA DAIDAI BA, ALLAH YA YAFE MUN, KUMA DA KUKA KARANTA YA YAFE MUKU, WANDA KUMA NAYI DAIDAI ALLAH YA BANI LADA, KUMA YA BAKU LADAN KARANTAWA. ALLAH YA BAMU IKON ƊAUKAN DARASIN DAKE CIKI.

INA MATUƘAR GODIYA GA WAƊANDA SUKA JURI KARANTA WANNAN LITTAFIN DAGA FARKO HAR ƘARSHE, NA GODE SOSAI DA KULAWARKU DA KUMA YAWAN ADDU'O'IN DA KUKE MUN DA FATAN ALKHAIRI, BA ZAN IYA BAYYANA MUKU FARINCIKIN DA KUKE SAKA NI BA KO DA YAUSHE, SAI DAI IN YI MUKU ADDU'AR ALLAH YA SAKA MUKU DA MAFIFICIN ALKHAIRINSA KUMA YA BAR MU TARE, LOVE U ALL. KAMAR YANDA MUKA GA ƘARSHEN WANNAN SHEKARA LAFIYA, ALLAH YA NUNA MANA SABUWAR SHEKARA LAFIYA, KUSKUREN DA MUKA AIKATA A WANNAN SHEKARAR ALLAH YA YAFE MANA, ALLAH YA SADA MU DA ALKHAIRAN DA KE CIKIN SABUWAR SHEKARA YA KUMA TSARE MU DAGA SHARRINSA, ALLAH YA JI ƘAN WAƊANDA SUKA RASU MU KUMA YA SA MU MUTU MUNA MASU CIKAKKEN IMANI....AMEEN

JINJINA TA MUSAMMAN GA ƳAR SENATOR FANS GROUP, INA MATUƘAR YINKU OVER, INA ƘAUNARKU SOSAI, SON SO NAKE MUKU FISABILILLAH🤗🥰🥰😍.......KAR A CE NAYI SON KAI😁....MU TARA DA KU CIKIN SABON LITTAFINA DA ZAN FARA SAKI A SABUWAR SHEKARA IN ALLAH YA YARDA WATO **HUMAIRA**, INA FATAN ZAI ƘAYATAR DA KU KAMAR DAI YANDA ƳAR SENATOR YAYI, TNX ALOT

AKA CE DUK WANDA YA BAR GIDA, GIDA YA BAR SHI, TO BAN MANTA DA KU BA JAMA'AR MOONLIGHT WRITERS ASSOCIATION, INA ALFAHARI DA KU OVER OVER🤍🌹✨, ALLAH YA ƘARA ƊAUKAKA MOONLIGHT DA MARUBUTANTA, KUMA YA ƘARA HAƊA KANMU....AMEEN YA HAYYU YA QAYYUM

ALHAMDULILLAH!!!

♦💫♦💫♦
*ƳAR SENATOR*
♦💫♦💫♦

*LIKE*
*SHARE*
*COMMENT*